# BIJIREWA A WAKOKIN SIYASA: BINCIKE KAN WAKOKIN 1903-2015

**Na**

**YAHAYA IDRIS**

**Ph. D/Arts/3352/2011-2012**

**Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria**

**May, 2016.**

# BIJIREWA A WAKOKIN SIYASA: BINCIKE KAN WAKOKIN 1903-2015

**Na**

**YAHAYA IDRIS**

**NCE, B A ABU (2002), M A ABU (2010), PhD/Arts/3352/2011-2012**

**A Thesis submitted to the School of Post Graduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria, In Partial Fulfilment of the requirements for the Award of Doctorate Degree in African Literature (Hausa),**
**Department of African Languages and Cultures, Faculty of Arts,**
**Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.**

## Declaration

I hereby declare that the work in this thesis titled "Bijirewa a Wakokin Siyasa: Bincike Kan Wakokin 1903-2015"(Resistance in Political Poetry: A Research On 1903-2015 Poems) was performed by me in the Department of African Languages and Cultures, under the supervision of Professor Dalhatu Muhammad, Doctor Magaji Yakawada Tsoho and Professor Muhammad Lawal Amin. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this work has been presented for another degree or diploma at any institution.

| | | |
|---|---|---|
| Yahaya IDRIS | ………………… | …………… |
| | Signature | Date |

## Certification

This thesis titled "Bijirewa A Wadodin Siyasa: Bincike Kan Wakokin 1903-2015" (Resistance in Political Poetry: A Research On 1903-2015 Poems) meets the regulations governing the award of the degree of Doctor of Philosophy of the Ahmadu Bello University, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

| | | |
|---|---|---|
| ---------------------------------------- | --------------- | ------------ |
| (Professor Dalhatu Muhammad)<br>Chairman, Supervisory Committee | (Signature) | (Date) |
| ----------------------------------------- | ---------------- | -------------- |
| (Doctor Magaji Yakawada Tsoho)<br>Member, Supervisory Committee | (Signature) | (Date) |
| ------------------------------------------ | --------------- | ------------ |
| (Professor Muhammad Lawal Amin)<br>Member, Supervisory Committee | (Signature) | (Date) |
| --------------------------------------- | -------------- | ------------- |
| (Doctor Salisu Garba)<br>Head of Department | (Signature) | (Date) |
| --------------------------------------- | ---------------- | ------------- |
| (Professor Kabiru Bala)<br>Dean, School of Post Graduate Studies | (Signature) | (Date) |

## Godiya

Godiya ta tabbata ga Allah Madaukakin Sarki da a cikin ikonsa ya kawo mu wannan zango a nazarin “Bijirewa A Wakokin Siyasa Bincike Kan Wakokin 1903-2015” tsira da amincin Allah su dara tabbata ga Manzonsa Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihim Wa sallam.

Ina mida godiyata marar yankewa ga Jagoran duba wannan aiki na farko, Farfesa Dalhatu Muhammad da Dr. Magaji Yakawada Tsoho jagoran duba aikin na biyu da Farfesa Muhammad Lawal Amin jagoran duba aikin na uku, wadanda su ne suka yi dawainiya da aikin wajen duba shi da gyara shi da bayar da kyawawan shawarwari da muhimman takardu da littatafai da suka taimaka wajen zaman aikin da gindinsa daram. Haka kuma ina mida godiyata ga Dr. Balarabe Abdullahi, tsohon Shugaban Sashen Harsunan Afirka da Al’adu, jami’ar Ahmadu Bello, Zaria. Ina rokon Allah ya saka musu da mafificin alherinsa.

Ina godiya ga sauran malamai da masana wadanda suka tallafa mini wajen wannan bincike, kamar Farfesa Sani Abba Aliyu na Sashen Koyar da Harshe da Adabin Ingilishi, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya, wanda ya taimaka wajen gyara aikin ya zauna da gindinsa. Haka kuma ina mika godiya ta musamman ga malaman Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya wadanda suka hada da Farfesa Hafizu Miko Yakasai, da Farfesa Munir Mamman, da Dr. B. S. Y. Alhassan, da Dr. Haruna Aminu, da Farfesa Awwal Umar, da Malam Adamu Ibrahim Malumfashi da Malam Sani Usman, da Malam Shu’aibu Abdulmumuni, da Malam Abubakar Sarki, da Malam Jibirin B. Dambo, da Dr.

Isah I Sulaiman, da Dr. Salisu Garba, Shugaban Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. da Dr. Shu'aibu Hassan da Malama Halima Kabir Daura da Dr. Hauwa Muhammad Bugaje Allah ya saka da alheri. Haka kuma ina godiya ga Malam Abubakar Ayuba, da Malam Adamu Shede, da kuma Malam Abdulmalik Aminu Na gode da kulawa.

Daga bangaren malamai kuma abokan aiki a Sashen Harsunan Nijeriya, na Jami'ar Usmanu Kanfodiyo da ke Sakkwato ba zan manta da Farfesa Abdullahi Bayero Yahya ba da Dr. Bello Bala Usman saboda gyare-gyare masu amfani da suka yi wa wannan aikin. Farfesa Aliyu Muhammad Bunza ya yi dawainiya da kudurin wannan aiki tun farko, Allah ya saka da alheri. Haka kuma Dr. Ibrahim Abdullahi Sarkin Sudan Kwantagora da Dr. Yakubu Aliyu Gobir Allah ya saka da alheri. Ina godiya ga shugaban sashen Nazarin Harsunan Najeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sakkwato. Farfesa Muhammad Abdulahamid Dantumbishi wanda kowane lokaci yana cikin tambayar ina aka kwana da wannan aiki. Godiya ga iyaye kuma abokan aiki irin su Farfesa Salisu Ahmad Yakasai da Farfesa Atiku Ahmad Dunfawa da Farfesa Haruna Abdullahi Birniwa da Fafesa Haliru Ahmad Amfani. Haka kuma ba za a manta da abokai ba irin su Dr. Nasiru Aminu Kalgo da Dr. Umar Aliyu Bunza da Dr. Abdulbasir Ahmad Atuwo da Dr. Abdullahi S Gulbi. Saura sun hada da Malam Dano Balarabe Bunza da Malam Sama'ila Umar da Malam Isah Abdullahi da Malam Rabi'u Aliyu Rambo da Malam Muhammad Mustapha Umar da Malam Musa Shehu da kuma Malam Nazir Ibrahim Abbas. Abokan aiki wadanda ba malamai ba irin su Malam Abubakar Chika Malami da

Alhaji Babuga Tambuwal da Malam Hamisu da kuma malam Iliyasu, duka sun cancanci godiya. Allah ya bar zumunci.

Ina godiya ga Farfesa Kamal Babikir wanda a kowane lokaci yana cikin tambayar matsayin aikin. Haka kuma ina godiya ga Farfesa Sani Umar Musa da Dr. Gambo Hassan, wanda yana cikin mutanen farko da suka ba ni dwarin guiwar fara wannan karatu. Godiya ta musamman ga Farfesa Mukhtar Umar Bunza shugaban Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci, Jami'ar Usmanu Danfodiyo Sakkwato, da Farfesa Uba Ali na Sashen Koyar da Lissafi a Jami'ar Gwamnatin Tarayya, Dutse, Jihar Jigawa. Haka kuma ina mutukar godiya ga aminina kuma abokin aiki wanda kowane lokaci yake kwana da tashi da wannan aiki a cikin zuciyarsa ya kuma taimaka da karfinsa da tunaninsa wato Dr. Mu'awiya Dahiru Muhamud mukaddashin shugaban Tangayar Koyar da Karatun Aikin Lauya a Jami'ar Usmanu Kanfodiyo, Sakkwato, Allah ya bar zumunci. A sashen koyar da addinin Musulunci na Jami'ar Usmanu Danfodiyo, dake Sakkwato, ba zan manta da mida godiya ga Dr. Ahmad Maigari Dutsinma da kowane lokaci yana cikin ba ni kwarin guiwa a game da yin wannan karatu. Haka kuma ina godiya ga Malam Tambari Ibrahim Abbas da A. S. Mainiyo da Zayyanu Dogondaji. Ba zan rufe godiya a wannan Sashe ba tare da na mika cikakkiyar godiya ga dan uwa kuma yaya wato Farfesa Y Y Ibrahim ba, su duka ina addu'ar Allah ya saka da alheri.

A Sashen Nazarin Tarihi na Jami'ar Usmanu Danfodiyo kuwa, sashen da yake kamar gida ne a wurina, ina godiya ga Dr. Yasin Abubakar da Dr. Tukur Muhammad Mukhtar Haka kuma ina godiya ga Dr. Umar Muhammad Jabbi da

Dr. Isma'ila Abubakar Jabo da kuma Dr. Murtala Ahmad Rufa'i. Duk dai a Sashen Nazarin Tarihi, ina mida godiya ga Malam Zakariya Sambo da Malam Aminu Alkammawa da Dr. Mujitaba Arabu da kuma Malam Abdullahi Labbo na gode kwarai da gaske.

A Sashen Nazarin Harsuna da Harsunan Kasashen Turai na Jami'ar Usmanu Danfodiyo da ke Sakkwato, ina mika godiya ta musamman ga shugaban wannan sashe wato Dr. Muhammad Aminu Mode. A kowane lokaci muka hadu yana tambayar wannan aiki baya ga taimako na kayan aiki, Allah ya saka da alheri ya bar mana zumunci. Haka kuma ina godiya ga Malam Bello Dogondaji da Malam Aminu Bako da ma wadanda ban ambata ba Allah ya saka da alheri.

A cibiyar nazarin Harshen Hausa kuwa a Jami'ar Usmanu Kanfodiyo, ina mika godiya mai yawa ga Darakta ta wannan cibiya wato Dr. Sa'adiya Omar saboda irin taimakon da na samu daga wajenta, Allah ya saka da alheri. Ina godiya ga Dr. Hamza Alhaji Ainu Allah ya bar zumunci.

Ina mida godiya marar yankewa ga Malam Abubakar Sa'idu Garin-Ali mataimakin Shugaba a Kwalejin Gwamnatin Tarayya ta 'Yan mata da ke Gwandu tare da Malam Zayyanu Ado a Kwalejin Gwamnatin Tarayya ta Malali a Kaduna da kuma Alhaji Malamiyo da ke cikin garin Hadejia su duka na gode kwarai da gaske.

Ta bangaren gida ina godiya ta musamman mai tarin yawa marar yankewa ga A. I. G. Mu'azu Idris Hadejia (rtd), da Surv. Muhammad Idris, babban mai safiyo na

jihar Jigawa mai ritaya. Ina godiya ga mutumin da ya kafa asasin wannan karatu watau Farfesa Suleman Idris Hadejia, Malami a Sashen Kula da Lafiyar Al'umma na Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. Haka kuma wanda ya taimaka wajen yin wannan karatu. A karshe ina godiya ga sauran 'yan uwana, Allah ya yi jagora, ya saka da alheri.

Har wayau ba zan manta da mai dakina ba Rukayya (Ummi) saboda irin kwarabniyar karatun boko da aka sha da ita ba tun daga karatun digiri na farko har kawo wannan matsayi na karatun digirin digirgir. Ina godiya da irin hakuri da kula da tarbiyyar yara a lokacin da ba na gida. Haka kuma 'ya'yana, wadanda Allah ya kaddara samuwarsu a lokacin yin wadannan karatu da suka hada da Muhammad (Mutawassil) da Ahmad (Walid) da Amina da Muhammad (Mamman) da marigayiya Fatima da kuma Fatima Zara (Baba). Allah ya shirya su ya yi musu albarka, Wadda ta rasu kuma Allah ya lullube ta da rahamarsa Amin.

Abu ne mai wuya a ambaci duk wadanda suka taimaka wajen gudanar da wannan aiki da ma rayuwata ta karatu gaba daya. Duk ina fata Allah ya saka wa kowa da alherinsa.

Yahaya Idris,
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka,
Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria, Nijeriya.
10th May, 2016

**Abstract**

Poetry, whether oral or written, is a way of disseminating message in a particular way that educates and at times elicits pleasure. For long, Hausa poems are used in propagating political messages be it voters registration or campaigns or the conduct of election itself. The study of resistance in Hausa political poetry has received little attention. By the tradition of Hausa poetic studies, critics normally study theme, style and plot of literary works. Literary analysis on resistance in Hausa political poetry is to some extent a new a phenomenon in Hausa literature. Based on this, some poems written due to the emergence of colonialism and the ones during the first, second, third and fourth republics were studied, in order to understand how people showed their resistance towards leaders and some policies. At the end, it was understood that, in all the history of political dispensation since the time of colonialism to the present political regime, there have been some elements of resistance in most of the Hausa political poems. The work is devided into five chapters. Chapter one consists of general introduction, where the significance of the research, aim and objectives hypothesis and scope and delimitations were discussed. Chapter two constitute literature review which treated works related to the research whether positively or otherwise. While chapter three dealt with resistance poems during colonialism and the one before the advent of full democracy, chapter four is devoted to the analysis of resistance poems in Hausaland after the advent of full democracy as reflected in the poems studied. Chapter five, which is the concluding chapter, discussed the summary of the whole work, and research findings viz, till date there are political poems with some element of resistance, and to this time the 21$^{st}$ century there are resistance poems and most of the poems studied potray political theme with elements of resistance socially, economically and otherwise.

## Tsakure

Wada, walau ta baka ko rubutacciya hanya ce ta isar da sado a bisa wani tsari na musamman domin ilimantarwa da faDakarwa ko kuma nishaDantarwa. An daDe ana amfani da wadar Hausa domin isar da sadonnin siyasa walau na aikin rijistar zabe ko na kamfe ko kuma na yin zaben kansa. Amma, ba kasafai ake samun haka wajen amfani da wadodin Hausa na siyasa domin nazartar bijirewa a cikinsu ba. Bisa al'ada ta nazarin adabi a harshen Hausa, akan nazarci jigo ne, ko salo, ko kuma zubi da tsari. Nazari domin dodarin gano irin bijirewar da take cikin wadodin siyasa ana iya cewa sabon fage ne a adabin Hausa. An nazarci wadodin da aka yi sakamakon siyasar zuwan Turawan mulkin mallaka dasar Hausa da waDanda aka yi a zamunan siyasar jumhuriya ta farko da ta biyu da ta uku da kuma ta huDu, inda aka yi dodarin fito da yadda mutane suka nuna rashin amincewarsu da ire-iren manufofin aiwatar da mulki a tsarin siyasar dasar Hausa. Binciken ya dunshi babuka biyar, waDanda suke dunshe da gundarin aiki, tare da bayaninsu filla-filla. Babi na Daya ya dunshi shimfiDa ce, inda aka yi bayani a kan dalilin bincike, da manufar bincike, da muradin bincike, sai kuma hasashe, da farfajiyar bincike, da kuma hujjar ci gaba da bincike da sauransu. Babi na biyu ya dunshi waiwayen ayyukan da aka gudanar. Babi na uku ya yi dubi ne akan ire-iren bijirewa cikin wadodin Hausa lokacin mulkin mallaka da kuma zamunan siyasar farko. Babi na huDu ya dunshi wadodin da aka yi sakamakon kafuwar mulkin DimokiraDiyya, inda aka nuna bijirewa tsakanin jam'iyyun siyasa, da kuma mulkin siyasa. Babi na biyar yana Dauke da naDewa da sakamakon bincike inda aka gano cewa; Har ya zuwa wannan lokaci ana jin Duriyar wadodi na Hausa masu Dauke da bijirewa, Haka kuma a yanzu wato darni na ashirin da Daya ana samun wadodi masu Dauke da bijirewa. Da yawa daga cikin wadodin da aka nazarta suna Dauke da jigo na siyasa mai ratsin bijirewa al'adu da addini da kuma waDanda suke da dangantaka da tattalin arzidin dasa.

Cover Page……………………………………………………………………i
Declaration…………………………………………………………………..iii
Certification…………………………………………………………………iv
Godiya………………………………………………………………………..v
Abstract………………………………………………………………………x
Tsakure………………………………………………………………………xi

**BABI NA DAYA**

**SHIMFIDA**

1.1 Gabatarwa: ..……………………………………………………..……..1
1.2 Dalilin Bimcike: ..………………………...……………………….….2
1.3 Manufar Bincike: ...……………………………..……………..……..5
1.4 Muradin Bincike: ..……………………..……………………………5
1.5 Hasashen Bincike: ……………………………………………...........6
1.6 Farfajiyar Bincike…………………………………………………..6
1.7 Hujjar Ci Gaba da Bincike…………………………………………..…7
1.8 Hanyoyin Gudanar da Bincike………………………………………...8
1.8.1 Hanyoyin Tattara Bayanai Na farko………………………………...8
1.8.1.1 Hira…………………………………..………………………………9
1.8.1.2 Ziyara…………………………………………………....................9
1.8.2 Sauran Hanyoyin Tattara Bayanai………………..……………………..11
1.8.2.1 Kundayen Kammala Karatun Digiri na Uku da Biyu……………………11
1.8.2.2 Makalu…………………………………………………………...11
1.8.2.3 Litattafai….…………………………………………………………12
1.8.3 Tambayoyin Bincike……………………………………………….13

1.9 Lokutan da aka Aiwatar da Wakoki……….……………………………......13
1.10 Dalilan Zabo Wakoki……...………………………………………….....15
1.11 Yankunan da Wakokin Suka Fito…………….……………………….……16
1.12 Bayani Kan Kalmar Bijirewa……………………………………………….18
1.13 Ma’anar Bijirewa………………………………………………………...19
1.14 Rabe-raben Bijirewa………………………………………………………..24
1.14.1 Bijirewa Zazzafa……………………………………………………….24
1.14.2 Bijirewa Sassanya……………...………………………………………25
1.15 Ra’in Bincike……………………………………………………………….27
1.16 Kammalawa……………………………..……………………...……..30

**BABI NA BIYU**

**WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA**

2.1 Gabatarwa…………………………………………….……………...31
2.2 Kasar Hausa…………………………………………………..…………...31
2.3 Ginuwar Mulki a Kasar Hausa………………………………………………35
2.4 Tarihin Wakokin Bijirewa a Kasar Hausa…………………………….……..39
2.5 Ma’anar Siyasa…………………………………………………….…....47
2.6 Ginuwar Siyasar Zamani a Kasar Hausa……….……………………………50
2.6.1 Kafuwar Jam’iyyar NPC……………………………………………...51
2.6.2 Kafuwar Jam’iyyar NEPU……………………………………….…...53
2.7 Dimokiradiya……….……….…………………………………….……55
2.7.1 Kafuwar Jam’iyyun Siyasa Lokacin DimokuraDiyya………..…………..58
2.8 Kishin Kasa…………………………………………………………………..60
2.9 Neman Sauyi a Siyasar Kasar Hausa……………………...………….….61

2.10 Gwagwarmaya Tsakanin Malaman Addinin Musulunci da Turawan Mulkin Mallaka……………………….……………………………….……………..…..68

2.11 Gwagwarmayar 'Yan Shi'a da Gwamnati……………………………..…72

2.12 Rashin Jituwa Tsakanin Sarakunan Kasar Hausa da Turawan Mulkin Mallaka……………………………………………………………………..74

2.13 Gwagwarmayar Neman 'Yanci Daga Turawan Mulkin Mallaka…………..78

2.14 Gwagwarmayar Satirawa da Turawan Mulkin Mallaka…………………...83

2.15 Bore a Daular Usumaniya………………..……………………….……….85

2.16 Kammalawa…………………………………………………..….……....86

## BABI NA UKU

## BIJIREWA A WAKOKIN JAM'IYYUN SIYASA TA FARKO (1903-1991)

3.1 Gabatarwa……………………………………………………….……..…88

3.2 Bijire wa Mulkin Mallaka…………………………………………………..89

3.2.1 Bijire wa Zama Tare da Annasara………………...….……..……………92

3.2.1.1 Zagi………………………………………………………………….…...97

3.2.1.2 Kirari………………………..…………………………………........98

3.2.1.3 Karatun Boko……………………..………………………………….…....100

3.2.2 Hijira a Matsayin Hanyar Bijire wa Annasara………….…………….…..104

3.2.3 Shahada a Matsayin Hanyar Bijire wa Annasara………….………........…108

3.3 Jumhuriya ta Farko……………………………...…..…………..…….111

3.3.1 Kamfe……………………………………………………………..113

3.3.1.1 Kamfe Na Wakoki……………………………………………………...113

3.3.2 Shari'ar Zabe……………………………………………………..117

3.3.3 Zagi…………………………………………………………………118

3.3.4 Kirari……………………………………………………………………..120
3.3.5 Addu'a………………………………………………………………….121
3.4 Jumhuriya ta Biyu..……………………………………………………..…..123
3.4.1 Kamfe……………………………………………………………………..124
3.4.1.1 Kamfe Na Wakoki……………………………………………………...125
3.4.2 Shugabannin Mulkin Siyasa……………………………………………...131
3.4.3 Zabe…………………………………………………………………….132
3.4.4 Abokan Adawa…………………………………………………………134
3.4.4.1 Hamayya………………………………………………………………..135
3.4.5 Farfaganda……………………………………………………………...137
3.5 Jumhuriya ta Uku……………………………………………….……..142
3.5.1 Kamfe……………………………………………………………………..145
3.5.1.1 Kamfe Na Wakoki……………………………………………………...145
3.5.2 Kushewa………………………………………………………………..148
3.5.3 Rashin Adalci……………………………………………………………..150
3.6 Bijire Wa Shugabancin Gargajiya……………………………………….151
3.6.1 Bijire Wa Wasu Al'adun Gargajiya…..………..…………………….157
3.7 Nazarin Bijirewa a Cikin Wadar NEPU ta "Jiya Da Yau"………….....…..160
3.8 Kammalawa……………………………………………………...…166

**BABI NA HUKU**

**BIJIREWA A WAKOKIN DIMOKURAKIYYA (1991-2015)**

4.1 Gabatarwa…………………………………………………………......167
4.2 Bijirewa Tsakanin Jam'iyyun Siyasa……………………………………....168
4.2.1 Abokan Adawa………………………………..…………………….168

4.2.2 Gamayyar Jam'iyyu……………………………………………..…….175

4.3 Bijire wa Shugabanin Mulkin Siyasa……………..………..…………177

4.3.1 Rashin Kishin kasa……………………………………….……………182

4.3.2 Rashin Adalci…………………………………………………..…187

4.3.3 Yin Mulki……………………………………………………………192

4.3.4 Yaudara……………………………………………………………...196

4.4 Bijire Wa Rusa Tattalin Arzikin kasa………………..…….……………200

4.4.1 Cin Hanci……………………………………………………………203

4.5 Bijirewa ta Fuskar Farfaganda…………………………………….…..211

4.5.1 Zalunci……………………………..…………………………..223

4.5.2 Tonon Silili………………………………………………………….226

4.5.3 Zambo……………………………………………………………….228

4.6 Bajire Wa Tsarin Gudanar da Gwamnati……………………………..231

4.6.1 Fito-na-Fito………………………………………………….……232

4.6.2 Bijirewa ta Siyasa Mai Jibi da Addini…………………………..…..236

4.7 Nazarin Bijirewa a Cikin Wakar APC ta "Masu Gudu Su Gudu"….……..241

4.8 Kammalawa……………………………………………..……….246

**BABI NA BIYAR**

**NADEWA**

5.1 Kammalawa……………………………………………...………248

Sakamakon Bincike……………………………………………...……..250

Manazarta…………………………………………………………………….254

Ratayen Wasu Wakokin da Aka Yi Dogaro da Su……..………..…………...269

# BABI NA DAYA

# SHIMFIDA

## 1.1 Gabatarwa

Daya daga cikin hanyoyin da dan Adam yake more wa harshensa, shi ne furta kalamai ta sigar waka. Sauran hanyoyin kuma sun hada da wasa da kuma bayani a zube. A kasar Hausa amfani da waka domin isar da sako na addini ko na siyasa ko na wani abin da ya shafi rayuwa ba bakon abu ba ne, musamman bayan zuwan Musulunci a cikin karni na sha tara da na ashirin har ya zuwa yau (Idris 2010:1).

Haka kuma, za a ga cewa idan wani al'amari ya bullo wa Hausawa sukan yi amfani da waka domin magana a kansa. Dubi dai zamanin Shehu Usmanu Danfodiyo (1754-1817) da zuwan Turawa (1850-1906) da zamanin siyasar farko (1960-1966) da yakin Basasa (1966-1970) da juye-juyen mulki da shigowar mulkin dimokiradiya (1970 zuwa yau), da dai duk wani yanayi da ya taso wa al'umma kuma ake yin amfani da waka don isar da sako na fadakar da jama'a. A takaice, ana iya cewa, waka na daya daga cikin hanyoyin da Bahaushe ke bi domin amayar da abin da ke birnin zuciyarsa ga jama'a. Bugu da kari, waka na daya daga cikin hanyoyin da ake bi domin taskace wasu abubuwan tarihi da kuma al'adun Gargajiya.

Wannan babi, shimfida ce kan binciken da za a gudanar a kan "Bijirewa A Wakokin Siyasa: Bincike Kan Wakokin 1903-2015." A kokarin gabatar da aikin, a cikin babi na farko an kawo bayani a kan dalilin bincike, da manufar bincike, sai kuma Muradin bincike wato muradin da aka hango, kuma ake son cim mawa

wannan nazari. Wannan shi ya kai mu ga hasashen da aka yi idan aka gudanar da wannan aiki. Daga hasashe kuma, sai aka yi tsokaci kan Farfajiyar bincike da kuma hujjojin da aka dogara da su don gudanar da wannan bincike. Hanyoyin tattara bayanan binciken sun fada karkashin wannan babi, inda aka fayyace, dalla-dalla, duk wata hanya da aka bi domin ganin cewa haka ta cim ma ruwa. Haka kuma duk dai a karkashin hanyoyin tattara bayanai, an dubi dalilin da ya sa aka zabi wakokin da aka yi amfani da su, da kuma yankunan da wakokin suka fito. A karshe an kawo bayani a kan ra'in bincike, wato ra'in da aka dora wannan aiki a kansa.

## 1.2 Dalilan Bincike

Dalilan da ya jawo hankali ga yin wannan nazari sun hada da:

Babu wani aiki da hannu ya kai kansa da aka yi wanda ya taskace wakokin siyasa ya dubi bijirewa a cikinsu, musamman a matakin karatun digiri na uku. Ana sa ran wannan aiki ya zama wani kammalallen nazari a kan wakokin siyasa wadanda ke kunshe da bijirewa, domin amfanin dalibai da Malamai da duk wani mai sha'awar nazarin adabi musamman waka.

Kamar kowane bincike da ake yi, yana daga cikin dailan yin wannan aiki zakulo wasu abubuwa masu muhimmanci da ta yiwu ba a sani ba da farko, idan kuwa an sani, watakila ba a gane ba sosai da sosai. Ana fata binciken zai taimaka wajen ci gaban adabi kocankau musamman fagen nazarin waka wanda yake bukatar aiki sosai domin fayyace manufar masu yin ta.

Wani babban dalilin yin wannan bincike shi ne, ya kara iza wasu dalibai iri na su dukufa wajen fadada wannan batu ta hanyar bincike mai zurfi da gabatar da rubuce-rubuce a kansa. Yin haka zai sa a samar wa wakoki masu dauke da bijirewa cikakken gurbi cikin nazarin adabin Hausa.

Domin fito da matsayi da muhimmancin waka wajen habaka mulkin dimokiradiyya.

Ana fatar wannan bincike ya zama mai amfani ga masu nazarin kimiyyar siyasa, domin akwai dangantaka a tsakani. Za a sami jituwa tsakanin fagagen, manazarta adabi su nazarci abubuwan da za su gina al'umma, masu nazarin kimiyyar siyasa su nazarci abin da ya shafi adabi.

Ana kuma fatar wannan bincike zai zama mai fa'ida ga manazarta tarihi, wato ta yadda aka sami canji a yanayin siyasar Nijeriya, har ya haifar da wakoki masu dauke da bijirewa shi ma zai shiga cikin tarihin Nijeriya. Wannan zai taimaka wajen adana tarihi.

Manazarta adabi, su ma za su ci gajiyar wannan aiki, don aikin ya tabo wani ginshikin sashe na adabi, wato waka. Ko a cikin rabe-raben adabi, manazartan suna ji da waka, domin a iya cewa, an fi yi mata hidima fiye da sauran dangoginta. Sannan kuma, yadda aka sami cakuduwar nau'o'in wakokin Hausa a wuri daya, shi ma wani ci gaban adabi ne.

Yana daga cikin dalilin yin wannan aiki ya zama mai fa'ida ga hukuma, domin ta irin wadannan nazarce-nazarce ne hukuma za ta san yadda jama'a ke kallonta,

wato yadda take gudanar da harkokin mulki. Ana kuma sa ran samin canji ta hanyar taimakon ire-iren wadannan bincike.

Ga manazarta al'ada kuwa, wannan bincike ya zama mai dadi a gare su, yadda aka sami sauyin dabi'un Hausawa, musamman yadda Hausawa suke yin wakoki suna bijire wa gwamnati, bayan an san Hausawa da kawaici da kunya.

Ana sa ran wannan bincike zai zama jagora ga marubuta masu son wannan fanni da su kara kokari wajen abubuwa da suka danganci siyasa domin inganta mulkin dimokiradiyya a kasa.

Wani dalili na yin wannan aiki shi ne, irin rawar da wakokin da sha'irai ke takawa wajen wayar da kan jama'a cikin ruwan sanyi. Yana da muhimmanci a yi nazarin wakokin domin irin gagarumin yakin da suke yi wanda da wuya a sami wata hanya mai fa'ida irin wannan.

A takaice za a nazarci bijirewa kamar yadda ta fito a cikin wakokin da aka sami sakamakon siyasar mulkin mallaka, da kuma wakokin da aka sami a cikin Jumhuriya da daya zuwa ta uku. Haka kuma za a kalli ire-iren wakokin da aka yi sakamakon irin mulkin da sarakuna suke aiwatarwa. A gaba kuma za a dubi wakokin da aka yi sakamakon dawowar kasar nan mulkin dimokiradiyya, da kuma irin wakokin da aka yi domin yin watsi da yadda shugabanni suke tafiyar da mulkin kasa.

### 1.3 Manufar Bincike

Babu wani aiki da hannu ya kai kansa da aka yi wanda ya taskace wakokin siyasa ya dubi bijirewa a cikinsu, musamman a matakin karatun digiri na uku kamar wannan da aka yi. Ana sa ran wannan aiki ya zama wani kammalallen aiki a kan wakokin siyasa masu dauke da bijirewa, domin amfanin dalibai da Malamai da duk wani mai sha'awar nazarin adabi musamman waka. Kamar kowane bincike da ake yi, akan yi shi ne domin zakulo wasu abubuwa masu muhimmanci da ta yiwu ba a sani ba da farko, idan kuwa an sani, watakila ba a gane ba sosai da sosai.

### 1.4 Muradin Bincike

Tabbatar da cewa, akwai wakokin bijirewa a kasar Hausa sabanin da ake cewa, baya ga wakokin jihadi babu wakoki masu dauke da bijirewa.

Bijirewa fitaccen jigo ne a cikin jigogin wakokin Hausa. Ana samin wakoki masu dauke da bijirewa duk da cewa ba su ne suka fi yawa ba.

A yi kokarin gano cewa, ana samin ratsin jigon bijirewa a cikin rubutattun wakokin siyasa na Hausa.

A da ba a jin duriyar wakoki masu dauke da bijirewa, amma a baya-baya musamman daga goshin karni na ashirin da daya zuwa yau ana jin motsinsu.

Wakokin siyasa masu dauke da bijirewa ba za su kare ba a kasar Hausa.

Yana daga cikin muradin wannan aiki, a fito da matsayin waka ta fuskar wayar da kan jama'a musamman a harkokin siyasa.

Haka kuma, muradin wannan aiki ne fito da irin gudummuwar da marubuta wakoki suka bayar wajen habaka wannan manufa ta bijirewa a cikin wakokin siyasa da ba kasafai ake rubuta wani abu a kanta ba.

Akida tana daga cikin tubalin gina wakoki masu dauke da bijirewa a cikinsu. Wannan ya sa za a nazarci wakokin domin tabbatar da hakan.

**1.5 Hasashen Bincike**

Me ke haifar da bijirewa?

Wadanne irin jigogi ne wakoki masu dauke da bijirewa suke dauke da  shi na addini ne ko na siyasa ko kuma na addini mai jibi da siyasa ko kuwa na zamantakewa ne?

Yaya sigogin wakoki masu dauke da bijirewa suke?

**1.6 Farfajiyar Bincike**

Wannan bincike zai takaita ne a kan rubutattun wakoki na siyasa a tsakanin (1903-2015) Daga cikin wakokin da za a nazarta, akwai wadanda aka yi a lokacin mulkin mallaka da suka hada da;

Wakar Annasara ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu
Wakar Baturen Ingilishi ta Shehu Shagari
Haka kuma akwai wakoki masu dauke da bijirewa da aka yi a Jumhuriya ta farko da suka hada da;

Wakar NPC ta Muhammadu Gidado, wakar yabon Sardauna
Wakar NEPU ta Gambo Hawaja, ‘Yan Sawaba

Daga cikin wakokin da aka yi nazari a Jumhuriya ta biyu sun hada da;

Wakar Mu Mun Koma N.P.N. ta Muhammad Sulaiman Dundaye

Wakar P.R.P. Gumbar Dutse ta Muhammad Sulaiman Dundaye

A Jumhuriya ta uku kuwa sun hada da;

Wakar SDP ta Auwalu Isah

Wakar UNCP ta Haruna Aliyu Ningi

Za a yi amfani da wakoki masu dauke da bijirewa a Jumhuriya ta hudu da dama da suka hada da;

Wakar Siyasa Rigar ‘Yanci ta Abdul’Azizi Abdullahi Ningi

Wakar Baubawan Burmi ta Aminu Ala

Wakar CPC ta Kama shi Lado

Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu

**1.7 Hujjar Ci Gaba Da Bincike**

A fili yake cewa cikin ayyukan da aka duba an sami gudummuwa a kan adabin Hausa, musamman a fagen rubutacciyar waka. To amma ba abu mai wuya ba ne a lura da cewa a cikin duk wadannan ayyuka, bijirewa a cikin rubutattun wakokin siyasa a kasar Hausa ba ta sami zuzzurfan nazarin da ya kamace ta ba.

Aikin Harlow (1987) da mukalar Malumfashi (1988) da Mungadi (2000) da Imam (2002) da kuma Yakawada (2013) za a iya cewa, shimfida ce ko sharar fage ce ga manazarta wakokin bijirewa na Hausa. Ayyukan sun fito da nau’o’i da dama na wakokin Hausa masu dauke da bijirewa. Amma dukansu babu tsararre kuma kammalallen aiki irin wannan. Saboda haka ne ma aka sami kwarin guiwar

gudanar da wannan bincike a kan wakokin siyasa rubutattu a kasar Hausa masu dauke da bijirewa, wato da zimmar ganin binciken ya kasance fadada ga abubuwan da suka baro a baya da wadanda ba su tsinkayo ba da wadanda suka kubuce mu su, da kuma duk wata wakar baka ta siyasa da aka juye aka rubuce ta. Dalilin haka shi ne, yawancin wakokin baka musamman wadanda suka jibanci siyasa suna kan tsari mai kyau na rubutattun wakoki. Da yawa suna da kari mai kyau da za su iya hawa ma'aunin karin rubutacciyar waka. Duka-duka an tsakace wakoki 67 saboda bukatar wannan nazari an tafi bisa fahimta cewa, duk wakar da ta fuskanci shugabanci ko tsarin mulki ta zama wakar siyasa. Wadannan hujjoji, su suka ja hankali da a gudanar da wannan bincike domin a tantance rawar da bijirewa ta taka a cikin rubutattun wakokin siyasa a kasar Hausa.

### 1.8 Hanyoyin Gudanar Da Bincike

Hanyoyin da aka bi wajen tattara muhimman bayanai domin aiwatar da wannan bincike suna da yawa. An yi amfani da wadannan hanyoyin kamar haka:

#### 1.8.1 Hanyoyin Tattara Bayanai na Farko

Wannan hanya ita ce ta farko, wato mafi muhimmanci da aka bi domin samin muhimman bayanai da kuma yin tambayoyi ga wadansu mutane da suke da dangantaka da wakokin da aka yi amfani da su. Wadannan hanyoyi sun hada da;

Hira da tattaunawa da mutanen da suka mallaki kwafe na wasu wakokin da za a yi amfani da su, ko kuma suke da alaka da wasu daga cikin wakokin da ake nema.

#### 1.8.1.1 Hira

- Hira da marigayi Malam Ibrahim Gandi ranar 11-02-2012 a cibiyar nazarin Hausa da ke jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto

- Hira da Farfesa Sambo Wali Junaidu ranar 23-04 2012 a cikin ofis da ke sashen koyon Larabci, Jamia'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

- Hira da Farfesa Muhammad Bala Jega ranar 14-05-2012 na sashen kimiyyar siyasa da ke Jami'ar Usmanu Danfodoyo, Sokoto.

- Hira da Farfesa Bello Sa'id ranar 16-06-2012 a gidansa da ke unguwar Rijiyar Zaki a cikin garin Kano.

#### 1.8.1.2 Ziyara

An kai ziyara wurare da dama da niyyar tattatro muhimman bayanai da za su taimaka wajen zaman aikin daram. Wuraren da aka ziyarta sun hada da;

- Gidan Wazirin Sakkwato da ke unguwar gidadawa a cikin garin Sakkwato, sakamakon wannan ziyara an sami wakoki da dama, musamman wadanda aka yi lokacin mulkin mallaka. An sami wakokin Malam Abubakar Maikaturu, musamman wakar nan tasa mai suna "Gudun Duniya" da wakar Shehu Shagari mai suna "Baturen Ingilishi" da kuma wakar Malam Ibrahim Khalil Marinar Tsamiya Sakkwato mai suna "Dubi Musulmi." A wannan gida ne aka sami kwafe na wakar "Zuwan Annasara Kasar Hausa da aka danganta da Labbo Dan Mariya.

- Haka kuma an ziyarci Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero a Kano. A wannan cibiya an sami rubutattun wakoki na sha'irai daban-daban da suka hada da wakoki kamar: Wakar Annasara ta Mahrazu Barmu Kwasare, da Wakar 'Yan Santsi Gammon sabara, da Wakar Mu Mun Koma N.P.N. da Wakar P.R.P. Gumbar Dutse dukansu na Muhammad Sulaiman Dundaye, da Wakar 'Yan Sawaba ta Gambo Hawaja, da Wakar "Siyasa Zamanin Salama" ta Muhammadu Bello Gidadawa, da kuma Wakar "Yabon Sardauna" ta Muhammadu Gidado da sauransu.

- An ziyarci gidan tarihi na "Wazirin Sakkwato Junaidu' a cikin garin Sakkwato an sami muhimman takardu, musamman a game da garin Satiru a inda aka sami kundin kammala karatun digiri na biyu mai take The Satiru Revolt C 1804-1906, Mohammed, A.S. (1989), Department of Sociology A. B. U. Zaria. Haka kuma an sami gani da ido na wasu daga cikin kayan fadan da mutanen garin Satiru suka yi amfani da su a lokacin da suka bijire wa zuwan Turawan mulkin Mallaka garin Satiru.

- An ziyarci gidajen rediyo na "Rima Rediyo" ta jihar Sakkwato da gidan rediyon tarayya a Kaduna da kuma gidan rediyon jahar Kano, Jigawa da kuma Zamfara. Sakamakon wannan ziyara an sami wakoki da yawa wadanda suke da nasaba da wannan nazari. Wasu wakokin a cikin kaset-kaset aka same su aka juye su. Wasu kuwa a cikin CD-CD suke, su ma aka juye su aka rubuce. Ziyarar da aka kai gidan rediyon Rima na jihar

Sakkwato, kwalliya ta biya kudin sabulu saboda gamo da katar da aka yi da wakokin siyasa, musamman wadanda aka yi a zamanin siyasar Jumhuriya ta uku da kuma hudu.

### 1.8.2 Sauran Hanyoyin Tattara Bayanai

Haka kuma an yi amfani da wadansu karin hanyoyi wajen tattara muhimman bayanai da za su kai wannan bincike zuwa gaci. Sauran hanyoyin da aka bi sun hada da;

#### 1.8.2.1 Kundayen Kammala Karatun Digiri Na Uku Da Na Biyu

Kundayen kammala karatun digiri na uku da aka yi bita sun hada da: Patton (1975) da Muhammad (1977) da Furniss (1977) da Dangambo (1980) da Birniwa (1987) da Yahya (1987) da Sa'id (2002) da Yakawada (2002) da Birnin-Tudu (2007) da Ainu (2008) da Usman (2008) da sauransu. Haka kuma an duba kundayen kammala karatun digiri na biyu da suka hada da: Ahmad (1982) da Birniwa (1981) da Omar (1983) da Sa'id (1978) da Dunfawa (1983) da Mungadi (2000) da Dangulbi (2008) da Funtua (2003) da Sifawa (2011) da kuma Bunza (2012) da sauransu.

#### 1.8.2.2 Makalu

Kamar yadda aka dubi kundayen kammala karatun digiri na uku da na biyu, haka kuma an dubi makalu iri daban-daban domin nazari wadanda suka hada da: Malumfashi, A. (1988) "Resistance in Hausa Written Poetry : 1903 - 1960 da, Habib, A. (1988) "Rashin Jituwa Tsakanin Malaman Satiru da Turawan Mulkin

Mallaka, da Sa'id, B. (1995) " The Reaction of Hausa Poets to Western Civilisation" da, Amin, M. L. (1997) "Ra'ayin Sauyi a Wakokin Sa'adu Zungur" da, Mukhtar, I. (1999) "The Form and Content of Resistance to European Expansion in the Sokoto Caliphate: A Documented Evidence From a Hausa Literary Poem of Sultan Attahiru Ahmadu 1 (1902 - 1903)" da, Yakawada, M. T. (2013) "Adabi da Harkokin Siyasa: Bijirewa a Wakar Shegiyar Uwa mai Kashe 'Ya'yanta PDP" da, Isah, Z. (2013) "Gudummuwar Mawakan Hausa ga Ci Gaban Arewacin Nijeriya: Nazarin Wakar Ajanda" da sauransu da dama.

**1.8.2.3 Littafai**

An nazarci littatafai da dama a fannoni daban- daban da suke da dangantaka da wannan aiki. An nazarci littatafan da suke da nasaba da tarihi da siyasa da addini da zuwan Turawan mulkin mallaka da waka da kuma abin da ya shafi bore. Miasli an nazarci littatafai kamar Adeleye R. A. (1971) *Power and Diplomacy in Northern Nigeria,* da Duldey, B. J. (1968) *Parties and Politics in Northern Nigeria* da, da Paden, J. N. (1973) *Religion and Political Culture in Kano,* da Mani, A. (1956) *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa,* da kuma Abdukadir, A. (1977,1979) *Life, Poetry and Opinions of Sa'adu Zungur,* da kuma littafinsa mai suna, *Zababbun Wakokin Da na Yanzu,* da Yakubu, A. M. (1999) *Sa'adu Zungur : An Anthology of the Social and Political Writings of a Nigerian Nationalist,* da Jega, A, et al eds (2003) *The Public Poet : A Biography of Mudi Sipikin,* da Sokoto, M. (2008) In Darah, G. G. eds *Radical Eassys on Nigerian Literature* da sauransu da dama.

### 1.8.3 Tambayoyin Bincike

Sakamakon ganawa da aka yi da wadansu mutane an yi musu tambayoyi, daga cikin irin tambayoyin da aka musu sun hada da;

- Akwai wakokin Hausa na siyasa masu dauke da bijirewa?
- Wane lokaci ne aka fara samin wakokin Hausa masu dauke da bijirewa?
- Ko akwai dangantaka tsakanin wakokin da kuma wadanda suka rubuta su?

### 1.9 Lokutan Da Aka Aiwatar Da Wakokin

Bincike ya nuna cewa wakokin Hausa wadanda suke dauke da bijirewa a cikinsu, Hausawa sun fara aiwatar da su tun tsawon lokaci kafin zuwan Turawan mulkin mallaka, wato bayan sun yi cudanya da Larabawa. Misali wakar *"Ya Ghiyathul Mustagithina"* ta Hayatu Dan Bello. da wakar *"Tsarin Mulkin Musulunci"* da wakar *"Murnar cin birnin Alkalawa* dukansu na Abdullahi Fodiyo. Haka kuma akwai wakar Malam Muhammadu Na Birnin-Gwari mai suna *"Billahi Arumu"* da kuma wakar *"Kogi"* da limamin Daura ne Hassan ya yi ta (Malufashi 1988). Wadannan wakoki akwai bijirewa a cikinsu ganin manufar da take cikinsu, tana bayani ne a kan rashin adalcin sarakuna a kan talakawansu. Wakokin da aka nazarta a karkashin wannan bincike wadanda suke dauke da bijirewa a cikinsu, Hausawa sun same su ne bayan sun cudanya da Turawa da addinin Musulunci da kuma al'adun da suka zo da su musamman sababbin abubuwa na rayuwa kamar kayayyakin sawa da karatun boko da keke da ruwan famfo da sauran abubuwa da dama.

Zuwan Turawa ya yi mutukar tasiri wajen karkata hankulan marubuta wakokin Hausa, musamman wajen tsara wakokin da suke nuna rashin yarda da wadannan bakin al'ummu. A bangaren Malamai marubuta littatafai da wakoki nan abin ya fi bazuwa, marubuta daga cikin Malaman kamar su Malam Darho da Sarkin Musulmi Attahiru da Labbo dan Mariya da Malam Muharazu da Malam Abubakar Maikaturu da Malam Ibrahim Khalil Marinar Tsamiya da Alkali Haliru Wurno da Shehu Shagari da Sa'adu Zungur da sauransu. Dukansu sun yi 'yan tsarmi-tsarmin baitoci. Wadansu daga cikinsu kuma waka sosai suka rubuta ta kushe manufar Nasara da dasisarsa wadansu kuma a kan manufofin siyasunsu, suna kushe wa abokan gaba a wasu lokuta suna bijire wa gwamnati da sauran abubuwa.

Kafin Turawa su mika wa 'yan kasa jagorancin tafiyar da harkokin mulkin Nijeriya, an fito da maganar kafa jam'iyyun siyasa kamar su NPC da NEPU da AG da kuma NCNC. Bayan samin 'yancin kai da wadannan jam'iyyu aka kafa Jumhuriya ta farko. A Jumhuriya ta biyu an sami jam'iyyun NPN da PRP a nan yankin Arewa. A Jumhuriya ta uku kuwa da ake dauka a matsayin bararriyar Jumhuriya an sami jam'iyyun SDP da NRC. Haka kuma Jumhuriya ta hudu an sami jam'iyyun siyasa irin su APP da PDP da ANPP da AC da ACN da DPP da CPC da APC. Kasancewar wadannan Jam'iyyu na yankuna da farko kafin a gaba a sami su zama na kasa baki daya. Sakamakon haka an yi musu wakoki na Hausa masu yawa dauke da manufofi masu yawa da suka hada da bijirewa a tsakanin su jam'iyyun ko kuma a cikin jam'iyya ko kuma domin yin farfaganda ko tattalin arziki ko kuma a bijire wa masu mulki na siyasa ko Gargajiya. A takaice,

wadannan wakoki da aka zaba, aka yi nazarinsu sun sami ne lokacin mulkin mallaka zuwa Jumhuriya ta hudu.

### 1.10 Dalilan Zabo Wakoki

Wannan bincike an tsara gudanar da shi a kan wakokin Hausa na siyasa da suke dauke da bijirewa a cikinsu. Sakamakon haka, duk wata waka da aka ci karo da ita wadda take dauke da daya daga cikin mizanan da aka zayyana a kasa, za a yi amfani da ita domin yin wannan nazari. Wadannan mizanai sun hada da; neman ‘yanci, da akida, da kishin kasa, da fadakar da masu mulki, da ayyuka kan talaka, da rashin adalci, da fito-na-fito, da bore, da kuma Adawa.

wakokin sun shahara a kasar Hausa musamman ta fuskar kasancewarsu kaifi daya da kuma nuna son kasarsu kamar yadda yake fitowa a cikin wakokin. Misali, idan aka kalli ire-iren wakokin da aka yi a lokacin mulkin mallaka, za a tarar a cike suke da manufa ta kin aminta da Annasara gabadayansa da abubuwan da ya zo da su. Haka kuma wakokin suna dauke da gwagwarmaya ta neman ‘yancin kasa daga wajen Turawa. Wakoki irin na su Abubbakar Maikaturu da Amirul Muminin Attahiru Ahmadu da wakar Baturen Ingilishi ta Shehu Shagari da wakar Annasara ta Maharazu Kwasare da wakar Ku Dubi Musulmi ta Ibrahim Khalil duk cike suke da akida da kuma kishin kasa.

Haka abin yake idan aka yi la’akari da mafi yawan wakokin siyasa da aka sami musamman a Jumhuriya ta farko zuwa ta biyu. Wakokin NEPU da NPC da na PRP da NPN da yawansu akwai burbushi na akida da kishin kasa a cikinsu. Akilu Aliyu fitaccen mawakin NEPU ne mai tabbatacciyar akida ta siyasar NEPU.

Wakokinsa sun tsaya kai da fata wajen ceton talakawa daga cikin kangi na rashin walwala da ‘yanci da suke ciki. Haka Sa’adu Zungur, wakarsa ta Jihadin Neman Sawaba, waka ce da ta yi fice a wancan lokaci wajen fuskantar halin da talakawa suke ciki falan daya ba tare da wani gashi gashi ba.

Duk da cewa an sami canji kadan, amma haka abin ya gangaro har ya zuwa wannan lokaci da ake ciki na Jumhuriya ta hudu a halin yanzu. Mawaka musamman na jam’iyyun adawa suna nan a kan dabi’a ta son kasarsu da kuma kishin mutanensu.

**1.11 Yankuna Da Wakokin Suka Fito**

Wakokin da aka yi amfani da su a cikin wannan aiki sun fito daga yankuna daban-daban a cikin kasar Hausa, sai dai da yawa daga cikinsu sun fito daga yankin kasar Sakkwato. Wannan kuwa bai rasa nasaba da kasancewar Sakkwato cibiyar daular Usmaniyya, duk da cewa ba lokacin jihadi aka fara samin waka ba. Abdulkadir (1977:6) ya da ra’ayin, I, ba shakka a lokacin jihadi ne aka fi rubuta wakoki domin watsa manufar jihadi da dalilin yinsa, amma a kashin gaskiya tun kafin jihadi ana rubuta wakoki a wannan kasa.

Wakoki da suke dauke da bijirewa musamman lokacin mulkin mallaka, sun yawaita a lardin Sakkwato saboda tasirin jihadi wanda ya haifar da yawaitar maluman addinin Musulunci. Hiskett (1975:92) yana da ra’ayi, rubutattun wakoki a kasar Hausa suna kan tsari na addinin Musulunci, saboda ilimin da marubtan suke da shi na Musulunci ne, haka kuma tsarin rayuwarsu ma na Musulunci ne.

Ya kara da cewa rubuta wakoki na bore ba su zama daban ba a kan wannan tsari. Ba komai ya kawo haka ba, sai domin fahimtar marubutan ta cewa da yawa daga cikin mutane ba sa gudanar da rayuwar bisa koyarwar addinin Musulunci, sai son abun duniya da ya haifar da tazara tsakanin masu hali da talakawa.

Mani (1956:13) ya kawo ra'ayinsa inda yake fada, Mujaddadi Shehu Usmanu Danfodiyo ya fada a cikin wasiyyar da ya yi wa jama'ar kasar nan cewa zuwa gaba akwai wadanda za su zo. Idan mutum ya dubi ranar da jama'a suka yi wa Shehu mubaya'a a Gudu cikin watan Fabarariru 1804, watau kusan shekara dari kenan daidai da lokacin da Turawa suka ci Sakkwato. Daular Usmaniyya ta yi yunkurin kawar da Turawan mulkin mallaka da karfin Allah, da amfani da alkalami musamman wajen tsara wakoki da suka soki dasisar Annasara.

Haka kuma an sami wasu wakokin daga sauran larduna daban-daban a cikin kasar Hausa, wannan kuwa bai rasa nasaba da abin da Malumfashi (1988:2) yana ra'ayin cewa, "Ana amfani da rubutattun wakoki wajen bijire wa rashin adalci daga shugabanni ko sauran mutane da kuma kalubalantar duk wadansu tanade-tanade da suka saba da tsarin zamantakewa. Ya fada a cikin mukalarsa cewa, akwai waka mai suna "Kogi" da limamin Daura na wancan lokacin Hassan ya rubuta. Wakar tana bayyana ire-iren rashin adalci shugabanni na wancan lokaci.

**1.12 Bayani a Kan Kalmar Bijirewa.**

Bijirewa kalma ce da ake amfani da ita a harshen Hausa tilo mai dauke da jinsin mace da ta tsiro daga aiki *bijire* wadda take nufin kin yarda ko rashin amincewa musamman ta fuskar ra'ayi. Idan aka dubi tasirin wannan kalma, za a tarar ana

amfani da ita a fagen waka. kalmar bijirewa ‘yar aikatau ce watau bijire, sai aka dafa mata dafin suna dan aikatau na wa sai aka sami bijirewa.

Kalmar bijirewa tana da gaba hudu kamar haka = bi / ji / ree / waa

Tsarin karin sautin kalmar bijirewa zai kama kamar haka = b**í jì** r**eé** w**áá**

Kalmar bijirewa tana kunshe da kwayoyin ma’ana uku kamar haka, saiwa da dafi na farko ee da kuma dafi na biyu waa.

Saiwa → bijir

dafi na 1 → ee (dafin kalma ‘yar aji hudu, kuma budadde ne).

dafi na 3 → waa (dafi ne budadde wanda ba ya sauya tsarin karin sauti).

kalma = saiwa + dafi(1) + dafi(2) bijir ee waa (dafin suna dan aikatau)

Haka kuma wannan kalma tana daukar kari a farkonta da kuma a karshe. Kalmar tana daukar dafi biyu zuwa uku, misali zai yiwu a dafa mata alamar dafin n, a farkonta kamar dan/yan/masu da sauransu, a karshe kuma ta dauki dafi har guda biyu ee da kuma waa. A takaice ga yadda kalmar take, ana iya samin:

**Bijir**, a matsayin saiwar kalma sannan a sami,

**Bijire**, a matsayin kalma ‘yar aikatau dan aji hudu, haka kuma, ana samin

**Bijiro**, a matsayin kalma ‘yar aikatau dan aji shida. Sai kuma

**Bijirewa**, a matsayin kalma da aka yi wa dafi na biyu da take a matsayin sunan aiki kuma, ta na daga cikin kalmar da aka yi amfani da ita a cikin wannan aiki. Baya ga wannan, akwai tsari da kalmar take dauka ta zama:

**Bijire wa**, a matsayin kalmar aiki da take dauke da hannun aiki na wa, sannan akwai

**Bijirarru**, kalmar da take a matsayin jam'i.

### 1.13 Ma'anar Bijirewa

A cikin "Encyclopedia of Social Science vol 7 page 207 – 208" an bayyana kalmar bijirewa a fagen siyasa, tamkar ta 'yan ra'ayin rikau kuma tsari ne da 'yan gurguzu ke yi wa jagoranci. Edmund Burke shi ne ya assasa wannan tsari na bijirewa a cikin fagen siyasa tare da kafa misali daga bijirewar da 'yan juyin-juya-hali na kasar Faransa suka yi a shekarar 1790.

Bijirewa ita ce mutum ya zama mai cijewa ko ya zama dan turu ko sabawa ko fandArewa ga wata hukuma ko kungiya a siyasance ko a addinance. Wannan cijewa za ta iya haifar da fito-na-fito a tsakanin kungiyoyi biyu. Sau da yawa bijirewa takan faru cikin dangi ko cikin wata al'umma da suka yi tarayyar wurin zama a unguwa ko a gari ko kasa da sauransu (Imam :2002). Ya kara da cewa, ashe kenan, bijirewa za a iya sanya ta a cikin sahun abubuwan da suka zama tilas a sami hagu a kuma sami dama. A lokacin da wani ya ce zama, sai wani ya bijire ya ce shi mikewa zai yi. Haka dai kullum duniya take tafiya cikin sabanin ra'ayi.

Irin wannan sabanin ra'ayi ya fi samiwa a cikin gungun mutane masu ra'ayin siyasa ko addini iri daya. Haka tarihi ya nuna tun farkon duniya da Allah ya fara aiko da manzanni, idan an sami wadanda suka yi imani da su to za a sami wadanda suka bijire. Wannan irin tafiya ce ta dinga gangarowa tana malala har ta iso wannan lokaci da aka sami salon a cikin wakoki.

A cikin Kamusun Bargery (1934) an bayyana kalmar bijirewa kamar haka:

-Abu ya buwaya

-Abu ya wuce wuri, ya buwayi magani

Al-Maududi (1963) cewa ya yi, duk lokacin da wani ya dauki wani makami ya Allah takobi ne ko alkalami, sannan ya nuna kiyayya ga wata hukuma ko mai mulki ko tsarin da yake ganin ya saba da ra'ayinsa shi ne bijirewa.

Ahmad (1963) sai ya ce abin da ake nufi da bijirewa shi ne, mutum yana tafiya tare da wasu a kan ra'ayi na siyasa ko addini, amma saboda wani dalili na bambancin manufa sai ya kauce wa wannan ra'ayi ko ma ya kirkiri na kashin kansa. Idan ya yi haka ya nuna bijirewarsa ke nan.

Shi kuwa Skinner (1965:35) a cikin sabon kamus na Hausa zuwa Turanci ya bayyana kalmar bijirewa da cewa;

-Yin yaji

-Tawaye

-Kin amincewa

-Yin watsi da wani abu

Idan aka dubi bayanan da aka kawo a kan kalmar bijirewa sai a ce, ma'anar bijirewa tana iya daukar manufofi da dama. Na farko tana iya tafiya bisa zamantakewa, inda take nufin nuna kiyayya ga wani abu ko wani tsari na hukuma.

Manufa ta biyu ita ce, bangaren siyasa a inda take nuni da kin aminta da ra'ayin juna, haka kuma takan iya daukar manufa ta bayyana tsatstsauran ra'ayi a kan addini.

Shi kuwa Okoth (1979:121) sai ya ce, idan aka yi maganar bijirewa ana nufin, yunkurin da 'yan Afirka suka yi na kare kasashensu daga mamayar bakin haure wato Turawan mulkin mallaka. Ya kara da cewa ana iya daukar bijirewa a matsayin adawa da 'yan Afirka suka nuna wajen kokarin mulkarsu da aka zo a yi daga kasashen Turawa.

Ma'anar bijirewa ta farko za ta hau mizani na irin matakan da al'umomin Afirka suka dauka wajen yin gwagwarmaya da Turawan mulkin mallaka. Kadan daga cikin 'yan Afirkan da za a iya dangantawa da irin wannan gwagwarmaya sun hada da boren Abushiri's (1888 – 1889 a Afirka ta Gabas) da na Ndebele (1882 – 1890 a Afirka ta Kudu) da Naudi da Samory (c. 1830 – June 2, 1900 a kasar Guinea) da kuma Mubarak bin Rashid

Ma'anar bijirewa ta biyu kuwa, za ta  hau mizanin irin abin da ya faru lokacin da aka yi yakin Maji-Maji a kasar Tangayinka da kuma adawar da Mende Temne (1898 a kasar Sierra Leone) ya yi.

Ga abin da aka sami Ndebele (1882 - 1890) yana fada a game da bijire wa Turawa da mutanensu suka yi, cikin Talton (2006:3):

> Sun zo suna yin lalata da matanmu da 'ya'yanmu mata suna wulakan ta su sai muka ga abin ya wuce misali, sai muka yi niyyar yin fada da su domin mutuwa ta fi a gare mu a kan wulakancin da suke mana.

Sai kuma ya ce:

> Akwai bacin rai saboda an kwace mana shanu masu yawa, mun koma ba mu da komai na kanmu sai muka ce, zama haka ba zai yiwu ba, mutuwa ta fi a gare mu da wannan yanayi da muke ciki, kawai sai muka shiga yin fada da su.

A nan ana iya fahimtar cewa, kin yarda ita ce bijirewa kamar dai yadda aka gani, ‘yan Afirka sun ki yarda da Turawan mulkin mallaka. A gaba kuma, duk dai a game da abin da masana suka ce a kan kalmar bijirewa, ga abin da aka sami Dangambo (1984:35) ya fada;

> A ganina wakokin Hausa, yanzu suna neman bijirewa, su canza daga tsari na Larabci suna ginuwa ya zuwa siffar kansu. Muna iya ganin haka idan muka dubi halayyar yanaye-yanayen waka a yanzu, ta fuskar jigo da salo da zubi da tsari da kari ko murya da sauransu.

Wannan shi ne dalilina da nake ganin babu laifi idan an kalli kalmar bijirewa ta fuskoki da dama da suka shafi bangarorin rayuwa na jama’a gaba daya kamar yadda za a gani nan gaba. Lokacin da Turawa suka zo kasar Hausa ba su sami karbuwa ba yadda suka so, domin tsarin rayuwarsu da al’adunsu sun saba wa na Hausawa. Wannan shi ya haifar da rashin jituwa wadda ta sa daga baya Hausawa suka bijire wa Turawa.

Shi kuwa Muhammad (2003:2) sai ya bayyana ma’anar bijirewa da cewa, mataki ne na amfani da karfi domin yin adawa ga wani mutum ko kuma wani abu. Ana samin bijirewa ta amfani da makami (zazzafa) ko kuma bijirewa ta hanyar da

babu tashin hankali (sassanya). Ya kara da cewa ma'anar bijirewa ta yau da kullum kuwa tana nufin, kim amincewa ko yin adawa da wani tsari.

A cikin Ask Encyclopedia ga abin da aka ce:

Bijirewa tana nufin yunkuri na wadansu mutane domin kalubalantar wani matsatsi ko takurawa. Haka kuma tana iya zama nuna adawa ga wadansu dokoki, misali bijire wa gwamnati.

A cikin Kids.net.av

Bijirewa mataki ne na yin adawa da wani abu sabo da ba a yarda da shi ba.

A cikin "www.Leanersdictionary.com" kuwa sai aka ce, bijirewa tana nufin kin yarda da wani abu sabo.

Ke nan idan aka kalli ma'anonin bijirewa sai a ce, sun shafi bangarorin rayuwar dan Adam da suka hada da magana ko aiki ko wani tsari da mutum yake a kansa. A takaice bijirewa tana nufin canza wani abu da nufin neman sauyi ko biyan wata bukata, ko kuma nuna kin yarda ta hanyar amfani da makami ko kuma ta hanyar ruwan sanyi.

**1.14 Rabe-Raben Bijirewa**

Bijirewa ta rabu zuwa gida biyu. Akwai bijirewa zazzafa, watau (Active Resistance). Akwai kuma bijirewa sassanya da ake kira da Turanci (Passive Resistance). A nan za a yi kokarin kawo bayanin wadannan rabe-rabe domin fahimtar yadda suke.

### 1.14.1Bijirewa Zazzafa

Kunshiyar bijirewa zazzafa tana da wahalar fayyacewa ta fuskar gundarin ma'anarta saboda sassabawar kalmomin mizani da masana suke bayyana ta da shi. Duk da haka masana daban-daban sun kawo abin da suke ganin ita ce bijirewa zazzafa kamar haka;

Abbinket (2003) ya ce; Halayya kamar yin sata ko yin hijira ko fada ko kaurace wa wani abu gaba daya, zazzafar bijrewa ce.

Haka kuma wannan masani ya kara da cewa:

Zazzafar bijirewa ita ce, amfani da mataki kakkarfa domin yin adawa da wadansu da suka ki yarda da shawarar da aka zartar. Misali danne hakkokin mutane da sauransu Abbinket (2003).

A cikin yanar gizo, shafin "Changingminds.org" an bayyana zazzafar bijirewa da cewa ita ce, wadda mutane suke dagewa su jajirce su dauki mataki na kin yarda da wani abu. Irin wannan bijirewa za ta iya kasancewa a fili ta amfani da kalamai na nuna rashin amincewa da wani abu, haka kuma tana iya zama cikin sirri ta hanyar hada kn mutane su yi zagon kasa.

Kamar yadda aka sami a cikin Ask.com (Encyclopedia), an bayyana zazzafar bijirewa da cewa, yunkuri ne na mutum ko mutane da ake yin sa domin kalubalantar wata takurawa, ko adawa da wadansu dokoki da gwamnati ta kafa.

A takaice ana iya cewa, zazzafar bijirewa tana nufin yin adawa da wata manufa domin neman sauyi ko kin yarda da canji ta hanyar yin fito-na-fito.

### 1.14.2 Bijirewa Sassanya

Bijirewa sassanya tana nufin yin bore cikin lumana ko kuma nuna finjirewa ga hukuma. Abu muhimmi wajen yin wannan bijirewa shi ne zabi na masu aiwatarwa na kin yin amfani da hanyar tashin hankali ko da kuwa abin ya hada da tashin hankali. An fara amfani da wannan nau'i na bijirewa a lokacin gwagwarmayar neman 'yancin kasar Indiya tsakanin shekarar 1920 zuwa 1948. Mutanen da ba ma'aikatan hukuma ba, su suka fi amfani da wannan hanya, wannan ya sa ake kiranta "Makamin Talakawa".

Sassanyar bijirewa ta samo asali ne cikin tsarin siyasa, yanayin da wadansu suke gani gibi ne da ake sami tsakanin masu mulki da wadanda ake mulka. Daya daga cikin fitattun masana ilimin siyasa da yake da wannan ra'ayi shi ne Gene Sharp.

Idan aka dubi faffadar manufar sassanyar bijirewa tana da tarihi mai tsawo. Hanyoyin amfani da ita suna da yawa kamar yadda aka sami a cikin littafin "Aristophanes' Play Lysistrata (411BCE)" a inda mata suka ki yarda da niyyar mazajensu ta zuwa yaki, a lokacin yakin neman 'yancin kai a kasar Amerika shekara ta 1775-1783. Haka kuma a kasashen da kasar Ingila take yi wa mulkin mallaka mutane suka ki biyan haraji.

An sami misalai na sassanyar bijirewa a wurare da dama a karshen karni na ashirin da kuma farkon na ashirin da daya. Zanga-zangar dalibai da suka mamaye

“Tiananmen Squre” a Beijing a shekarar 1989 fitaccen misali ne. Haka kuma irin wannan bijirewa ita ta kawo karshen mulkin kwamunasanci a kasashen gabashin tarayyar Turai a shekarar 1989.

A cikin shekara ta 2000 irin wannan bijirewa ta kawo karshen mulkin shugaban Sabia mai mulkin kama karya “Slobodun Milosevic 1941-2006. Fararen hula a yankin a Palastine da kasar Israel ta mamaye sun yi amfani da wannan hanya. A shekarar 2005 ‘yan kasar Bolivia sun yi amfani da irin wannan hanya ta sassanyar bijirewa wajen kifar da gwamnati mai mulki ta hanyar zanga-zanga da kuma hana ma’aikata zuwa wajen aiki.

Haka kuma wannan hanya ‘yan kasar Masar masu adawa da kungiyar ‘yan uwa Musulmi suka yi amfani da ita ta fuskar zaman dirshan, kafin ta canza ta zama zazzafar bijirewa a shekarar 2013, domin kawar da zababben shugaban kasa na wancan lokacin wato, shugaba Morsi.

Kodayake bijrewa sassanya tana iya zama mai zafi amma wadda babu tashin hankali a cikinta musamman a tsarin gwagwarmaya na zamantakewa. Matakan da suka fado karkashin sassanyar bijirewa sun hada da ire-iren abubuwan da mutane suke yi da suka hada da nuna rashin amincewa (Refusal) da zaman dirshan (Sit-ins) da kin-yarda (Boycott) da rufe hanya (Blockades) da mamaye gine-gine (Occupations of buildings) da kin biyan haraji (Tax refusal) da kuma yin rubutu lokaci-lokaci da kuma amfani da kafafen yada labarai (Alternative publications and media). Kari a kan wannan na irin wadannan matakai sun hada da yajin aiki (Strike) da ficewa daga wurin taro (Walkouts) da jerin gwano (Protest marches)

da nuna bijirewa cikin wasa (Theatrical protest) da kuma yajin cin abinci (Hunger strike).

A takaice, sassanyar bijirewa tana nufin, nuna kin yarda ga yin canji domin wata manufa ta hanyar da babu tashin hankali.

A karshe bijirewa zazzafa ko sassanya aba ce da ta shafi rayuwar mutane ta yau da kullum. Hanya ce ta amfani da 'yanci wajen nuna rashin gamsuwa da duk wani tsari a siyasance ko a addinance da ya saba da tanade-tanaden gudanar da rayuwa mai inganci.

**1.15 Ra'in Bincike.**

Ra'in Makisanci wanda Karl Marx (1818-1883) mafalsafi dan kasar Germany da Friedrich Engles (1820-1895) masanin ilimin halayyar dan Adam su ne suka kafa wannan mazahaba ta ra'in makisanci wanda a kansa ne aka dora wannan bincike. Barry (1995) ya ruwaito, ita falsafa irin ta Markisanci ta samo asali ne daga wadanda suka kirkire ta wato Jamusawan nan Karl Marx (1818-1883) da abokinsa Friedrich Engels (1820-1895). Su dai wadannan abokan ba su lakaba wa falsafar tasu sunan Markisanci ba, sun kira ta da sunan Kwaminisanci ne. Wannan sunan ya sami ne daga baya. A ra'in makisanci gwagwarmayar neman iko a tsakanin masu mulki da wadanda ake mulka tana haifar da ci gaba. Irin wannan gwagwarmaya ta hada da bangaren tattalin arziki da walwala da kuma harkokin siyasa. A tunaninsu, tattalin arzikin kasa na 'yan kasa ne. A ganinsu, ba wai wani ne ko wasu 'yan tsiraru za su mallake komai ba. Ta hanyar da wannan

falsafar ta sha bamban da sauran falsafofi irin su jari-hujja ita ce, ta kokarin sauya abu daga yadda ta gan shi, domin ta sanya shi daidai da yadda ya dace da falsafar (Abdullahi 2013:102).

Idan aka waiwayo wajen adabi kuwa, ita wannan falsafar ba ta fito karara ba dangane da abin da mafalsafan suka ruwaito. Sun dai ce, lallai alaihin matsayin fasihi a cikin al'umma da irin tunanin al'ummar tana da muhimmanci a kan irin fasahar da zai kirkira. Abin lura a nan shi ne, ba dole ne fasihi ya danganta fasaharsa da markisanci ba. Abubuwan da ke damunsa a cikin al'umma kawai za a gani a cikin aikin: alal misali, rikice-rikice dangane da yadda mahukunta suke wawure arzikin kasa su mayar nasu. Da yadda talakawa suke dandana kudarsu a hannun wadannan 'yan tsirarun mutanen. A irin wannan adabin, marubuci zai yi amfani da fasaharsa ne ya nuna yadda talakawa suka jajirce wajen kwatar kawunansu daga kangin bautar da mahukunta suka tsunduma su ciki. A takaice dai, a ganin magajin Marx wato Lenin (1905) dole adabi ya san yadda zai yi ya sauya al'umma ko da ta hanyar farfaganda ce.

Masu ra'in sun kara da cewa, Sa-in-sa tsakanin masu hali ko masu mulki (the bourgeis) da kuma talakawa ko marasa hali (fuedal overlords). Gwagwarmaya ce tsakanin masu mulki ko masu hali saboda morewa da suke yi sakamakon matsayinsu, da kuma marasa hali ko mulki saboda irin matsin da suke ciki sakamakon yanayin da aka sami kai a ciki. (Wilmot eds p 204) yana cewa, wanda yake kan mulki a kullum yana kokarin ya ci gaba da zama a kan mulki, shi kuma wanda ake mulka da yake kasa yana neman mafita a game da hali na matsi da

kuntata da yake ciki a wurin musu mulki. Irin wannan gwagwarmaya a hankali takan zama juyin-juya-hali. (Wilmot eds p 292).

Lenin a shekarar 1905 ya ce, ya kamata adabi ya kasance makami ne na siyasa. Ya kuma jaddada cewa, adabi ya kasance bangare ne a siyasa, haka ya sake fada cewa, adabi ya kasance tsararriyar hanya a cikin siyasar "Social Democratic Party." Lenin ya kara da cewa, fasaha ta kasance makamin yakin siyasa ne na talakawa.

Lee T. Lemon da Marion J Reis 1965 suka ce, harshen fasaha a cikin Adabi ba kamar harshen maganar yau da kullum yake ba, harshe ne da yake dauke da ka'idoji da manufofi masu tasiri wajen kaiwa sako. Shklousky sai ya ce, harshen fasaha a cikin adabi shi ne wanda yake canza duniya ya mayar da ita tamkar sabuwa ga al'umma ta zama kamar lokacin mutane suka fara rayuwa a cikinta.

## 1.16 Kammalawa

Kamar yadda aka gani, sunan wannan aiki "Bijirewa A Wakokin Siyasa:Bincike Kan Wakokin 1903-2015" A kokarin gabatar da wannan babi an kawo bayani a kan Dalilin bincike, wato dalilin da aka hango, kuma aka kuduri aniyar yin wannan bincike. Wannan shi ya kai mu ga manufar bincike, sai kuma Muradin bincike, wato Muradin da ake sa ran wannan bincike ya samar. Bayan nan sai aka yi bayani a kan Hasashen bincike. Daga hasashe kuma, sai aka yi tsokaci kan Farfajiyar bincike da kuma hujjojin da aka dogara da su don gudanar da wannan bincike. Hanyoyin Tattara bayanai sun fada karkashin wannan babi, inda aka

fayyace, dalla-dalla, duk wata hanya da za a bi domin ganin cewa haka ta cim ma ruwa. Haka kuma an kawo wasu daga cikin irin tambayoyin da aka yi amfani da su wajen tattaro bayanai. An kawo bayani a kan lokutan da aka yi wakokin da dalilin zabo wakokin da kuma yankunan da aka yi su. A karshe an kawo bayani a kan ra'in bincike, wato ra'in da aka dora wannan aiki a kansa.

# BABI NA BIYU

# WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

## 2.1 Gabatarwa

A kokarin yin bita domin wannan nazari, an kasa abubuwan da za a nazarta kashi-kashi kamar haka, za a yi bitar ma'anar bijirewa da kuma kasar Hausa. Sannan za a dubi rubuce-rubucen da suke da dangantaka da siyasa da masu nasaba da addini da wadanda suka shafi zuwan Turawan mulkin mallaka da tarihi da kuma abin da ya shafi bore.

## 2.2 Kasar Hausa

Kasar Hausa, kasa ce mai girman gaske musamman dangane da fili, tsari da kuma irin albarkatun da ke tattare a cikinta. Kasar Hausa, tana da girma da fadin gaske, domin idan muka duba iyaka za mu ga cewa ta yi wani irin zagaye ne mai yawa. Kasacewar kasar Hausa ba karkashin jagorancin shugaba daya take kafin jihadin Shehu Usmanu Danfodiyoba, shi ya sa masana suke ta mamaren ina ne iyakacin kasar take, ta kowane bangare. A bayanin wasu masana, sukan shata kasar ne ta la'akari da wuraren da masu magana da harshen Hausa suke zaune (Gobir 2012:32).

Masana da suka hada da Ibrahim (1982) da Zarruk da wasu(1986) da Yakasai (1988) da Adamu (1997) da Sarki (2000) da Dunfawa da wasu (2007) da Abdullahi (2008) da Adamu (2010) da kuma Amfani (2011, 2012) sun kawo ra'ayinsu a game da kasar Hausa.

Ibrahim (1982:1) ya ce a wata fadar an bayyana cewa, kasar Hausa tana shimfide ne a can Arewacin Nijeriya da kuma kudancin Nijar cikin Afirka ta yamma. Daga gabas ta yi iyaka da kasashen Borno. Daga yamma ta yi iyaka da kasar Adar a cikin jamhuriyar Nijar. Daga wajen kudu kuma ta yi iyaka da kabilun Gwari da kuma kudancin Zariya da na kudancin Bauchi.

Kasar Hausa tana Afirka ta yamma ne, a farfajiyar nan da ke tsakanin hamadar sahara da mahadar kogin Kwara da Binuwai. Daga Arewa zuwa kudu ke nan. Gabas da yamma kuwa, kasar tana tsakanin tafkin Cadi da guiwar kogin Kwara. A wannan wuri; duk inda ba a bukatar a nada sarkin Hausawa, ko a ware wuri a kira shi unguwar Hausawa, to kasar Hausa ke nan.

Kasar Hausa yawancinta shimfidaddiya ce, mai yawan sarari. Akwai ta da rafuka da koramu, sai dai kuma babu manyan taffuka. Manyan koguna ma biyu kadai ne suka bi tsakiyar kasar kuma su ne kogin Rima da kogin Hadejiya (Zarruk da wasu 1986).

Haka kuma (Zarruk da wasu 1988) sun ce, kasar Hausa tana a yankin Afirka tana a yankin Afirka ta yamma ne. a kan taswira kuma ana saminta a layi na goma sha biyar (15) zuwa layi na goma sha takwas (18) na Arewa da ikwata, wato tsakanin layi na takwas (8) da na goma sha biyu (12) a gabas da layin Greenwhich.

Yakasai (1988:2) kuwa cewa ya yi, A mike kasar Hausa ta fara ne daga Arewa zuwa kudu daga Azben a cikin jamhuriyar Nijar har zuwa kusurwar Arewa maso gabas ta tsaunukan kasar Jos. Daga nan sai ta kwasa ta yi yamma har ya zuwa

inda kogin Kaduna ya yi wani babban doro. Daga nan kuma sai ta buga ta yi Arewa maso yamma har sai da ta dangana da wani katon kwari na gulbin Kebbi. Daga wannan wuri sai ta karkata ta nufi Arewa maso gabas har Azben. Wannan zagaye shi ya fitar da iyakar kasar Hausa gabas da yamma, kudu da Arewa.

A gaba sai (Adamu 1997:11) ya ce kasar Hausa ta ainihi, za a iya lalubo ta a cikin Afirka ta yamma, wato a farfajiyar nan da ke tsakanin dazuzzukan da ke kurkusa da gabar tekun Atalantika daga kudu cikin Nijeriya zuwa hamadar Sahara a Arewa cikin kasar Nijar. Adamu ya kara kawo bayanin ra'ayin wadansu masana masu ganin cewa, kasar Hausa tana nan daga abin da ya kama tsakanin tafkin Cadi daga gabas, zuwa guiwar kogin Kwara a can yamma, don haka ne ma suke kiran ta da suna Bilal Sudan wato kasar "bakaken fata."

Sai kuma (Sarki 2000:10) inda ya ce, A yammacin Afirka, yankin kudancin Sahara Arewa da kurmi inda Larabawa ke kira Bilad-ul-Sudan wato kasar bakar fata. Yanki ne da ya kunshi kasashe da dauloli da dama a cikinsu har da kasar Hausa, wacce ta kafu a yammacin Sudan din tsakanin tafkin Cadi daga gabas, da guiwar kogin Kwara daga yamma, da hamadar Sahara daga Arewa da kuma dazuzzukan gabar tekun Atalantika daga kudu. Dangane da kasashe da kabilu da kasar Hausa ta yi iyaka da su kuwa, a gabas ta yi iyaka da Kenem Borno, a shiyyar kudu kuma ta yi iyaka da Kwararrafa (kasar Tibi), da Nufe, da Gwari, da sauran tsirarun kabilu. A yamma kuma ta yi iyaka da tsohuwar daular Songai, daga shiyyar Arewa kuma kasar Hausa ta yi gaba da garuruwan Buzaye (Agadas)

a cikin kasar Nijar. A halin yanzu kasar Hausa ta na cikin Arewacin Nijeriya da kuma wani sashe a cikin jamhuriyar Nijar.

Dunfawa da wasu (2007: 99) sun tafi a kan fahimatar cewa, kasar Hausa ta asali tana a Afirka ta yamma ne, a farfajiyar nan da ke shimfide tsakanin hamadar Sahara da dazuzzukan da suka doshi gabar tekun Atalantika daga kudu. Fadin wannan kasa ya faro ne tun daga Lalle da Asadu, can Arewa maso gabas da Agadas (a cikin jamhuriyar Nijar), har zuwa Yauri da Zariya a kudu (cikin Nijeriya). Daga gabas kuwa ta fara ne daga Garun-Gabas (Birom) har zuwa kasar Filinge (a cikin Nijar) a yamma.

Kasar Hausa ba dunkulalliyar kasa daya ce ba, gungun kasashe ne daban-daban a karkashin mulkin sarakuna daban-daban wadanda ke kunshe da mutane da suka bambanta da juna ta fuskar al'adunsu da zamantakewarsu da yanayin mulkinsu. Abin da kawai ya hada wadannan kassashen har ake kiran su kasar Hausa shi ne kasancewar mafi yawan mutanen da ke zaune a wannan yankin suna amfani ne da harshe daya (wato Hausa) wurin sadarwa a tsakaninsu (Abdullahi 2008: 38).

Kasar Hausa da ake kira (Al-bilad al Hausiyya ko kuma Hausiyya al-Sudaniyya da harshen Larabci a cikin karni na sha takwas da sha tara), yanki ne mai girma a da da kuma yanzu wanda kusan rabin yankin yana cikin kasar jamhuriyar Nijar rabin kuma a cikin Nijeriya. Kusan a ce duk yankin kasar Nijar ba komai in ban da yankin kasar Hausa da yake a Arewacin kasar. Kasar Hausa ta kama tun daga Azben daga Arewa har ya zuwa yankin kudu kusa da dutsin Kufena da Turunku a kasar Zazzau. Sannan ta tashi daga tsakiyar kogin Neja daga yamma ta hada da

iyakar gabashin jamhuriyar Nijar da kuma Arewacin Nijeriya daga gabas Adamu (2010: 15).

Amfani (2011,2012: 2) ya ce, an ce gidan Hausawa na gado shi ne Arewacin Nijeriya da kudancin kasar Nijar. Kasar Hausa tana da girma kwarai da gaske. A mike, daga Arewa zuwa kudu, kasar Hausa ta fara daga Azben har i zuwa kusurwar Arewa maso gabas da tsaunukan kasar Jos. Daga nan sai ta kwasa ta yi yamma har i zuwa inda kogin Kaduna ya yi babban doro. Daga nan sai ta buga ta yi Arewa maso yamma sai da ta dangana da wani katon kwari na gulbin Kebbi. Daga wannan wuri sai ta karkata ta nufi Arewa maso gabas har Azben.

Bisa fahimta ra'ayoyin da masana suka kawo ya nuna cewa, kasar Hausa ita ce yankin Arewacin kasar Nijeriya da kuma kudancin kasar Nijar.

### 2.3 Ginuwar Mulki A Kasar Hausa

Kowace al'umma ta duniya ba ta iya rayuwa sai da jagoranci bisa shugabancin wani babba daga cikinta. Tun kafin zuwan baki (Wangarawa da Fulani da Larabawa da Turawa), Hausawa al'umma ce mai tsarin mulki irin na Gargajiya a inda jama'arta suke zabar wani wanda ya cancanta daga cikinta domin ya shugabance ta Adamu (2003: 18).

A cewar su Palmer (1928) da Greenberg (1946) da Smith (1987) irin wannan shugabanci, yana faruwa ne tsakanin mai gida da iyalansa, inda yake shugabantar matansa da 'ya'yansa, har ma da danginsa. Shugabanci irin na unguwa, ya samo asali ne a dalilin zama irin na gandu, inda jama'ar wannan yanki kan dubi wanda

ya fi kwazon noma daga cikinsu, domin ya zama shugabansu. Saboda albarkar noma da wani sashe yake da shi, mutane da dama kan so, su zauna a wannan wuri, wanda yawan jama'a kan samar da unguwa. Haka nan daga cikin mazauna unguwa, sai a duba wanda ya cancanta, musamman ta fuskar kwazo da jaruntaka, sai a ba shi mai unguwa, wanda shi ne yake da hakkin kare dukkan wadanda ke karkashin ikonsa ta kowace fuska.

Bayan irin wannan zama na ciyar da kai gaba ta fuskar noma da tsarin shugabanci, akwai kuma zama irin na dangantakar rayuwa da abin bauta, wadda ita ma dadaddiyar al'ada ce. Masana da dama sun yi nuni da cewa, mazauna wannan yanki na kasar Hausa a rayuwarsu ta farko, ba su da wani addini da ya wuce na Gargajiya, wato bautar Iskoki da Dodanni. A kowane gida akwai abin da ake kira kangida, wasu suna da macizai, wasu duwatsu, wasu saniya, wasu zakaru, har ma akwai masu uwar gona. Haka abin yake a unguwanni da kauyuka da garuruwa inda ake gudanar da irin wannan nau'in bauta (Abdullahi 1998:39)

Hausawa na cikin wanzar da irin wannan tsarin mulki da bauta irin ta Gargajiya ne, sai Musulunci daga Afirka ta Arewa ya kunno kai zuwa yammacin Afirka, ta hanyar hada-hadar ciniki da saye da sayarwa. A irin wadannan tafiye-tafiye ne Musulunci ya biyo 'yan kasuwa zuwa wuraren mazauna yammacin Afirka, ya kuma sami gindin zama duk da cewar ba musuluntar da jama'a aka zo yi kai tsaye ba (Abdullahi 1998:40).

Nazari ya nuna cewa, bayan 'yan kasuwa, akwai kungiyoyin Malamai daban-daban wadanda suka shigo kasar Hausa domin aikin watsa addinin Musulunci.

Daga cikin wadannan kungiyoyi akwai Fulani da Torankawa da Sullubawa a karkashin Shehun Malami, Waliyyi mai suna Musa Jokolo. Wadannan sun iso kasar Hausa daga Futa-Toro ta kasar Melle (Mali). Sun kawo addinin Musulunci da ilimi da littatafan addini masu tarin yawa a kan fannonin fikhu da shari'a da lugga a daidai shekarun 1452-1463. Haka kuma akwai wata kungiya ta Wangarawa a karkashin jagorancin Malam AbdurRahman Zagaiti, wadda ta taso daga Sanagal da niyyar zuwa aikin Hajji. Daga cikinta ne wasu suka wuce Katsina, wasu kuwa kimanin arba'in suka wuce Kano daga shekarar 1463-1499 (Yahaya 1988:10).

Sai wani Malami, waliyyi mai suna Abdulkarim Almagili, wanda ya taso daga Tilmisan (Tuwat) ta kasar Maroko, ya isa Katsina a zamanin sarkin Katsina Ibrahim Maje, wajen shekarar 1494. Wannan Malami ya tarar akwai Malamai da masallatai a Katsina. Tarihi ya nuna cewa, kafin Shehu Almagili ya bar Katsina, sai da ya kafa makarantar koyon addinin Musulunci da ilimin shari'a da yadda za a gudanar da ita. Daga nan ne ya zarce Kano inda ya tarar da Muhammadu Rumfa kan mulki. Sarki ya roke shi ya rubuta masa littafi wanda zai zama jagora a gare shi kan hanyoyin gudanar da mulki da shari'a kan tafarkin da Musulunci ya tsara, wanda sakamakon haka ne Almagili ya rubuta masa littafi mai suna *TAJ AL-DIN FI MA YAJIBU ALAL MULK.*

A cikin littafin, Almagili ya bayyana ka'idojin mulki, musamman irin huldodin da sarki zai yi da jama'arsa, da irin shigar da zai yi da sassauta murya, da hardewar

da zai yi wajen zama, da yadda zai gudanar da kotunan alkalai da tsaron kasa da sauransu (Yahaya 1988:10 cikin Ibrahim 2002).

Mujaddadi Shehu Usmanu Danfodiyo da kanensa, Abdullahi Danfodiyo duk sun ambaci wannan littafi na Almagili a cikin ayyukansu. Bayan rubuta wannan littafi, Almagili ya sa an gina makaranta, da masallaci a unguwar Sharifai, aka nada limamin Juma'a da ladan, aka kuma nada alkali mai gudanar da shari'a da sauransu (Yahaya 1988:10-11). Ga dukkan alamu, daga bayanan da suka gabata, Hausawa, bayan zuwan Larabawa masu cinikayya da masu yada addinin Musulunci sun sami tsarin mulki iri biyu. Tsari na farko shi ne kamar yadda muka gani, wato na Gargajiya ne, wanda ya ginu a bisa wata sabga ta sana'a misali noma inda ake samin sarkin noma. Sai jagoranci na addinin Gargajiya, wanda ya samar da shugaban da ya zama tsani tsakanin Dodanni da Iskoki da kuma jama'a, misali kamar Barbushe.

Al'amuran Hausawa na gudana kan wadannan nau'o'in tsarin mulki na Gargajiya ne, sai suka sami tsarin addinin Musulunci wanda baki suka zo da shi kamar dai yadda ya gabata a cikin littafin Almagili wanda ya rubuta wa sarkin Kano, Muhammadu Rumfa.

Bayan kusan shekara dari (100) da samiwa tare da kafuwar tsarin mulki na addinin Musulunci a kasar Hausa, Turawa sun shigo da nasu tsarin mulki da addini da kasuwanci irin na kasashensu zuwa kasar Hausa, shigowar ita ce ta kawo wakafi ga dorewar ci gaban tsarin mulki irin na addinin Musulunci a hukumance a kasar Hausa.

Tun farkon kafuwar kasar Hausa zuwa yau, Hausawa suna gudanar da al'amuran rayuwarsu kan tsari daban-daban a lokuta daban-daban, tsari na al'adun Gargajiya da na addinin Gargajiya da tsarin shari'ar Musulunci, sannan da tsari na Turawa. Tsari irin na Turawa, shi ya ba 'yan Arewacin Nijerya damar kafa kungiyoyi da jam'iyyun siyasa, domin gina kasa da kare 'yanci musamman a lokacin da ake shirye-shiryen karbar mulki daga Turawan mulkin mallaka (Ahmad 2003:21-22).

## 2.4 Tarihin Wakokin Bijirewa A Kasar Hausa

Marubuta wakoki da dama sukan rubuta wakoki a kokarinsu na bayyana manufarsu ta kin amincewarsu da sabon abu, ko kuma wanda suka canza ra'ayi a kansa, domin bayyana wa jama'a abin da yake zuciyarsu. Sukan tsara irin wadannan wakoki cikin kausasan harshe. Wannan kuwa ba bakon al'amari ba ne kuma ba Hausawa kadai ne suke amfani da wakoki wajen bayyana abin da yake cikin zukatansu musamman na kin yarda ba. Tarihi ya nuna cewa, Larabawa da Indiyawa da wasu al'umomin duniya sukan rera waka ga abin da suke so ko wanda ba su so ba (Gusau 2014:13).

Hiskett (1975:94) yana da ra'ayin cewa, waka a kowane lokaci hanya ce ta yada farfagandar siyasa a cikin Musulunci, saboda yin suka a game da yadda ake tafiyar da harkokin mulki yana daga cikin irin sakonnin da maluman Musulunci sha'irai suke isarwa ga jama'a. Wannan ya sa sha'iran Hausa na farko suka yi amfani da wannan dama wajen sukar dabi'o'i da miyagun al'adu na sarakunan Habe a wancan lokaci.

Hiskett (1975:95) yana da ra'ayin cewa, Hausawa sun fara cin karo da rubutattun wakoki sakamakon haduwarsu da Larabawa, ko kuma a ce lokacin da suka karbi Musulnci. A wancan lokaci wadanda suka iya harshen Larabci su ne Malamai a cikin al'umma. Haka kuma, duk wadanda suke iya karanta wakokin Larabci, kuma suke iya rubuta waka da ajami, dukansu Malamai ne. Wannan matsayi nasu shi ya mayar da waka ta zama tana daga cikin hanyar bayyana ra'ayi mai tsauri. A bayyane yake cikin addinin Musulunci, Hadisin Al-nawawi na 34 da bayyana cewa wajibi ne ga dukkan Musulmi idan ya ga barna ya gyara da hannunsa, idan bai yiwu ba ya gyara ta da harshensa, idan haka bai sami ba ya ki abin a cikin zuciyarsa, wannan shi ne mafi rauni. Wannan shi ya sa sha'irai ba wai na dauri ba har da na yanzu wadanda ake samin bijirewa a cikin wakokinsu, yin wakoki da suke kalubalantar duk wani abu da suka gani wanda ya saba ka'ida kama daga kan sarakuna da ahalin masu jihadi da 'yan mulkin mallaka da kuma 'yan barandansu.

A kashin gaskiya, tun kafin jihadi ana rubuta wakoki a kasar Hausa. A yanzu haka kwanan nan aka binciko wata waka da wani Malami mai suna Shitu Dan Abdurr'ufu ya rubuta tun kafin bayyanar Shehu Usmanu (Abdulkadir 1979:6). A cikin kasar Hausa ana iya cewa an fara samin wakoki na bijirewa tun a cikin karni na sha tara, lokacin da aka sami wakar *Ya Ghiyathul Mustagithina* daga Hayatu bin Sa'id da kuma wakar *Cin Birnin Alkalawa* da ta *Tsarin Mulkin Musulunci* ta Abdullahi Fodiyo. Idan aka auna wakar *Tsarin Mulkin Musulunci* a ma'aunin bijirewa za a gani a cikin wani bangare na wakar, Abdullahi bin Fodiyo ya yi kokarin bijire wa wasu munanan al'adu na sarakuna da suke yi a wancan lokaci. Ana iya fahimtar haka, ta la'akari da kakkausar suka ga halayyar sarakunan

wanda tamkar bijirewa ce gare su. Sannan, ya ja ra'ayin jama'a a kan cewa wadannan dabi'u ba su da kyau kuma ba a son a yi su. A karshe ya kawo bayani a kan tsarin mulki mai kyau wanda sarakunan suna iya amfani da shi. Haka kuma, akwai wakar *Kogi* ta Limamin Daura, Hassan (1899). Wannan waka an rubuta ta ne a daidai lokacin da Turawa suka shigo Arewacin Nijeriya. Wakar tana kira ga sarakunan da su daina zalunci, ya kuma nusar da talakawa illar zalunci. A dalilin rubuta wakar, sarakunan Fulani na Daura suka kore shi, inda ya tsere zuwa Sakkwato (Malumfashi 1988).

Malumfashi (1998) yana da ra'ayin cewa, a cikin karni na ashirin, an sami yawaitar wakoki na bijirewa da kuma wadanda suke da bijirewa a cikinsu. Ana iya cewa wakar *Zuwan An Nasara Kasar Hausa* ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu Shi ne Sarkin Musulmi na karshe, kafin mulkin Turawa. Ya rasu a Burmi a ran 27 ga watan Yuli, 1903, bayan sun kafsa da Turawan mulkin mallaka. Ya ki amincewa da Turawan da kuma tsare-tsaren da suka zo masa da su. A saboda haka ne ma, ya rubuta wannan wakar, domin ya fadakar da mutanensa illar zama karkashin mulkin Nasara. Hakan ya jawo bore a kasar Hausa, wanda ya sanya Turawan suka yi fito-na-fito da shi. A cikin wakar ya nuna bijirewarsa a fili cikin kalamai masu kaushi da zafi ga Turawa. Haka kuma, ya yi kokari wajen jawo hankalin jama'a a kan su kyamaci Annasara, har ma ya bayar da zabi ga duk Musulmi a kan cewar ko dai a tashi a bar wa Annasara kasar Hausa, a yi hijira a koma kasar Makka, ko kuma a yi yaki da Annasara ko kuma a yi sulhu da shi. Ganin haka ne, ya sa ya bar garin Sakkwato, inda ya yi niyyar yin

hijira zuwa kasa mai tsarki. Ya rasu tare da mutane da dama, kuma an kama jama'a da dama, cikinsu kuwa har da Sarkin Kano, Alu.

Furniss (1996:206) ya ce, an sami wakar wani shahararren Malami da ake kira Imam Umaru daga Salaga a cikin kasar Ghana da ake jin an yi ta a wajejan shekara ta 1903. An tsara wakar ne a kan gwarzaye da suka bijire wa bayyanar Turawa ‘yan mulkin mallaka a cikin Afirka ta Yamma. Ana iya cewa wakar tana aji guda da wakar “Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Attahiru Ahmadu” (Pilaszweicz:1975:56).

A tsakanin shekarun 1903 da 1950, lokaci ne da aka sami markar wakoki daga marubuta wakoki na Hausa masu dauke da manufa ta kin aminta da yarda da sarakunan Gargajiya da Annasara da duk wani abu da ya kawo. Hatta Musulmi wadanda suka yarda su yi aiki da Annasara sai dai aka yi Allah wadai da su Sa’id, (1995:12). Haka kuma, Musulmi wadanda yawancinsu Hausawa ne, sun kyamaci Annasara saboda tsoron da suke yi na addinin Annasara da kuma gudun kada a raba su da nasu. Sha’irai da suka hada da Malam Abubakar Maikaturu (1897-1947) da ya rubuta wakar *Gudun Duniya* da kuma Malam Ibrahim Khalilu Marinar Tsamiya, Sakkwato (1920-1975) da ya rubuta wakar *Ku Dubi Musulmi*. suna cikin wadanda suka bayar da gudummuwa. Haka kuma a daidai wannan lokaci ne aka sami wakar Annasara ta Malam Maharazu Barmo Kwasare (1915-1978), Maharazu dalibin daya daga bijirarrun Malaman Satiru ne da suka yi tawaye a shekarar 1906. Ya yi waka yana sukan ‘yan mulkin mallaka da kuma yadda suka yi wa mutanen kasar Hausa tarko suka kwashe al’adunsu da dabi’unsu

suka canza da nasu. Alhaji Shehu Shagari ya yi waka mai suna *Wakar Baturen Ingilishi* a shekarar (1947). Wakar ta fito da irin yadda aka fahimci kissar Bature da gane manufarsa a siyasar kasa. Ga dukkan alamu tana bayyana tsananin adawa ga Turawa (Usman 2012:593).

A shekarar 1906 aka sami waka mai suna *Shahada Zahira:Wakar Begen Yakin Shahadar Hadejia* (Hiskett, 1975:144-147 da 294-295). Waka ce ta juyayin wadanda suka yi shahada sakamakon yaki tsakanin Sarkin Hadejia Muhammadu Mai Shahada da Turawan mulkin mallaka a shekarar 1906. Wani mutum da ake tsammnai shi ne limamin Hadejia na wancan lokacin mai suna Liman Muhammadu shi ne ya tsara ta (Birniwa, 2006:2).

Wakokin bijirewa da aka sami a shekarar 1960 wadanda su ne suka kunshi wakokin siyasar jumhuriyya ta farko, suna dauke da manufofi masu yawa da suka hada da burbushin mulkin mallaka da kuma manufofin gwamnati da sarakuna, musamman wadanda ake ganin suna tafiya sabanin yadda ya kamata. Jam'iyyar NEPU tana zargin jam'iyyar NPC da hada baki da 'yan mulkin mallaka, wannan ta sa 'yan NEPU suka rika yin wakoki na sukar irin wannan dabi'a, ta 'yan jam'iyyar NPC da nufin mayar da raddi na kariyar kai. Fitattu daga cikin sha'iran NEPU sun hada da Yusufu Kantu *Wakar 'Yan Sawaba* Gambo Hawaja *Wakar Ba Maki NEPU Sai Wawa* Akilu Aliyu *Wakar Baki Uku Sharrin NPC* da kuma Sa'adu Zungur *Wakar Jihadin Neman Sawaba* da sauransu. Daga bangaren NPC akwai sha'irai kamar Alkali Bello Gidadawa *Wakar Siyasa Zamanin Salama* da

Shekara Sa'ad *Wakar Ya Allah Ya Sa Musulunci Ya Danne Kafirci* da sauransu da yawa.

Idan aka gangaro zuwa jumhuriyya ta biyu da aka dauka ta wanzu daga shekarar (1979-1983). Jam'iyyun siyasa da suka wanzu a cikin wannan jumhuriyya, kowace daga cikinsu ta sami wakoki daidai da manufofinta. Kamar yadda Birniwa (1987:252) ya ce, A ranar 21-09-1978 aka daga takunkumin yin siyasa a Nijeriya. Daga nan sai jam'iyyun siyasa suka fara fitowa. Daga cikin jama'iyyun da suka fara fitowa akwai UPN ta Obafemi Awolowo da NPP ta Dr. Nnamdi Azikwe wadda daga baya Waziri Ibrahim ya balle daga cikinta ya kafa jam'iyyar GNPP ta sai kuma jama'iyyar NPN da kuma PRP ta Aminu Kano da kuma wadansu kananan Jam'iyyun. Gabadaya an sami jama'iyyun siyasa sama da hamsin (Birniwa 1987:252). Daga cikin wadannan, jam'iyyun siyasa guda biyar ne kawai suka sami rijista domin su ne suka cika sharuddan da hukumar zabe ta kasa ta bayar. Jam'iyyun su ne UPN da NPP da GNPP da NPN da kuma PRP.

Ta la'akari da wadannan jama'iyyu mutum yana iya fahimtar inda aka kwana, domin jama'iyyun suna da nasaba da zamanin jumhuriyya ta farko. Jam'iyyar UPN tana da alaka da AG haka Jam'iyyar NPP tana da nasaba da NCNC. Ita kuma NPN da NPC yayin da PRP take da NEPU. Jam'iyyar GNPP ce kawai ba za a iya alakanta da wata jam'iyya ba a jumhuriyya ta farko ba (Birniwa 1987:253). Wadannan jam'iyyu sun yi ta hamayya da adawa da juna, wannan tana sukar waccan, wannan tana rikici da waccan. Waka tana daga cikin hanyoyin da aka yi amfani da su wajen cim ma manufa. Daga cikin wakokin da suke yi ana samin

masu dauke da bijirewa a cikinsu. Daga cikin sha'iran jam'iyyar NPN da suka yi wakoki masu nuna rashin yarda da jam'iyyar NEPU akwai; Musa Madugu *Rabbana Nuna Mana Gaskiya Mu bi NPN Baki Daya* da Yakubu Labara Wakar *'Yan Santsi Sun Ji Kunya* daga cikin na jam'iyyar PRP akwai; Magaji Ciroma Sudawa Wakar *Maso Ceto Ya Amsa Kira, PRP Na Kiran Kowa* da kuma Auwalu Isa Bungudu Wakar *Mun Gode Allah Yai Baiwa Ya Kawo Nasarar Talakawa*. da sauransu da yawa

An fara yunkurin kafa jumhuriyya ta uku tun a cikin shekara ta 1987 a zamanin da gwamnatin Babangida ta kuduri niyyar dawo da mulkin farar hula a shekarar 1992 amma bisa mataki-mataki. Kowane zango na siyasa yana zuwa da mawakansa, ko da yake dai ana samin wasu mawakan su bayyana a fiye da zango daya na siyasa. Babban abin da aka fi sani dai shi ne kowace jumhuriyya tana zuwa da wakokin siyasarta daban da sauran jumhuriyoyi da aka yi a baya. A jumhuriyya ta uku kamar saura takwarorinta na baya, an sami rukunin mawaka da kuma wakokin siyasa na Hausa da dama.

Kamar yadda tarihi ya nuna, marubuta wakoki na farko akasari Malamai ne wadanda suke da ilimin addinin Musulunci (Hiskett 1975:92). Haka ya sa ake samin tasirin addinin a cikin wakokinsu. Haka kuma tarihi ya nuna cewa ainihin halayen mawakan siyasa na farko 'yan kishin kasa ne, masu kishin jam'iyyu. Don haka wakokin da suka rika yi wa jam'iyyu suna yi ba domin su sami wani Abin hasafi ba. A wannan lokaci an sami jam'iyyun siyasa kuma an yi musu wakoki na yada manufofi a tsakanin siyasun, duk da cewa a daidai wannan lokaci kishin kasa

ya yi rauni a cikin zukatan mawakan siyasa. Kusan a wannan lokaci ne aka fara samin mawaka suna yi wa siyasa sama da guda waka. Daga cikin mawakan wasu siyasun da aka sami a wannan lokaci sun hada da; Ibrahim Aminu Dandago "Wakar NCPN" da Haruna Aliyu Ningi "Wakar UNCP" da kuma Garba Gashua "Wakar NRC" da kuma Auwalu Isa "Wakar SDP."

Jumhuriyya ta hudu ta fara ne daga shekarar 1999 zuwa wannan lokaci da ake ciki a yanzu. Jumhuriyya ta hudu ta rabu ya zuwa zanguna hudu an kuma shiga zango na biyar a halin yanzu. Zango na farko ya kama daga watan Mayu 1999 zuwa farkonn shekara ta 2003, zango na biyu kuwa ya fara daga watan Mayu 2003 zuwa farkon shekara ta 2007, a yayin da zango na uku na jumhuriyya ta hudu ya fara daga watan Mayu 2007 zuwa shekara ta 2011. Sai kuma zango na hudu da ya fara daga watan Mayu 2011 ya zuwa wannan lokaci (Dan'Illela 2010:32).

A cikin jumhuriyya ta hudu an fahimta cewa, an sami wakoki kashi biyu. Kashi na farko su ne, wakokin siyasa wadanda ba a danganta su da jam'iyyun siyasa ba misali; wakar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala da wakar *Mafarkin Mulki ta I* da ta *II* ta Jibirin Jalatu da wakar *Rigar 'Yanci* ta Abdul'aziz Abdullahi Ningi da kuma wakar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi da sauransu da dama. Sai kuma kashi na biyu da ya kunshi wakokin siyasa da aka danganta su da jam'iyyun siyasa. A nan saboda yawaitar wakoki ba zai yiwu a ce za a kawo sunayen mawaka da ire-iren wakokin da suka yi ba, domin takaitawa za a ambaci sunayen wasu daga cikin jam'iyyun da aka yi wa wakoki. Daga cikin jam'iyyun siyasar da

suka wanzu a cikin wannan jumhuriya sun hada da APP, da PDP da AC, da CAN, da CPC, da APC, da sauransu.

A cikin wadannan wakoki, mawakan sun yi kokarin kallon salon mulkin da shugabanni, wadanda aka zaba da masu son a zabe su, ta yadda suke zame wa al'umma kadangaren bakin tulu. Wannan ya sa suka tsara wakoki masu manufa ta bijirewa suna bayyana matsayinsu da na sauran mutane a game da wadannan matsaloli. A takaice ana iya cewa kusan duk wakokin siyasa da sha'irai suke tsarawa ana samin ratsin bijirewa a cikinsu.

## 2.5 Ma'anar Siyasa

Babban kundin nan na kamusun Larabci mai suna *Lisanul Arab* ya nuna kalmar siyasa a matsayin tafiyar da abu ta hanyar da zai yi daidai da abin. Ya kara da cewa har ma idan aka ga mutum ya tsaya a kan dabbobi, kuma sun yarda da shi sai a ce wane ya siyasance dabbobin, ko kuma a ce shugaba ya siyasance talakawansa in an ji suna zaune lafiya.

A kamusun *Almunjid-Abjadi* an nuna siyasa na da ma'ana guda biyu. Ta farko dai, siyasa na nufin ingantar da al'umma da shiryar da su zuwa ga hanyar tsira. Ko a kusa ko a nesa. Ma'ana ta biyu ita ce, siyasa na nufin gudanar da fannin mulki da ayyukan kasa a cikin kasar ko a wajenta, ta haka ake samin siyasar harkokin cikin gida da siyasar harkokin kasashen waje.

Kamusoshin Hausa da masana Harshen Hausa da dama sun ba da ma'anar siyasa. Wadannan masana ko litattatafai sun hada da Bargery (1934) da Abraham (1962)

da Lawal (1983) da Gusau (1984) da Kamusun Hausa (2006). Beargery (1934) yana cewa siyasa tana nufin ko dai rangwame a farashin kowane abu ko kuwa tausasawa a cikin al'amura. Wannan ra'ayi ya yi daidai da na Abraham (1962).

A cikin Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero ta Kano kuwa an kawo ma'anonin siyasa har guda hudu da suka hada da:

-Tafiyar da al'amuran jama'a ta hanyar neman ra'ayinsu da shawarwari da su.

- Ko kuma rangwame musanman a ciniki.

-Da kuma ma'anar siyasa da ke cewa, dabara ce ko wayo.

-Da kuma ma'anar siyasa ta iya hulda da jama'a.

Wadannan ra'ayoyi sun sha bamban da na Lawal (1983). Domin shi cewa ya yi siyasa, tana nufin halayyar cim ma wani buri dangane da mutane ko kuma gwamnati.

Shi kuwa Gusau (1984) ya yi tsokaci a kan ma'anonin siyasa har guda biyu inda yake cewa: Ma'anar ta farko ita ce; siyasa tana nufin gudanar da mulki ko tafiyar da mulkin jama'a ta ba wa kowa hakkinsa. Ma'ana ta biyu kuwa ita ce; a wajen Bahaushe idan ya ce ya yi min siyasa yana nufin:

-Yaudara ko dabara

-Sauki ko rangwame

-Lumana ko lallami

Siyasa wata hanya ce ta gudanar da zababbiyar gwamnati ta hanyar DimokuraDiyya a karkashin tsarin mulkin kasa, inda za a zabi shugabanni masu tafiyar da ita a karkashin kafaffun jama'iyyur. Ta wata fuskar kuma, siyasa tana iya ba da ma'anar kwArewa wajen iya tafiyar da jama'a da jure wa duk wata matsala tasu (Sa'id 2002:172).

A takaice, siyasa tana nufin hanya ta tafiyar da mulkin jama'a a zamanance ko a Gargajiyance. Kuma dabara ce ta iya jan hankalin mutane ta hanyar karkata inda suka sa gaba, a kowane fage. Misali idan dan siyasa ya lura da abin da mutane suke so, shi ma sai ya nuna yana tare da su ko da kuwa ba da gaske yake ba. Ke nan ta haka a iya cewa duk wanda ya iya shan kan mutane ya iya siyasa ko da kuwa hanyar yaudara ce (Imam 2002). 'Yan siyasa suna yin amfani da mawaka a wannan fanni don su bayyana siyasar da suka fuskanta. Kuma tun zamanin Shehu Usmanu Danfodiyo ake amfani da wakar siyasa a bayyana manufar siyasa, da ra'ayin mabiyanta da kuma ire-iren manufofin da za ta fuskanci al'umma da su (Imam 2002).

Dar-El-Mashreq (1960:107) ya kawo ma'anar siyasa kamar haka; Wannan kalma ta siyasa asalinta ta sami ne daga kalmar "saasa" saboda ka'idar ta sarifi na nahawun Larabci sai ta komo *siyaasa*. Wannan kalma tana da ma'anoni kamar haka: Juyawa a kan wani lamari ko kuma yarda da wani abu ko jibantar al'amarin al'umma tare da sanin su ne ko ba tare da sanin su ba. Idan mutum ya dauki nauyin mutane a kan rayuwarsu sai a ce "saasa fulaanun" ma'ana wane ya dauki nauyin mutanensa.

Wannan littafi ya nuna *siyaasa* maslaha ce ga halaye da shiryarwa zuwa ga al'umma don su bi hanya madaidaiciya. Ko kuma fanni ne na hikima da iya gudanar da al'umma a kan wani aiki ko harkokinsu na yau da kullum a cikin kasa ne ko a wajen kasa ne.

A karkashin bitar siyasa an kalato abubuwan da suke da dangantaka da tafiyar da mulkin kasa kamar haka;

## 2.6 Ginuwar Siyasar Zamani A Kasar Hausa

Captain C. D. Morney a lokacin da ya iso Arewacin Nijeriya, kamar yadda Dudley (1968:73-115) ya bayyana cewa, ya zo ne domin ya binciki shirin da 'yan Arewacin Nijeriya suka yi a siyasance na karbar mulkin kai, kamar yadda 'yan kudu suka bukata daga Turawan mulkin mallaka. Amma ga alama a cewarsa, 'yan Arewa ba su yi wani shiri ba. Matsalar kuwa ita ce, rashin jituwar ra'ayoyin kungiyoyin da suka rayu a wancan lokaci.

Cikin shekarar 1934 ne, kungiyoyin siyasa suka fara zama da gindinsu a kudancin Nijeriya, amma a Arewaci, ko labarinsu babu. Wasu daga cikin 'yan Arewa masu kishi da son ci gaban Arewa musamman wadanda suka koyi yadda ake mulki irin na siyasa a kasancewar zamansu da 'yan kudanci, kamar Malam Sa'adu Zungur da Malam Aminu Kano da wasu da dama sun yunkura domin kafa wasu kungiyoyi ko jam'iyyun siyasa wadanda daya daga cikinsu reshe ne na siyasar kudu a Arewa tare da goyon bayan su Azikwe, a shekarar 1943 Coleman

(1958:353). Kafin ma a kafa reshen jam'iyyar NCNC a kudu, a Arewa, akwai wasu kungiyoyi wadanda 'yan Arewa suka kafa.

Daga cikin misalan wadannan kungiyoyi, akwai kungiyar Inganta Rayuwar Mutanen Bauchi (BGIU 1934) da kungiyar tattaunawa ta mutanen Bauchi (BDC 1944) da kungiyar Zumunta ta Sakkwato (SYC 1948), akwai kungiyar Matasa ta Kano (KYA 1948) da kungiyar Abokai ta Kano (FAK 1947) sai kungiyar Malamai ta Arewa (NTA 1947) da kungiyar Matasan Zariya (ZYA 1948). Akwai kungiyoyi da dama musamman na kabilun larduna daban-daban da suka rayu kafin da bayan samin 'yancin kai. Amma, kusan duk wadanda suka rayu kafin shekarun 1950, su ne suka narke a matsayin babbar jam'iyyar nan ta Mutanen Arewa, wato NPC. Daga baya, wasu suka balle daga NPC suka kafa NEPU (Ahmad 2003).

Su kuma manyan jam'iyyun nan NEPU da NPC, sun kafu ne bisa hadewar da kungiyoyin da larduna suka kafa a wuri daya, domin a samar da jam'iyya daya, mai kare 'yanci da martabar Arewa.

### 2.6.1 Kafuwar Jam'iyyar NPC

A ranar daya ga watan Oktoba, 1951 aka kaddamar da jam'iyyar siyasa ta NPC bisa ra'ayin sarakuna da shugabannin jam'iyyar a bisa manufofi da dama. NPC jam'iyya ce wadda ta samo asali daga kungiyoyin larduna da bangarori daban-daban na Arewa (Birniwa 1987:28-29). Ita dai jam'iyyar mutanen Arewa (NPC), ta kunshi hadakar kungiyoyi da suka hada da jam'iyyar mutanen Arewa, da

Kungiyar Inganta Rayuwar Mutanen Bauchi (BGIU) da Kungiyar Zumunta ta Sakkwato (SYA) da kuma Kungiyar ‘Yan KASA ta Kano (KCA) (Malumfashi 1998).

Babbar manufar jam’iyyar ita ce yaki da jahilci da lalaci da zalunci da yin gyaran fuska ga hukumar En’e, domin ta dace da zamani. Wannan ne ya sa daga farko, Arewa ta kasance mai jam’iyya daya, saboda ganin cewa NPC jam’iyyar neman sauyi da neman ci gaba da yakar ‘yan mulkin mallaka ce, wanda wannan shi ya sa daga farko aka hana jami’an gwamnati na wannan lokaci, shiga jam’iyyar, (Coleman 1958:364). Amma lokacin da ‘yan jam’iyyar suka fahimci ba su samin goyon bayan sarakuna da makarrabansu da samari da ma’ikata, sai suka dawo daga rakiyarsu ra’ayinsu da manufarsu ta farko, domin su sami jama’ar da za su cika jam’iyyar a kokarinsu na karbar mulkin da neman rinjaye a wajen zabe. Wannan amai da lashewar manufofi da jam’iyyar NPC ta yi, ya jawo mata farin jini da kwarjini daga wurin sarakuna da ma’ikatan En’e har ma da manya-manyan mutanen Arewa, suka rika kwarara a cikinta, wanda hakan ya jawo mata gagarumin rinjaye a matakan zabe daban-daban da aka gudanar a Arewa, har ma a matakin gwamnatin tarayya, in ba a watan Satumba na shekarar 1951 ba, inda jam’iyyar NEPU ta lashe kujeru 12 daga cikin 26, saraun jam’iyyu kuma suka raba sauran kaso a zaben farko na majalisar wakilai ta tarayya da aka gudanar (Dudley 1968:80).

Wani dalili wanda jam’iyyar ta yi amfani da shi, wanda shi ne ya kai ta ga samin galaba, musamman ta fuskar magoya baya, shi ne samin shugabanni kamar su

Alhaji Sa Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato wanda ya sami girmamawa daga talakawa har ma da masu kudi a dalilin dangantakar da yake da ita da Mujaddadi Shehu Usmanu Dan Fodiyo, wanda martabarsa ce ta samar da sarakunan da ke mulkin kasar Hausa.

Bayanan da aka yi a sama dangane da asali da kafuwa, da samin nasara da manufofin jam'iyyar NPC da aka bayyana, an gane cewa NPC ita ce jam'iyyar da ta kafa gwamnati a Arewa, har ma a Nijeriya baki daya, a dalilin rinjayen da jam'iyyar ta sami a kididdigar zabe a mataki daban-daban, da magoya baya da kuma manyan mutane masu fada a ji a gwamnatin tarayya da suke cikinta.

### 2.6.2 Kafuwar Jam'iyyar NEPU

Coleman (1958) da Dudley (1968) da Yusuf (1975) da Danbazau (1981) da Birniwa (1987) da Yakubu (1999) da Kuna (2000) da Bako, A. eds (2014), duk sun ce wani abu game da kafuwar wannan jam'iyya da kuma abubuwa daban-daban da suka faru, ko dai a kan shugabanninta, ko magoya bayanta ko ita kanta jam'iyyar, tsakaninta da hukuma a wancan lokaci.

A takaice, jam'iyyar NEPU ta sami a bisa shawarar da Bello Ijumu ya kawo ta kafa wata jam'iyya mai manufar kin yarda da cutar da sarakuna da Turawan mulkin mallaka ke yi wa talakawa. Samar da wata kungiyar siyasa mai ra'ayin neman canji daga mulkin danniya na Turawa da 'yan korensu, sarakuna; shi ne mafi alheri, domin jam'iyyar mutanen Arewa, ta kasa fitowa fili ta zama ta siyasa, sai dai ta kabila kawai. An sami nasarar kafa wannan kungiya a ranar takwas ga

watan takwas da minti takwas da mutane takwas a shekarar 1950 (Danbazau 1981:84).

A wani ra'ayin kuma, jam'iyyar NEPU, ta sami asali ne daga kungiyoyi biyu masu kama da juna. Kungiya ta farko ita ce ta 'yan neman kawo canji da suka baro jam'iyyar NPC, bayan an kaddamar da jam'iyyar a 1950, sai kuma uwar kungiyar ta asali wato NEPA wadda aka kafa tun a shekarar 1946 da niyyar hada kan jama'ar Arewa da kuma bayyana wa jama'a cewa mutanen Arewa sun yi shiru game da harkokin siyasa, ba wai don sun gamsu da abin da ke faruwa ba. Dangane da haka ne za a iya cewa NEPA tun fil azal ba ta da wani haufi na inda ta sa gaba, ba ta dai kaunar tsarin mulkin mallaka da kuma sarakunan da suka daure musu gindi.

A ci gaba da bayanin yadda jam'iyyar NEPU ta sami kafuwa, Coleman (1958:364-6) cewa ya yi, gungun mutane, wadanda ba su gamsu da manufofin jam'iyyar NPC ba, su ne suka kafa jam'iyyar NEPU. A cewar shugabannin jam'iyyar NEPU, dole ne talakawa su tashi tsaye domin su sami damar kafa ingantacciyar gwamnatin siyasa domin ci gaban Arewa. Ken nan ana iya cewa jam'iyyar NEPU ta sha bamban da jam'iyyar NPC ta kowace fuska. Babban burin NEPU shi ne ci gaba daga inda NEPA ta tsaya, ciyar da tattalin arzikin kasa gaba da kuma fitar da talaka daga kangin bauta, musamman na Turawan mulkin mallaka da sarakuna. NEPU jam'iyya ce ta talakawa, shugabanninta da magoya bayanta ba su wuce Malaman makaranta ba, sai manoma da 'yan garuwa da masunta da majema da madunka da masu faskare da sauran masu sana'ar hannu

(Birniwa 1987). A kokarinta na neman kawo sauyi a siyasar Arewa, jam'iyyar NEPU ba ruwanta da neman fada a wurin Turawan mulkin mallaka, ko sarakuna kamar yadda jam'iyyar NPC take yi. Wannan yana daya daga cikin dalilan da suka sa NEPU ta zama jam'iyyar adawa, ta shiga Allah-wadai da danniya da tsarin mulkin mallaka da mulukiya. Wannan shi ya jawo rashin jituwa tsakanin NEPU da hukuma. Saboda haka ne gwamnatin mulkin mallaka ta shiga shirya da tsara hanyoyin da zai sa NPC ta gaje ta ba NEPU ba.

### 2.7 Dimokiradiyya

Tsarin dimokiradiyya ya ginu ne a kan wasu ginshikai kamar adalci, da daidaito tsakanin jama'a, da 'yanci da walwalar al'umma, da bin diddigin yadda ake kashe kudin al'umma, da kuma bayyana komai baro-baro cikin sha'anin mulki (Hassan:2013). Babban makamin dimokiradiyya shi ne jama'a masu rinjaye na hakika ko akasin haka. Da wadannan jama'a za a labe karkashin kungiya daya, da sunan ita ce kungiyar jama'a masu rinjaye (Bunza 2013).

A game da dimokiradiyya an lalubo abubuwan da masana da manazarta suka kawo kamar haka:

Abraham Lincoln (1809-1865), ya bayyana ma'anar dimokiradiyya da cewa "Gwamnatin jama'a, da jama'a suka zaba, kuma take aiki domin jama'ar.

Skinner (1965) ya bayyana dimokiradiyya da cewa, hanyar mulkin kasa ce wadda kowa ke da hannu a cikinta.

Oyediran da wasu (2001) sun bayyana dimokiradiyya da cewa, nau'in mulki ne wadda 'yan kasa za su zabi wakilansu da za su musu jagora ta hanyar bayyana yardarsu.

Joyce (2003) ya ce, dimokiradiyya ita ce yadda al'umma gaba daya suke fita domin zabar wa kansu wanda suke so ya wakilce su, kuma suke da damar tsige shi daga wannan wakilcin idan sun ga ba ya yin abin da ya dace ko kuma idan ba su gamsu da abubuwan da yake yi ba.

Kamusun Hausa (2006) an bayyana dimokiradiyya da cewa, tafarkin mulkin mutanen kasa da ake zabar shugabanni ta hanyar jefa kuri'a.

Nasir (2011: 4) ya fassara dimokiradiyya da cewa: dimokiradiyya kalma ce da aka samo ta daga harshen Girka, wacce take nufin gwamnati ta kowa da kowa, wacce aka gina ta ta hanyar zabe, na hanyar 'yar tinki ko kuma na jefa kuri'a a cikin akwati.

Ta la'akari da gudummuwar da masana suka kawo a sama a kan dimokiradiyya ana iya cewa, dimokiradiyya ita ce hanyar zaben shugaba bisa 'yanci da walwala cikin kayyadadden tsarin da doka ta aminta da shi.

Sakamakon taron kara wa juna sani na kasa irinsa na farko da Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero ta Kano ta shirya a kan "Harshe Adabi da Al'adu" an ci karo da gudummuwar masana da manazarta a kan Kalmar dimokiradiyya. wadannan masana da manazarta sun hada da: Bunza (2013), da

Abdullahi (2013), da Adamu (2013), da Hassan (2013), da kuma Abubakar da wasu (2013).

A yayin da Bunza (2013) yake cewa, Dimokuradiya ita ce tsarin gudanar da shugabancin mutane ta hanyar ba mutane cikakkiyar damar zaben wanda zai jagorance su.

Shi kuwa Abdullahi (2013) sai ya ce, Dimokuradiya wani tsari ne na shugabanci ko jagorancin jama'a ta hanyar ba su 'yancin zaben mutumin da ake dammahar an yarda ya yi jagoranci bisa wasu dalilai na musamman. Wadannan dalilai sun hada da kasancewa mutum ya zama mai kirki, mai rikon amana, mai kyakkyawar nasaba. Haka kuma akan bukaci ya kasance mai kyakkyawar hulda da mutane, kuma maras tabo na laifi ko abin kunya ko tarihin tsoro a rayuwarsa (Abdullahi 2013:754).

Adamu (2013:631) ya nuna cewa, kalmar dimokiradiyya ararriyar kalma ce wadda a ka aro ta daga harshen Girkanci: a harshen ana kiranta "Dimokratus" a harshen Ingilishi tana nufin mulkin al'umma ta hanyar amfani da fararen hula ba sojoji ba, ta hanyar gudanar da zabe.

Abubakar et al (2013:428) suna da ra'ayin cewa, kalmar dimokiradiyya an samo ta ne daga kalmomi biyu na harshen Greek wato Girkawa "Demos" wadda take nufin mutane, da kuma "Kratis" wadda take nufin mulki na mutane. Dimokiradiyya tsarin mulki ne da ya ginu a kan yadda jama'a suke zabar wakilansu domin su shugabance su. Shi tsarin mulkin dimokiradiyya ya ginu ne a

kan adalci, da daidaito tsakanin jama’a da ‘yanci da walwala da bin diddigin yadda ake kashe kudaden al’umma ta hanyar samar musu da tsaro, da inganta lafiyarsu da kuma iliminsu

Shi kuwa Hassan (2013:389) ya ce, a gwari-gwari dimokiradiyya tana nufin bayar da dama ga ‘yan kasa su zabi shugabanninsu. Wannan a takaice yana nuni da cewa, tsarin ya yi hannun riga da tsarin sarautar Gargajiya, wadda talakawa ba su da baki a cikin zaben wanda zai shugabance su.

A karshe, abin da aka fahimta da dimokiradiyya ita ce, tsarin tafiyar da shugabancin al’umma ta hanyar zaben wakilai da nufin aiwatar da manufofi na gina kasa da al’umma baki daya.

### 2.7.1 Kafuwar Jam’iyyun Siyasa Lokacin Dimokiradiyya

Jumhuriya ta hudu ta fara ne daga shekarar 1999 zuwa wannan lokaci da ake ciki a yanzu. Jumhuriya ta hudu ta rabu ya zuwa zanguna hudu ana kuma shirin shiga zango na biyar nan ba da dadewa ba. Zango na farko ya kama daga watan Mayu 1999 zuwa farkonn shekara ta 2003, zango na biyu kuwa ya fara daga watan Mayu 2003 zuwa farkon shekara ta 2007, a yayin da zango na uku na Jumhuriya ta hudu ya fara daga watan Mayu 2007 zuwa shekara ta 2011, sai kuma zango na hudu da ya fara daga watan Mayu 2011 ya zuwa wannan lokaci, a yayin da ake shirin yin zabe domin shiga zango na biyar a cikin Jumhuriya ta hudu nan ba da dadewa ba (Dan’Illela 2010:32).

A zango na farko an kafa jam'iyyun siyasa uku da suka hada da; Alliance for Democracy (A.D.) da All People's Party (A.P.P.) da kuma jam'iyyar People's Democratic Party (P.D.P.). Wadannan jam'iyyu su aka maimaita a zango na biyu, sai dai an yi wa jam'iyyar APP kwaskwarima inda ta koma All Nigeria People's Party (ANPP). A zango na uku na Jumhuriya ta hudu an sami karuwar jam'iyyun siyasa wannan ya kawo yawaitarsu. Fitattu a nan yankin Arewa sun hada da; All Nigeria People's Party (A.N.P.P.) da kuma jam'iyyar People's Democratic Party (P.D.P.), saura sun hada da Democratic people's Party (D.P.P.) da kuma jam'iyyar Action Congress (A.C.). Haka abin ya kasance a zango na hudu wadancan jam'iyyu biyar sun ci gaba da kasancewa kuma aka sami karin jam'iyyu da yawa duk da cewa ba su yi wani tasiri ba. Duk da haka a nan Arewa an sami jam'iyyar Consensus People Congress (C.P.C), sannan aka yi wa Action Congress (A.C.) kwaskwarima ta koma Action Congress of Nigeria (A.C.N.). Ya zuwa wannan lokaci da ake ciki na karshen Jumhuriya ta hudu zango na hudu da kuma karatowar lokacin yin zabe a Jumhuriya ta hudu zango na biyar akwai jam'iyyun siyasa kusan hamsin a wannan kasa. An kafa wani tarihi a siyasar Nijeriya a inda aka sami hadewar jam'iyyu uku, (Masu wannan ra'ayi sun tafi a kan cewa ban da jam'iyyar APGA, a cikin jam'iyyun da suka kafa jam'iyyar APC) zuwa hudu (Haka kuma wadanda suke a kan wannan hujja sun bayyana jam'iyyu hudu da suka hadu suka kafa jam'iyyar APC, jam'iyyun su ne, ANPP, da CPC, da CAN da APGA) suka zama jam'iyya daya wato Action People's Congress a matsayin jam'iyyar adawa mafi girma a Nijeriya.

## 2.8 Kishin Kasa

Abdullahi (1999:57-58) ya ce; kamar yadda Pachai ya ce a shekarar 1884 wata guguwar canji ta sake kadawa musamman sakamakon kafuwar jarida ta farko a nahiyar Afirka a kasar Afirka ta kudu wanda fitaccen dan jaridar nan na Afirka wato John Tego Jabavu ya kafa mai suna "Imvo Zabatsundu." Jaridar ta taka muhimmiyar rawa a siyasar garin Cape a inda ta mayar da hankali a kan abin da ya shafi kasa da kwadago, wanda a wannan lokaci ya kai wa kowa ko'ina a kasar Afirka ta Kudu.

Yakubu (1999:106 ) cewa ya yi; Ta kowane hali ana iya cewa, Sa'adu Zungur ne ya assasa irin bijirewar da siyasar NEPU ta fara yi. Haka kuma shi ne ya fadakar da talakawa 'yan siyasar NEPU irin bijirewar da za su yi wa gwamnati. Ya kara da cewa, Sa'adu mutum ne maras tsoro, ba ya tsoron shugabannin Turawan mulkin mallaka. Ya yi Allah wadai da duk wata tursasawa da suke yi wa mutane. Hasali ma shi ya fito da salon mun ki (we refuse) saboda kin amincewa da umarnin da Sarkin Bauchi ya bayar na a fitar da 'yan kungiyar "BGIU"(Bauchi General Improvement Union) daga dakin karatu na gwamnatin lardi ( NA Library). Duk da cewa a wancan lokaci, abu ne mai mutukar wahala a sami fitowar irin wannan kalami daga bakin talaka. Bayan wani lokaci sai wannan salo ya zama karbabbe musamman a wajen mabiya Aminu Kano a zamanin siyasa.

Malam (2001:47) ya kawo fahimtarsa a cikin wata makala. Wannan makala an gina ta ne a kan manufa ta kishin kasa da mutanenta, da kuma kokarin 'yantar da mutane daga cin mutunci da nuna wariyar launin fata. Hakan ya sa aka dauko

misalai daga wakokin “Dennis Brutus.” Wannan mutum da aka kawo misalin wakokinsa fitacce ne wajen wallafa wakokin bijirewa da bore, musamman ga Turawa a Afirka ta kudu

Jega da wasu (2003) sai suka ce talauci da tsangwama ba su kawar da Mudi Sipikin daga akidar rubuta waka ba. Wakokin Mudi Sipikin sun wuce yada manufofin jama’iyar NEPU kawai. Ya rubuta wakoki da suke wayar wa talakawa da kawunansu domin su sami ‘yancin kansu da hakkokinsu daga wajen Turawan mulkin mallaka. Haka kuma wakokin suna ilimantar da su dangane da illar mulkin mallaka da kuma zaluncin Sarakuna. Fitacciyar waka a kan wannan ita ce “wakar yabon Malam Aminu Kano”

Mudi Sipikin ya tsara waka a kan batutuwa daban-daban, wadanda suka hada da, addini da soyayya da mutuwa da hisabi da sauransu. Wakokinsa na farko-farko sun karkata a kan Turawan mulkin mallaka domin nuna bijirewa.

Wadannan batutuwa dukansu waiwaye ne a kan kishin kasa a tarihin siyasar Nijeriya. Bayanan suna da nasaba ta kusa da wannan aiki domin yin kishi sai da jajircewa a kan manufa. Jajircewa kuma tana tare da bijirewa wadda ita ce lakar wannan aiki.

### 2.9 Neman Sauyi A Siyasar Kasar Hausa

Fitattun masana a fagen wakokin siyasa da suka hada da Birniwa (1987) da kuma Amin (2004 da 2006) sun baje kolin hajar tunani a kan wannan batu na neman sauyi siyasar Nijeriya musamman yankin Arewa.

Sun mayar da hankalinsu a kan wakokin Sa'adu Zungur a inda suka sha bamban. Kowannen su ya kawo hujjoji domin kare manufarsa. Bayan wadannan an sami wadansu ra'ayoyi daga masana da manazarta da suka hada da Malumfashi (1984) da Sklar (1963). Bari mu matsa gaba kadan domin saduwa da irin wadannan fa'idoji na kare kai dangane da akida.

Karon battar ra'ayi da aka sami tsakanin, Birniwa (1987) da kuma Amin (2004) ta ta'allaka ne a kan fitaccen dan kishin kasar nan Sa'adu Zungur. Birniwa ya bayyana Sa'adu a matsayin mai ra'ayin rikau bisa tsarin yadda ake tafiyar da mulkin Arewacin Nijeriya ba don komai ba, sai don wannan wakar tasa mai suna "Arewa Jumhuriya ko mulukiya." Ya kafa hujja da wadansu baitoci daga cikin wakar wandanda a ganin sa nuna goyon baya ne ga Sarakunan Gargajiya a fili, idan ba haka ba me zai sa ya ce:

Shaihu laminu shi da Mujaddadi,
Sun bar mana girman duniya.

Yalla za mu kiyaye har mu bar,
'Ya'yanmu su gaji halaliya.

Sarki Abdallah ka taimaka,
Ga Ciroma Sunusi da tarbiya.

Ka kiyaye al'ummarka duk,
Don kasarmu ta wanzu mulukiya.

Birni da fage da Tudun Wada,
Kauyuka bukokin tsangaya.

Kar ku bar arna su shige musu,
Don su watsa dafin Jumhuriya.
(Arewa Jumhuriya ko Mulukiya, Sa'adu Zungur)

Shi kuwa Amin (2001:86) sai ya ka da baki da hanzari ya ce, Birniwa ya yi kuskuren fahimtar Sa'adu Zungur da cewa shi ba dan neman sauyi ba ne, don kawai ya nuna goyon baya ga sarakunan Gargajiya. Amin ya ce, idan aka tsaya aka dubi Sa'adu ta fuskar addini da kuma zamantowar sa kaifi daya da kuma amfani da ra'ayin kansa, za a gane kiran da yake na a koma wa mulikiya ba rashin son sauyi ba ne, a' a sai dai fadakar da sarakuna da ya yi don su lura da hakkokin talakawa da suka rataya a wuyansu. Amin ya kafa hujja da wadansu baitoci daga cikin wakar "Arewa Jumhuriya ko Mulukiya"

Tutocin Shehu Mujaddadi,
Goma sha biyu ne Nijeriya.
Sir assadiku Abubakar,
Ga Arewa tana kan shan wuya.
Shehu Alkanemi a Yarwa ko,
Za ka yarda a rushe mulukiya.
(Arewa Jumhuriya ko Mulukiya, Sa'adu Zungur)

Da aka matsa gaba sai aka sake samin karon battar ra'ayi tare da samiwar kwararan hujjoji a tsakanin Birniwa da Amin tare da samiwar matallafa ga kowannen su. A yayin da Amin (2004) da Malumfashi (1984) suke cewa, nuna yarda da sarakunan Gargajiya da Sa'adu ya yi, ba yana nuna cewa shi ba mai neman sauyi ba ne. Mutukar dai mutum ya yarda ra'ayin sauyi shi ne kalubalantar wasu tsare-tsare da dabi'u da ta'doji da aka saba da su don burin ci gaban al'umma, to tilas a yarda da Sa'adu mai neman sauyi ne. Misali, dubi yadda ba tare da shayi ko tsoron a ce ga-shi-ga-shi ba Sa'adu ya fito karara ya yi Allah wadai da yadda walwalar jama'ar Hausawa take a wancan zamani, Hasali ma

Sa’adu bai gushe ba, sai da ya yi hasashen muddin dai ba a magance wadancan miyagun halaye a tsakanin mutane ba, to babu shakka Arewa tana kan shan wuya:

Mutukar a Arewa da karuwai,
Walla za mu yi kunya duniya.

Mutukar ‘yan iska na gari,
Dandaudu da shi da magajiya.

Da samari masu ruwan kudi,
Ga maroka can a gidan giya.

Mutukar yaranmu suna bara,
Allah ba ku mu sami abin miya.

A gidan birni da na kauyuka,
Da cikin makarantar tsangaya.

Sun yafu da fatar bunsuru,
Babu shakka sai mun sha wuya.
(Arewa Jumhuriya ko Mulukiya, Sa’adu Zungur)

Shi ma Malumfashi ya yi karin haske a kan wannan ra’ayi na Sa’adu dan neman sauyi ne, duk kuwa da bai kafa hujja da wani baiti na wakar Sa’adu ba.

Bisa fahimta, Sa’adu ya cancanta a kira shi dan neman sauyi saboda akida da kuma manufarsa ta kishin kasa. A lokacin da yake yin gwagwarmaya, babu sani ba sabo sai dai cancanta da kuma gaskiya.

Sklar (1963) da Birniwa (1987) kuwa sun tafi a kan Sa’adu mai ra’ayin rikau ne. Birniwa ya ce, Sa’adu fitaccen dan siyasa ne, ya kuwa nuna hakan cikin wakar “Arewa Jumhuriya ko Mulukiya”. Haka kuma ya ce kamar Mu’azu Hadeja, Zungur ma ya ba da dauki ga sarakunan Gargajiya inda ya nuna su a matsayin halastattun shugabannin Musulunci.Ya kuma nuna ya kamata su ci gaba da mulki

bayan samin ‘yancin kai. Wannan ra’ayi na Birniwa ya yi kama da na Sklar, duk da Sklar, kamar Malumfashi, bai kafa hujja da wata waka ta Sa’adu ba. Birniwa ya kara da kawo misali daga *Arewa Jumhuriya ko Mulukiya*:

An sha bamban bisa kan nufi,
Na shirin mulkin Nijeriya.

Niyyar kudu in suka daukaka,
Duk kasa ta zamo janhuriya.

Mu kam niyyar mu a karkasa,
Don Arewa ta zabi mulukiya.
(Arewa Jumhuriya ko Mulukiya, Sa’adu Zungur)

Haka kuma Amin (1997:135) A cikin wata makala, ya kawo hujjoji masu karfi domin kawai ya kare batunsa na cewa lalle-lalle Zungur mai neman sauyi ne. Da gani ba tambaya, lalle Sa’adu ya kule da dabi’ar Bahaushe ta rashin shiri ko kintsi. Shi Bahaushe galibi ya fi yin fargar-jaji, ya ki tsara iliminsa, da tsara lamarin daularsa da ciniki, don haka ne Sa’adu yake kira ga Bahaushe ya sauya. Sa’adu ya nuna ba a fi Bahaushe yawan ilimi ba, sai dai ba ya lura da abin da zai kai ya komo bare ya yi amfani da iliminsa. Abin mamaki Bahaushe ne yake cewa, “Amfanin ilimi aiki da shi”.

Amin ya kara da cewa, ba ta fannin walwalar jama’a kurum ba, hatta al’adu marasa kan gado na Bahaushe sai da Sa’adu ya yi kira da a sauya su. A “Wakar Bidi’a” Sa’adu ya ce, a kiyayi bidi’a a kama gaskiya kurum. Ya nuna wanda duk zai yi kira ga jama’a, musamman Hausawa, da su sauya wasu tsirfa da suka saba, to sai ya toshe kunnuwansa saboda irin jafa’in da zai sha kamar haka:

Ka jure suka da kibiyoyi na jahilai,
Don za su harbe ka, ka zarge su kan bidi'a.

In sunka cije a kan zargin ka ce Allah,
Sannan ka bar su cikin rudunsu 'yan bidi'a.

Farko sukan ce karambanin ka zai ja ka,
Zuwa ga halakar ka don ka zargi 'yan bidi'a.

Sannan su juya ta hanyoyi na bata mutum,
Har masu kafirta al'ummarka kan bidi'a.

Su ce kai zindiki, don rashin takawa,
Don ka yi suka ga al'ada ta 'yan bidi'a.
(Wakar 'Yan bidi'a, Sa'adu Zungur)

Duk dai a game da wakar siyasa Amin (1998) ya nuna, duk da ana goshin karni na ashirin da daya (21), har a lokacin ana jin duriyar wakoki masu jigon jihadi kamar yadda aka rika sami. Ya ba da misali da wakar "Ba za mu bi kwansitushin ba" ta Aliyu Rabi'u. Masanin ya yi sharhin wannan waka a inda ya rika danganta ta da wadansu wakoki na zamanin Shehu Usmanu Danfodiyo. Misali ya nuna kiran da sha'irin yake yi na a watsar da duk wani tsari, a kama Alkur'ani shi kadai domin shi ne hanyar samin tsira. Abdullahi fodiyo ma ya fadi haka a wakarsa mai suna *Tsarin Mulki na Musulunci* yana cewa:

Ku saurara gabatan muslimina,
Ku bi ta ku bar sarautak kafirina.
Su taru su dauki alwashi na da'a,
Ga foron nan na Alkur'ani da sunna.
(Tsarin Mulki na Musulunci, Abdullahi Fodiyo)

Shi kuma Aliyu Kurna cewa ya yi;

Mu amsa kira na addini,
Ba za mu bi kwansitushin ba.
Kur'ani babu ma makawa,
Sai ya zama shi yake a gaba.
(Ba za mu bi Kwansitushin ba, Aliyu Kurna )

Amin (2006:240-1) ya ce Kasancewar kasar Nijeriya tana da kabilu daban-daban mabiya addinai daban-daban, wannan ya haifar da mabambantan ra'ayoyi da tunani kan shirin mulkin Nijeriya. Masu neman sauyi sun yi suka da kakkausan harshe ga gwamnati a kan tsare da kuma daure wasu daga cikin 'yan kungiyarsu ta "JTI"(Jama'atu Tajjadidul Islam) don kawai sun yi imani da addininsu suna fadin abin da ya dace a yi. Suka kara da cewa wannan ya saba wa dokar da ta tabbatar da hakkinsu na 'yan kasa masu 'yancin gudanar da addini. Sai suka ce amma duk da wannan hali da ake ciki, bai hana wasu masu uwa a gindin murhu yin abin da suka ga dama ba. Sha'iri Aliyu Kurna a wakarsa da ya ba wa suna, *Rayuwar Musulunci* ya ce;

Katafawa ko sun dage,
Su na ta famar katafanci,

Suna ta karkashe bayin Allah,
Da taimakon gwamnatin zalunci,

Gwamnati ce take taimakon su,
Suke ta famar katafanci.
(Baza mu bi Kwansitushin ba, Aliyu Kurna)

A nan za a gane wakokin siyasa na addini irin wadanda aka yi a da, har yanzu ma suna nan kuma kyawawan makamai ne da suke taimaka wa al'ummar Musulmi wajen bayyana manufofinsu na bijirewa, musamman kan abin da ya shafi addini da siyasa.

A takaice idan muka dubi wadancan jerin hujjoji da masana suka kawo game da wadancan fitattun marubuta, za a ga cewa kaconkau suna da ruwa da tsaki game da wannan bincike na bijirewa a cikin wakokin siyasa.

Bayan bitar abubuwan da suka shafi siyasa, abu na gaba da za a duba shi ne addini;

## 2.10 Gwagwarmaya Tsakanin Malaman Addinin Musulunci Da Turawan Mulkin Mallaka

Orr (1911:177) da Mani (1956:63) sun yi tarraya a kan finjirewar da wadansu Malamai Musulmi mutane suka yi a garin Bauchi. Orr (1911) cewa ya yi a farkon shekara, an sami wadansu ‘yan tsirarun mutane masu tsaurin ra’ayi na addini suna kokarin tayar da tarzoma a lardin Bauchi. Sun yi kokari su sami hadin kan mutane domin a yi jihadi. Sarkin Bauchi tare da hadin kan Razdan sun yi kokari wajen kwantar da tarzomar. A karshe aka tsare shugabansu aka kai shi kotun lardi aka zartar masa da hukuncin kisa aka kuma kashe shi. Mani (1956) ya ce; wata rana a Bauchi bayan Turawa sun kama kasar, wani Malami ya zo yana cewa, ya kamata mutane su tashi tsaye su yi jihadi, wato su yi fada da Turawa, su kashe karnuka wadanda suka ci kasarsu suka kunyatar da su. Da jama’ar gari suka ji haka, sai suka yarda da abin da Malamin ya fada. Gari duk ya dauka, ana cewa ai ana nan ana shirin yin tawaye a kashe Turawa.

Dukkan kunshiyar Abin da Orr (1911:177) da kuma Mani (1956:63) suka kawo yana da dangantaka da addini musamman ire-iren tayar da kayar baya da wadansu mutane suka yi a lardin Bauchi. Ayyukansu suna da nasaba da wannan aiki, domin za a yi kokarin fahimtar yadda Hausawa suka nuna bijirewa a game da abin da ya shafi hanyar tafiyar da rayuwarsu.

Paden (1973:52-53) ya ce a Kano mutane da yawa sun bijire wa zuwan Turawan Ingila, musamman ta fuskar hanyar rayuwa. Sun tafi a kan cewa zuwansu karshen duniya ne ya zo. Hakan ya sa aka sami wani Malami mai suna Malam Ishaq Kano ya yi waka da ba a sami sunanta ba, ya yi bayani a zube kamar yadda aka sami. A cikin wakar yana cewa;

> Su kiristoci Allah Ya hore musu ni'ima idan aka kwatanta su da sauran mutane. Wannan ta sa duk wanda bai bi ra'ayinsu ba, sai ya hadu da fushinsu a duk wurin da suka je a kowanne gari. Haka kuma sun kakkafa coci-coci domin su batar da mutane, sun kuma bude makarantu domin amfanin mabiyansu, da babu komai a ciki sai dai mutum ya koyi karya da munanan dabi'u da tabewa. Addu'o'insu kuma ba su kunshe da komai sai neman abin duniya.

Ya kara da cewa;

> Sun zo sun saka mana haraji, kuma dole ne mutum ya biya a duk inda yake, birni da kauye. Sannan kuma suka dauki yaki da garuruwan da suka hada da; Masina da Zabarma daga nan suka shiga Munshi da Bussa da kuma kasar Jukun wadanda su ba tubabbu ba ne. sun ci gaba da mamayar kasar Hausa har zuwa garin Bidda da Hadejia da Gumel da Katagum, daga nan kuma suka afka wa baraden Rabeh "Rabeh's Army" suka je Sakkwato da makamai masu karfi da suka yi imani da su. Suka kawar da sarkin Musulmi daga kan mulki, shi kuma ya rabu da su saboda kar ya kauce a kan imaninsa. Haka nan suka kawar da Zubairu sarkin Yola, wanda ya kama hanyar tafiya Makka ba shiri. Bayan nan suka saka sarkin Kano Aliyu ya yi gudun hijira zuwa garin Lakwaja su kuma suka gaje garin. Allah ka kare mu daga sharrin makiyanmu.

Paden (1973: 53-54); ya bayyana cewa, a tsakiyar watan biyar a Kano, bijirewar da ake yi wa Turawan mulkin mallaka ta dauki salo na jihadi.

Wannan waka da aka sami a cikin Paden duk da cewa a tsarin zube take, tana da ruwa da tsaki a cikin wannan aiki. Idan aka dubi wakar da idon basira, za a tarar babu komai cikinta illa bijirewa. An bayyana yadda aka ki jinin Turawan mulkin mallaka da duk wani abu da suka zo da shi haihata-haihata. Don haka aikin zai bayar da haske na ganin hanyar tafiya ga wannan bincike.

Zagga da wasu (2004:75) cewa suka yi Kalifa Abdurahaman a shekarar 1902 ya ce:

> Ban amince da zaman ko dayanku ba tare da mu ba. Ba za mu taba yarda da ku ba. Tsakaninmu babu wata dangantaka sai ta tsakanin Musulmi da kafiri, kuma sai yaki kamar yadda Allah (SWA) ya umarce mu da yi. Babu karfi da iko sai wajen Allah mai girma.

Wannan ne bayanin da Kalifa Abdurahaman (d.1902) ya mayar wa Jakadan kasar Ingila a Nijeriya Turawan mulkin mallaka a lokacin da suka kawo hari Sakkwato a watan Mayu 1902.

Haka kuma suka kara da cewa; ranar 15 – 03 - 1903 kujerar Kalifan Musulmi ta fada hannun sojojin kasar Ingila. An sami cikin Sulaiman (1987) yana cewa, wannan ya faru ne bayan an kashe baraden Musulunci hamsin wadanda suka yi kokarin tabbatar da tutar Musulunci a tsaye.

Nasarar da Turawa suka sami a kan Kalifa Attahiru a shekarar 1903, ba ta kawo karshen bijirewar da ake yi wa Turawan Ingila ba. Kaurace wa wuraren da Turawa suka mamaye ya haifar da barazana ga aiwatar da manufofin mulkin kasar Ingila.

Suka kara da cewa, wani mawaki da ba a sami sunan wakar ba, yana cewa:

Kasar kuma tai cirri birni da kauye,
Ana fadin ba mu son mulkin Nasara.
(Wakar Al – Hajj Umoru)

Abin da Zagga da wasu suka kawo, yana da ruwa da tsaki a kan wannan bincike. Bayanansu wani karin tagomashi ne ga tafiyar wannan aiki, ganin cewa abin da suka kawo haske ne a kan abin da bijirewa ta kunsa musamman a zamantakewar Hausawa wadanda mafiya yawansu Musulmi ne.

Adeleye (1971) a cikin Umar (2006: 2, 3) Ya ce; bijirewa da zargi a game da mulkin Turawa a daular Sakkwato, abu ne fitacce tun daga kafuwar daular. Umar ya kara da cewa, a cikin nazarinsu na baya-baya, Abu-Manga da Bello sun yi matsaya da Adeleye kan cewa yin hijira manufa ce ta dace da tanade-tanaden Hausawa wadanda mafi yawansu Musulmi ne maimakon mika wuya ga Turawan mulkin mallaka.

Sa'id (1995:13) ya ce a karni na sha tara aka sami Mujaddadi Shehu Usmanu Danfodiyo, wanda ya kaddamar da jihadi kan ilahirin sarakunan kasar Hausa da suka kauce hanya. Nasarar da ya sami ta sa ya kafa kasashen Musulunci a fadin kasar Hausa. Haka aka ci gaba har tsawon shekaru dari (100), har zuwa lokacin da Turawa suka mamaye Arewacin Nijeriya, suka kuma kawo mulki mai shamaki (indirect rule). A wannan lokaci Hausawa suka fara dari-dari da cewa, za a kawo musu sabon tsarin rayuwa. Wannan ya sa Hausawa suka tashi tsaye wajen wayar da kan 'yan'uwa dangane da hatsarin da yake tattare da Turawa. Sai suka fara wa'azi suna rubuta kasidu suna yin wakoki. Haka kuma suka tafi bisa fahimta ta

cewa, komai na Nasara ba shi da kyau, domin haka marubuta wakoki suka shiga aikinsu na rubutu wakoki masu jigon bijirewa. Kyamar Turawa ta yi tasiri a zukatan Hausawa ta yadda duk abin da aka ce Turawa sun kawo mai kyau ko marar kyau sai a yi watsi da shi.

A karshe , bayanan da aka sami karkashin wannan batu za su taimaka wa wannan aiki domin kusan duk a kan kin aminta da Hausawa wadanda da yawancinsu Musulmi ne suka yi da Turawan mulkin mallaka aka kawo su.

**2.11 Gwagwarmayar 'Yan Shi'a Da Gwamnati**

Amin (2000:72) ya nazarci wata waka "*Ba za mu bi Kwansitushin ba.*" ya nuna cewa, babban jigon wakar shi ne bore da kuma tawaye ga gwamnatin Nijeriya, wadda aka bayyana da cewa ba ta Allah ba ce. An bayyana cewa, gwamnatin ba ta ga tafarkin Allah wato shari'a da Alkur'ani. Duk da cewa Shehu Usmanu Danfodiyo ya bayyana cewa, akasarin Malamai sun bayyana cewa bai halasta a yi wa shugaba tawaye ko bore mutukar yana tabbatar da adalci sai dai in ya yi ridda ko kuma ya tabu, to a nan sai a cire shi (diya'ul Hukkam:13). Ga alamu Malamin yana karin bayani ne ga Hadisin ma'aiki da ke bayyana cewa ba a tawaye ga shugabanci sai an ga kafircinsa ya bayyana karara.

"Ba wai ba inke" abin da masanin ya kawo a kan hanya daya yake tafe da wannan aiki da aka kuduri niyyar aiwatarwa. Bayani na farko a kan ra'ayin sauyi ne wanda salo ne a cikin tsarin siyasa, na biyu kuma a bore ne, wanda shugabannin

da aka zaba ta hanyar siyasa ake yi wa. Wadannan bayanai suna da nasaba da aikin da za a yi.

Miles (2003:80) Masani ne da ya tofa tofa albarkacin baki a kan fahimtarsa a game da bijirewa. Miles ya lura da cewa kauracewar da 'yan'uwa ('yan brothers) suka ce a yi wa gwamnati karkashin shugabancin El' Zazzaky suna kira ne da a sami juyin juya hali na addinin Musulunci a kasar Nijeriya.

An ci karo da Bunza (2005: 232-233) wanda ya nuna cewa, 'yan buraza ('yan shi'a) yana daya daga cikin sunayen da ake kiran su da shi. Koyarwarsu ita ce yunkurin yin bore ga Gwamnatin Nijeriya da Sarakunan Gargajiya da kuma Sarkin Musulmi. Haka kuma ya kara da cewa, magana a kan shari'a a Arewacin Nijeriya, abu ne da ake yin kwan-gaba-kwan-baya tun lokacin da Turawan mulkin mallaka suka mamaye daular Sakkwato a shekara ta 1903. Gwamnatin mulkin mallaka ta dakatar da amfani da sashen hukunta manyan laifuffuka, amma ta amince da a duba na kananan laifuffuka a kotunan shari'ar Musulunci.

Bayanin Bunza (2005) duk da cewa ba a raba shi da waka ba amma yana da fa'ida sosai, ana iya cewa mafi yawan wakokin 'yan shi'a jigon bijirewa suke dauke da shi. Don haka bayanin zai kara wa wannan bincike hasken tafiya.

Haka kuma a cikin shekara ta (2001), an sami wani littafi da aka wallafa wanda yake da nasaba da wannan aiki. Umar (2001:136) Ya ce akwai wata kungiya ta 'yan neman sauyi wadda take da alaka da kasar Farisa (Iran) mai suna Kungiyar 'yan uwa Musulmi "Muslims Brothers" karkashin jagorancin Ibrahim El'Zakzaky

Kungiyar tana tafiya ne a kan akidar shi'a. Ya kara da cewa, kungiyar a fili ta fito ta kira gwamnatin Nijeriya da cewa kafira ce (Kufr) don haka suka bukaci a kaurace mata kamar yadda suka yi.

Sauyi yana samiwa ta hanyar bijire wa abubuwan da ba a so. Bayanin Umar (2001), bayani ne na hikima da yake gwada bijirewa kamar yadda kungiyoyi suke yi. Aikin yana da kyakkyawar nasaba da aikin da za a yi.

## 2.12 Rashin Jituwa Tsakanin Sarakunan Kasar Hausa Da Turawan Mulkin Mallaka

Al-Hajj (1973:147,179,182) ya yi bayanin a shekarar alif dari takwas da casa'in da bakwai "1897" Amir al-mumin ya ki karbar ziyarar ban girma da Turawan mulkin mallaka suke kai masa duk shekara, a yayin da kamfanin Neja ya mamaye Bidda. Ya ce wannan mamaya ta saba da yarjejeniyar da suka wa hannu tsakaninsu.

Bayan da Turawa suka kama Yola a watan tara na shekara alif dari tara da daya (Sept 1901). Sarkin Adamawa Zubayru ya rubuta takarda zuwa Sakkwato yana cewa;

> Ba zan kasance na raba hankali biyu ba, ina tare da kai kuma na ce ina tare da Kafirai. Biyayya ta tana nan gareka tsakani da Allah da Manzonsa, da kuma kai jagora da kuma Mahadi. (Lamido of Adamawa)

An nada Amir al-mumin Attahiru ranar 13/10/1902, Turawa kuma sun kama Sakkwato ranar 15/3/1903. Bayan da Turawa suka kama Sakkwato, abin tambaya shi ne, zabin da ya rage wa mazauna Sakkwato guda uku ne. Ko dai a bijire wa

Turawa ko kuma a yake su ko kuma a yi hijira kamar yadda alQadi cAbd Allah ya fada a cikin littafinsa RISALAH ILA ‘L-MUc ASIRIN.

Siyasa ita ce harsashin tsarin shugabanci, a nan an bayyana irin gwagwarmayar da ta kasance ne tsakanin Sarakuna da Turawan mulkin mallaka. Bayanin yana da nasaba da tafiyar wannan aiki.

Har wa yau Junaidu (1990) ya kawo bayanin cewa; Sarakuna sun nuna rashin amincewarsu ga Nasara mutuka. Hatta ma gaisuwa idan ta wajaba sukan sanya hannuwansu cikin riga kafin su gaisa, kuma su wanke da ruwa mai tsarki bayan gaisuwar. Malamai ‘yan boko daga cikin ‘yan kasa, dole suturarsu ta kasance ta Musulunci ba tsarin Nasara ba. Mata ‘yan boko suka zama banzar gari. Dole su auri mazaje wadanda ko “ e bi si di” ba su sani ba idan suna da bukatar aure. Mata ‘yan boko a idon Hausawa Musulmi, ‘yan bariki ne wato karuwai a takaice. Wani muhimmin abin lura a game da wannan bijirewa tsakanin Musulmi Hausawa da Turawa ita ce; rashin yarda da tsarin mulkin Nasara, wanda shi ne sanadiyar yin yaki a tsakaninsu

Tibenderana (1988:61) ya ce Sarki Muhammadu Aliyu ake dangantawa da tashin wata gobara a garin Jega da ta jawo asara mai yawa a shekarar 1905. Don haka a watan takwas na wannan shekara shugaban lardi Burdon, ya nemi izini daga wajen Gwamna Lugard domin cire Aliyu daga sarautar Gwandu. Ya danganta cirewar da rashin iya shugabanci da gallaza wa talakawa da kuma rashin taimakon gwamnati na tsawon shekaru biyu da rabi.

Bayanin da Tibenderena ya kawo sun bayyana cewa, akwai rashin daidaiton ra'ayi mutuka tsakanin sarakunan Gwandu da Sakkwato da Turawan mulkin mallaka. Wannan rashin daidaito shi ya haifar da bijirewa dangane da duk wani abu da Turawan suka zo da shi. Bijirewar ta kai a yi Hijira da kuma cire Sarki daga gadon sarauta, kamar yadda aka sami Attahiru Ahmadu ya yi aka kuma cire sarki Aliyu na Gwandu. Wannan bayani a kan bijirewa ne domin haka bayanin yana da dangantaka da wannan nazari da za a yi.

Bunza (2001:1, 4) ya kawo fahimtarsa inda ya ce, duniyar bakar fata ta sha yunkure-yunkure a kan nuna kin amincewarta ga kin mulkin Nasara da miyagun dabi'unsa. A wadansu wuraren, yunkurin akan yi shi da sunan addini. Wasu wurare da niyyar tunkude bakin haure 'yan mu-kadai-muka-iya. A wasu wuraren kuwa akan yi yunkurin kawar da Turawan mulkin mallaka da karfin Allah tare da neman yardarsa da yunkurinsu na jihadi. A gundumomin kasar Hausa da dama an sami wadanda suka yi yunkurin nuna rashin yardarsu a bayyane game da kin aminta da zama da nasara wuri daya. Fittattun mazaje daga cikinsu akwai sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu da sarkin Hadejia da jama'arsa da Malaman Satiru da sarkin Jega da jama'arsa da sarkin Keffi da jama'arsa da talakawan Ambursa da Sambawa da Kurya da Sangelu da Kalgo da Raha, duk wadannan sun yi fito-na-fito aka yi accakwama da su suka tsira da mutuncinsu.

A bangaren gwagwarmayar sari-ka-noke kuwa, Hausawa sun yi abin a zo a gani. A fannin wasannin yara da takkai duk an sami irin wannan yunkurin tsarmi-tsarmi. A bangaren Malamai marubuta littafai da wakoki nan abin ya fi bazuwa

sosai. Marubuta daga cikin Malaman kamar su Malam Darho da sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu da Malam Maharazu da Malam Muhammadu Huci da Alkali Bello Gidadawa da Alkali Khalilu Wurno da Malam Garba Gwandu da Sambo Wali da sauransu.

Ganin cewa wannan nazari zai daddagi wakoki ne domin fito da bijirewa, tabbas wadannan bayani da Bunza ya kawo yana da nasaba da nazarin da za a yi.

Wakili (2005: 137-138 da kuma 146-147) ya ce, bayanai sun tabbatar cewa, masarautar Hadejia, kasa ce ta Musulmi da suka yi Allah wadai da mika wuya ga Turawa wadanda ba Musulmi ba. Haka kuma ya ci gaba da cewa, wadansu masarautu mafi yawa a cikin daular Usmaniya, sun bijire wa Turawa amma cikin ruwan sanyi. Manufa sun tafi a kan cewa, Turawa sun fi karfinsu, a karshe dai ana iya cewa sulhu suka yi .

Haka kuma ya nuna cewa, an tafi da hankalin mutane wajen bijire wa Turawa. Ana yada jita-jita cewa, Turawa za su wargaza addinin Musulunci da tsarin siyasa. A lokacin da wannan magana ta kama jikin mutane, sai aka yi wa Turawan mulkin mallaka bore. Haka su ma Turawan sun kara kunna wutar boren ta hanyar ba mutanen Hadejia wa'adi na a mika wuya ko kuma a yi yaki, bayan sun san karbar wa'adi a wannan hali zai yi wuya.

Bayani na farko da Wakili (2005) ya kawo a kan hanya yake. Domin bijirewar da mutanen Hadejia suka yi, ta kai su ga gwabza yaki, haka ya sa aka sami wani mai suna liman Muhammadu ya tsara "wakar begen yakin shahadar Hadejia." Za a

dubi wannan waka da idon basira domin fitowa da nau'in bijirewar da take cikinta musamman bijirewa ta shahada.

Haka kuma Umar (2006:24) ya ce; Gwamna Lugga yakan amince da mulkin duk wani sarkin da aka fi karfi idan ya mika wuya. A daya hannun kuma, yakan cire duk wani sarki da ya ki tafiya da su, domin kawar da duk wata irin bijirewa da ake tunanin nuna musu, sai su nada sarkin da yake ra'ayinsu. A lokacin da Gwamna Lugga ya rubuta wa sarkin Musulmi Abdurahaman takarda cewa, ya kama Bauchi sai sarkin Musulmi ya ba shi amsa cewa;

> Ina fada maka ba mu umarce ku da ku shiga lardin Bauchi ba, idan kuma kun shiga, ba mu bukatar komai daga wajenku sai daga wurin Allah. Kuna da addiniku muna da namu. Muna neman taimako ne kawai daga wajen Allah mataimaki Rahimi, kuma babu karfi da iko sai daga wajensa, subahanahu wata'ala." (Caliph Abdur Rahman ibn Atiku 1891-1903 in The Sokoto Caliphate: *A Legacy of Scholarship and Good Governance*)

Wadannan bayanai suna kan hanya daya da wannan aiki domin an nazarci wakoki a cikinsu masu nuna bijirewa ga Turawa misali wakar "Shahada Zahira." Haka kuma Junaidu (1990) ya nazarci wakar Abubakar Maikaturu ta "Gudun Duniya" wadda bijirewa ce a cikinta tsantsa.

### 2.13 Gwagwarmayar Neman 'Yanci Daga Turawan Mulkin Mallaka.

Abdulkadir (1974:100) a tasa fahimtar, Sa'adu dan neman sauyi ne kuma mai bijire wa wadansu miyagun al'adu na Hausawa. Idan aka dubi wakarsa ta "Arewa Jumhuriya ko Mulukiya" yana cewa;

> In za ka fadi, fadi gaskiya,
> Ko me taka ja maka ka biya.

(Sa'adu Zungur Wakar Arewa, Jumhuriya Ko Mulukiya)

Ta la'akari da kunshiyar wannan waka, an fahimta cewa, Sa'adu ya fara da jan hankalin mai karatu kan cewa, duk abin da mutum zai fada ya tsaya kan gaskiya, kuma ya kaddara karbar duk wani abu da zai bijiro masa sakamakon tsayawa kan gaskiyar nan. Wannan kauli da ya kawo ba duk marubuta wakoki ne za su iya kawo shi ba. Babu ja, wannan bayani haka yake, bijirewa ta hada da nuna rashin goyon bayan duk wani abu da ake ganin ba daidai ba ne. Haka kuma wasu daga cikin wakokin Sa'adu suna daga cikin wadanda za a yi wa sharhi nan gaba, don haka wannan bayani yana da abota da wannan bincike.

Masana sun yi rubuce-rubuce masu muhimmanci da yawa a game da gwagwarmayar masu neman 'yanci 'yan Nijeriya a wajen Turawan mulkin mallaka. A nan za a dubi abin da Yakubu (1999:1-4, da kuma 106) ya kawo a cikin littafin da ya rubuta a kan gwarzo dan kishin kasa Sa'adu Zungur.

Yakubu (1999:1) Duk da yake an fadi abubuwa da yawa a game da batun neman 'yanci, sai dai ba a fadi mutanen da suka yi wannan fafatawa ba. Musamman mutanen da suke adawa da manufofin Turawan mulkin mallaka. Haka kuma ya ce 'yan Arewa, wadanda suka hadu da 'yan kudu, domin kawo karshen mulkin mallaka su ake dauka masu tsattsauran ra'ayi 'yan neman sauyi (Yakubu 1999:4), ya kara da cewa, Hausawa Musulmi sun bayar da gagarumar gudummuwa wajen kawar da Turawan Ingila 'yan mulkin mallaka.

An sami bayanai masu muhimmanci daga Junaidu (1990: 238-245) ya ce: A lokacin da Turawan Ingila suka ci daular Sakkwato a shekarar 1903, suka kuma kashe Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu da mabiyansa a garin Burmi cikin jihar Bauchi, Gombe a halin yanzu. Sun dauka sun gama da Musulunci ke nan. Haka ya sa wani jami'in mulkin mallaka mai kula da lardin Bauchi ya yi galatsi saboda nasarar da sojojinsa suka sami ya ce;

> Karshen masu addinin Muhammadu ya zo, ba za a kara samin su ba.
> (The Colonial Resident in Bauchi Remark)

Masanin ya kara da cewa; duk abin da ya faru, Hausawa wadanda da yawansu Musulmi ne ba su karaya ba wajen bijire wa Turawan mulkin mallaka. An lura da cewa, yaki da alkalami ya fi yaki da takobi. Wannan ta sa Musulmi suka bayyana duk wanda ya bi Nasara a matsayin kafiri. Marubuta wakoki da suka rubuta waka sakamakon bijire wa Turawa sun hada da Malam Labbo Dan Mariya Kwasare wanda ya rubuta fitacciyar wakar nan "Wakar Zuwan Annasara." Kamar yadda aka sami Junaidu (2009) ya kawo a cikin wata takarda da ya rubuta "Resistance to Western Culture in the Sokoto Caliphate: A Lesson to Generation yet Unborn."

Wannan bayani da Junaidu ya kawo yana da nasaba da wannan aiki domin, an fito fili an bayyana yadda Hausawa da mafi yawansu Musulmi ne suka ki aminta da Nasara da kuma abubuwan da ya zo da su wato suka bijire musu. Haka zalika da ma a kan bijirewar aka tsara gina wannan aiki.

Danbazau (2001) ya bayyana yadda gwagwarmayar neman 'yancin kai ta gudana da yunkurin raba Nijeriya da wasu suka yi. Waka tana daya daga cikin makaman

da aka yi amfani da su wajen neman ‘yanci. Irin wakokin da aka yi amfani da su, mafiya yawa masu jigon bijirewa ne. Bayanin da ya fito a cikin wannan littafi da Danbazau ya rubuta ko shakka babu zai zame wa wannan aiki fitila ta ganin hasken hanya. Aikin gaba dayansa a kan wakokin siyasa ne, kamar yadda wannan aiki ma zai ta’allaka a kan wakokin siyasa domin haka suna da nasaba.

Maishanu da wasu (2004) Sun ce, Malam Ibrahim Khalil ya yi rubuce-rubuce a kan batutuwa daban-daban da suka shafi al’umma. Daya daga cikinsu ya hada da mayar da hankali a kan yanayin mulkin mallaka wanda abu ne da ya faru lokacin yana raye. Canje-canje da suka faru ga al’ummar Musulmi sakamakon mulkin mallaka suna daga cikin abin da ya jawo hankalin Malamin har ya rubuta waka “Dubi Musulmi.” A cikin wakar ya bayyana yadda wasu Musulmi suka fandare suka saki hanyar shari’ar Musulunci. Haka kuma ya yi Allah wadai da wadansu manufofi da Turawan mulkin mallaka suka kawo kamar jangali da haraji wadanda babu su lokacin Usmanu Danfodiyo.

Abin da aka kalato a cikin wannan mukala zai taimaka wajen kara fahimtar ayyukan Malamin. Domin wakarsa ta “Dubi Muslmi” tana cikin wakokin da za a yi amfani da su wajen sharhi.

Umar (2006:102) ya ce an ci karo da bayanin mamayar da Turawan mulkin mallaka ta haifar. Abubuwa uku ne ake ganin mamayar ta haifar da suka hada da kauracewa (Hijira) da mika wuya da kuma sulhu. Kowanne daga cikinsu idan aka duba nau’i ne na bijirewa.

Wadannan bayanai suna da nasaba ta kut-da-kut da wannan bincike. Hasali ma, bayanan sun fito mana da abin da ake ganin sakamakon bijirewa ne ko kuma abin da ya faru bayan da aka bijire wa Turawan mulkin mallaka. Wadannan bayanai za su yi mutukar tasiri wajen fashin bakin bijirewa a cikin rubutattun wakoki kamar yadda ake sa ran yi nan gaba.

Umar (2006: 22) yana cewa, fitaccen mataki na gaggawa da Turawa suka dauka shi ne, abin da suka yi a kan garin Satiru ranar 13- 2-1906. Mai rikon Razdan na Sakkwato ya jagoranci sojojin Ingila su kama mai garin Satiru Malam Isa bisa dalilin bayyana kansa a matsayin Mahadi. Mutanen Satiru suka yi wa sojojin Ingila kwanton bauna suka kashe sojoji ashirin da bakwai (27) da kuma jagoransu Mr Hillary hade da wasu Turawa biyu. Turawa sun sake yunkuri na biyu a Satiru, duk da cewa ba su yi nasara ba, amma an kashe mai garin Malam Isa. Bayan mutuwarsa sai aka nada Malam Danmakaho a matsayin sabon mai gari.

Da aka waiwayi abin da Jumare da wasu a (2007) suka fada a kan Satiru, sai aka tarar yana da amfani wanda zai kaifafa tunaninmu a game da abin da aka yi a Satiru. Sun ce nan da nan sai Satiru ta zama cibiyar ‘yan adawar Turawan mulkin mallaka. Domin haka mutane daga ko’ina masu ra’ayin kin jinin Turawan mulkin mallaka suka yi tururuwa zuwa Satiru. Satirawa Malamai ne talakawa wadanda ba su kaunar mulkin Turawa da kuma duk abin da ya jibance su. Ana ganin kusan duk mutanen da suka hadu a garin ra’ayinsu daya ne. Sun kara da cewa, yunkurin bijire wa mulkin mallaka da Satirawa suka yi, ba wai a kan kasar Ingila ba ne, a a har ma da duk wata kasa ta Turawa.

Khalid da wasu (2008:140-141) suka ce daga cikin abubuwan da masarutar Jega ta kyamata sakamakon zuwan Turawa ya hada da duk abubuwan da Turawa suka zo da shi, kamar abubuwan da suka shafi rayuwa irin siyasa da tattalin arziki da kuma abin da ya shafi zamantakewa. Malamai suna a gaba-gaba wajen bijire wa duk wani abu da Turawa suka kawo. Amfani da waka wajen bayyana damuwar mutane a kan Turawan mulkin mallaka yana daga cikin hanyar da marubuta wakoki suka yi amfani da ita, wakar "Zuwan Annasara Kasar Hausa" da aka danganta da Malam Auwwalu Namajida fitaccen misali ne.

Malam Auwwal Na-majida yana daga cikin fitattun maluma da suke yin waka domin nuna abubuwa na rashin jin dadi da zuwan Turawa 'yan mulkin mallaka. A matsayinsa na marubucin waka, ya yi waka mai jigon farkar da jama'a mamayar da Turawa suka yi wa Daular Sakkwato. Daga nan ya tsara wakar " Zuwan Annasara"

Wannan bayani yana da muhimmanci ga tafiyar wannan bincike. Duk da cewa an sami a nan cewa, wakar "Zuwan Nasara" Auwwalu Na-majida ne ya yi ta, sabanin ra'ayin wasu na cewa Attahiru Ahmadu ne ya yi.

**2.14 Gwagwarmayar Satirawa Da Turawan Mulkin Mallaka**

Orr (1911: 17-18, 176-177) ya ce wani Malamin siddabaru dan kama-karya daga yankin da kasar Faransa ta mallaka, ya sauka a wani kauye da ba shi da nisa daga cikin garin Sakkwato da ake kira Satiru. Malamin yana yada tsauraran manufofin addinin Musulunci, kuma yana kira da a yi jihadi tare da kawar da duk wani

wanda ba Musulmi ba. Ya kara da cewa, irin wannan ba wani sabon abu ba ne, musamman a cikin kasashen da suke bin addinin da Annabi Muhammadu ya zo da shi. Ana haka sai Turawa suka mamaye garin. Orr ya kara da cewa, Kaftin Hillary bai yi magana ba a lokacin da Satirawa suke dauke da makamai irin su takubba da gatura, suna nuna shi suna tsawa da bakaken maganganu suna kuma wasa makamansu. Kafin a fara maganar sulhu, Satirawa sun afka wa Turawa, nan take aka kama Mr. Hillary da mataimakinsa da wani babban soja Bature. Aka kuma kashe sojoji ashirin da biyar. Likitan Turawa ya sha da kyar.

Mani (1956:63, 141-142, 153-154) ya kawo tasa fahimtar a game da bijirewar da Satirawa suka yi wa Turawan Ingila. Yana cewa, Satiru tana kimanin mil goma sha hudu (14) daga kudancin Sakkwato. Kamar shekaru biyu da suka wuce (1904) mai garin Satiru ya ce shi ne Mahadi. A cikin shekarar 1906 sai ga wani mutum wanda ake kira Danmakaho ya zo daga yankin da kasar Faransa ta mallaka, yana cewa ya kashe Turawa biyu daga inda ya fito kafin ya zo Satiru. Sunan Danmakaho na yanka "Saibou" Daga wannan sunan aka sami kirarin garin:

Satiru
Sa turu turu da idanu
Ta Malam Siba.
(Kirarin Garin Satiru Abubakar Sokoto Mohammed 1989:160)

An sami Mohammed (1989:32) yana cewa, bijirewar da mutanen Satiru suka yi , ta ginu ne a kan mamayar da Turawan Mulkin-mallaka suka yi wa Daular Usmaniya. Yunkuri ne da bayi da talakawa suka yi da niyyar kifar da gwamnatin mulkin mallaka. Sun yi wakokin da suke dauke da kirari ga garinsu ta sigar

bijirewa a kokarinsu na cimma manufar gwagwarmayarsu. Suna yi wa garinsu kirari da cewa;

Satiru
Sa turu – turu da idanu
Ta Malam Siba.
(Kirarin Garin Satiru Abubakar Sokoto Mohammed 1989:160)

Wannan kirari yana bayyana sunan wanda ya kafa garin Satiru ne. Haka kuma yana bayyana bijirewar al'ummar garin shi ya sa suka ce garin Satiru yana sa idanun makiyansu (Turawa) ya kumbure ya yi ja domin wahala. Wannan kuwa ba zai rasa nasaba da nasarar da Satirawa suka yi ba a kan Turawan Mulkin mallaka a farkon karawarsu.

Ganin cewa, an sami gudummuwa da fuskar adabi (kirari) da aka yi domin nuna rashin amincewa da Turawa a garin Satiru ta sa wannan bayani da aka kawo a sama zai zama mai alfanu ga wannan aiki.

**2.15 Bore A Daular Usumaniya**

Patton (1975:1-2) ya ce, adabi a game da bijirewar da mutanen Afirka suka rubuta a game da Turawa yana da yawa, sai dai rubuce- rubuce a kan bijirewa tsakanin 'yan Afirka babu yawa. Bijirewa a kasar Ningi ta tsiro ne sakamakon tawayen da aka yi dangane da wadansu manufofi na daular Sakkwato. Wannan bore ya ginu a dalilin abubuwa da suka hada da samiwar dariku shekaru aru-aru da suka wuce da kuma rikici tsakanin wani basarake da ake yi wa lakabi da Dansarki da wani Malami a garin Tsakuwa sakamakon kin biyan haraji da Malamin ya yi. Malamin ya ki biyan haraji don haka sai ya fice daga garin Tsakuwa ya koma kan dutsi

tsakanin kasar Ningi da Kano a inda ya hadu da kabilun Butawa, da Warjawa, da Kudawa, da Pa'awa, da kuma Sirwa da suke zaune kara zube ba tare da wani jagoranci ba. Malamin ya yi nasarar hada kansu ta yadda a karshe suka yi tawaye ga manufofin daular Sakkwato.

Wannan bayanai da Patton (1975) ya kawo, zai taimaka mutuka wajen sanin inda za a dosa, musamman a kan abin da ya shafi irin bijirewar da faru a kasar Ningi.

Wannan bayani da aka cirato a cikin littafi na sama yana dauke da wakoki da suka kunshi bijirewa, don haka sinadarai ne na tafiyar wannan aiki.

## 2.16 Kammalawa

A wannan babi an nazarci abubuwan da masana da manazarta suka kawo wadanda suke da nasaba da wannan bincike, da kuma ma'anonin wadansu muhimman batutuwa, domin fayyacewa. An nazarci littatafai da makaloli da kundayen kammala karatun digiri na uku da kuma na kammala karatun digiri na biyu daga jami'o'i da kuma cibiyoyin bincike da dakunan karatu daban da daban. Kamar yadda aka kalato, wadansu bayanan suna da nasaba da binciken kai tsaye wadansu kuma nasabar ta nesa ce. Da farko an fara da kawo asalin kalmar bijirewa, sai kuma ma'anarta da rabe-rabenta da kuma fahimtar masana da manazarta a kan kasar Hausa a takaice. An kawo bayani a kan ginuwar mulki a kasar Hausa, da tarihin wakokin bijirewa a kasar Hausa. An karkasa bayanan da aka yi bitar su zuwa muhimman sassa da suka hada da siyasa, da addini, da kuma bore. A karkashin siyasa an tabo ma'anar siyasa da kuma ginuwar siyasar zamani

da ya hada da kafuwar jam'iyyun siyasa sai kuma kishin kasa da neman sauyi a siyasar Nijeriya. Bitar addini ta hada da ma'anar addini da gwagwarmaya tsakanin Malaman addinin Musulunci da Turawan mulkin mallaka da kuma gwagwarmayar 'yan shi'a da gwamnati. Sai abu na gaba wato bita a game da Turawan mulkin mallaka. A nan an kawo rashin jituwa tsakanin sarakunan kasar Hausa da Turawan mulkin mallaka da gwagwarmayar neman 'yanci a wajen Turawan mulkin mallaka da kuma gwagwarmayar Satirawa da Turawan mulkin mallaka. Bitar bore ta hada da ma'anar bore da bore a daular Usmaniyya da kuma bore na mata.

Sakamakon wannan bita da aka yi, abu ne mai sauki a fahimta cewa har ya zuwa wannan lokaci hannu bai kai kan wani aiki da aka aiwatar ba a kan bijirewa. Wannan ya haifar da gibi a nazarin wakokin siyasa a kasar Hausa, hakan ya sa aka tsiri yin wannan bincike, domin kokarin cike gibin da aka hango.

# BABI NA UKU

# BIJIREWA A WAKOKIN SIYASA TA FARKO (1903-1991)

## 3.1 Gabatarwa

A nan za a dubi yadda siyasar zuwan mulkin mallaka ta gudana, da kuma zamanin siyasar farko da ya kama daga Jumhuriya ta daya zuwa ta uku. Haka kuma za a dubi irin bijirewar da aka rika nuna wa Sarakunan Gargajiya, saboda yadda suka rika tafiyar da harkokin mulkinsu a kasar Hausa. A karshe za a dauki waka daya a cikin wadannan zamunna a dubi yadda bijirewa ta fito a cikinta.

Siyasa ta farko a nan, tana nufin irin tsarin siyasar da aka fara yi a Najeriya tun kafin a sami mulkin kai da kuma bayan an sami mulkin kai A takaice, lokacin da ake yin siyasa a kan tsarin siyasa na kasar Ingila. Ga abin da aka sami wani masani ya fada game da haka;

> Nigerian's set a precedent in breaking from their colonial constitutional heritage rejecting Britain's parliamentary form of democracy, which they had continued after their independence in 1960, they chose, in their first wholly Nigerian-made constitution, to follow the American model instead (Herskovits 1979).
>
> 'Yan Najeriya sun kafa tarihi a tsarin siyasarsu ta hanyar ballewa daga abin da suka gada na tsarin wakilci a Dimokiradiyyar Birtaniya da suke yi tun kafin samin mulkin mallaka a shekarar 1960. Sun sauya tsarin mulki a karon farko yadda zai dace da irin Dimokiradiyyar Amurka (Herskovits 1979).

Tsarin Dimokiradiyyar da ake amfani da shi a farko ba shi ne ake yi yanzu ba. A yanzu ana amfani da tsarin da kasar Amurka take amfani da shi ne. A cikin wadannan zanguna da aka ambata da farko (1903-1991) za a dubi yadda aka yi wakoki na kin aminta da duk wani abu da ya zo wa Hausawa da ba su yarda da shi ba, musamman lokacin mulkin mallaka. Haka kuma, za a nazarci irin bijirewar da ta fito a cikin wakokin siyasa, musamman na Jumhuriya ta daya zuwa ta uku. A karshe za a dubi irin bijirewar da aka rika nuna wa sarakunan Gargajiya saboda yadda suka rika tafiyar da harkokin mulkinsu a kasar Hausa, tsarin da ake ganin akwai rashin adalci da kuma tursasawa a ciki, musamman ga talakawa.

A takaice, a cikin dukkan wadannan zanguna da aka kawo a cikin wannan babi, an sami wakoki masu dauke da bijirewa a cikinsu. Irin bijirewar da aka nuna a kan Nasara da kuma abubuwan da suka faru a cikin Jumhuriya ta farko zuwa ta uku, da kuma irin bakin mulkin sarakuna kamar yadda aka fito da su a cikin wakokin suna daga cikin abin da za a kalla a cikin wannan babi.

### 3.2 Bijire wa  Mulkin Mallaka

Mulkin mallaka wani tsari ne na tafiyar da gwamnati da jama'ar kasashe masu tasowa, musamman wadanda Turawa suka ci da yaki ko suka mamaye su da karfi wanda ba lalle ne kuma ya zamana kasashen sun gamsu da wannan hanyar ta gudanarwa ba (Sa'id 2002:150).

A shekarar 1885 Turawa suka yi nasarar mallake kasashen Afirka. A lokacin ne suka fito da dabarar rarraba kasashen Afirka suka kuma mulke su, daga ciki akwai kasar Ingila da Faransa da Italiya da Potigul da Spain da kuma Belgium (Talton

2006). A wannan hali sai Turawa suka karkato da hankulansu zuwa kasashen Afirka da Asiya da Pacific da sauransu domin su sami ma'adanai da abubuwan sarrafawa a masana'antun kasashensu. A kokarinsu na yin haka suka nemi hadin kan sarakuna da shugabannin al'umma domin cim ma burinsu. Sakamakon haka sai mutanen Afirka suka yunkuro domin bijire wa wannan manufa ta Turawa (Talton 2006).

Zuwan Turawan mulkin mallaka Nijeriya ya ci karo da matsaloli iri-iri. A yankin kudu, sai da Turawa suka yi yake-yake da kabilu daban-daban. Fitattu daga cikin yake-yakensu akwai wanda suka yi da 'yan Ijebu a Ijebu Ode cikin shekarar 1892, da wanda suka yi da Aro- Chukwu na kasar Inyamurai a shekarar 1902, da kuma wanda suka yi da 'yan Aniocha na kabilar Ijaw a cikin yankin Ogwashi Uku cikin jihar Delta a yanzu a shekarar 1914. A ranar daya ga watan Janairu 1900, Turawan Ingila suka yi furucin mamaye yankin Arewacin Nijeriya zuwa mallakarsu. Wannan ne ya zama sanadin nuna bijirewa daga sarkin Musulmi da sarakunansa, da wasu yake-yake da suka biyo baya, har lokacin da sojojin Ingila suka mamaye Sakkwato a 1903 (Umar 2006).

Mafiya yawan marubuta wakokin Hausa Musulmi ne kuma Malamai. A cikin karni na goma sha tara Mujaddadi Shehu Usmanu Danfodiyo ya bayyana domin ya jaddada addinin Musulunci a kasar Hausa. Wannan shi ya haifar da kaddamar da Jihadi a kan Sarakunan Hausawa (Habe) wadanda ake ganin sun kauce wa tsarin Musulunci. Nasarar da ta sami sakamakon wannan Jihadi ta sa aka kafa

Daular Musulunci (Daular Usmaniya) a kasar Hausa a inda aka sami tsarin mulki na masarautu bisa ka'idar Musulunci (Sa'id 1995:13).

An kasance bisa wannan tsari a kasar Hausa tsawon shekaru dari kafin Turawan mulkin mallaka su mallake Arewacin Nijeriya a inda suka kawo tsarin mulki mai shamaki. Musulmi sun zauna cikin tsoro da rashin tabbas na sababbin abubuwa da aka zo musu da su ciki har da sabon addini da kuma rashin 'yanci na aiwatar da addinin da suka saba da shi. Duk wannan rashin 'yanci Turawa ne suka kawo wadanda kafirai ne. Wannan ya saka maluma a cikin Musulmi suka dukufa wajen ayyukan wayar da kai game da barazanar da take fuskantar addinin Musulunci da kuma zamantakewa. Haka kuma suka fara wa'azi a kan miyagun dabi'u na Turawa, da kuma rubuta wakoki da kuma gabatar da hudubobi a masallatai. Duk wani abu da Turawan Mulkin Mallaka suka kawo sai Hausawa su yi watsi da shi haka kuma wadanda da suka yarda su yi aiki da Turawan sai da aka yi Allah wadai da su da kuma duk wani abu da ya fito daga wajen Turawan Mulkin Mallaka komin kyansa, sai a yi watsi da shi (Sa'id 1995:13).

Wani abin lura a game da wakokin da aka sami a wannan lokaci shi ne, kamar yadda tarihi ya nuna, mawakan farko da aka sami walau rubutattu ko na baka, akasari Malamai ne wadanda suke da ilimin addini. Haka ya sa ake samin tasirin addinin a cikin wakokinsu. Haka kuma, tarihi ya nuna cewa ainihin halayen mawakan siyasa na farko 'yan kishin kasa ne, masu kishin jam'iyyu. Don haka, wakokin da suka rika yi wa jam'iyyu suna yi ba domin su sami wani abin hasafi ba.

An yi wakoki a kan wannan manufa ta kin Bature, wasu kuma suka yi a kan Nasara wasu kuwa kayayyakin da suka zo da su aka kushe. Irin wadannan abubuwa su aka hade aka dubi yadda Hausawa suka yi Allah wadai da Nasara ko Bature ko kuma Mulkin Mallaka. A nan, za a rattabbo abubuwan da hannu ya kai kansu.

### 3.2.1. Bijire wa Zama Tare Da Annasara

> Ban amince zama tare da ku ba. Ba za mu yarda da ku ba, tsakaninmu babu wata dangantaka sai ta tsakanin Musulmi da kafiri, kuma sai yaki kamar yadda Allah (S.W.A.) ya umarce mu da yi. Babu karfi babu dabara sai a wajen Allah mai girima
> (Kalifa AbdurRahaman d. 1902 ga babban jikadan kasar Ingila a Nijeriya Mayu, 1902 in The Sokoto Caliphate: A Legacy of Scholarship and Good Governance)

An bayyana zamantakewa a matsayin zaman tare wanda kan jawo shakuwa da juna. (Kamusun Hausa 2006:489)

Ta fuskar zaman tare Hausawa wadanda dayawansu Musulmi ne ba su amince da Nasara ba sam-sam. Saboda a tasu fahimtar, zama tare da Nasara yanayi na ubangida da Bawa ne domin, haka ba su yarda ba. Haka kuma Musulmi sun kyamaci kusan duk abubuwan da Nasara suka kawo komai kyawunsa ko muninsa (Sa'id :1995:12). Haka kuma Junaidu (1990:238) yana cewa, an kyamaci Nasara sosai ta yadda ko gaisawa da sarakuna za su yi da su sai sun saka hannunsu a cikin riga kana su gaisa da su, bayan gaisuwar kuma sai su wanke da ruwa mai tsarki.

Malam Ibrahim Khalilu Marinar Tsamiya yana cewa:

5.Dauki zama tare da Salihina,
Ban da zama tare da murjifina.

21.Dubi Musulmi ka biyat Bature,
Sun zama dai da shi batun ya dore.

28.Dubi Musulmi aka jingacewa,
Shi dora aiki na gidan Bawbawa.

44.Dubi Musulmi ka biyat Nasara,
Gidanku dai gobe da Dan Mugira.

67.Kowane kag gani shina mu'amala,
Da kafiri shina zama dai don ka kula.

71.A'uzu Billahi da yin soyayya,
Da kafiri mun fi da son kiyayya.
(Wakar Dubi Musulmi ta Ibrahim Khalilu Marinar Tsamiya, Sakkwato.)

Mutukar dai mutum ya yarda da cewa ra'ayin bijire wa Nasara shi ne kalubalantar mu'amala da daukar dabi'u da tadoji da aka san Nasara da yin su, tilas mutum ya yarda Ibrahim Khalilu mai neman sauyi ne daga sha'anin Nasara. Misali dubi yadda Ibrahim Khalilu ba tare da shayi ko tsoron a ce ga-shi-ga-shi ba, ya fito karara ya yi Allah wadai da duk wanda yake zama ko mu'amala tare da Nasara. Haka kuma ya ce duk wanda ya biye wa Nasara ya zama tamkar shi wato kafiri kenan, hatta ma Bahaushe Musulmi ya yi wa Nasara aikin kwadago, Malam Ibrahim Khalilu ya yi watsi da yin haka. Dadin dadawa idan aka dubi wannan Abin da marubucin ya kawo, ya zama tamkar gwagwarmaya tsakanin mai bauta da wanda ake bauta wa. A karshe Malamin addu'a ya yi, inda ya yi Allah wadai da kafiri ya nuna cewa da soyayya da shi gara kiyayya.

Alhaji Shehu Shagari cewa ya yi;

7.Halin alheri ko guda bai san shi ba,
Komi shi ke don kansa dai yai yi shi.

8.Motsi kadan duk sai shi ce mana ci gaba,
To baya dai zai kai mu in mun bi shi.

10.Dada bai da da a cikinmu balle dan uwa,
Ya ce diya muke ga mu ko bayinshi.
(Wakar Baturen Inglishi ta Alhaji Shehu Shagari)

Haka kuma a wannan bangare na nuna bijire wa dangane da zamantakewa da Nasara an sami tofin albarka daga Shehu Shagari a cikin wakarsa ta Baturen Ingilishi. Ba tunanin zama tare da Nasara kurum sha'irai suka bijire wa ba, har ma da mu'amala da Nasara kanta. Misali Shehu Shagari ya nuna cewa Nasara ba ya yin alheri sai halin yaudara haka kuma a duk lokacin da ya ce yana son ka to, son dan maciji ne, manufa ga kyau ga mugunta.

Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu kuwa sai ya ce;

18.Idan sun ba ka kyauta kada ka amsa,
Dafi na sunka ba ka guba Nasara

30.Talakka da mai gari duk dai gare su,
Wulakanci akwai shi ga Annasara.

34.Da masu zuwa cikinsu suna jiyayya,
Munafukkanmu ke ga ga Annasara.

37.Da mai cewa abinsu shina da kyawo,
Ku bar fis sai ku sa shi cikin Nasara.

38.Da mai gama 'yan uwa don sui kiyayya,
Shi bar kewa akwai wasu Annasara.

40.Da mai cin dukiyar wani babu hujja,
Ku bar fis sai ku sa shi cikin Nasara.

41.Da mai majanga ya kauce ga hanya,
Muna nan zaune tare da su Nasara.

45.Nasara fari gare su bisa jikinsu,
Cikinsu baki kirin shi ke Annasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

Bayani a kan bijire wa Nasara ba zai cika ba sai an kawo abin da aka sami a cikin wakar *Zuwan Annasara Kasar Hausa* ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu ne ya yi, kamar yadda Abdulkadir (1979) da Sa'id (1995) suka bayyana. Duk da cewa Junaidu (1990) da Usman (2003) su na da ra'ayin cewa Malam Labbo Dan Mariya Kwasare ne ya rubuta ta da kuma masu ra'ayin cewa Malam Awwal Na-Majida Jega ne ya yi ta kamar yadda Khalid at el (2008) ya kawo. Wadansu da suka hada da Dangambo (1980) da Sa'id (1978) suna da ra'ayin Malam Darho ne ya rubuta wakar.

A cikin baitukan wakar kamar yadda da aka rattabbo a sama an ja hankalin Musulmi wadanda mafiya yawansu Hausawa ne musamman wadanda suka kulla abota da Nasara. An zargi wasu da munafurci da kuma yin algushi wadanda aka nuna dukansu sun zamo kamar Nasara, saboda Nasara aka sani da yin wadannan abubuwan. An bayyana cewa, ko kyauta Nasara ya ba ka saboda tsananin kiyayya an ce kar ka karba, domin guba ce suka ba ka. Nasara farin jiki ne da shi, amma zuciyarsa baka ce, saboda rashin alherin da yake cikinta.

An sami Maharazu Barmu Kwasare ya kawo fahimtarsa a game da bijre wa Nasara ta fuskar zamantakewa kamar haka;

12.Haka nan shara'o'i na aAlkalai ga yau,
An fara kowace babu sai ta Nasara

75.Wani yanzu in yaj ji ta sai ka ji yai zuma,
Ko ko shi ce sai ya fado ma Nasara.

77.Ya kwashe kaya nai ga Shehu Mujaddadi,
Ya rataya su ga Almasihu Nasara.
(Wakar Maharazu Barmu Kwasare ta Annasara)

Bijirewar da aka sami a nan dangane da Nasara ta samo asali ta fuskar canza tsarin shari'ar Musulunci da aka yi da ta "Penal code". Baya ga nan sha'irin ya yi tofin Allah tsine a kan munafukan cikin Hausawa (Musulmi). Mutanen da suna cikin al'umma amma suna yi wa Nasara tsegunguma da gulma da munafurci da leken asiri. Hasali kuma, duk inda Nasara yake, ya fi so ya mayar da mutum bawa duk da irin soyayyar da yake yi wa mutum.

Shi kuwa Sa'adu Zungur sai ya ce;

31.'Yan fince da su da Nasaransu,
Sun kulla abotar masu gari.

53.Mun gane gizo na Nasara bare,
Na baransu Minista 'yan garari.
(Wakar Jihadin Neman Sawaba ta Sa'adu Zungur)

Bayanan da aka kawo a sama kusan kara jaddada manufarsu ce Sa'adu ya kawo a nan. A nan an sake bayyana illar munafukan da suke cikin mutane, suna zaune wuri guda da Hausawa ta daya bangare kuma suna yi wa Nasara hidima ta munafurci domin samin Abin duniya.

A sanadiyar mu'amula da Hausawa suka yi watsi da ita ta kasancewa tare da Annasara, an sami har zaginsa ake yi a cikin waka domin tsaninin kin yarda da amincewa da shi. A wani wurin kuwa kirari aka sami mutane suna yi kansu a kan Annasara, inda suke nunawa sun fi karfinsa, Misali;

#### 3.1.1.1 Zagi

Kusan dukkan bayanan da aka ci karo da su, masu bayyana ma'anar zagi, suna a luggance ne, Bargery (1934:1155) ya bayyana zagi da cewa: abaiban baki ko jafa'i ko alfasha, ko mugun baki ne zagi kuma yana iya zama zambo.

Hawkins (1981:2), cewa ya yi, zagi na iya kasancewa kai farmaki da miyagun kalmomi.

Fada wa mutum bakar magana ko bacin iyayensa (Kamusun Hausa, 2006:487). Kalmar zagi ba ta bukatar dogon sharhi a game da kunshiyarta. Abu ne da yake faruwa a rayuwar yau da kullum, ita kalmar zagi ta kunshi ambatar sunan mahaifin mutum ko mahaifiya ko kuma danganta shi da rashin mahaifi, misali shege ko dan banza da sauran miyagun maganganu da suka yi kama da haka. An yi amfani da zagi wajen nuna rashin yarda ko amincewa da Nasara lokacin da suka zo kasar nan musamman a cikin rubutattun wakoki na Hausa musamman na siyasa.

Wannan ya sa aka ci karo da wakar "Baturen Ingilishi" ta Shehu Shagari a inda ya yi amfani da miyagun kalmomi a kan Bature wadanda a tsarin zamantakewa tamkar zagi suke. Ya yi haka ne domin ya bayyana cewa, Bature kansa ya sani ba ya son kowa da ci gaba, shi dai a masa wahala amma shi ba zai yi wa kowa ba, wato irin tsarin da Turawa suke yi a kasashensu kafin juyin-juya-hali. Ya yi amfani da kalmomi masu nauyi domin nuna bijirewa ga Bature inda ya ce;

3.Na roki mai girma shi yo mini budi,

In zagi kafirin da ba su biyar da shi.

4.Don wajibina gun Musulmi duk shi fal-
Lasa kafiri, har dai Bature, don shi,
(Wakar Shehu Shagari ta Baturen Ingilishi)

Ya kara labta wasu kalmomin domin jaddada manufa, a nan sai ya ce:

6.Don ja'irina, kafiri, kuma makiri,
Ga halinsa kwas san shi bai kaunarshi.

A gaba kuma sai ya ce:

14.Mi ag gare shi abin yabo, ba ko guda,
Karya munafunci da kissa gare shi.
(Wakar Shehu Shagari ta Baturen Ingilishi)

Yana daga cikin zagi mai nauyi ka ce mutum kafiri ko ja'iri ko kuma makiri, dukkansu kalmomi ne na batanci ga mutum. Ba tare da jin nauyin wadannan kalmomi ba, Shehu Shagari ya labta su a kan Bature, domin tsananin nuna rashin yarda.

**3.1.1.2 Kirari**

Kirari yana zuwa ne da sigar siffanta ko kamanta abin da ake yi wa kirarin da wani abu ko mutum mai shahararren karfi, ko alfarma, ko daraja, ko dai wani hali na musamman da ya fifita. Kirari tsararriyar magana ce, 'yar doguwa, ta hikima, da akan shirya. Musamman, don kambama mutum ko wani abu (Umar 1987:24).

A takaice ana iya cewa, kirari zababbun kalmomi ne na hikima da fasaha da ake yi wa mutum ko mutum ya yi wa kansa ko gari ko kuma wani abu domin kambamawa ko ciccibawa na nufin siffanta shi da wani hali ko nagarta mai kyau.

Nuna rashin amincewa da Nasara ya fito ta sigar kirari kamar yadda za a ga misalai daga kirarin da Bahaushe yake yi wa Nasara da kuma kirarin garin Satiru da kuma su kansu Satirawa.

Daga cikin irin kirarin da Hausawa suke yi Nasara sun hada da;

Nasara uban Kare
Kana ganin gari ka kwana a daji
Funtu Ubangijin Mairiga
Ba saukar ka ba, inda za ka ajiye Majayin wando

Tsiyar Nasara sai za shi gida

Nasara asarar duniya
Dan tasalla ki sallah, mai fitsari a tsaye

Wadannan suna daga cikin irin kirarin da Hausawa suke yi Nasara, ba domin komai ba sai don a nuna rashin amincewa da kuma yarda da shi. Kirari na farko ya bayyana irin yadda dabi'arsa da mu'amalarsa take na kin zama a cikin mutane da kuma yin rayuwa tare da kare. A gaba kuma, Hausawa sun dawo daga rakiyar Nasara ta fuskar kin fadin gaskiya, duk irin zaman da ka yi da Nasara ba zai fada maka wata illa day a gani tattare da rayurwarka ba sai ya tashi tafiya garinsu. Haka kuma yana daga halin Nasara da Bahaushe ba ya so na lalata masa tsarin al'adu da addini da yake yi, sai kuma dabi'ar kafirci, wato rashin son addinin Muslunci da sauransu.

Kiararin garin Satiru yana nuni ne da sunan mutumin da ya kafa garin Satiru wato Malam Siba. Haka kuma kirarin yana nuni da irin shaharar garin wajen yin tawaye. Sakamakon jajircewa wajen yin tawaye sukan sa idanun makiyinsu ya yi tulu-tulu saboda wahala. A nan Satirawa suna misali ne da lokacin da suka ci

Turawa da dakarun Sarkin Musulmi da yaki har suka kama Bature mai suna Mr. Hilary shi ya sa suke cewa:

Satiru,
Sa turu-turu da idanu,
Ta Malam Siba.
(Kirarin Garin Satiru Sokoto 1989:160)

Satirawa,
Arnan farko madauka magana,
Ko an kashe ku kun kashe Hilliri.
(Kirarin SatirawaSokoto 1989:227)

Sakamakon bijire wa mu'amala da Annasara, haka kuma an bijire wa duk wani abu da ya kawo wanda ake ganin ba shi da amfani a wancan lokaci. Karatun boko wanda ya sami ne sakamakon zuwan Annasara kasar Hausa, yana daga cikin abin da aka ki aminta da yin sa.

### 3.1.1.3 Karatun Boko

Hausawa wadanda Musulunci yake da rinjaye a cikinsu sun fito da salon bijirewa kan karatun boko da bakin al'adu domin su kare addininsu (Junaidu,1990:239). A kasar Hausa, bayan shigowar Mulkin Mallaka mutane da yawa a Arewacin Nijeriya sun dauki karatun boko a matsayin biri-boko, wato abu maras amfani. An dauki haka ne saboda ba shi da amfani a rayuwar lahira. Yadda ake yin rubutun boko daga hagu zuwa dama ya kara tabbatar da kyamar karatun boko daga wajen Musulmi wadanda da yawansu Hausawa ne (Tsiga 2014:8).

Shigowar karatun boko yankin Arewacin Nijeriya, ya saka shakku ta sahihancinsa a zukatan mutane da yawa. Wannan bai rasa nasaba da fahimtar da aka yi cewa,

Turawan farko musamman Mishan sun rika saka sassan *Bible* cikin darrusan makaranta. Wannan ta sa ake bijire masa aka kuma yi watsi da shi (Inuwa:1987: 2). Mutane da yawa musamman a Arewa sun ki amincewa da tura yaransu makarantun boko saboda a fadarsu, ba za su yarda da makiyansu su karantar da 'ya'yansu ba (Tibendarana 1988:263).

Hausawa sun yi watsi da tsarin karatun boko da kuma al'adun Nasara, sun kuma bayyana cewa duk wanda ya yarda da Nasara shi ma ya zama kamar shi (Kafiri) kuma ya tafka babban sabo wanda sai ya nemi gafara. A wancan lokaci idan Hausawa (Musulmi) suka amince da karatun da karatun boko tamkar sun canza tsarin rayuwarsu ne ta yadda za ta zama irin ta Nasara.

Masana musamman sha'irai a kasar Hausa sun bayyana adawarsu da karatun boko da kuma wanda ya yi karatun da kuma Nasara wanda shi ne ya kawo karatun. Ana kyamatar wadanda suka yi karatun boko ta yadda wadanda suka yi karatun ba sa iya saka irin kayan da Nasara yake sakawa. Wadanda suke aikin koyarwa suna daga cikin wadanda suke samin wannan tsangwama. Ba sa iya saka wani irin kaya in ba irin na Gargajiya ba, dole sai su saka doguwar riga da wando buje su kuma saka hula dara su yi rawani (Junaidu 1990:239).

Irin wannan bijire wa karatun boko ta sa Maikaturu yake cewa;

15.Hausas su kwas san ta ya halaka,
Daidai da mai kirat dan mabudi.

16.Hausa don Allah ka yo irin taku,
Naka halshe don kak ka juye shi.
(Wakar Abubakar Maikaturu ta Gudun Duniya)

Saka yara makarantar boko a wancan lokacin da kiristoci suka kawo, ya kasance kuma suke yi wa harkar shugabanci sai ya zama tamkar an kiristan da yara ne da kuma koya musu al'adun Nasara, haka ta sa aka sami wani sha'iri yana cewa;

49.Wajen ilimi a can ne yay yi tushe,
Kujerin 'yan maza a hade da mata.

50.A ce wai diskashin ake yi tsakani,
Ga al'adarmu sam haka ba irinta.

(Wakar Haliru Wurno ta Muhimmancin Al'adunmu:Hadarin Rungumar na Waje)

Kyamar karatun boko ba ta tsaya ga shigowarsa ba kamar yadda aka sami hakan tun da farko, har ya zuwa wannan lokaci ba a daina bijire wa karatun boko ba duk da cewa an ga amfaninsa kuma ana cin amfanin nasa. Irin wannan kyama ta sa aka sami wani sha'iri ya fadi albarkacin bakinsa ta sigar bijire wa matakan ilimi da ake sami a tsarin karatun boko hade da irin mukaman da ake sami idan mutum ya kai ga samin irin matakan da ya bayyana. Ga abin da ka sami ya fada;

1.Digirin banza digirin wofi,
Iliminmu da ba shi da dan tofi.

2.Digirinmu na labari soko,
Ilimin ga na tulu ba rafi.

3.Digirinmu na zance ratata,
Ilimin wauta na ganin ka fi.

4.Ilimin ga a don shi kar ka tsaya,
Ilimin da kana tsaye sai ya tafi.

5.Ilimin fitina, ilimin wasa,
Ilimin a yi shewa ai tafi.

(Wakar Karamin Sani ta Auwal Anwar)

A nan ya nuna rashin amfanin ilimin gaba daya. Ya bayyana shi a matsayin wasa da babu wani taimako da mutum zai sami sakamakon yin sa sai dai sharholiya.

8. Ilimin a ci dadi ai galla,
Ilimin ga na karfafa ‘yan wofi.

9.Ilimin gaye na shiga mota,
Na kiran mata a ga dan tofi.

10. Ilimin ga na tushen iskanci,
Ilimin banza ilimin wofi.
(Wakar Karamin Sani ta Auwal Anwar)

A gaba kuma ya bayyana karatun boko a matsayin tushen iskanci da sharholiya da rashin sanin mutuncin kai bare na sauran jama’a.

13.Digirinmu na farko har na biyu,
Na ukunsu na ‘dokta’ cin zarafi.

14.A saman na ukun aka sa ‘reader’,
Mai ridar ‘ya’ya dan wofi.

15.A wuce ‘reader’ har Farfesa,
Mai feso karya sha-ka-tafi.

16.Digirinmu na zagin jahilci,
Tsananin jahilci shi muka fi.
(Wakar Karamin Sani ta Auwal Anwar)

Marubucin wannan waka ya tsine wa dukkan matakan ilimi na karatun boko. Ya bayyana su da cewa cin zarafi ne da karya, ya ce ilimi ne da ba ya kawar da jahilci sai dai karfafa fadada shi.

21.Ilimin ga na hasken fajirci,
Ilimin kwadayi, na bidar hasafi.

22.Digirin ga na kwandon shashanci,
Ga su wane da ‘Dokta’ ‘yan wofi.

23.Ilimin ga na shirme ni ban so,
Digirinku ku amshe ni in tafi.

24. Digirin wasa ilimin karya,
Ilimin a tsaya tsai ai kazafi.
(Wakar Karamin Sani ta Auwal nwar)

Kamar yadda ya rattabo baitoci na sama, ya bayyana karatun boko da cewa hanyar kudi da shashanci ne. Karatu ne da yake koya wa mutane kazafi da shirme da kuma uwa uba kwadayi.

### 3.2.2 Hijira A Matsayin Hanyar Bijire wa Annasara

Wanan hanya tana daya daga cikin hanyoyin da aka bijirwa Nasara kamar yadda bayani ya zo a cikin wakoki. Wannan hanya ita ce zabin da Amirul Mumunina Ahmadu Attahiru ya dauka na guje wa zama wuri daya da Nasara. Kamar yadda bayanai suka tabbata a cikin *Al Risalat Al-Wazir ila Al-ilmi Wa'tadbur Adeleye, R.A. 1968,* a lokacin zabi uku ne ga Musulmi cikinsu a dauki daya, ko dai a yaki Nasara, ko a yi zaman amana da shi ko kuma a yi hijira. Zabin yin hijira shi ne Amirul Mumunina Ahmadu Attahiru ya dauka, inda ya yi niyyar tafiya Makka wurin da babu Nasara. Sakamakon haka suka yi yaki da Nasara a garin Burmi wurin da aka kashe shi.

> Ban ga wani abu mai amfani ga dukkanin Musulmai ba da kuma mu (Kanmu) da kuma kai, face mu duka mu bar wannan kasa, domin wadannan karnuka sun yi muna kawanya kuma suna yi muna barazanar rinjayarmu. (Kalamin Sarkin Kano Aliyu 24th – February - 1903)

Hijira tana nufin mutum ya bar garin da yake ya koma wani gari a dalilin kaurace wa wani abu ko kuma dalili na ganin dama. Mutanen Makka su ne (Muhajirun) sahabban Annabi Muhammadu (SAW) da suka bar garin Makka saboda tsangwama suka yi hijira zuwa Madina suka fara sabuwar rayuwa a can.

Haka kuma, Hijira tana nufin kaurace wa sabon Allah da kuma komawa wurin da ba a sabonsa. A kan haka an sami hujoji daga Kur'ani mai tsarki da Sunna.

A cikin Suratul Tauba sura ta tara aya ta dari (09:100) Allah yana fada;

> Kuma masu tserewa na farko daga Muhajiruna da Ansar da wadanda suka bi su da kyautatawa, Allah ya yarda daga gare Shi, kuma Ya yi tattalin gidajen Aljanna: koramu suna gudana a karkashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan ne babban rabo mai girma.
>
> (Alkur'ani mai Girma da Kuma Tarjamar Ma'anoninsa Zuwa ga Harshen Hausa.Tauba sura ta 09 Aya ta100 shafi na 294)

A cikin Hadisi kuwa ga abin da aka sami game da hijira;

> Cikakken Musulmi shi ne wannan wanda 'yan uwa Musulmi suka kubuta daga kalaman harshensa da hannunsa. Muhajiruna su ne wadanda suka nesanta daga abin da Allah ya haramta. (Bukhari da Muslim daga Abdullahi bin Amrou Al -as)

Hijirar da Manzon Allah (SAW) ya yi daga Makka garin da aka haife shi ya koma Madina misali na ma'anar hijira da take nufin mutum ya tashi daga garinsu ko kasarsu ya koma wani gari ko wata kasa. Hijirar da Manzon Allah ya yi ta zo ne a lokacin da Kuraishawan Makka suke tsangwamar Musulmi ta yadda babu wani Bakuraishe da yake sha'awar shiga Musulunci. Haka kuma suka tilasta Manzon Allah (SAW) tare da mutanensa zama kan wani dutse da niyyar ware su da kuma hana musu abinci. Wannan ya sa Annabi Muhammadu (SAW) ya umarci

Musulmi da su bar Makka su koma Madina wurin ‘yan uwansu da suka karbi Musulunci.

Zuwan Nasara kasar Hausa ya haifar da abubuwa da dama ta yadda wadansu daga cikin mutane suna da ra’ayin a yi hijira a tafi Makka inda babu Nasara. A can Musulmi wadanda Hausawa ne za su yi addininsu yadda ya kamata ba tare da tsangwama ba. Wannan ta sa aka sami waka ta *Zuwan Annasara Kasar Hausa* wadda ake danganta ta da Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu kamar yadda aka rigaya aka ambata can da farko. Ga abin da Attahiru Ahmadu ya kawo a game da yin hijira yana cewa;

2.Muna roko ga Sarki mai sarauta,
Mu sami fita mu bar jama’ar Nasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

A gaba kuma ya kara bayani a kan nuna adawa da Nasara ta hanyar yin hijira ko kuma a kore Nasara ya bar kasar Hausa ya kawo. Irin wannan yakan faru a tsakanin masu mulki da wadanda ake mulka, ko kuma tsakanin masu hali da talakawa. A duk lokacin da tura ta kai bango sai su yi bore su kori duk wanda yake kan mulki ko shugabanci. Gargadi ga talakawa da kar su amince da kafirai. kamar yadda ya furta, idan Allah ya kaddara za su zauna to suna roko a bata makircin Nasara, idan kuwa bukatar hijira ta biya to suna addu’ar Allah ya kai su Makka inda babu Nasara kamar yadda ya fada kasa:

4.Idan Allahu ka nufi sai mu zamna,
Muna roko ka bata nufin Nasara.

5.Idan mun sami iko munka tashi,

Ka kai mu Madina nesa ga Annasara.

6.Idan Allahu ka nufi za mu tashi,
Mu ya da wurin ga sai jama'an Nasara.

7. Idan an so idan ba a so a tashi,
Zama sun ta da wansu maza Nasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

A cikin layukan waka na kasa, marubucin ya yi hasashen gurbata al'ummar Musulmi da Nasara za su yi wadanda ya bayyana a matsayin kafirai. haka ta sa ya yi kira da babbar murya da a kaurace musu a tashi a bar zama tare da su domin wannan ita ce mafitar halin da aka sami kai a ciki.

10.Idan ni dai ka tashi ba ni zamni,
Zama wallahi ba ni biyat Nasara.

11.Cikin biyu sai a zabi guda a dauka,
Walau tashi walau a bi Annasara.

12.Sarakai sun fito sun bar garinsu,
Bale moro da kanka ka zam Nasara.

16.Idan ka ce akwai wahala ga tashi,
Lahan duka na ga masu biyan Nasara.

17.Idan iko kakai kak ko ki tashi,
Ina iko shi kai ikon Nasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

Ya fito fili ya bayyana irin kiyayyarsa ga Nasara ta rashin son zama tare da shi cewa zai tashi ya ba shi wuri, amma cikin hikima sai ya ce, kafin yin hakan idan ya sami dama sai ya yi fada da shi a cikin gidansa kafin ya tafi hijira wannan bayani ta sa ya ce:

22.Ku bar jin masu cewa ba a tashi,
Ina halin zama ga Annasara.

23.Mu mai da gabanmu Makka mu zo Madina,
Madina da Makka dai ab ba Nasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

Ko ta wane hali Attahiru Ahmadu ya nuna ba zai bi Nasara ba, ya ki shi ya guje shi ya bijire masa ba kuma shi kadai ba, ya umarci duk wani Musulmi da ya yi haka. Wannan ta sa tun da ba za a bi Nasara ba, neman guzuri ya kama kowa domin yin hijira zuwa inda babu Nasara sai ya ce:

28. Bidag guzuri ga kowa wajibi na,
Musulmi kar mu yarda biyar Nasara.
(Wakar Zuwan Annasara Kasar Hausa ta Sarkin Musulmi Attahiru Ahmadu)

### 3.2.3 Shahada A Matsayin Hanyar Bijre wa Annasara

Kasar Hadejia kasa ce da Hausawa Musulmi suke da rinjaye, domin haka sun ki jinin Turawan mulkin mallaka da suke kafirai hai-hata hai-hata. Zuwan Turawan mulkin mallaka ya karfafa gwagwarmayar zuwan Mahadi a tsakanin Musulmi a daular Sakkwato da ta Borno. Yakin Burmi da na Satiru yana daga cikin abubuwan da batun zuwan Mahadi ya yi tasiri a cikinsu (Wakili 1985:137). Haka kuma, wani abu da ya yi kama da batun zuwan Mahadi shi ne maganar yin jihadi da manufar kare Musulunci da Musulmi daga barazanar kafirai. Mutuwa a irin wannan yanayi ita ake kira shahada (martydom). Irin wannan shi ya faru a garin Hadejia har aka yi wa yakin lakabi da *Yakin Shahadar Hadejia* aka kuma sami waka da aka ce wani mai suna Limam Muhammadu (Ana sa ran shi ne limamin garin Hadejia a wancan lokacin Birniwa (2006:2) ya yi dangane da yakin ya kuma ba ta suna *Shahada Zahira.* Rashin jituwa tsakanin mutanen Hadejia da Turawa mulkin mallaka ba abu ne da ya tsiru rana tsaka ba, da ma can tsakin da tsakuwa.

Haka abin ya ci gaba da kasancewa ana ta samin faruwar ‘yan kananan dauki-ba-dadi. Wannan yasa an yi yaki wanda shi ne karon battar da aka yi na bijire wa Turawan Mulkin Mallaka a kasar Hadejia. Kafin wannan lokaci ga abin da aka sami kwamandojin sarkin Hadejia aka ji sun fada

Kowa ya je gida ya shirya in ya so gobe duk mu kwana lahira.

Garin Hadejia shi ne gari na karshe a cikin daular Usumaniya da Turawa suka kama, garuruwa kamar Katsina da Kano da kuma Katagum cikin ruwan sanyi suka mika wuya, amma a Sakkwato an yi accakwama. Duk da haka babu wani gari da ya yi hasara kamar Hadejia sakamakon fada da Turawa (Wakili 1985).

Wakar *Shahada Zahira:Wakar Begen Shahadar Hadejia* ko begen yakin shahadar Hadejia (Hiskett 1975:144-147) and (249-251). Waka ce ta ta’aziya domin tunawa da shahidai a yakin da Hadejawa suka yi da Turawa mulkin mallaka a garin Hadejia a shekarar 1906.

A cikin wakar an sami fitowar kalmomi wadanda tamkar na mizani ne da suke nuna bijirewa ga Nasara misali *ba gudu*, da *ba kamu,* da *ba gudu sai faduwa*, da kuma *ba su tsoro ba gudu*, mutanen garin Hadejia sun yi imanin cewa, da su mika wuya ga Nasara gara su kwana lahira. Nasaba tsakanin mutanen Hadejia da Nasara tamkar ta Maigida da yaronsa ne, saboda idan aka yi la’akari da tursasawa da kuntatawa da aka sami, wannan ta sa aka tabbatar da haka. Ga Abin da aka samu

12.Ranar talata mun ga tashin duniya,
Rannan Muhammadu yai shahada zahira.

13.Yai jawabi ya cane baya gudu,
Shi ba shi mai kamu a darad duniya.

14.Rago ake kora a bi shi a kamansa,
Amma sadauki bai gudu sai faduwa.

15.Sarki Muhammadu yai jawabi ya cane,
Shi ba shi mai kamu ya ja shi ya tinkiya.
(Wakar Shahada Zahira ta Liman Muhammadu)

A cikin wakar, ya nuna cewa, Sarkin Hadejia ba zai kau daga kan akidarsa ba domin Nasara ba. Ya ce dabba kamar rago ko tunkiya ita ake ja ko a kora ta gudu, amma shi ya fi karfin Nasara ya ja shi ko ya kora kamar dabba. Ya kara da cewa, sadauki ba ya gudu sai dai a kafsa ya fadi.

18. Manyan gari suka taru kayin shawara,
Suka ce shahada za ta fi kamun karkiya.
(Wakar Shahada Zahira ta Liman Muhammadu)

A gaba kuma, an sami makarraban sarki sun yi mubaya'a a gare shi domin a bijre wa Nasara. Sun ce sun yarda su bi shi su yi shahada maimakon su amince da Nasara ya yi musu kamun tinkiya.

31.Kowa yana sallama cikin iyalinsa,
Sun sa gabansu a lahira ba duniya.

32.Jama'ar Hadejiya daidai suka hallara,
Kowa yana ce yau mun zama shahidai.

33.Shi bai kamar tsoro bare yai razana,
Ba san gudu dan Garba sarki jarumi.
(Wakar Shahada Zahira ta Liman Muhammadu)

Ya kara da cewa, jama'ar gari kowa ya yarda ya yi shahada maimakon mika wuya ga Nasara. Abin da har kullum Shugaba yake so ya sami daga wajen magoyansa

ko mai kudi da talakawa ko kuma ma sarki da talakawa. Wannan ta sa jama'a kowa ya yi sallama da iyalinsa domin sun sani idan sun tafi bai zama lalle su dawo ba. Haka ta sa marubucin wakar ya kawo baitoci na sama.

68.Sadaukan Muhammadu ba su tsoro ba gudu,
Sun da ka ce kofar gida sai faduwa.

70.Na raba gado na hakika kun jiya,
Domin na san mutuwar shahada zahira.

73. Sarki Muhammadu ba shi tsoro ba gudu,
Allah, Ma'aiki su yake tsoro shiya.
(Wakar Shahada Zahira ta Liman Muhammadu)

A mafiya yawan lokuta sakamakon bijirewa mika wuya, amma a garin Hadejia a wancan lokacin abin ba haka ya kasance ba. Sakamakon bijrewar da suka yi shi ne mutuwar shahada. Wannan ya nuna cewa an nuna wa Nasara iyakar bijirewa ke nan. Kamar yadda suka faru a garuruwa da yawa, a duk lokacin da aka ki biyar Nasara sai yaki tun da ya san yana da mugayen makamai domin haka sai a saki a mika wuya. Amma abin ba haka ya kasance ba ga Nasara a garin Hadejia a shekarar 1906. An yi ciri da gumurzu da kuma accakwama.

**3.3 Jumhuriya Ta Farko**

Hassan (2010:99-100) ya ce, a Jumhuriya ta farko wato kafin samin 'yancin kai zuwa 1966 lokacin da aka yi juyin mulki na farko, siyasun da ake da su na yankuna ne. a tsohon yankin Arewa akwai manyan siyasu guda biyu wato NPC da NEPU wacce ta zama babbar siyasar adawa a Arewa. NPC ta sami rinjaye ta amfani da jami'an gwamnati NA da Sarakuna, ita kuma takwararta ta NEPU ta sami goyon bayan talakawa da matasa da masu aikin gwamnati da kananan

kabilu. A takaice ana iya cewa tsakanin NPC da NEPU kamar dangantaka ce ta tsakanin mai mulki da wanda ake mulka.

Tun lokacin da kasar nan ta sami ‘yanci a shekarar 1960, siyasa ta zauna da gindinta. Jama’iyyar NPC ce ta fara kafa gwamnatin tarayya, a lokacin jihohi uku ne rak ake da su a Nijeriya, wato jahar Arewa da jahar gabas da jihar yamma. Jama’iyyar NPC ta kafa gwamnati ta yin kawance da jama’iyyar NCNC. Wannan gwamnati ta kai har shekarar 1966 lokacin da sojoji suka yi juyin mulki.

Siyasa wata hanya ce ta gudanar da zababbiyar gwamnati ta hanyar DimokuraDiyya a karkashin tsarin mulkin kasa, inda za a zabi shugabanni masu tafiyar da ita a karkashin kafaffun jama’iyyur. Ta wata fuskar kuma, siyasa tana iya ba da ma’anar kwArewa wajen iya tafiyar da jama’a da jure wa duk wata matsala tasu (Sa’id 2002:172).

Tun daga Jumhuriya ta farko bayan samin ‘yanci, mawaka na baka da masu rubutawa suke baje kolinsu a fagen sana’arsu ta waka. Masu zuga da yabon jama’iyyun da shugabanni sun yi iyakar yin su; masu zuga da zagi a bangaren hamayya ma sun yi nasu. A sakamakon haka ne aka sami wakokin siyasa a Jumhuriya ta farko masu dauke da kalamai na mizani da ake ganin na nuna bijirewa ne ga masu mulki da mabiya har ma da lokacin kamfe da sauransu da yawa.

A nan za a dubi rawar da marubuta wakoki (sha’irai) ke bayarwa wajen wayar da kan jama’a ga shiga harkokin siyasa da kuma jan hankalin jama’iyya ko gwamnati

da ta yi ayyuka kyawawa, tare kuma da yi mata nuni da ta daina aikata ko zartar da wasu abubuwa da jama’a ba sa so. Yin watsi da abin da jama’a ke so, da rungumar son zuciya suke saka jama’a musamman marubuta, masu yi wa jama’iyya farfaganda su fito fili su bayyana rashin jin dadinsu, da na jama’a, tare da bayyana turjiya ko bijirewa idan shugaba ko kuma jama’iyya ba su gyara ba (Yakawada 2013:360).

A dangane da haka, ga abin da hannu ya kai kansu a cikin wakokin Jumhuriya ta farko.

### 3.3.1 Kamfe

Barnhart (1977: 288); Na ganin kamfen a matsayin wani sha’ani na kiran taron jama’a. Shi kuma (Hawkins 1981: 56) cewa ya yi kamfen wani gangamin jama’a ne don bayyana manufofin jam’iyya, domin neman goyon baya. Daga bayanan wadannan masana, za a iya cewa kamfen na nufin gabatar da wata manufa a cikin sigar magana, zuwa ga taron jama’a, domin neman goyon baya.

Kamfen ya rabu kashi-kashi, ciki akwai kamfen na dandali da kamfen na hukuma da kuma kamfen na wakoki. Kamfen na wakoki bisa tsarin wannan bincike kusan shi ne ya fi saura jan hankali da ra’ayi, kuma shi ne wanda hankali zai karkata a kansa, domin bukatar binciken.

#### 3.3.1.1 Kamfe na Wakoki

Ba wani hoto da ya fi waka nuna badakalar da ta faru a Arewacin Nijeriya da kuma wayar da kan jama’a. Tun kafin samiwar jaridun Larduna na Hausa, jigon

siyasa ya sami gindin zama a cikin wakokin sarauta, kasancewa waka wani zance na hikima da fasaha wanda ake tsarawa domin isar da wani sako zuwa ga jama'a Adamu (2003:53).

Jam'iyyun NEPU da NPC dukansu sun yi amfani da wakoki domin yin kamfen, wanda a cikinsu ne suka bayyana manufofinsu da yin suka, da kawo hanyoyin gyara ko yin zambo har ma da zagi ga abokan hamayya da nufin bijire wa akidar juna a tsakaninsu.

Ganin jam'iyyar NEPU tana sukar irin mulkin da ake aiwatarwa a wancan lokacin saboda ita ce jam'iyyar adawa kuma ta talakawa, sai aka zargi 'yan jam'iyyar da cewa majusawa ne wato masu bautar wuta. Duk da cewa mafiya yawan 'yan NEPU Musulmi ne, wannan ba ta hana a danganta su da wannan kalma ba. A takaice duka wanda yake a wannan hali to kamar ya fita daga Musulunci ne ya yi ridda. Wannan ta sa sha'irin ya ce:

19.Yau ba masoyin NEPU sai ko jahili,
Sai ko majusai kin Sardauna.

22.Dan NEPU shi da majusu daidai kafiri,
Matsa shi kar ka raga masa Sardauna.
(Wakar NPC ta Muhammadu Gidado: Wakar Yabon Sardauna)

Bisa tsari duk mutumin da aka ji ya ce wayyo yana cikin damuwa kuma yana bukatar tanyo, haka jam'iyyar NPC ta soki 'yan jam'iyyar NEPU da yi. Wannan ta sa aka ji wani sha'iri yana cewa:

37.Fa ya kahharu kaddara za su koka,
Su ce wayyo! su nemi bidar salama.
(Wakar Muhammadu Bello Gidadawa ta Wakar Siyasa Zamanin Salama NPC)

Duk wani abu da za a yi ko a fada da zai dallashe farin jini ko tagomashin jam'iya ana iya fadarsa a lokacin kamfen ko lacca. Fitowar ire-iren wadancan kalamai ba zai zama da mamaki ba domin jam'iyyar adawa ce suna ganin an danne su. Ganin irin suka da jam'iyyar NEPU take yi wa NPC da shugabanta ya sa wani sha'iri yake cewa

17.'Yan AG, NEPU ku tabbata,
Allah ku na zai kunyata,
Jikan Usmanu ku tabbata,
Duk Nauzan rijin tashi ta,
Allah ka taimaki Bubakar sarkinmu shi da Firimiya.
(Wakar Mai-Gwandu Sha'iri ta NPC:Wakar Yabon Sardauna da Sarkin Musulmi)

Masu iya magana suna cewa, idan mutum ya ce bai san asalinsa ba, ko kuma bai iya rashin kunya ba to ya shiga siyasa. Duk wani cin mutunci da mutum bai taba tsammani ba, idan yana siyasa zai ci karo da shi ko wani na kusa da shi. Rayuwar mutum ko kusa ba ta yi kama da ta dabba ba in ana Magana da hankali, amma sai ga shi jam'iyyar NEPU tana sukar jam'iyyar NPC da cewa halin dabbobi yana daga halayyar 'yan NPC. Kowa ya san yadda dabbobi suke rayuwa babu sutura ba rufin asiri da yana bin uwa uba yana bin 'ya da sauransu. Dalilin kawo wannan bayani ba zai rasa nasaba da abin da aka ji Akilu Aliyu yana fada cewa:

13.Rashin sutura da rashin kunya,
Irin ta awaki kan hanya,
Da cinye amanar mai kunya,
Saboda kawai ba ya shanya.
Yana daga halin NPC.

19. Ku tabbata ni ba na sonta,
Da rai da jikina na ki ta,
Habibu da Garba kuna sonta?
Ina! Ba mu so ta ba, mun ki ta,

Saboda muguntar NPC

25.Ku ji ni ina fadakarshe ku,
Ku ki ta kwarai a zukatanku,
Nufinta ta kwace abincinku,
Da ta cinye shi ta yashe ku,
Saboda butulcin NPC
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Baki uku Sharrin NPC)

Taken jam'iyyar NPC Salama, amma a nan an zarge su da cewa ba sa yin salama wato aminci a maimakon haka sai suke yin Zalama wato zalunci. Irin wannan duk yana cikin gwagwarmayar neman madafun iko. Ga Abin da Sa'adu ya ce:

50.Su ke kasa 'SA' a mazaunin 'ZA'
Sun furta Salama ba ahuri.
(Wakar NEPU ta Sa'adu Zungur ta Jihadin Neman Sawaba.)

"Riga ita take sayar da kanta" in ji masu iya magana. NEPU ce take sukar NPC a kokarinta na samin goyon bayan talakawa. Magoya bayan NEPU dayawa masu karamin karfi ne da suke karkashin mulkin NPC kuma suke ganin ba a musu adalci. Irin wannan kama-karya da suke zargi shi ne suka bayyana za su kawo karshensa. Haka kuma danganta NPC da ake yi da Mujaddadi Shehu Usmanu Danfodiyo ba zai kai su ko ina ba. Ga abin da suka fada:

12.Ita jama'iyyan nan NEPU ta dau aniya,
Sai ta ga bayan zaluman ga masha giya.

19 .Ga NEPU dutse ba a far maka nan da nan,
In munka far wa zalumi zai sha wuya.

26.Ku jakunan shaidan ba za ku ga Shehu ba,
Bar sanya Shehu cikin batunku na jam'iyya.
(Wakar NEPU ta Gambo Hawaja: 'Yan Sawaba)

### 3.3.2 Shari'ar Zabe

A karkashin tsarin Dimukuradiyya mutane da Hukumomi da kungiyoyi sukan tafi kotu domin samin mafita a kan wata matsala cikin har da karar zabe. Jama'iyyun siyasa da 'yan takara har da sauran talakawa, kowa kotu yake kai wa kara domin samin masalaha. Wannan yana faruwa ne, sakamakon kasancewar shari'a ce take daidaita al'amuran rayuwa (Ashiru 2009:96). Haka Abin ya kasace a Jumhuriya ta daya da sauran Jamhuriyoyi, inda jam'iyyu suka yi ta shigar da kara a duk lokacin da wata matsala ta auku musamman a kan harkar kamfe da zabe da sauransu, haka wannan abu yake faruwa har ya zuwa yau.

Ga abin da ya kasance tsakanin Jam'iyyar NPC da ta NEPU a game da shari'ar zabe.

Jam'iyyar NPC ce ta yi batanci ga NEPU domin nuna rashin amincewa da manufofinta, hakan ta sa suka kira su da kafirai. A sakamakon zaben da aka yi, jam'iyyar NEPU ta shigar da kara a kotun Ingila. Wannan magana da NPC ta yi magana ce da take da nauyi, domin kusan dukkan mabiya NEPU Musulmi ne kamar yadda 'yan NPC suke. Muhammadu Gidado sai ya ce;

> 24.Sun je Ingila sun yi kara kafirai,
> Aka ce su zo su ka bincika Sardauna.
> (Wakar NPC ta Muhammadu Gidado: Wakar Yabon Sardauna)

Malam Akilu Aliyu ya shirya wannan waka ta "Inkwariya" a shekarar 1958, a garin Kano sakamakon wani hukunci da aka yanke, wanda NEPU ta sami nasara, a sanadin haka wannan waka tana dauke da bayanin yadda hukuncin ya kasance,

wanda akwai bijirewa zuwa ga NPC, kamar yadda baitocin da suke rubuce kasa suka nuna an danganta ‘yan jam’iyyar da kare, an kuma bayyana wasu daga cikin ‘yan NPC da cewa suna huzunu watau bacin rayi. Ga Abin da ya fada;

7.Da talakawwa har masu gari,
Da mutum ya zarci dubu da dari,
Mun duru a kotu muna nazari,
Sai ga NPC ta yi bari,
Don ta rasa hujja ko ta dari.

8.Nwaja Lauya mazan sha’ani,
Yai aikin nasa irin na gwani,
Ya darji hukuma ba mahani,
Sai ga fatala ta hau rawani,
NPC ta rasa alkadari.

9.An nemi dalili ba su da shi,
Cutar mu suke su ci har da kashi,
Tausai da adala ba su da shi,
Su ci namu, gama su ba su da shi,
Sai girman kai da yawan fahari.

11.Sai ga wasu an kama hannu,
Fuskarsu kamar sun kurbi kunu,
Rayinsu a bace suna huznu,
Wannan shi ne juyin zamanu,
Sai ga talakawa mun yi ‘firi’
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Inkwariya)

### 3.2.3 Zagi

Bargery (1934:1155) Ya bayyana zagi da cewa: *abaiban baki ko jafa’i ko alfasha, ko mugun baki ne*. Zagi kuma na iya zama zambo.

Hawkins (1981:2), cewa ya yi zagi na iya kasancewa *kai farmaki da miyagun kalmomi.*

Fada wa mutum bakar magana ko bacin iyayensa (Kamusun Hausa 2006:487). Kalmar zagi ba ta bukatar dogon sharhi a game da kunshiyarta. Abu ne da yake

faruwa a rayuwar yau da kullum, ita kalmar zagi ta kunshi ambatar sunan mahaifin mutum ko mahaifiya ko kuma danganta shi da rashin mahaifi, misali shege ko dan banza da sauran miyagun maganganu da suka yi kama da haka. An yi amfani da zagi wajen nuna rashin yarda ko amincewa da Nasara lokacin da suka zo kasar nan musamman a cikin rubutattun wakoki na Hausa musamman na siyasa

Zalunci da rashin adalci suna daga cikin abubuwan da jam'iyyun siyasa suke famar zargin juna a kansu. A yayin da siyasar adawa ta ke korafin, ana musu zalunci da rashin adalci, ita kuwa jam'iyya mai mulki sai take kokarin kare manufofinta da maradunta. a cikin wannan baiti na kasa an sami cewa;

4.Da mu da ku mutan NPC,
A tsine wanda ke zalunci,
Har duk da wanda ke cin hanci,
Da masu taimakon makirci,
DON TSORON TSIYA.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: 'Yar Fulani)

A cikin wannan baiti na wakar "Tauraron Zamani" Akilu ya ce ba su da shakkar uban kowa. Gaskiya ce ko a ina za su fade ta, maganar tsoro da yi musu burga duk ta wuce, haka ta sa ya ce:

4.Mai gaskiya fadi ko a gaban uban kowa,
Da za a ki ta a dauka san da ba kowa,
Yau babu sauran abin tsoro da burgewa,
Kowak kira mu mu amsa ko gaban kowa,
Wani ba ya fi ga waninsa sai da imani.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Tauraron Zamani)

Gambo Hawaja ma ba a bar shi a baya ba, a nan ya kawo baitin da yake dauke da kalmar zagi a matsayin nuna ta sa bijirewa ga siyasar abokan adawarsu. Ya kawo

zagi a kan wani dan jam'iyyar NPC da ya bayyana a matsayin kafiri wato mutumin da ba ya yin sallah kamar yadda ya fada a cikin baiti na kasa.

> 79.Zan matsa gyare in ji kukan kafiri,
> Jama'a idan kun yarda kwa sha dariya.
> (Wakar NEPU ta Gambo Hawaja: 'Yan Sawaba)

**3.2.4 Kirari**

A kullum kirari yana zuwa ne da sigar siffanta ko kamanta abin da ake yi wa kirarin da wani abu ko mutum mai shahararren karfi, ko alfarma, ko daraja, ko dai wani hali na musamman da ya fifita. Kirari tsararriyar magana ce, 'yar doguwa, ta hikima, da akan shirya. Musamman, don kambama mutum ko wani abu (Umar 1987:24).

A takaice ana iya cewa, kirari zababbun kalmomi ne na hikima da fasaha da ake yi wa mutum ko mutum ya yi wa kansa ko gari ko kuma wani abu domin kambamawa ko ciccibawa na nufin siffanta shi da wani hali ko nagarta mai kyau.

Kirari irin na kai shi ne Akilu Aliyu ya yi amfani da shi domin bayyana kiyayyarsa ga jam'iyyar NPC ta hanyar nuna cewa masu sharri ne. Saboda haka ya nuna babu gudu ba ja da baya ya ayyana cewa shi ya fada.

> 20.Sharrinsu dubu, daya tak na fada,
> Kan sun ce wane ne ya fada,
> Akilu madinki ne ya fada,
> Ligal Adibaiza Borno hada,
> Baban Muhammadu a Maiduguri.
> (Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Inkwariya)

Akilu ya sake amfani da kirarin kai wajen bayyana yardarsa da jam'iyyar NEPU a daya hannu yana nuna kyamarsa ga jam'iyyar NPC. Ya ce ko ana daure shi ana yankan jikinsa bai fasa NEPU ba kuma ba zai yi NPC ba, ga dai Abin da ya ce;

28. Fa ba zan kinaya ga sunana ba don na fake,
Ni ne Akilu madinki, Maiduguri nake,
Da dare da rana ina yin NEPU, babu sake,
Dauri da duka da yanka kan gabarsu nake,
Allah Ta'ala ya sa mu cika da imani.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Tauraron Zamani)

Masu iya magana suna cewa 'duk wanda ya kuna ba ya tsoron tafasa' Abin da ya faru ke nan a nan, Akilu ya riga ya yanke kauna da NPC kuma ya bayyana dukkan adawarsa a kansu ya nuna bai yarda da ita ba, hakan ta sa ya bayyana kansa da inda yake ba tare da shayin duk Abin da zai je ya koma ba.

Shi ja da baya ba tsoro ba,
Bakinmu ya riga ya saba,
P. O. Box Sabin uku lamba
Malam Akilu Yarwa Sawaba,
BABAN MARIYA.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: ;Yar Fulani)

### 3.3.5 Addu'a

Kamar yadda aka rigaya aka bayyana ma'anar addu'a tun da farko, addu'a tana nufin hanyar fuskantar Ubangiji Allah (S.W.T.) da kiran sa da ganawa da shi da kaskantar da kai da nuna kasawar bawa zuwa ga muhaliccinsa Allah, domin kwadayin samin taimakonsa na alheri duniya da lahira (Ainu 2007:52).

A takaice addu'a na nufin roko wani abu daga Allah shi kadai ta amfani da wadansu lafuza na musamman. Mawakan Siyasa suna amfani da wannan salo na addu'a musamman a wajen nuna rashin kaunar wata jam'iyya watakila saboda

rashin adalcin shugabanninta wadanda su ke da madafun iko a lokacin. Wakokin NEPU sun yi fice wajen yin irin wannan addu'a, wannan ba zai rasa nasaba da irin tarin cin zarafi da cin mutunci da suke zargin ana nuna musu ba.

38. Mu ce Allah wadarai nasu,
Mu ce Allah dakushe bakinsu,
Mu ce Allah juye kwakwalwarsu,
Mu ce Allah fallashi karyarsu,
Mu ce Allah tsine NPC
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Baki uku Sharrin NPC)

Addu'a aka yi a nan, a kan jam'iyyar adawa ta NPC wadanda aka ce suna ci da gumin mutane. mawakin ya yi addu'ar Allah ya mayar da su baya.

33.Allah tsine mayaudarinmu,
Wanda sun ci da taimakonmu,
Don su je gaba can su ki mu,
Rabbana maishe su baya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

Sa'adu a cikin ta sa wakar "Jihadin Neman Sawaba" ya yi addu'ar Allah ya fitar da yankin Arewa daga cikin hadari. Hadarin da Sa'adu yake nufi a nan bai wuce mulkin Jumhuriya ba da ya yi hani da kada a goyi baya ya sami wurin zama a yankin Arewacin Nijeriya.

137.Ya rabbi ka fid da Arewa cikin,
Mulkin fitina da kisan garari.

138.Ya Ta'ala ya sarki witiri,
Ka fitar da Arewa cikin hadari.
(Wakar NEPU ta Sa'adu Zungur: Jihadin Neman Sawaba.)

### 3.4 Jumhuriya ta Biyu

A ranar 21-09-1978 aka daga takunkumin yin siyasa a Njeriya. Daga nan sai jam'iyyun siyasa suka fara fitowa. Daga cikin jama'iyyun da suka fara fitowa akwai UPN ta Obafemi Awolowo da NPP wacce daga baya ta koma GNPP ta Waziri Ibrahim sai kuma jama'iyyar NPN da kuma PRP ta Aminu Kano da kuma wadansu kananan Jam'iyyun. Duka-duka an sami jama'iyyun siyasa sama da hamsin (Birniwa 1987:252). Daga cikin wadannan, jam'iyyun siyasa guda biyar ne kawai suka sami rijista domin su ne suka cika sharuddan da Hukumar zabe ta kasa ta bayar. Jam'iyyun su ne UPN da NPP da GNPP da NPN da kuma PRP.

Ta la'akari da wadannan jama'iyyu mutum yana iya fahimtar inda aka kwana, domin jama'iyyun suna da nasaba da zamanin Jumhuriya ta farko. Jam'iyyar UPN tana da alaka da AG haka Jam'iyyar NPP tana da nasaba da NCNC. Ita kuma NPN da NPC yayin da PRP take da NEPU. Jam'iyyar GNPP ce kawai ba za a iya alakanta da wata jam'iyya ba a Jumhuriya ta farko ba (Birniwa 1987:253).

Sa'id (2002:176-180) ya bayyana cewa jam'iyyar NPN a Jumhuriya ta biyu aka kafa ta, ita kuma ta kafa gwamnati a wannan karon. Masu hamayya da ita sun nuna cewa ita gyauron NPC ce a Jumhuriya ta farko, domin kusan yanayinsu daya ne, dangane da manufofinta da akidarta. ita kuma PRP jam'iyya ce da aka kafa a Jumhuriya ta biyu. Manufarta ita ce kwato 'yancin talakawa da kuma kawar da zalunci, ta kuma kafa adalci. Shugabanta shi ne Malam Aminu Kano, abin kauna mai kwato hakkin talakawa daga masu mulkin kama-karya, ya warware dukkan kangi.

Wannan babi zai mayar da hankali ne a kan jama'iyyu biyu wato NPN da PRP saboda su ne aka fi yi wa wakoki da Hausa da yawa ganin suna yankin Arewa inda mafi rinjayen mutanensa kabilar Hausa da Fulani ne da suke amfani da harshen a matsayin hanyar sadarwa.

Jam'iyyun NPN da PRP su ne manyan siyasu a Arewa da suke adawa da juna, wannan ta sa marubuta wakokinsu suka kaifafa takubbansu a kokarinsu na sukar juna da nuna kin yarda da juna ta hanyar fadakarwa cikin wakoki. Sun yi wakoki da dama, a ciki suka bayyana hanyoyin daban daban domin hakar su ta cim ma ruwa kamar yadda za a gani biye;

**3.4.1 Kamfe**

Barnhart (1977: 288); Na ganin kamfen a matsayin wani sha'ani na kiran taron jama'a. Shi kuma Hawkins (1981: 56) cewa ya yi kamfen wani gangamin jama'a ne don bayyana manufofin jam'iyya, domin neman goyon baya. Daga bayanan wadannan masana, za a iya cewa kamfen na nufin gabatar da wata manufa a cikin sigar magana, zuwa ga taron jama'a, domin neman goyon baya.

Kamfen ya rabu kashi-kashi, ciki akwai kamfen na dandali da kamfen na hukuma da kuma kamfen na wakoki. Kamfen na wakoki bisa tsarin wannan bincike kusan shi ne ya fi saura jan hankali da ra'ayi, kuma shi ne wanda hankali zai karkata a kansa domin bukatar binciken.

### 3.4.1.1 Kamfe na Wakoki

Ba wani hoto da ya fi waka nuna badakalar da ta faru a Arewacin Nijeriya da kuma wayar da kan jama'a. Tun kafin samiwar jaridun Larduna na Hausa, jigon siyasa ya sami gindin zama a cikin wakokin sarauta, kasancewa waka wani zance na hikima da fasaha wanda ake tsarawa domin isar da wani sako zuwa ga jama'a Adamu (2003:53).

A Jumhuriya ta biyu, an sami jam'iyyu suna bayyana bijire wa juna ta sigar kamfe. An sami jam'iyyu irin su NPN da kuma PRP ganin cewa, su ne jam'iyyun da aka yi waka da harshen Hausa da yawa. Irin wannan manufa ce jam'iyyar NPN take kokarin bayyana wa mutane za ta aiwatar. A ciki, ta nuna za ta kawar da jahilci wanda shi ne sanadin dakile rayuwa, kamar dai yadda aka sami  Mu'azu Hadeja ya fada a cikin wakarsa ta 'Mu Yaki Jahilci. Bayan nan NPN ta siffanta sauran jam'iyyu da fakara da balbela wadanda tsuntsaye ne da ba a cika amfani da su ba, domin ba na kirki ba ne. A takaice sauran jam'iyyu ba na kirki ba ne, ita kadai ce ta kirki. Sai marubucin wakar ya ce;

26.Fakara mun san ki da ketarki,
Mai gina duk na leken ki,
Ki sani mu ba mu bukatarki,
Domin shuka ce kotonki,
Hairi muka shuka ba shakki,
Ya fito mu ci domin 'Yanfi'yan.

27.Balbela mun san cutarki,
Dogon bakinki ya sare ki,
Sun gan ki fara sun zabe ki,
Mun tona cikinki da namanki,
Kowa ya ce bai kaunarki,
Daga nan aka taru ga 'Yanfi'yan.

(Wakar NPN ta Malami Attahiru Yabo:A zabi 'Yanfi'yan)

NPN ta nuna rashin yardarta da sauran jam'iyyu saboda ta ce makaryata ne, wato ba sa cika alkawuran da suke yi wa mutane lokacin kamfe, ta ayyana su da cewa su ne suke cutar Nijeriya. Ta daya hannu kuma ta bayyana cewa ba sa son zumunci, kuma don haka suke gudu suna barin gidajensu har da garuruwansu. Guduwa da barin gari ba zai rasa nasaba da korafin 'yan jam'iyyar NEPU ba, da suka yi koken an gallaza musu. Wannan ta sa suke barin garuruwansu suke komawa wadansu garuruwa kamar dai yadda Lawan Danbazau ya bayyana a cikin littafinsa "Tarihin gwagwarmayar NEPU da PRP 1950-1981."

30.Wasu jam'iyyun Nijeriya,
Sun furta karairai sun shirya,
Da nufin cutar Nijeriya,
Sai zagin juna da hamayya,
Domin haka duk mai son shiriya,
Ya tsaya ya yi zaben 'Yanfi'yan.

31.Wasu sun ki gidansu da danginsu,
Sun manta gida don haukar su,
Sun dau daji don haukar su,
Sun yarda da duk mai zambar su,
Su sani haka duk bai fisshe su,
Wallahi ku koma 'Yanfi'yan.

(Wakar NPN ta Malami Attahiru Yabo:A Zabi 'Yanfi'yan)

A nan kuma Muhammadu Suleiman Dundaye ne ya yi wawar kora na bijire wa PRP, ya kira ta da sunaye marasa amfani ya kuma nuna cewa duk 'yan jam'iyyar sun rude domin sun gigice ga kuma rashin rike amana a karshe sai ya ce 'yan PRP sun zama ganyen taba. Kamar yadda mutane suke fada, duk wannda ya sayi taba (sigari) ya yi hasarar kudinsa domin babu amfani tattare da ita sai ma ta kawo wa mutum sanadin rashin lafiya. A wannan lokaci idan aka duba jikin kwalin sigari

za a ga irin gargadin da aka rubuta (cigerrete smoking is dangerous to health) domin jan hankalin mutane kada su saya. Wannan ta sa ake mata kirari da Hausa ana cewa, ‘Sigari shan ki banza barinki banza. Domin haka sai sha’irin ya ce;

16. Ku guje wa ‘yan PRP,
Jama’iyyar ta cika haufi,
Da yawan cewa su sun fi,
Kowa sun maisai wofi,
Bayan kuma sun gigita.

24.PRP ba ta amana,
Ba alheri mun auna,
Kuma ba kwazo mun raina,
Sharri karya da hiyana,
Ta firgita duk ‘ya’yanta.

35.PRP ganyen taba,
Kwash sha ba don dadi ba,
Zai sha ba don dadi ba,
Don ba aikin lada ba,
Ai gara ka bar ta ka huta.

(Wakar NPN ta Muhammad Sulaiman Dundaye: PRP ta Zama Kaya)

Yana daga cikin sigogin kamfe a kushe wani abu na jam’iyya wada aka san ta da shi fitacce. A nan ganin cewa alamar tutar jam’iyyar PRP ja ce, wannan ta sa sha’iran jam’iyyar NPN suka kwatanta ta da gobara, wadda babu wanda yake son gobara. Duk dai a kokarin bayyana manufarsu ta kin amincewa da PRP sai ‘yan NPN suka kira ta gammon sabara. Gammon sabara amfanin lokaci guda yake yi da shi, daga nan sai a jefar. Ga baitukan da suka yi wannan bayani:

14.Yau dai jama’ar Nijeriya,
Ba sa kaunar mai fariya,
Bisalla da Dinka da fariya,
Allahu ya sa suka dulmiya,
Balle mai fatan gobara.

31.Ya ku jama’ar Nijeriya,

NPN ce mai gaskiya,
Da ta zabi a zauna lafiya,
Ki gujewa masu ashariya,
'Yan santsi gammon sabara.
(Wakar NPN ta Muhammad Sulaiman Dundaye:'Yan santsi Gammon Sabara)

Masu iya magana suna cewa 'daidai din wani karkataccen wani' wannan shi ne Abin da ya faru ga Muhammad Sulaiman Dundaye. Wannan ta sa ya yi wa NPN waka ya kuma yi wa PRP kamar yadda Biniwa (1987:338-339) ya bayyan). Mawakin ya nuna adawarsu da juna. A nan wakar Dundaye ce amma ta PRP inda yake bayyana bijirewar PRP a kan NPN.

A cikin baitukan da suke biye, Muhammadu Dundaye ya nuna rashin yardar jam'iyyar PRP a kan sauran jam'iyyu. Ya nuna cewa rashin amincewa da jam'iyyar GNPP, inda ya bayyana cewa su ba sa son kwakwa domin maciyinta wahalallu ne, haka kuma ya ce, alamar UPN haske ne wanda wuta ce da take iya kawo gobara babu kuwa mai son gobara. Alamar NPN kuwa da yake daki da masara ne sai ya ce, dakin ya zama na kurkuku domin haka ba da shi ba shi ne dalilinsa na fadar;

17.Farko zan bayanin kwakwa,
Don ban san ku kai mu ga kuka,
In ko har ka yarda ka auka,
Sai ka sha wuya ka ci kwakwa,
Na bidi taimako gun Allah.

18.Can na ga gobara ta kama,
Nufinta ta kona duk al'umma,
'Yan Nijeriya na kyama,
UPN bala'i ce ma,
Mun gudu taimaka mana Allah.

19.Dakin kurkuku ba kirki,
Ba na son zuwa ko taki,

Dan masara da sharru da maki,
Sai gemu awa na mafarki,
Tun bayar uwarsa ya falla.
(Wakar PRP ta Muhammad Suliman Dundaye: PRP Gumbar Dutse)

Daga cikin manufofin da aka kafa jam'iyyar PRP a kansu sun hada da kawar da zalunci da rashin adalcin shugabanni da cuta da sauransu. A nan PRP ta nuna rashin yardarta a kan duk wani mulkin danniya da rashin adalci daga bangaren NPN musamman da yake su suka kafa gwamnati.

24.Kiranmu a nan ya san makabuli,
Fi'arfi muna da dalili,
Za mu tsaya ta kowane hali,
Sai mun ka da mai cin zali,
Mai danne hakkin talakawa.

31.Su aikinsu ne su yi cuta,
Ko taro na kulla mugunta,
Duk talakan da ya arzuta,
Hanyoyinsa sa lalata,
Bai da zaman wajen hutawa.
(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama'iyyarmu ce Fi'arfi)

Dadin dadawa PRP ta yunkuro da rashin yarda da wasoso da ake yi da kudin talakawa Abin da ya sa Magaji Sudawa ya kira 'yan PRP da su bijire wa NPN kuma su kyamace ta. Wannan ta sa ya ce;

34.A harkoki sukan yi shigege,
Su halinsu ne su yi kage,
A sami mutum kwatsam nan a buge,
Su aka tankade aka rege,
Kan satar kudin talakawa.

38.To jama'a a nan ku fahimta,
Jama'iyyar da za ta yi cuta,
Har jama'a su kai kyamar ta,
Yau mu ma ku zo mu guje ta,
Mu zabo jama'iyyar talakawa.
(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama'iyyarmu ce Fi'arfi)

Daga cikin hanyoyin kamfe da PRP ta yi amfani da su, sun hada da wayar wa talakawa kawunan a kan manufofin jam'iyya. Ta daya hannu suna nuna musu cewa wannan jam'iyya ita ce za ta yi maganin duk wata zamba kamar yadda ake samin kalubale daga jam'iyya mai mulki. Ga Abin da aka sami Magaji Sudawa yana fada;

40.Mai mana jagaban jama'iyya,
Shi ra'ayinsu babu kiyayya,
To jama'a mu dau soyayya,
Shehu Aminu ba jayayya,

47.Shi ne shugaba gun kowa.
Mutan birni gami da na kauye,
An yi dare gari ya waye,
Ba sauran macutan boye,
Mai cutar mu yau ko waye,
Doka ta hana shi fakewa.
(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama'iyyarmu ce Fi'arfi)

Garba Gashuwa ya kara jaddada manufar jam'iyyar PRP a nan, kamar yadda ya fada ya nuna da NPC da NPN duk daya ne. wannn ta sa sha'irin ya bayyana cewa da NPN da NPC duka daya ne. Duk Abin da NPC ta yi shi ne NPN take maimaitawa, masu iya magana suna cewa, 'BArewa ba ta gudu, danta ya yi rarrafe.' wannan ta sa ya ce;

2.Ya jama'a 'yan uwa ku tashi mu bar barci,
Mu kau da bakin danne-danne mulkin fisanci,
Ita 'yanfi'yan nufinta muddin kan ta ci,
Ta mai da haraji da jangalin nan mai kunci,
Allah ka hane ta dai ba za ta ci zabe ba.

13.Ina so na fada wa 'yan uwana magidanta,
Samari mata mazanku du sai ku fahimta,
Ku bar 'yanfi'yan ku daina ma jin maganarta,
Saboda shirin nata babu gyara sai cuta,

Wannan abu ka sani ba za na fada ma ba.

14.Mu kam daga yanzu ba a kawo mana burga,
A keta mutunci a je a yaga mana riga,
A yau ba duka idan ka zage mu mu zaga,
Wani ma yai rawa bare dan mai ganga,
Mugun cutar da kai ba za ka dada min ba.
(Wakar Garba Gashuwa ta PRP: Danhakin da ka Raina)

**3.4.2 Shugabanin Mulkin Siyasa**

> "Shugaba shi ne wanda ya san hanya, ya kuma bi hanya, ya kuma nuna wa mutane hanya."
>
> John C. Maxwell

An bayyana shugabanci da cewa "wani abu ne da ya shafi mu'amala ta yau da kullum a inda mutum zai nemi taimako da goyon bayan sauran mutane, domin sauke nauyin da yake kansa. Misali, wasu suna da fahimtar cewa, shugaba mutum ne da yake da mabiya ko kuma mutumin da yake  yi wa mutane jagora ko taimako. A cikin duniya kowace al'umma tana da irin nata tsarin shugabanci, shugabanci ya iya zama jagorancin al'umma, ta fuskar addini ko  siyasa ko kuma jagoranci na kamfe, domin yakin neman zabe.

A lokacin da shugabanni suke gudanar da mulki, ana sa ran a sami wanzuwar adalci da aminci a tsakanin 'yan kasa ko da kuwa a karkashin wace jam'iyya aka zabi wannan shugaba. Babu zancen wannan dan jam'iyyar mu ne wane ba namu ba ne. a duk lokacin da aka rasa irin wannan dattako daga shugaba to la budda wadanda ake tsangwama za su bijire wa duk wasu manufofi da ake aiwatarwa. Sakamakon wannan ne za a dubi yadda wasu marubuta wakokin siyasa a kasar Hausa suka yi Allah wadai da manufofin da ba su musu dadi ba wadanda ake aiwatarwa a cikin kasa.

Nuna bijirewa a tsakanin ‘yan siyasa ba ga harkar zabe da kamfe ya tsaya ba, Abin ya kai har ga shugabanni saboda irin shugabancin da suke gudanarwa na nuna rashin tausayi da adalci.

Ciroma Sudawa ya koka da rashin nasihar da ake yi musu, ya ce ana dukan ‘yan PRP ana karkashe su ana tsare su ba bisa doka ba, amma da alama marubucin yana tuna baya ne musamman lokacin NEPU da NPC, kasancewar PRP da NEPU a kan manufa daya aka gina su Birniwa (1987:338-339). Ciroma Sudawa sai ya ce:

32.Da su ne su kai mulkin mu,
A bi mu gida ana dukan mu,
Su suka karkashe wassunmu,
Ba wani wanda zai cece mu,
Zamaninsu ba walawa.

42.Sun dauki salon siyasar hauka,
Kome ba su yi bisa doka,
Kai abu kankani a tsare ka,
Suna da’awar akwai ‘yan doka,
Alkalansu na daurewa.

(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama’iyyar mu ce Fi’arfi)

### 3.4.3 Zabe

Bayan shafe shekaru sha uku ana mulkin soja a Nijeriya, sai aka sake buga kugen siyasa a shekarar 1978, a yayin da aka tsara jadawalin mayar da mulki ga hannun farar hula daga (1975-1979). Sakamakon haka aka sami jam’iyyun siyasu sha tara suna neman rijista daga hukumar zabe ta kasa (FEDECO). Daga cikinsu biyar sun sami rijista da suka hada da NPN da UPN da NPP da GNPP da kuma PRP (Nnadozie 2007:45).

Duk da cewa zaben 1979 ya yi tsafta idan aka kwatanta da zabunka da aka yi na baya, duk da haka an dan sami korafe-korafe da zargin juna da 'yan siyasa suka rika yi a tsakaninsu. Wannan ya kama daga zargin abokan hamayya sun buga jabun takardun zabe zuwa zargin magudi (Kirk-Grenne da Rimmer 1981:31-45). Jam'iyyun siyasu sun ci gaba da yin kamfe saboda zaben da yake tafe suna tallata manufofinsu domin samin goyan baya, cikin hanyoyin da suka yi amfani da su har da wakoki musamman a yankin Arewa.

Zabe tsari ne na jefa kuri'a domin amincewa ko rashin amincewa ga wani mutum zuwa kan wani mukami karkashin jam'iyyar siyasa, ko kuma amincewa da yin rijista domin neman mukamin jam'iyya. Haka kuma zabe yana nufin hanyar tsara al'umma da daukar matakan da za su inganta al'ummar (Gwinn da Norton 1992).

(Eya 2003) Zabe yana nufin zaben mutum ko mutane a tsakanin 'yan takara domin rike wani mukami ta amfani da takardar zabe.

Bisa fahimta ana iya cewa, zabe yana nufin kada kuri'a ga 'yan takara da niyyar fitar da gwani a karkashin jam'iyyun siyasa.

A kokarinsu na amfani da wakoki, jam'iyyu sukan bayyana adawarsu da juna domin nuna kin yarda musamman a tsakanin jam'iyyun NPN da PRP. Irin wannan nuna kin yarda ta hanyar zabe shi ne Abin da hankali zai karkata a kai a nan.

A cikin wadannan baituka da Musa Madugu ya kawo, abubuwa uku ne ya soki jam'iyyar adawa da su, da ake kyautata zaton da  PRP yake. Abubuwan da ya yi

zargin a kansu sun hada da tabewa da jahilci da kuma hasadar da suke yi da zababben shugaban kasa. Domin nuna rashin yarda da manufarsu, ya ce wadanda ba ‘yan NPN ba, kangararru ne kuma jahilai ne saboda suna adawa da Abin da Allah ya yi. Kasancewar Alhaji Shehu Shagari shugaban kasa ba shi ya nada kansa ba, Allah ne ya ba shi amma kuma ‘yan PRP suna yin hasada da haka dalilinsa ke nan na fadin;

67.Yau Allah fa kai yaz zabe,
Wanda ya ki ka ko ya tabe,
Nan gaba ran da za a yi zabe,
Dangi kar mu taru mu tabe,
‘Yanfi’yan ba za mu bari ba.

69.Mulki dai suna da kala’i,
Shi yas sa suke ta jafa’i,
Su manufarsu ai ta bala’i,
Allah sai ya kawo jaza’i,
Zabe sai ba sui nasara ba.

71.Ko kun ki shi ko kun so shi,
Tilas yau ku taru ku bi shi,
Duk fitinarku sai kun bar shi,
Allah ya riga ya ba shi,
Ba kuma za shi bar mulki ba.

(Wakar NPN ta Musa Madugu:Ya Allah Ka Ba Mu Aminci)

### 3.4.4 Abokan Adawa

Kalmar adawa Balarabiya ce watau “Adawatu” ma’anarta kiyayya. Bayan an samar da kalmar aiki sai aka samar da mai yin aiki watau “Adawu” ma’ana makiyi.

Ma’anar adawa kamar yadda aka kalato a cikin (Kamusu Hausa 2006:2) an bayyana ta da cewa, gaba ko hamayya ko kiyayya tsakanin mutum biyu ko fiye.

A cikin Wikipedia the Free Encyclopedia kuwa ga abin da aka sami a game da adawa.

### 3.4.4.1 Hamayya

Ma'anar kalmar hamayya ita ce, 'kishi ko gasa, ko neman mulki' a duk lokacin da mutane biyu ko fiye suke neman wani abu guda daya, to ya zama hamayya. Hamayya ba ta hana jituwa tsakanin wanda ya yi nasara da wanda bai yi ba. A tsarin hamayya ba ya hana idan gwamnati ta yi mai kyau, mai yin hamayya ya yi yabo, idan kuma an taba gwamnati bisa son zuciya ko kabilanci, ba wuya sai ka ji 'yan kishin kasa sun yi magana.

A lokacin da 'yan adawa ko hamayya suka soki gwamnatin da take kan mulki suka mai ma'ana da babu son zuciya a ciki, ana iya daukar wannan a matsayin hamayya. Ta daya hannu kuma, sukar da babu hujja a ciki ta zama adawa. Ta la'akari da ire-iren abubuwan da suke faruwa a tsarin siyasunmu, ana iya cewa adawa ce kawai ake yi. Wannan ta sa aka tsinkayi irin wannan yanayi musamman yadda ake amfani da shi a bayyana bijirewa.

A cikin abokan adawar an bayyana wani mutum da siffar (baleri) wannan kalma tana nufin bakin abu da Fulatanci haka kuma aka bayyana dayan da (Jatau) wada take nufin abu fari da Hausa, daga kalmar Ja. Duk wanda aka ce da shi baleri, baki wuluk yake haka wanda aka cewa Jatau, ya zama ja wanda ba na sha'awa ba. Haka ya siffanta 'yan santsi, da siffa maras kyau ta yadda babu wanda zai yarda

da irin wannan siffar a ce masa ya zama kamar haka. Wannan ta nuna yana adawa da PRP ke nan kuma ba ya son talakawa su shige ta. A game da haka sai ya ce;

19.Dama karshen su baleri,
Jawo fitina asharari,
Domin bakinsa da sheri,
Tusar ta yi mugun wari,
Kuma duk jama'a sun ji ta.

20.Shi Jatau shashasha ne,
Da halinsa da gwaggo guda ne,
Da biri ja duk daidai ne,
Aikinsa ma barna ne,
Ga raini ga son mata.

(Wakar NPN ta Muhammad Sulaiman Dundaye: PRP ta Zama Kaya)

A cikin martanin da ya mayar ga jam'iyyar NPN Ciroma Sudawa cewa ya yi, wasu 'yan jam'iyyar NPN ba 'yan kasa ba ne, irin su ne Shugaban kasa Murtala ya kora daga Nijeriya, domin haka babu kishin kasa tattare da su sai sharholiya. Ya ce sai muguwar manufa a tare da su da bata harkar shari'a, tun da ba kasarsu ba ce, sai ya ce;

33.Kai da ma da ka dube su,
Ba mutumin kwarai a cikinsu,
Sai mugun nufi a gare su,
Korar Murtala galibinsu,
barayi ne na kin karawa.

35.Bakin halinsu sai mu takaita,
Su ne masu yanke zumunta,
Gun shari'a sukan bata ta,
Hakinka na kanka ya salwanta,
Kai Magana ta kai tsArewa.

(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama'iyyar mu ce Fi'arfi)

### 3.4.5 Farfaganda

Farfaganda wata hanya ce da ake amfani da ita domin a cusa ra'ayi don a jawo hankalin jama'a ga wani al'amari ya alla sabo ne ko tsoho don Abin ya sami karbuwa sosai da sosai. ana yin farfaganda don a nuna kyama ko adawa ga wani abu, don a muzanta ko tallata Abin Isah (2012:87).

A takaice farfaganda hanya ce ta baza ra'ayi domin lallashi da jawo hankalin jama'a domin isar da wani sabon tunani zuwa na wani ra'ayi ko tunani, da a da ta riga ta runguma, kuma ake son yanzu a karbi sabon abin da aka zo da shi.

Irin wannan tsari ne wasu marubuta wakokin Hausa suke bi suna ilimantar da mutane kan wani shiri da su marubutan ke ganin bai da tasiri ga rayuwar mutane, watakila abu ne mai amfani ko maras shi ga al'umma. A kan yada farfaganda a gidajen rediyo da talabijin, a jaridu da mujallu, da fina-finai da wakoki kamar yadda aka yi kokarin kawowa a nan kasa.

Wasu daga cikin rubutattun wakokin siyasa na Hausa, wakoki ne na farfaganda da ke kokarin bijire wa wani tsari da ake aiwatarwa a gwamnatance ko kuma wanda bai yi daidai da tsarin harkokin siyasa ko manufofinta ba. 'Yan siyasa kan yi amfani da farfaganda su bijire a kokarinsu na yada manufofinsu domin su yi tasiri a tunanin jama'a, da kuma jawo hankali da lallashi domin haka ta cim ma ruwa.

Ga abin da aka sami na nuna bijirewa ta hanyar farfaganda a cikin wakokin siyasa;

A cikin wakar ‘PRP ta zama kaya” Sulaiman Dundaye yana fadakar da mutane game da abubuwan da suke cikin PRP saboda mutane su guje ta su ki shigar ta. A kokarinsa na jawo hankulan mutane sai ya ce, PRP kamar mugun doki take. Duk wanda ya hau mugun doki kuwa ya san makomarsa domin sai ya kayar da shi. Kuma ya ce, babu komai a cikin PRP in ban da tarkace kamar jakuna da kuraye da bera da kuma barayi wanda babu wanda zai yarda a danganta shi da su. A karshe sai ya ce shi ba ya kwadayi manufa, duk wanda ya je PRP to makwadaici ne shi ya sa ya ce;

13.PRP mugun doki,
Wai don ka hau bari doki,
Sai ka ga abin mamaki,
Domin ba ka sami tafarki,
Hanyar shanu lalata.

41.In wancan dan jaki ne,
Ai wannan dan bera ne,
Dan satar bin jirgi ne,
Wannan ko dan kura ne,
Kowa ya san kwadayinta.

42.Ni ba na jin tsoransu,
Ban kwadayin kayansu,
Ban sauraron hirarsu,
Da rashin ladabin nasu,
Shi ne hanyar lalata.
(Wakar NPN ta Muhammad Sulaiman Dundaye: PRP Ta Zama Kaya)

A kokarinsa na jan hakalin mata da su shiga jam’iyyar NPN Dundaye ya bayyana matan da suke cikin PRP da karuwai marasa kintsi. Saboda tsananin yawo a dandi har da manajan giya suke bakanta. Sai ya ce;

16.Ku guje wa barayin jama’iyya,
Wata karuwa mai satar miya,
Ita ce farkar manajan giya,

Daga jin reza ba tambaya,
Sharri bakinta ya damfara.
(Wakar NPN ta Muhammad Sulaiman Dundaye: ‘Yan santsi Gammon Sabara)

A nan kuma farfaganda ce aka yi wa ‘yan PRP domin a guji shiga jam’iyyarsu ita kuwa NPN ta sami karbuwa a wurin mutane. Ya bayyana cewa, ‘Yan PRP suna guje wa iyayensu don haka duk wanda ya guje wa gidansu babu wani gida da zai je a karbe shi, domin ya kara kassara PRP sai ya yi kokarin hada su da masu sarauta yana cewa suna kin sarakunan Gargajiya. A gaba kuma ya zage su ya ce ‘yan neman sababi ne da yawan rikici. Kamar yadda za a gani a nan yana ambaton ‘yan PRP da sunan ‘yan santsi wannan ya faru sakamakon rabuwar kai da aka sami a cikin jam’iyyar PRP. Wannan ta sa aka sami Santsi da Tabo Birniwa (1987:261).

14.Duk dan da yake gudun ubansa,
A makwabta babu mai rikarsa,
A gari ba inda za ya zauna.

28.Santsi makiya jinin sarauta,
Ba sa kaunar mai wadata,
Burinsu na kwace gonaki na.

29. ‘Yan santsi sai yawan jafa’i,
Matsayinta sai yawan jafa’i,
Ba sa son lafiya ta zauna.
(Wakar NPN ta Muhammadu Sulaiman Dundaye: ‘Yan santsi Karnukan Farauta)

Domin jam’iyyar NPN ta kara samin tagomashi ita kuma ta PRP ta sami rauni a wajen al’umma wannan sha’iri ya bayyana cewa, an kama ‘yan santsi da hotunan batsa a kasar Makka. Wannan gari shi ne kololuwar wurin ibada na Musulmi duk duniya, idan aka ce Musulmi ya yi wani abu na fajirci a wannan wuri an ci mutuncinsa. Ga Abin da sha’irin ya ce;

33.Wasu sun karyar zuwa ziyara,
Aka gansu da hotunan tsirara,
A kasar Makka wai fa Malamai na.

36.Jarababbu ba nufin saduda,
Sun kai zina gun da ke ibada,
Allah wadaransu fasikai na.
37.Sun bai wa kasar ubansu kunya,
A idanun al'umad duniya,
Zabo ku ashe kiran tsiya na.

38.Allah wadaren Karen farauta,
Mulki a hannunku ya haramta,
Daga wannan sai ka je ka zauna.
(Wakar NPN ta Muhammadu Sulaiman Dundaye: 'Yan santsi Karnukan Farauta)

Abin da ya fito fili a nan shi ne, 'yan NPN sun wanke kansu daga munafurci, Abin da ya rage a kan maganar munafurci a tuhumi abokan adawarsu wato 'yan PRP, shi ya sa ya ce;

59.Ni dai kam ba ni cin amana,
Kuma ban kaunar ma ci amana,
Kuma alkawarinmu mai cika na.

63.Dan santsi kar ka manta Allah,
Ba ka kaunar mu masu sallah,
Da ka zabi karen giya ka zauna.
(Wakar NPN taMuhammadu Sulaiman Dundaye: 'Yan santsi Karnukan Farauta.)

Jam'iyyar NEPU ita ta haifi PRP Birniwa (1987:338-339). Domin haka manufofinsu kusan daya ne duk abubuwan da NEPU ta yi korafin ana yi wa 'yan jam'iyyarta da suka hada da biyan haraji mai tsanani da jangali da aikin gandu da duk wani nau'i na tursasawa, su ne Jam'iyyar PRP ta fadada gwagwarmayarta a kansu. A nan an bayyana cewa, 'yan PRP wadanda su ne 'yan NEPU a baya kamar yadda aka bayyana sun bayyana turjewarsu ga duk wata cuta da ake musu wanda suka zargi 'yan NPN wadanda su ne 'yan NPC  a baya. Shi ya sa ya ce;

5.Ba hujja wurin mai kin ta,
Mu dai mun riga mun fahimta,
Ko a cikin maza ko mata,
In ka ji wanda ke sukan ta,
Macuci ne wajen talakawa.
(Wakar PRP ta Magaji Ciroma Sudawa: Jama'iyyarmu ce Fi'arfi)

Marubucin wannan waka da baitukanta suka zo kasa ta NPN Sulieman Dundaye ya jero wadannan baituka ne ga jam'iyyar adawa ta PRP, domin mutane su guje su ki ta su bijire mata su finjire su kuma yi tofin alatsine su kuma shiga jam'iyyarsa, dalilinsa ke nan na cewa;

21.Laifinai za mu auna,
Jatau Sarkin hiyana,
Kare maciyin amana,
Allah tsine wa gwamna,
Da ke yin fasikanci.

25. Tsinanne dan kunama,
Sarkin neman husuma,
Wai 'yanfifi ya koma,
Yana neman mukami,
Saboda rashin mutunci.

27.'Yan sunna sun guje ta,
Ga Jatau ya shige ta,
Du shegu ne diyanta.
Dan sunna kar ka yi ta,
Don ba 'yanci cikinta.

62.Du wanda ya ce a canja,
Shege shi za mu canja,
Domin mun sami hujja,
Ga Bawa Rijau a Neja,
Ya zarce cin mutunci.
(Wakar NPN ta Muhammadu Sulaiman Dundaye: 'Yan santsi Karnukan Farauta)

### 3.5 Jumhuriya ta Uku

An fara yunkurin kafa Jumhuriya ta uku tun a cikin shekara ta 1987 a zamanin da gwamnatin Babangida ta kuduri niyyar dawo da mulkin farar hula a shekarar 1992 amma bisa mataki-mataki. An sami sabanin ra'ayi daga wasu masana a game da kasancewar Jumhuriya ta uku, a yayin da wasu suke da ra'ayin cewa akwai ta kuma ta cika dukkan sharuda na zamanta Jumhuriya in ban da abu guda daya watau rantsar da shugaban kasa da ba a yi ba. Wannan ta sa ake kiran ta bararriyar Jumhuriya, domin haka yanzu muna cikin jihuriya ta hudu. Wadansu masanan sun tafi da ra'ayin cewa babu Jumhuriya ta uku a tarihin siyasar Nijeriya, domin haka wannan zamanin siyasa da ake ciki yanzu Jumhuriya ta uku ce. A cikin wannan shekara ta 1987 aka kaddamar da zaben kananan hukumomi ba bisa jam'iyyu ba. Sannan kuma aka kawo sabon zabe na 'yar tinke (zaben kai da halinka). Daga nan kuma sai aka ba mutane damar kafa jam'iyyun siyasa. Wannan ya sa aka sami kungiyoyi irin su:

> People Front of Nigeria (PFN) da People's Soldiarity Party (PSP) da Nigeria Labour Congress (NLC) da Nigeria National Congress (NNC) da All Nigeria People's Party (ANPP) da Ideal People's Party (IDP) da Nigeriann People's Welfare Party (NPWP) da Nigerian Union Party (NUP) da People's Patrotic Party (PPP) da Patrotic Nigeria Party (PNP) da Republican Party of Nigeria (RPN) da United National Democratic Party (UNDP) da kuma Liberal Convention (LC) Funtua (2003:56).

Wadannan kungiyoyi sun mika wa hukumar zabe ta kasa (NEC) bukatar yi musu rijista su zama jam'iyyun siyasa. Amma da hukumar zabe ta mika wa da gwamnati shawarwarinta sai gwamnati ta soke su duka, sannan ta kirkiro jam'iyyu biyu na NRC da PDP. A karkashin wadannan jam'iyyu aka gudanar da zaben shugaban kasa a ranar 12 ga watan Yuni 1993, wanda kuma daga baya gwamnati ta soke. Dalilin soke wannan zabe ne rikici ya barke a cikin kasa. Wannan rikici ya yi sanadiyyar raba kan al'ummar Nijeriya musamman mutanen kudu maso yamma da kuma na Arewa. A ranar 27/08/1993 ce gwamnatin Janar Babangida ta sauka aka nada shugaban rikon kwarya karkashin Cif Earnest Shonekan. Ita ma wannan gwamnati ba ta kai labari ba domin a ranar 17/11/1993 ta fadi sojoji suka dawo a karkashin Janar Sani Abacha. Sani Abacha ya yi kokarin dawo da mulkin siyasa a inda ya shirya taron tattauna makomar Nijeriya a shekarar 1994. A cikin watan Maris, 1995 ne aka gudanar da zaben kananan Hukumomi ba bisa jam'iyyu ba. Daga nan kuma sai aka kafa hukumar zabe ta kasa (NECON), sannan aka yi wa jam'iyyu biyar rijista. Jam'iyyun kuwa su ne:

> United Nigeria Congress Party (UNCP) da National Center Party of Nigeria (NCPN) da Congress for Natonal Concensus (CNC) da Grassroot Democratic Movement (GDM) da kuma Democratic Party of Nigeria (DPN).

A ranar 15/03/1997 ne aka gudanar da zaben kananan hukumomi karkashin wadannan jam'iyyu, sannan aka yi niyyar gudanar da zaben gwamnoni da na shugaban kasa a cikin shekarar 1998. Amma a cikin shekarar 1998 shugaban kasa

Janar Abacha ya rasu. Wannan ta sa an sami sabuwar gwamnati amma ta shugaban soja a karkashin Janar Abdulsalami Abubakar. Shi ma ya yi alkawarin mayar da mulki a karkashin farar hula a ranar 29/05/1999 wanda wannan lokaci ne ya zama farkon Jumhuriya ta hudu.

Kowane zango na siyasa yana zuwa da mawakansa, kodayake dai ana samin wasu mawakan su bayyana a fiye da zango daya na siyasa. Babban abin da aka fi sani dai shi ne kowace Jumhuriya tana zuwa da wakokin siyasarta daban da sauran Jumhuriyoyi da aka yi a baya. A Jumhuriya ta uku kamar saura takwarorinta na baya, an sami rukunin mawaka da kuma wakokin siyasa na Hausa da dama.

Kamar yadda tarihi ya nuna, mawakan farko da aka sami walau rubutattu ko na baka akasari Malamai ne wadanda suke da ilimin addini. Haka ya sa ake samin tasirin addinin a cikin wakokinsu. Haka kuma tarihi ya nuna cewa ainihin halayen mawakan siyasa na farko ‘yan kishin kasa ne, masu kishin jam’iyyu. Don haka wakokin da suka rika yi wa jam’iyyu suna yi ba domin su sami wani abun hasafi ba. Amma a Jumhuriya ta uku ba a sami irin wadannan mawaka ‘yan kishin kasa ba. Misali, akan sami mawaki ya yi wa jam’iyya fiye da daya waka. haka kuma akan sami mawakan suna yawo, ko kuma ana dauko su haya jiha-jiha ana neman su yi waka ga dan siyasa a biya su. Wannan ta sa ba a faye samin abubuwa masu kame zuciya ko sosa ta ba a cikin wakokinsu, hasali ma dai abin da kawai aka fi sami a cikin wakokinsu su ne habaici da shagube ko gugar zana ga abokan hamayya a matsayin hanyar nuna rashin yarda da ra’ayinsu. Ire-iren wadannan

abubuwa da aka yi amfani da su wajen bayyana bijirewa, su ne hankali zai karkata a kansu a nan a cikin wakokin Jumhuriya ta uku.

### 3.5.1 Kamfe

Barnhart (1977: 288): Na ganin kamfen a matsayin wani sha'ani na kiran taron jama'a. Shi kuma Hawkins (1981: 56) cewa ya yi kamfen wani gangamin jama'a ne don bayyana manufofin jam'iyya, domin neman goyon baya. Daga bayanan wadannan masana, za a iya cewa kamfen na nufin gabatar da wata manufa a cikin sigar Magana, zuwa ga taron jama'a, domin neman goyon baya.

Kamfen ya rabu kashi-kashi, ciki akwai kamfen na dandali da kamfen na hukuma da kuma kamfen na wakoki. Kamfen na wakoki bisa ra'ayin wannan bincike kusan shi ne ya fi saura jan hankali da ra'ayi, kuma shi ne wanda hankali zai karkata a kansa domin bukatar binciken.

#### 3.5.1.1 Kamfe na Wakoki

Aminu Dandago a cikin wadansu baitoci ya yi amfani da wannan dabara ta kamfe, a bangare daya ya ja hankalin mutane dangane da irin halin da jam'iyya mai mulki ta saka mutane a ciki domin haka yake fadakar da mutane da su guje mata. Ya bayyana cewa, masu mulki na cutar da talakawa ta saka su cikin rashin tabbas a rayuwa, babu shiri na inganta harkar lafiya, cuce-cuce sun addabi mutane, ga kuma rashin ilimi, jahilci ya yi wa mutanen kasa katutu. Ta daya bangare kuwa, sai ya nuna muddin mutanen kasa suka bijire wa waccan jam'iyyar suka kuma zabi ta sa, babu shakka za ta zama uwa ga dukkan sauran jam'iyyu a Nijeriya.

Haka kuma jam'iyyarsa za ta kawo magunguna kyauta a asibiti da kati da gado an daina biyan kudinsu. Ba a nan za su tsaya ba kamar yadda ya ce, za su inganta harkar ilimi da harkar kiwo, Fulanin kasar nan za su shakata su wala, damuwarsu duka za a kawar da ita. Dangane da hakan ne ya jero baitoci kamar haka;

3.Ya Jalla ka zama ja gaba,
Yaz zam daga wannan kasar mu ta bar wata fargaba,
In dai ga tamu ta zan gaba,
Jalla gwani ka taimaka ta zama babba,
Ko kuma ta zam uwa a dukkan Nijeriya.

9.Ceci kasarmu ga baki daya,
Ba da juyin rashin kudi gun mara lafaiya,
Kati da gado da magani ba ka biyan ko daya,
Za ai aiki kamar a Turai don lafiya,
Ta zam ingatacciya ga 'yan Nijeriya.

10.Za a rabautar da kai kana da sanin ilimi,
Kyauta ba mai biyan kwabo ba wani zullimi,
Wanda hali yai kadan bare ma har yai gumi,
Ba ma mun rantse kasar kyauta ga ilimi,
Ba a biyan ko kwabo a yankin Nijeriya.

16.Kun sami rabautuwa Fulanin Nijeriya,
Bana za ku yi dariya wajen kiwon saniya,
Ba mai duban ku bana ya kara yi muku dariya,
Za ku ji dadi idan ta kame Nijeriya,
Kado da Jauro Inyamuri Yoruba gaba daya.
(Wakar NCPN ta Ibrahim Aminu Dandago)

A gaba ya gargadi 'yan Nijeriya da su kaurace wa sauran jam'iyyu domin ba masu son ci gaban talakawa ba ne, halakar da mutane za su yi domin ba su da tausayi. Da ya karkato ga ta sa jam'iyyar sai ya ce, ita ce za ta fitar da talaka daga cikin wuya ya ji dadi ya more rayuwarsa. Ya kara da cewa jam'iyyarsa tamkar

jirgin tsira ce daga takura a Nijeriya, kuma ba ruwanta da nuna bambanci da ‘yangaranci ko na yanki ko na kabila. Wannan ne dalilinsa na cewa;

20.NCP na cire kusa talaka ya san hali,
Ya sami sukuni ya debi daularsa da cokali,
Ba mai duban sa ko gida ko ko dandali,
Ya yi masa kallon mara kwabo ko mara hankali,
Daidai da kasarmu jam’iyyar ‘yan Nijeriya.

21.Kowa na son shigar ta ban da maki ci gaba,
NCP na ga ita da dace ta zame gaba,
Ku duba ku gani tana da siffar ta wuce gaba,
Jagorar ‘yan kasarmu ita muka sa gaba,
Zo ki aiki don mu tsira a yankin Nijeriya.

22.Ma su muradin a jingine tamu waje daya,
Ga ta da hali da ba tunanin yin danniya,
Mai nera har talakka duk za a ci moriya,
Don haka a fito a tsai da tamu a Nijeriya.

23.Bana Yarabawan kasarmu za ku zamo kan gaba,
Dukkan lamuranku ba a canja shi ba,
Na gado da ku kai a gaban iyaye har nan gaba,
An yarda ku tura jami’a ya ga shaida babba,
Da take nuna daukakarku a Nijeriya.
(Wakar NCPN ta Ibrahim Aminu Dandago)

A nan kuma mawakin a kokarinsa na watsi da sauran jam’iyyu abokan hamayya ta sa ya yi luguden rashi har guda hudu wadanda yake so talakawa su yi karatun ta nutsu a kansu, ta yadda za su fahimci cewa, lalle sauran siyasu Abin a bijire musu ne. Da farko ya ce akwai rashin tsaro a kasar nan ga kuma rashin walwala, mutane suna zaune cikin kasa kamar an saka musu karkiya, na uku kuma ga rashin gaskiya sai kuma rashin shiriya wato babu da’a, duk Abin da kowa ya yi daidai ne. Wadannan matsaloli su ne yake ganin halin da ake ciki a Nijeriya, domin haka ya ce, mutane su shiga siyasar NCPN ko ba komai ita rumfa ce da za ta zama

wurin hutawa ga kowa da kowa. Ga baitocin da suka dunkule wannan manufa kamar haka:

32.Taron dangi ba za ya sa mu ji tsoronsu ba,
Wanda kuka yi da saboda mu bai cuce mu ba,
Tarin da kuke a yau ba za kuma ya rage mu ba,
An san mu sarai ubanmu naci ba a fushi ba,
Shiryo damararka baba yanke musu cibiya.

50.Na gane mutan kasarmu an sa mana karkiya,
An yi mana tarnaki ana bi da tsumangiya,
Ga duka ga rashin kwaba da rashin gaskiya,
Ga rumfar jam'iyyar da ba su matsi ba wuya,
NCP wadda ba irin ta a Njeriya.

52.Ruwa ya ci mutan kasarmu an rasa mai fid da mu,
An bar mu muna ta lalube a ciki mulu-mulu,
Mun rasa jirgin da za mu hau ya haye da mu,
Gwarzon yaki na shekara ya sa mun yi tsumu,
Ku taho nan mu kyankyashe kwan zinariya.
(Wakar NCPN ta Ibrahim Aminu Dandago)

Haka kuma a gaba an sake cin karo da Haruna Aliyu Ningi, a cikin baitin da ya zo na kasa yana kushewa 'yan jam'iyyar adawa da cewa ba su da hali na kwarai, amma 'yan ta sa siyasar ita ce mai nagarta kuma abar zabe. wannan ta sa ya ce;

14.Ku taho ku taho mata bana mun yi kira ba ku kyale ba,
Mu saka ku a mulkinmu wannan maganar ba mu fasa ba,
Mun bincika halinku a ciki duk babu halin zaba,
Mu fito ranar zabe dukanmu mu zabi abar kauna.
(Wakar UNCP ta Haruna Aliyu Ningi)

### 3.5.2 Kushewa

Kamusun Hausa (2006 : 257) an bayyana ma'anar kushewa da cewar "nuna aibu ko laifi game da wani abu." Marubuta wakokin Hausa, sukan kushe abu ta sanadiyar dalili da dama, daga ciki ana iya samin yaudara ko zalunci da sauran makamantan haka. Saboda haka a cikin wakokin Jumhuriya ta uku masu dauke da

bijirewa, za a yi kokarin kalato *kushe* a matsayin mizanin bijirewa kamar yadda ya fito a cikin wakokin. Misali;

Aminu Ibrahim Dandago ya kushe abokan adawa ta sigar nuna rashin amfaninsu a tsarin rayuwa baki daya. Duk Abin da aka kwatanta shi a matsayin kashin kare iyakar rashin amfani kenan. Kashin kare ko taki ba ya yi a wajen shuka bare ya yi magani ko wani abu daban. Abin da ya sa mawakin ya kawo wannan ba zai rasa nasaba da rashin amfanin shugabanni ga talakawa ba. Yana kokarin jan hankalin magoya bayan siyasar su cewa, duk wanda ya bi abokan hamayyarsu, babu wani amfani da zai sami. A kan haka ne yake cewa:

6.Karya kashin kare ya zamo taki na gani,
Ba a sayarwa a kasuwa ku sani tuntuni,
Ba a jikawa a sha shi don neman magani,
Ba wani mai tanadinsa don ajiya har da ni,
Ku zo zan fasa kwai ku ji ni in ba mu da gaskiya.
(Wakar NCPN ta Ibrahim Aminu Dandago)

A nan kuwa, mawakin kushe jam'iyyun adawa ya yi a kokarinsa na sama wa ta sa jam'iyyar magoya baya. Ya fasalta jam'iyyun adawa a matsayin na shirme, ta sa jam'iyyar ce tsararriya kuma ingantacciya. A nan mawakin ya yi kokarin jan hankalin talakawa ne da su tsaya a kan jam'iyyarsu, domin haka ta cim ma ruwa. Ga abin da aka sami ya fada a cikin baiti na 9.

9.Kai yo fartanya yau karyar masara karyar kwando,
Da hannu aka san su ko sun rikide sun zam dodo,
Kuma ban da batunka ba wai zai ki hanu masakin wando,
To ku bar wata in'ina ku zo ku rungumi fatina.
(Wakar UNCP ta Haruna Aliyu Ningi)

### 3.5.3 Rashin Adalci

Rashin tausayawa a kan gaskiya ko yin hukunci ba bisa gaskiya babu rangwantawa shi ne rashin adalci (Kamusun Hausa 2006:2). Rashin adalci dabara ce da mawakan siyasa suke amfani da ita wajen finjire wa jam'iyyar abokan adawa. Auwalu Isa a cikin wakar da ya yi wa SDP ya yi amfani da irin wannan hanya wajen bijire wa jam'iyyar adawa wato NRC inda ya bayyana shaho wanda hotonsa ita ce alamar jam'iyyar adawa da cewa, shaho da shirwa 'yan danniya ne kuma shaho dan fashi ne. Duka wadannan halaye da aka bayyana na rashin adalci ne don haka ya ce halayyar jam'iyyar adawa ke nan magoya baya su yi hattara. Idan suna son inda ake yin gaskiya da adalci su dawo tasu jam'iyyar:

23.Shaho da shirwa bana nai batan kai,
Shaho da shirwa da babba-da-jaka,
Kullum manufarsu danne talakka,
In yai magana su ce ya yi hauka,
wai har a kama shi ya karye doka,
Ta fuskas su ba za ya san rangwame ba.

27.Ga Dokta Shatanmu manyan mayaka,
Baban su Mamuda zakin mawaka,
Babba na Bilkisu inuwar maroka,
Sai ya kashe shaho ko ta kaka,
Shi bai amince da cin za'ida ba.

52.Ban yadda da shaho dan fashi ba,
Don bai iya cutar al'umma ba,
Ba za mu bi mai cin za'ida ba,
Mu Ummaru Musa za mu zaba,
Ba zalbe mai nuna dogon wuya ba.
(Wakar SDP ta Auwalu Isah)

### 3.6 Bijire Wa Shugabancin Gargajiya

Al'umomi ko'ina a duniya, ba su zaunuwa sai da wani tsarin mulki, wanda zai tafiyar da al'amurransu. Idan ana magana kan tsarin mulki na kowace al'umma, ya dace a taba masu mulki da wadanda ake mulki. A kasar Hausa, galibi sarakuna ne suke mulkin talakawansu, musamman a tsarin sarautu na Gargajiya (Zarruk da wasu 1982:74). A karkashin ikon kowane shugaba, akwai zababbun mutane masu taimaka masa ga tafiyar da mulkinsa. Irin wadannan zababbun mutane, akan rarraba musu mukamai daban-daban. Irin wannan tsari da yanayin mulki, shi ne ginshikin rayuwar mulkin Gargajiya. Shi irin wannan mulki ya kunshi zama na cude-ni-in-cude-ka, tsakanin shugabannin Gargajiya da talakawansu. Hakan, shi ya kawo dorewar mulki da kwarjini da zaman tare. Amma idan wani abu ya biyo baya, misali rashin adalci da kwace daga wajen shugaba, ko rashin biyayya daga wajen talaka, to sai dangantaka ta raunana (Zarruk da wasu, 1982:81).

Hanyoyin samin kudi ga sarakuna su ne, ganimar yaki da gaisuwa daga dagatai da haraji kan kayan da talakawa suke kawowa kasuwa da harin kamun bayi da sauransu. A wancan lokci, duk wani mai sana'a sai ya ba da haraji. Haka kuma kowane kauye sai mazaunansa sun ba da wani sashe na abin da suka noma ga sarki. Wata hanya kuma ita ce, aikin gayya da ake tilasta talakawa yi a gonar sarakuna ba tare da an biya su ba. Akwai ajin jangali ko kudin haki ga masu dabbobi ko fataken da ke shigowa ko fita da haja (kayan sayarwa), sai sun kai su gaban sarki ya zabi wanda yake so ya saya bashi, kafin su kai kasuwa, ko sun so ko sun ki. Sarki zai biya lokacin da yake so da yadda yake so. Akan mayar da

talaka bawa a sayar koda bai yi laifin komai ba, balle in ya yi laifi. Sau da yawa idan an ga talaka da dukiya, sai a kwace ta domin bai cancanta ya riki wani abu na dukiya ba, a ganinsu (Adamu 2003:27).

Ta fuskar shari'a, akwai alkalai, sai dai ba su da iko, saboda doka ke aiki ba shari'a ba. Ma fi yawan hukunce-hukuncen da ake yi, sarakuna ne ke yi a gidajensu. Idan sun saurari kara, sarakunan birane ko dagatai, suna da ikon yin tara ga kananan laifuffuka, amma manya-manya, kamar su maita da fashi, sai dai fadar sarki. Idan sarki ya kama mutum da laifi, ya zama bawan da za a sayar. Idan sarki na da bukatu da yawa, sai kawai a dubi wani magidanci da iyalinsa, a kawo su gaban sarki da cewar ana zargin su da aikata wani laifi, daga nan, sai a yi musu tara, in sun kasa biya, sai a sayar da su a matsayin bayi (Adamu 2003:29)

Irin wadannan abubuwa, da ba za a rasa ba da kan taso tsakanin shugaba ko wani mai mulki da talakawansa ko mabiyansa shi ke haifar da bijirewar talakawa zuwa ga shugaba ko shugabanni. Irin wannan bijirewa an fahimta tana samiwa a cikin wakokin Hausa musamman wadanda suka shafi siyasa. Irin wadannan wakoki da aka yi masu nuna bijirewa sarakunan Gargajiya, su ne abubuwan da hankali zai karkata a kanua a nan. Misali:

13.Hakana Sarakai masu ikon duniya,
Wasu inda kad dube su ka ga Nasara

31.An yanka albashi gare shi ana biya,
Ya zam awa Inyamuri da Nasara.
(Wakar Nasara ta Maharazu Barmu Kwasare)

Bayanai sun tabbata cewa, Nasara sun mayar da sarakuna tamkar bayinsu. Wannan ta sa ake kira a gare su da kada su mayar da talaka tamkar yadda Turawa suka mayar da su. idan su sun yarda da Nasara, to ba haka abin yake ba a wajen sauran mutane shi ya sa ya ce:

44.Saraki kar a mai da talakka bawa,
A bautas sai awa bautan Nasara.
(Wakar Attahiru Ahmadu ta Zuwan Annasara Kasar Hausa)

Daga cikin irin abubuwan da suka haifar da rashin aminci tsakanin sarakuna da talakawansu, akwai maganar biyan haraji. Kudin haraji da ake tsugawa talakawa, ana kara musu kudin haraji duk shekara, bayan nan ga biyan kudin neman izini na gudanar da wani abu da mawakin ya kira kudin lasisi, ga kuma biyan kudin rumfar kasuwa da sauransu. Ire-iren wadannan suna haifar da bjire wa shugabanni musamman na mulkin Gargajiya, ba domin komai ba, da yawa daga cikin wadancan abubuwa ba a kan ka'ida suke ba, Misali ga abin da aka sami Sa'adu Zungur yake fada a cikin wakarsa ta "Jihadin Neman Sawaba" yana cewa;

16.A aza masa kurdi don garari,
Tilas ya biya ya kiyayi mari.

17.Sarka, gigar, ankwa da mari,
Duk makamai ne na kisan garari.

18. Mu biya gandu mu biya ushuri,
Mu biya tara da shiga hadari.

19.Da kudin lasin da kudin ushuri
Mu biya tikitin mota a gari.

20.Da kudin rumfar mazari
Da dukkan hajja har mandawari.

21.Da kudin karar dukkan lamari,
A gaban Alkalin masu gari.
(Wakar Sa'adu Zungur ta "Jihadin Neman Sawaba)

A tsarin mulki na sarautun Gargajiya, ana sakawa talakawa su biya haraji kala-kala da babu ka'ida a cikinsu. A wadansu lokuta akan sa talakawa su biya kudin da su kansu ba su san dalilinsa ba. A wasu lokutan kuma, akan umarce su, su biyan kudin kasuwa da kudin saka kara a kotu. Aikin gandu yana nan dole sai talaka ya yi shi, irin wadannan kudade da aka lissafa dole mutum ya biya ko kuma ya yi ayyukan da aka shata masa, idan kuwa ya ki biya ko yin aikin ya san makomarsa. Kai tsaye za a kai mutum fursuna a daure shi.

Bayan haraji da ake dorawa talakawa wanda hakan tasa suke nuna rashin amincewarsu da sarakunan Gargajiya. Abu na gaba da ake tursasawa talakawa da shi, shi ne rashin adalci musamman a wajen shari'a. Sakamakon haka ga abun da aka sami a cikin waka:

22.A kama mutum ba gaira bare
Sababi da dalali sai fahari.

21. In ka yi afil ma ka yi barin
Kurdin ka a tafkin 'yan garari.

24.Sun mai da talakka kamar dabba,
Dokin sukuwar sun a masu gari.
(Wakar Sa'adu Zungur ta Jihadin Neman Sawaba)

A cikin wannan waka kamar yadda ta zo a sama, an bayyana yadda ake kama talaka a daure kuma ko ya kai kara kotu ya yi a banza. Ko shari'a aka yi wa talaka

bai gamsu ba, ya daukaka kara ya yi a banza. Talaka ya zama kamar dabba bai san kansa ba sai yadda aka yi da shi.

110.Ba faran ne ba a daure mutum,
A duhun zaluncin masu gari.

111.An ci tarar wassu kudi da yawa,
Bisa cin rashawa ta kisan garari.

112.In don dauri an dauri wasu,
Bisa zamba da zaluncin masu gari.

113. Hakimai, Alkalai har dagatai,
Sun sha dauri na kisan garari.

114.A cikin daular birnin Bauchi,
An daure mutane sun fi dari.
(Wakar Sa'adu Zungur ta Jihadin Neman Sawaba)

A cikin baiti na 110 zuwa 114 an bayyana yadda aka kalubalanci ire-iren hukunce-hukunce da ba su da kan gado da sarakuna suke aiwatarwa a kan talakawa. Abin da sha'irin yake bayani shi ne, talakawa suna farke da ire-iren kama-karyar da ake yi musu, domin haka ba za su yarda sai a canza. An bayyana cewa an sha daure mutane a kan zalunci manufa ba su yi wani laifi ba, haka abin yake wajen cin tarar talakawa, abin babu ko dadin ji, domin ya wuce hankali. Haka kuma su ma Alkalai da ake ganin su ne gatan talaka wanda bai san kowa ba, su ma ba a bar su a baya ba wajen aiwatar da shari'ar son zuciya, suna daure mutane ba tare da hujja ba.

A gaba kuma an kawo baituka da suke nuni da yanayin da sarakuna suke ciki wanda ya yi daidai da halin da masarautunsu da mulkinsu yake ciki. Ya ce, su na da ilimi, amma wanda ba shi da amfani. Wannan ta sa sha'irin ya ce, yadda

girman rigarsu take, haka yanayin masarautun na su yake ga yawa da girma amma babu amfani. wannan ta sa ya ce:

25. Komai na Arewa da bambanci
Da al'umomi sun fi dari.

26.Daularsu daban, cinikinsu daban,
Iliminsu daban don ba nazari.

27.Daularsu kamar rigarsu take,
Ga yawa ba amfani nagari.

28.Cinikinsu kamar wandonsu yake,
Bujensu da ba shi da alkadari.

29.Iliminsu kamar rawaninsu yake,
Daure-dauren banza ba nazari.
(Wakar Sa'adu Zungur ta Jihadin Neman Sawaba)

Bayan da sha'irin ya bayyana adawar talakawa musamman a game da yadda sarakuna suke aiwatar da mulkin daulolinsu, sai kuma ya kara gaba ya ce, daga yanzu sun farka kuma za su dauki makaminsu domin su yi maganin zaluncin da sarakuna suke yi. Ya ce za su yi amfani da makami na harshe domin bayanawa da rubutawa duk wani nau'i na zalunci da sarakuna suka yi. Ya nuna cewa, yanzu babu maganar tsoro babu maganar sanayya, za su yi iyakacin iyawarsu domin su kwato 'yancinsu. Ga abin da ya ce a kasa:

68.Daga yau mun dauki makamanmu,
Na kisan zalumcin masu gari.

69.Domin halshe shi ne kansakali,
Mashi kuwa alkalami na gari.

70.Kai kyalkyal banza masu gari,
Wa ya sa ka a tarkon 'yan hadari.

(Wakar Sa'adu Zungur ta Jihadin Neman Sawaba)

### 3.6.1 Bijire Wa Wasu Al'adun Gargajiya

Camfi wata dadaddiyar al'ada ce da Hausawa suka tarar kaka da kakanni. Wasu na ganin Camfi al'ada ce kawai kamar irin kowace al'ada; wasu kuwa na ganin abin ya kai matsayin addini daga cikin addinan Gargajiya Bahaushe (Bunza 2006:58). Wannan hanya da wasu suka dauka tamkar addini, a yayin da wasu suka dauke ta al'ada, ita ce aka sami cikin waka mai suna "Gadar Zare" a inda marbucin ya bayyana bijirewarsa a kan haka. Ga abin da ya ce:

3.Ko dai da na san fa kun san su jimla,
Ba wani laifi dadin mai ga fitla,
Ta nan za mu gane mu kara kula,
Mu kauce wa hanyar shirin masu hila,
Suna ta batarwa a duk safiya.

6.Shi ne nake son mu taru mu gane,
Camfi da kage rashin ilimi ne,
Tsafi su bori rashin hankali ne,
Aminci da su ko hakikar bata ne,
Da wauta da shirme da sharholiya.
(Wakar Gadar Zare ta Mudi Sipikin)

A cikin baituka biyu na sama marubucin ya yi Allah wadai da al'adar Camfi, ya bayyana cewa duk da cewa wadansu sun sani cewa Camfi babu kyau, duk da haka ba laifi ba ne idan ya kara tunatar da mutane a kan batun. Ya yi kira da a kauce wa Camfi ba abu ne mai kyau domin haka, kada a yarda da shi. A gaba kuma ya ce, da Camfi da Tsafi duka hanyoyin bata ne domin haka, a guje su, wauta ne da shirme da rashin hankali.

7.Ku gane mutane fa ba wata inna,
Da ke shanye hannu kafa don fitinna,
Rashin lafiya ne kawai ku shina,
Wajen likitoci akwai maguna,
Ku zan tambaya don sanin gaskiya

8.Sa'annan ku gane fa babu fatalwa,
Shirme kawai ne ku daina kulawa,
Kar dai ku yarda da masu batarwa,
Su maishe ku "bol" duk suna ta bugawa,
Ga ku da ranku cikin duniya.
(Wakar Gadar Zare ta Mudi Sipikin)

Mawakin ya ce, maganar Inna duk rudin mutane ne babu wata Inna da take shanye hanu ko kafa rashin lafiya ce irin ta asibiti. Maganar fatalwa da mutane suke danganta da wata ko wani da ya mutu ya ce, duk sharri ne babu gaskiya a ciki. Ya ce, kar a yarda da masu fadar irin wadannan maganganu. Ya kawo wannan bayani a cikin baitoci biyu da ke sama.

A gaba kuma, cikin baitoci uku da suke biye, mawakin har rantsuwa ya yi da cewa babu abin da Hausawa suke cewa Nakada. Wannan sunan wani aljani da ake hawa bori da shi. Ba karamar bijirewa b ace, a ce ga mutum ya fito fili yana yin Allah wadai da wadannan ire-iren abubuwan da wasu daga cikin Hausawa suka yarda da shi. Mawakin bai tsaya a nan ba sai da ya yi watsi da duk wata al'ada ta bori. Hakan ta sa yake cewa:

9.Wallahi Tallahi babu nakada,
Kar ma ku ce za kun an wata shaida,
Matsafa kawai ne suke farfaganda,
Su ja hankalinku zuwa kasada,
Su sa ku a hanyar rashin gaskiya.

10.Sun ce a bori akwai Alhaji,
Ya jama's duk kuna nan kuna ji,
Sun yi dabara su bata Haji,

Wallahi Tallahi duk kar ku ji,
Karya suke yi ga baki daya.

11.Sun ce akwai wani bebe da kure,
Wai su suke magana da dare,
Duk babu su kar ku dau kuskure,
Duk wanda ya hau gada ta zare,
Zai sullube kuma zai dulmiya.
(Wakar Gadar Zare ta Mudi Sipikin)

A cikin wannan tsari na bijire wa wadannan al'adu na Hausawa, mawakin ya nausa cikin al'adar rashin tsafta da take kawo jinyace-jinyace iri-iri. Ya yi Allah wadai da masu cewa ranar Larabgana ba a yin wanka, ya ce duk wannan jahilci ne. Haka kuma, masu cewa ba a yin shara da daddare, suma ya kira su da kazamai kuma wawaye. Ga abin da ya ce:

12.Ina masu cewa akwai Iwaja,
Masu fadin haka ba su da hujja,
Tatsuniya ce kawai har ku ja,
Babu musu babu yin ja-in-ja,
An bincika babu shi ko daya.

15.A larabgana sai su ce ba a wanka,
Sun kauce hanya ta tsafta duka,
Sun shanya dubbai cikin yin shakka,
Sun dauki zance na wauta da hauka,
Ku nissanci zancensu kar ku jiya.

16.Shara cikin dare wai an hana,
Tana sa talauci ji karya da fitina,
Dabararsu tsafta su zam sun hana,
Ku nisanci wannan a 'yan uwana,
Nasiha nake muku don ku jiya.
(Wakar Gadar Zare ta Mudi Sipikin)

## 3.7 BIJIREWA A CIKIN WAKAR NEPU TA JIYA DA YAU TA AKILU ALIYU

Wannan waka tana daya daga cikin jerin wakokin jam'iyyar NEPU da marigayi Dr. Akilu Aliyu ya rubuta kamar yadda aka sami a cikin littafin "JIYA DA YAU" wanda Abdullahi Kafin-Hausa ya rubuta a shekarar 1983. Bisa fahimta wakar tana dauke da bijirewa ta gaske musamman ga jam'iyyar NPC ganin cewa jam'iyyar ce take rike da madafun iko, a yayin da jam'iyyar NEPU take matsayin jam'iyyar adawa.

Da farko mawakin ya fara da takalar dan adawa wanda ake zaton dan jam'iyyar NPC ne, ya bayyani da matsayin mutumin da ba shi da daraja kuma, mutum ne da ake gani kamar yana da kwarjini da kima da kuma haiba amma kuma, ba haka yake ba. Ya kara da cewa makaryaci ne kuma mayaudari. Ga dai abin da ya zo a cikin baitocin da suke biye:

5. Ga abin ajabi a Yarwa,  
   Mun ga karo ba muruwwa,  
   Ai shirin ne babu inuwa,  
   Mun wuce mun bar shi baya.

6. Ya aro bakin hukuma,  
   Ya yi karya don shi kama,  
   Sai shi zauna shi ta homa,  
   Kaito ango ba amarya.

(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A gaba kuma, mawakin ya kara bayyana ra'ayinsa na kin yarda da wancan mutum da ake jin ya fito ne daga jam'iyyar NPC a inda ya bayyana shi a matsayin raggon dan siyasa wanda babu wahala a kayar da shi zabe. Wannan ta sa yake cewa:

7. Mun fada masa, 'Wane fasa',
Ya ki shi ya cuci kansa,
Ba wuya mu ci daguminsa,
Har ya karya wuya da baya.

8. Babu dama ba alama,
Kar ka kuskura ma ka soma,
So suke su zuga ka dama,
Don ka fadi su ja da baya.

9. Borno 'yus' NEPU 'alayans,
Yarwa 'Nos' har Yarwa 'Sawus',
Mu muke magana a 'Hawus',
Babu shakka babu karya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A jumhuriya ta farko, an yi takarar zabe tsakanin manyan siyasun Arewa guda biyu wato NEPU, da NPC. Dangantaka tsakanin wadannan jam'iyyu, dangantaka ce tsakanin mai mulki da wanda ake mulka ko kuma, mai hali da maras hali. Irin wannan yanayi tasa a lokuta da dama duk jam'iyyar da ta fadi zabe sai ta bayyana rashin amincewarta. An sami baituka da Akilu Aliyu ya yi a cikin wannan waka da suke nuna irin wancan kin yarda wanda yana daya daga cikin hanyoyin nuna bijirewa.

A cikin wakar ya bayyana yadda aka musu magudi a zabe yana cewa abokan hamayyarsu sun yi tsafi hakan tasa suka ci zabe, ga abun da ya ce:

13. Ba hilafa babu shakka,
Mai mutum da hali ya naka,
Hankali ba za shi dauka,
Faduwarka ba, sun yi karya.

14. Sun ki Allah sun yi tsafi,
Sun yi al'ada ta camfi,
Sun ci barkono da zafi,
Lahirarsu akwai karaya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A nan kuma, mawakin ya sake bayyana yadda ya raba gari da abokan adawa a inda ya labta musu maganganu masu zafi da nauyi. Ya kira wani dan adawa da suna wawa ya kuma bayyana shi a matsayin wanda aka Haifa ba tare da aure ba tsakanin iyayensa. Ana iya fahimtar wannan a cikin baitocin da suka biyo baya kamar haka:

15. Wane wawa ka yi shirka,
Kai ka cuci na karkashinka,
Don bukatar duniyarka,
Lahirarka ta bar ka baya.

16. Dan kuyanga duk abinsa,
Ba shi rama halin ubansa,
Ko da dai maman uwarsa,
Shi yake waige a baya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A nan, adawa ta kai adawa domin mawakin ya ce ba sa so ya mutu ya bar su, manufa sun fi so a zuba tsakanin su da shi a ga wanda zai sha kashi. Ya kara nuna rashin yardarsa ta hanyar bayyana wani dan adawa da cewa makaryaci ne kuma, mutum ne wanda bai san kansa ba.

17. To fada mar kar ya fasa,
Mu da shi mu zuba shi kasa,
Gare ma tafi arzikinsa,
Taiba sai ya ci tasa gaya.

18. Ba mu so ya mace ya bar mu,
Mun fi so Allah ya ba mu,
Tabbatar ‘yancin kasarmu,
Ban da shi a cikin kidaya.

19. Ka ga dan gatan jidali,
Bankadadde fankashali,
Wane mene ne dalili,
Ba ka kunyar fesa karya.

(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

Da aka matsa gaba kuma, sai aka sami karin bayani a cikin wadansu baitoci a inda mawakin ya nuna fau-fau ba ya tare da waccan jam'iyya domin a cikinta akwai 'yan fasadi wato masu yin aikin abin da ba shi da kyau. Ya nuna cewa saboda tsabar aikin asha a kowane lokaci kuma a kowace ran har da ta juma'a, rana mai alfarma suna yin aikin badala, a karshe ya ce sun yi abin kunya a yankin Arewa.

20. Ya yi kyau ka kiyaye haddi,
Ka ki sai zafin fasadi,
Juma'a Asabar da ladi,
Ko da yaushe kana mashaya.

21. Kun abin kunya a 'NOZAN',
Kun ki kun so ma fada zan,
Ya kamar kai wanda ya zan,
Babba zai gudu har ya buya?

22. Da kana ji kai mutum ne,
Wanda ke da dubun mutane,
Ba ka zabar toshe kunne,
Ka ki jin zargi a baya.

(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A nan kuma ya kwarzanta jam'iyyarsa ya cicciba ta ya nuna kwarjininta a kan sauran jam'iyyu, ya nuna ba sa tsoron kowace jam'iyya indai a wajen shiga zabe. Ya soki jam'iyyar adawa da cewa mayaudara ne, wadanda ba sa yin dogaro ga Allah sai dai wani sabaninsa, domin haka irin wannan dabi'a da suke yi ita ta kawo rashin ci gaba ga yankin Arewa. Sakamakon haka sai ya ce:

26. So nake in tsara baiti,
Mai yawa kanshi ya zaiti,
Babu karya babu fenti,
NEPU ba ma ja da baya.

33. Allah tsine mayaudarinmu,
Wanda sun ci da taimakonmu,
Don su je gaba can su ki mu,
Rabbana maishe su baya.

34. Dogaro shi ne imadu,
Fassarar FISI, FASADU,
Gatarinsu na ‘yan aradu,
Shi ya kauce Arewa baya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A nan kuma, mawakin ya nuna sam bai yarda da jam’iyyar da suke adawa da ita ba da manufofinta domin, babu komai a cikinta sai mugunta da kuma, nuna fin karfi ga talakawa da cin zali da rashin adalci da karya da kuma munafirci kamar yadda ya ce:

35. Ban da ‘yan fisi macuta,
Masu keta da kin zumunta,
Masu takidin mugunta,
Masu son danne na baya.

36. Ya ake hada kwai da dutse,
Su su san lemo su tsotse,
Mu mu danki kaho su tatse,
Babu nono babu kwarya.

37. Ni abin da ya sa na ki su,
Yara har manya cikinsu,
So suke su ci ba guminsu,
Ga munafunci da karya.
(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

A gaba kuma, sai ya ce, abin da ya sa ya ce bai yarda da jam’iyyar adawa ba kuma, ba ya ra’ayinsu shi ne, ‘yan jam’iyyar fasikai ne kuma, ba su san komai ba sai cin hanci sai sata da karya. Haka kuma, ya bayyana ‘yan jam’iyyar da masu yawan banza.

38. Ba su kunyar fasikanci,

Ba su aiki don karimci,
Ko suna tsare sa ci hanci,
Sa yi sata, sa yi karya.

44. Fangami wawan Bahaushe,
Mai jiran a kasa ya kwashe,
Rijiya kan za ka yashe,
Sai su shata su bar ka baya.

45. Ko su Alhaji kyau da bashi,
Yaushe za a rabonku bashi,
Randa tulu ya yi gashi,
Ko a girka tuwo a kwarya.

46. Wane bai gajiya da yawo,
Don ya nuna waje ya dawo,
Kai! KURURURU bARAWO,
Zai kashe mu ya kwashe kaya.

47. Kai ya kai ya dubu kamarka,
NEPU ta wuce arzikinka,
'Yan gaba-gadi sun ishe ka,
Yarwa yau sai kuka buya.

(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

Haka kuma, a karshe ya bayyana rashin amincewarsa da 'yan adawa kuma ya ce, tsakaninsu babu amana domin haka, ra'ayi ba zai taba zama daya ba.

51. Mu da kai ba ma amana,
Ba mu son ka dare da rana,
Kan muna gu kar ka zauna,
Zakuda can ja da baya.

54. Mai basira ya fahimta,
Mai shige dawa ya bakinta,
Sha-mu-dora Karen farauta,
Ya kake ja baya-baya?

(Wakar NEPU ta Akilu Aliyu: Jiya da Yau)

**3.8 Kammalawa**

Wannan babi ya tattaro abubuwa muhimmai masu dama a tarihin wakokin siyasa a kasar Hausa. Ya tabo zamunna da suka hada da zuwan turawan mulkin mallaka

kasar Hausa, irin yadda aka yi gwagwarmaya da su ta yadda har wakoki aka rinka rubutawa ana karantawa a game da nuna rashin yarda da zuwan nasu. Haka kuma an nazarci wakokin da aka yi wa siyasun Jumhuriya ta farko, wadannan siyasu sun hada da NEPU da NPC wadanda su ne manyan siyasu a nan yankin Arewa, kuma wadanda aka yi musu wakoki cikin harshen Hausa. A gaba kuma an dubi wakokin da aka sami a cikin Jumhuriya ta biyu, kamar 'yar uwarta Jumhuriya ta farko, a nan ma jam'iyu biyu ne suka yi fice a yankin Arewa duk da cewa ba su ke nan ba. Wakokin  jam'iyyun da aka kalla a wannan Jumhuriya sun hada da NPN da kuma PRP. A cikin Jumhuriya ta uku an nazarci bijirewa a cikin wasu wakokin jam'iyyun da suka zo hannu. An nazarci wakokin jam'iyyar SDP da NRC haka kuma an zakulo wadansu abubuwa a cikin jam'iyyar UNCP da kuma ta NCPN. A karshen wannan babi an nazarci bijirewa a cikin wakokin da aka yi sakamakon irin mulkin da sarakuna suke shimfidawa a kasar Hausa, wanda yake cike da rashin adalci da kuma da kin bin doka, abin da ya kai har wakoki aka sami sha'irai sun rubuta domin fadakar da talakawa

# BABI NA HUDU

## BIJIREWA A WAKOKIN DIMOKIRADIYYA (1991-2015).

### 4.1 Gabatarwa

Jumhuriya ta hudu ta fara ne daga shekarar 1999 zuwa wannan lokaci da ake ciki a yanzu. Ana kira wannan zamanin siyasa Dimokiradiyya domin, Jumhuriya ta hudu ta rabu ya zuwa zanguna biyar. Zango na farko ya kama daga watan Mayu 1999 zuwa farkonn shekara ta 2003, zango na biyu kuwa ya fara daga watan Mayu 2003 zuwa farkon shekara ta 2007, a yayin da zango na uku na Jumhuriya ta hudu ya fara daga watan Mayu 2007 zuwa shekara ta 2011, sai kuma zango na hudu da ya fara daga watan Mayu 2011 ya zuwa 2015, a yayin da aka shiga zango na biyar a ranar 29th-Mayu, 2015. A zango na farko an kafa jam'iyyun siyasa uku da suka hada da AD, da APP, da kuma PDP, daga baya APP ta canza zuwa ANPP, sai kuma aka sami karin jam'iyyar DPP, da AC, da kuma CPC, da ACN. An kafa wani tarihi a siyasar Nijeriya a inda aka sami hadewar jam'iyyu uku zuwa hudu suka zama jam'iyya daya wato Action Peoples Congress (APC) a matsayin jam'iyyar adawa mafi girma a Nijeriya, kuma ta yi nasarar karbe mulki daga jam'iyyar PDP da ta shafe shekaru 16 tana mulki. Duka wadannan siyasu da aka yi, kusan kowacce an yi mata waka domin yin kamfe domin haka ta cim ma ruwa. A cikin irin wakokin da ake yi musu, akan sami suna bayyana ra'ayi na kin aminta ko yarda da juna.

A sakamakon haka ne aka sami wakokin siyasa a Jumhuriya ta hudu masu dauke da kalamai na mizani da ake ganin na nuna bijirewa ne ga masu mulki da mabiya har ma da lokacin kamfe da sauransu da yawa.

A takaice a wannan babi za a yi tsokaci ne a kan abubuwan da suka faru na game da bijirewa musamman cikin rubutattun wakoki a kasar Hausa lokacin mulkin Dimokiradiyya, da kuma duk wata wakar baka ta siyasa da aka juye aka rubuce ta. Dalilin haka shi ne, yawancin wakokin baka musamman wadanda suke jibanci siyasa lokacin Dimokuradiyya suna kan tsari mai kyau na rubutattun wakoki. Da yawa suna da kari mai kyau da za su iya hawa ma'aunin karin rubutacciyar waka. Za a dubi yadda aka yi amfani da bijirewa a cikin wakoki wajen nuna rashin yarda da manufofin juna. A karshe za a dauki waka daya a cikin wannan zamanin siya a yi nazarinta, domin fitowa da irin bijirewar da take cikin wakar.

### 4.2 Bijirewa A Tsakanin Jam'iyyun Siyasa

Abu ne sananne jam'iyyun siyasa sun fito fili suna nuna adawa a tsakaninsu, wannan tana sukar wannan, waccan tana yi wannan zambo da sauran abubuwan na nuna rashin yarda da junansu. Jam'iyyun siyasa suna amfani da hanyoyi daban wajen bayyana bijirewa a junansu. Ire-iren wadannan hanyoyi sun hada da;

#### 4.2.1 Abokan Adawa

Kalmar adawa Balarabiya ce wato *Adawatu* ma'anarta kiyayya. Bayan an samar da kalmar aiki sai aka samar da mai yin aiki wato *Adawu* ma'ana makiyi.

Ma'anar adawa kamar yadda aka kalato a cikin (Kamusu Hausa 2006:2) an bayyana ta da cewa, gaba ko hamayya ko kiyayya tsakanin mutum biyu ko fiye.

A lokacin da 'yan adawa ko hamayya suka soki gwamnatin da take kan mulki suka mai ma'ana da babu son zuciya a ciki, ana iya daukar wannan a matsayin hamayya. Ta daya hannu kuma, sukar da babu hujja a ciki ta zama adawa. Ta la'akari da ire-iren abubuwan da suke faruwa a tsarin siyasunmu, ana iya cewa adawa ce kawai ake yi. Wannan ta sa aka tsinkayi irin wannan yanayi musamman yadda ake amfani da shi a bayyana bijirewa.

Abdullahi Ningi ya jaddada ta sa adawar ne ta fuskar samin 'yanci kamar yadda yake a cikin tsarin Dimokiradiyya. Ya ce kowane dan kasa yana da 'yanci kuma yana da damar yin ra'ayin duk wanda ya ga dama ba tare da an tursasa masa ba, ya ce ako ina talaka yake yana da dama babu lalle babu tilasa a bar kowa ya yi ra'ayinsa. idan mutum ya ce yana yi a kyale shi haka kuma duk lokacin da ya canza ra'ayi ya ce ba ya yi sai a kyale shi. Haka ne ta sa ya kawo wadannan baitoci;

6. Manufar dimukradiya damar fadar kowa,
'Yancinka ne dan adam kai ra'ayin kowa,
In ba ka so babu tilas ko gaban kowa,
Ra'ayinka tamkar ka kone har da ba kowa,
Duk fadarsu ba yi ba ne, ra'ayinmu sai mun yi.

20.Ladabi, biyayya da kyau, in ba rashin gaskiya,
Za kai wa babban mutum mai son fadar gaskiya,
Ra'ayinka ko naka ne, ba mai yi ma danniya,
Bin shugaba dole ne, in yai rashin gaskiya,
Ko shi yake ci da kai ka canza hanyoyi.

(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdu'Aziz Abdullahi Ningi)

A cikin *Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi ya fito karara ya ce ba za a hana su adawa ba idan ma ba a yarda da batunsu na kin tazarce ba kamar yadda suka saka shi cikin waka.  Ya ce canji a ko'ina ne ana son sa don haka maganar wai zababbun wakilai su dauwama a kan mulki ba ta ko taso ba, ya kara da cewa abu ne zaunanne cikin tsarin mulkin kasa cewa, shugabanni su yi mulki sau biyu, amma sai ga shi wadansu masu son zuciya suna neman a canza tsarin mulkin ta yadda za su dawwama a kan mulki. ga Abin da ya fada a kasa;

10.Tura ta kai bango, kun gan ta amma ku hakikance,
Wai ko da tsiya ku, dai ku sake zama a gurin kwace,
Sai kun gama holoko, da cin zarafinku ta susuce,
Ko kun hana jin waken, ba za ku hana mu adawa ba.

37. Ko kun iya aikinmu, irin haka dole ta bata ku,
Ku bari wa wadansu su yi, domin kuwa kun gama aikinku,
Magana ta ta zarce ce, ta sa jama'a suka kushe ku,
Ai ko a kiyoma ne, wadansu ba za su ki canji ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A kokarinsa na bayyana adawarsa ta fuskar kin yarda da jam'iyyarsa, Aliyu Ningi ya ayyana jam'iyyar a matsayin masifa domin kamar yadda ya fada, kusan dukkan shugabannin jam'iyyar da wadanda suka kafa ta wato iyayen jam'iyya ta yi watsi da su. Samiwar irin wannnan ba komai ba ne a wajen masu ra'ayin jari hujja. Kamar yadda ya ce wasu ta hallaka su a siyasance wasu kuma ta sa sun rasa tasiri a cikin al'umma sakamakon haka sai ya ce, ko ana harbi da bindiga sai sun bar ta domin ta zama sakakkiyar saniya sai da haramun, domin kara bayyana adawarsa da jam'iyyar ya aibanta da cewa ta zama "Kurga" wato cuta  dangane da haka sai ya ce:

8.Shekaru bakwai mun yi a karkashinki,
Har zuwa takwas za a yi karkashinki,
Mun ga ja'iba mun ga ta'annatinki,
Ko da bindiga ban kuma bin ki tun da na farga.

10.Ta kashe Lar ya gama zamaninsa,
Ta ci Gamade ta fasa tambarinsa,
Audu Ogbeh ta kar shi a saurayinsa,
Wa take bari dole mu bar ta shegiya kurga.

11.Ta kashe Alex Baba Ekweme namu,
Ta ci Rimi ta sa shi a ayarinmu,
Ta zubar su Musan Musawa namu,
Yanzu saniya sai da haram gidanta yai tsaga.
(Wakar PDP Shegiyar Uwa ta Haruna Aliyu Ningi)

Haka kuma, ya yi karin haske kan cewa, da ma su suka tara wa jam'iyyar magoya baya domin haka tun da ta zama shegiyar uwa za su janye magoya bayan da suke cikin jam'iyyar. Ya fito fili ya nuna bijirewa ga jam'iyyar PDP inda ya ce za su fita daga PDP shegiyar uwa za su koma wajen kishiyarta wato jam'iyyar adawa. Ya kara jaddadawa cewa, jam'iyyar shegiyar uwa masu handama ne a cikinta shi ya sa ta mutu kuma ta zama ramin kura daga ita sai 'ya'yanta kamar yadda ya kawo a cikin baitocin da suke kasa (bt na 18, da 19, da kuma na 43).

18.Jam'iyyar ce mu muka ce a bi ta,
Mu mu kai kirayi aka rungume ta,
Yanzu tun da ta nuna halin tsiyarta,
Dole mui kira don a guje ta shegiyar kurga.

21.'Yan kasarmu in za a yi kar a yi ta,
Gara duk mu taru mu bi kishiyarta,
Tun da goggo ya karya shika-shikanta,
Ba jana'iza ko haka sai mu binne 'yar banza.

43.Jam'iyyar kisa, duk tawagarsu ce PDP,
Masu handama, dole mu bar zama da ke ya fi,
Za ku sake bi? Ba mai sake bin ki PDP,
Mun fahimci tsarinsu Mobutu ce da ke alga.
(Wakar PDP Shegiyar Uwa ta Haruna Aliyu Ningi)

A gaba kuma, wakar APC ce mai suna *APC maganin PDP*. A cikin wakar an bayyana adawar APC a matakinta na kin amincewa da PDP a inda ta ce, PDP jam'iyya ce ta 'yan iskan duniya, jam'iyya ce wadda ta lalata tsari na mulkin gaskiya. APC ta nuna cewa ita ce jam'iyyar da za ta yi mulkin gaskiya ta kuma tabbatar da gskiya a cikin kasa.

Sai ya kara da cewa,

PDP ba ta son ai gaskiya,
Ba ta bukatar mai yin gaskiya,
Burinta kau da masoyin gaskiya,
Bakar uwa mara kishin gaskiya,
Karshenki ya zama iska yau APC sai tai mulkin Nijeriya.
(Wakar APC Maganin PDP ta Funtua)

A gaba kuma, jam'iyyar APC ta yi wa takwararta PDP luguden kalmomin rashin gaskiya inda ta ce, ba ta son a yi gaskiya ba ta kuma kaunar mai yin gaskiya, kuma a kowane lokaci a shirye jam'iyyar take ta kawar da mai son gaskiya, dadin dadawa jam'iyyar PDP kamar yadda ta APC ta bayyana ba ta kishin mai yin gaskiya. A takaice, kamar yadda mawakin jam'iyyar APC ya fada, jam'iyyar PDP sun yi hannun riga da gaskiya. Wannan ta sa yake ganin ya kamata mutane su bar ta su koma APC jam'iyyar da za ta shimfida mulkin gaskiya.

A gaba kuma, wakar APP ce aka ci karo da ita kamar haka:

23.In ba don shiri irin na batattu ba,
Shi wake ba zai yi dan malili ba,
Haka ridi ba za shi yi mana biski ba,
Baragurbi ba za su ci mu da yaki ba,
In APP na cikin kuma Nijeriya.
(Wakar APP Kishin Kasa Bashir Sani Ringim)

A nan kuma, jam'iyyar APP ce take bayyana adawarta ga takwararta jam'iyya mai mulki ta PDP tana cewa, muddin jam'iyyar APP tana cikin Nijeriya ba za ta yarda ba, a ce za a yi abin da aka san ba mai yiwu wa ba ne. Kamar yadda ya kawo a cikin baitin yana cewa, shiri ne na batattu a ce za a yi dan malili da wake (nau'in abinci da akasari yara suke yi ta hanyar sarrafa garin masara) Haka kuma, ya ce da kamar wuya a ce za a yi biski da ridi (wannan ma wani nau'in cimaka da ake sarrafawa domin amfani ba a sarrafa ridi a matsayin abinci). A karshe, ya ce abu ne da ba zai yiwu ba a ce baragurbi manufa abu marar inganci da rashin kyau, a ce zai ci mutane nagartattu da yaki.

Shi kuwa Garba Gashua a cikin ta sa wakar ta APP ga Abin da ya fada:

10. PDP ta kashe mutane a guri-guri,
Zaben gaba dole za mu zauna a cikin shiri,
Komai muka gan shi yau baki dole ya zam fari,
Kai mai daure mu daure ankwarka da sasari,
Jallah taimaka taimaki jam'iyyar APP.

11. Ni na yi kira maza da matanmu gaba daya,
Gara mu shirya muna da fama da kwarabniya,
PDP za mu sanya wandonmu kafa daya,
Ba na shakkar ki kokawa ko a karangiya,
Jallah taimaka taimaki jam'iyyar APP.

12.PDP ta kashe al'ummar kasa,
Ta hallaka can na nesa har wanda suke kusa,
Su dai su yi karfa-karfa ko shirya manakisa,
Mu bana addu'a da mu da ke Allah ya isa,
Jallah taimaka taimaki jam'iyyar APP.
(Wakar APP Kowa Ya Yi Maka Kan Kara ta Garba Gashua)

Mawakin ya ce PDP ta kashe mutane a cikin kasar nan a wuri-wuri wannan kuwa bai zo da mamaki ba domin ita ce jam'iyyar masu mulkin da talakawa suka ce ba

a musu adalci sai zalunci babu arziki a cikin kasa sai talauci. Wannan ya sa mawakin ya ce, a halin yanzu babu maganar tsoro kuma babu gudu babu ja baya, a shirye suke su kawo canji. Ya kara da cewa su a halin yanzu ba sa fargabar dauri, duk wanda zai daure su ya gyara kayan dauri da kyau ba su da fargarba. Ya ce a shirye suke su yi fito-na-fito da PDP, wannan ta sa ya ce za su saka kafar wando daya da PDP. A kokarin jaddada manufarsa ta bijire wa jam'iyyar PDP mawakin APP ya yi wawar kora da cewa ba sa shakkar yin duk abin da za a yi a tsakaninsu har da yin kokawa a cikin karangiya a shirye suke a yi. A karshe ya ce sun yi Allah ya isa a kan jam'iyyar PDP saboda da irin halin wahalhalu da mutanen kasa suka sami kansu ciki. Wannan ya zo cikin baiti na 10, da 11, da kuma baiti na 12.

Wakar ACN ce a gaba:

15. Mun fara gyaran shirin yakin duk masu yin cin amana,
Mun wargaje duk shirin 'yan zambo masu shukar fitina,
Mu mun samo maganin 'yan banza masu son suy yi barna,
Allah muna addu'a karya dukkan shirin 'yan adawa.
(Wakar ACN ta Bafarawa)

A cikin wakar ACN da aka yi wa Dalhatu Bafarawa, mawakin ya zargi 'yan adawa ya ce maciya amana ne ba su san komai ba sai shuka fitina a cikin kasa da yin barna, wannan ta sa ya yi addu'a ya ce Allah ya karya shirin 'yan adawa tun da ba sa nufin kowa da alheri. wannan ya zo cikin (bt na 15) kamar yadda aka rattabo a sama.

Baiti na 14, da kuma 18, cikin wakar PDP ta *Bulaliya* ga abin da aka sami;

14.Sakainun bisa kan ruwa ba zan bi akidarku ba,
Iska ce ke kada ku ba wani karfinku ba,
Dan ba ku da gun zuwan da iska ba ta san shi ba,
Ni ba na bin abin da ban san manufarsa ba.

18. Jam'iyyar bakin-ciki ba zan yi ta ba,
ANPP a yau da gaske ba zan so ta ba,
Kura ce ko da sasari ba zan hau ta ba,
Allah wadaran shirinki ni ba zan bi ki ba.
(Wakar PDP Bulaliya ta Bala Ibrahim Ringim)

Ibrahim Ringim a cikin wakar da ya yi wa PDP ya bayyana rashin amincewarsa da jam'iyyar 'yan adawa, ya ce, 'yan adawa tamkar sakainar kan ruwa suke. Kamar yadda aka sani sakaina ba wani abu ne mai amfani ba tun da bangare ne na kwaryar da ta fashe. Haka kuma, sakaina a kan ruwa yawo take tana yin duk inda iska ta kada ta. Bai tsaya a nan ba sai ya ce, jam'iyyar ANPP jam'iyya ce ta bakin ciki kuma ya siffanta ta da dabba inda ya ce kura ce wadda ko cikin namun daji ba abar kauna ba ce saboda zalunci da kwadayi, a karshe ya yi addu'ar Allah ya watsa shirinsu.

### 4.2.2 Gamayyar Jam'iyyu

Gamayya a tsarin siyasa ko sha'anin mulki yana nufin haduwar kungiyoyin siyasa ko na fannin mulki biyu ko fiye da haka domin zama guda daya. Wannan yana kasancewa a yanayin da ake da wadannan kungiyoyi a wuri guda (www. Changing mindas.org). A game da abin da ya shafi wannan an sami wasu jam'iyyun siyasa sun hade sun zama daya, sakamakon haka, aka sami wakoki masu dauke da ra'ayoyi mabambanta da yake bayyana manufa ta kin aminta da juna.

Wani lokaci akan sami jam'iyyu su zama guda daya musamman daga bangaren 'yan adawa kamar yadda Abin ya faru a wannan kasa aka sami babbar jam'iyyar adawa ta APC.

Sakamakon haka, mawakan siyasa sukan yi la'akari da wannan tsari su bayyana rashin yardarsu ga ire-iren mutanen da suka dauki wannan mataki. A lokacin da jam'iyyar CPC da ANPP da AC da kuma wani bangare na jam'iyyar APGA, suka hade suka kafa jam'iyyar adawa guda daya ta APC, bayan an yi haka wasu 'yan jam'iyyun da ba su gamsu da wannan mataki ba sun fice sun koma jam'iyyar PDP mai mulki. A dalili da haka ne wannan mawaki ya mayar musu da martani yana cewa;

Wadanda suka fice daga jam'iyyarmu suka koma wata sun nuna ba su yarda da Allah ba, ba su yarda da cewa Allah ne yake bayar da mulki ba ga wanda ya so a kuma lokacin da ya so. Ya kuma bayyana su a matsayin shashashu wadanda ba su san Allah ba. Hakan ta sa ya ce;

39.Masu fita jam'iyya su koma PDP don ta ba su dama,
Kun ji wadanda sun raba Allah mai mulki shi ke ba da dama,
Shashashu marasa tauhidi mu Allah muka yo rike wa.
(Wakar CPC Chanji ta Yala Dan Kaduna)

A cikin baiti an 14, da 64, da kuma baiti na 109 na wakar *Sungumin Bugun Lema* wadda Aminu Ibrahim Dandago ya yi, ya bayyana yadda hadakar jam'iyyun siyasa ta auku aka samar da jam'iyyar APC da ya ce za ta kwato wa mutane 'yancinsu domin ya yi alwashin cewa, babu wata jam'iyyar da ta kai ta su girma a halin yanzu. Ya kara da cewa, tun da sun hade za su yunkuro ta yadda za su karbe

mulki daga hannun jam'iyya mai mulki. Ya yi wannan bayani a kokarinsa na fadakar da mutane su hankalta da abin da jam'iyya da take mulki take musu domin su rabu da ita su karbi ta sa jam'iyyar domin samin aminci. Ga abin da ya ce:

14.Tsarin da kukai a baya tufkar ta warware,
Za mui saka ta jam'iyya bana da farin zare,
Mun hada karfi guri guda ku ji mun tsattsare,
Dukkan dan jam'iyyarmu tabbas zai murmure,
An daina bugunmu bana da iccen tumfafiya.

64.An rufe kofa da kwartuwa kwarto na gani,
Ni na san dai a caca ba a yin lamuni,
In kuma an ce da masu yi to bana ma gani,
Makera jirgi daban da gun kera gArewani,
Ina jam'iyyar da tai ya tamu a Nijeriya.

109.Muna da kahon yin karo da kowa a kasa bana,
Bajiman shanu muke da su duka ba karsana,
Wa za kui wa hayaniya ko ko barazana,
Mun hada karfin takaita karfinku ta ko'ina,
Ku yi maza ku saki ku sallama mana Nijeriya.
(Sungumin Bugun Lema APC ta Aminu Ibrahim Dandago)

## 4.3 Bijire Wa Shugabanin Mulkin Siyasa

An bayyana shugabanci da cewa "wani abu ne da ya shafi mu'amala ta yau da kullum a inda mutum zai nemi taimako da goyon bayan sauran mutane domin sauke nauyin da yake kansa. Misali, wasu suna da fahimtar cewa, shugaba mutum ne da yake da mabiya ko kuma mutumin da yake  yi wa mutane jagora ko taimako. A cikin duniya, kowace al'umma tana da irin nata tsarin shugabanci,

shugabanci ya iya zama jagorancin al’umma ta fuskar addini ko siyasa ko kuma jagoranci na kamfe domin yakin neman zabe.

Nuna bijirewa a tsakanin ‘yan siyasa ba ga harkar zabe da kamfe ta tsaya ba, Abin ya kai har ga shugabanni saboda irin shugabancin da suke gudanarwa na nuna rashin tausayi da adalci. Bisa wannan fahimta, wasu shugabannin ba su iya sauke nauyin da aka dora musu na hakkokin talakawa. Wannan ya sa a cikin wasu wakokin siyasa aka bayyana alama ta rashin yarda da haka, har ta kawo ake kokarin yin bore ko wani abu makamancin haka. A cikin wakar Jibrin Jalatu ta *Mafarkin Mulki* yana cewa:

5.A yanzu zamanin nan, in ba ka son gaskiya hakika,
Kome kake bukata, ka zo da toshiyar baki in ba ka,
Kafin a bincike ni, babu kowa a daure fuska,
Idan ka nuna taurin kai, zan dau kudi in ba ka,
Idan ka fandare mun, zan sanya a addabe ka,
Ni in na kafa hukuma, wadda zan sa ta bincike ka,
Saboda gaskiyarka, za ta sa ka sha azaba.
(Wakar Mafarkin Mulki ta Jibrin Jalatu)

Ire-iren shugabannin da ake da suke nan a halin yanzu, idan ka fadi gaskiya kai mai laifi ne haka kuma idan ka ki aiki da karya nan ma ka yi laifi. Da zarar ka ki yin abin da ake so sai a nemi a raba ka da rayuwarka. Irin wannan rashin gaskiya da yake wakana a cikin kasar nan, shi ne mawakan suke kokarin bayyanawa domin a bijire wa shugabannin.

A gaba kuma, Aminu Ala ya nuna irin yadda zalunci yake wakana a cikin al’umma, ya nuna yadda danniya ta yi katutu a cikin tsarin da suke gudanarwa, da abin da ya ce:

30.Allah wanga kashin mulki,
Ya yi kama da kashin dankali,
Na sama ya danne na kasa.
(Wakar Baubawa Burmi ta Aminu Ala)

A gaba kuma sai Abdulaziz Ningi ya ce:

10. Mun kama bauta mu nai kuma babu tsira ba,
Ba Annabawa ba ne, kuma ba Sahabbai ba,
Balle mu ce za su kai mu zuwa ga tsira ba,
Ba wadda zai ma karatu ba da koyo ba,
Don mi muke bin su mui ta zama na hawa.

11. Mun bi su da mun gwada, ba su bar mugunta ba,
Wasu sun bi, sun sake bi, ba su canza riga ba,
Duk wadda yai kuskure in ba da gangan ba,
Bai sake yin kuskure in ba da keta ba,
Ya za mu zabe su, sun kuma mai da mu bayi.

15.Kimar mutum dan Adam an yi ta mai girma,
Kaf yau cikin duniya, an san mu mun girma,
Ga dukiya kaf a yabe kasarmu akwai dama,
Yau ga shi Nijeriyar talakanmu na fama,
Domin rashin shugabanci, dole mui sanyi.
(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdu'aziz Abdullahi Ningi)

Abdullahi Ningi ya caccaki shugabanni ya bayyana finjirewarsa a kansu saboda rashin tafiyar da tsari mai kyau na mulkin talakawa. Yau Abin da talaka yake yi wa shugaba a Nijeriya ya zama kamar bauta, bautar da ba ta samin tsira ba iyakarta nan duniya, domin haka sai ya ce "Wai me ya sa har yanzu ake tafiya a haka." Kamar yadda ya ce shugabannin da ake da su mamugunta ne ba sa yi wa talakawa amfani sun bar su cikin bakin talauci, a karshe sai ya ce tun da su suka zabi shugabannin nan kuma suka mayar da su bayi, za su ga yadda za a sake nemansu su sake zabensu don haka karo na gaba sai an yi canji.

A gaba kuma cikin baitoci biyu (baiti na 24, da na 25.) mawakin ya bayyana yadda shugabanni suke badalin rayuwa da dukiyar talakawa suna yin bushasha

tamkar babu matsalar kowa a gabansu, ya ce sun manta da cewa kafin su yi shugabanci wasu ne suka yi suka ba su kamar yadda su ma za su ba wa wadansu wata rana. Ya kara da cewa sun hau mulki sun kankane, Abin ya kai matsayin da ba su son su ji an ce wani yana neman mukamin nasu. Abin sha'awa a karshe mawakin sai ya yi tauwakali a madadin talakawa ya ce, mulki dai Allah ne yake bayarwa ga wanda ya so a kuma lokacin da ya so, ga Abin da ya ce;

24. Ita duniya hira ce wasu har da tabarma,
Cin duniyar ya musu sun dora bargo ma,
Sun shimfida sun baje, kar wadda zai hau ma,
Su ji suke sun haye, sun tara mai dama,
Da can fa kamun ku yi, wasu sun riga sun yi.

25. Su ji suke sun buge, hagu har zuwa dama,
Kuma ba su kaunar a ce wani ma yana nema,
Wataran da ku za a je rokonsu alfarma,
Don lokacin ba ku yi, kun tsufa ga girma,
Allah yake ba mutum in lokaci ya yi.

(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdul'Aziz Abdullahi Ningi)

A cikin wakar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* Haruna Aliyu Ningi ya yi daidai da masu goyon bayan zarcewar da Obasanjo ya shirya yi a kan mulki. Ya ce mutane sun ki Allah sai fajirci sun kuma mayar da kasa da arzikinta tamkar kashin wani abu kowa ya debi nasa. Ya fada cewa, babu jin kunya yana iya nuna duk wadanda suke goyon bayan wannan shiri, a cewarsa Abin ya zama tamkar munafurci domin a lokacin da Shugaban kasa Abacha ya ayyana zarcewa a kan mulki sai mutane suka ce a'a, amma kuma sai ga shi yanzu lokacin Obasanjo ya ce zai wuce kuma sun yi na'am. A gaba ya zayyana sunayen 'yan gaban goshi na wannan shiri. Ya yi Allah wadai da wannan manufa dalili kuwa shi ne, a cikin kundin tsarin mulki na kasa babu tazarce wa'adi biyu kawai mutum zai yi ya sauka, a

karshe ya ce muddin ba a fasa tazarce ba, su ma ba za su fasa ba su yarda ba, kamar yadda ya ce;

3. Da akwai wasu gungun ‘yan kasarmu a bar kauna,
Ba su yarda da Allah ba, sun mai da kasarmu kamar waina,
Yau na daga yatsana, ku zo a idonku in nunnuna,
Sun bad da Abacha a da, a yanzu ma ba su kyale ba.

4.Farkonsu akwai Mantau, ban mance tsiyar da ya shuka ba,
Na biyunsu akwai Ojo, dama ba mu san shi da kishi ba,
Sai Tom kuma and Jerry, ba wai na Fred da Quimby ba,
Da babu tawagar nan, da mu ba mu sami tazarce ba.

24.Wa’adinmu na da na nan, idan ka yi sau biyu shi kenan,
Ba a dagula tsarin ba, ka ce mana ba ka cikin wancan,
In ba ka cikin wancan, to mu kuwa ba mu cikin wannan,
To, idan ba ka fasa ba, mu ma ba mu yarda mu kyale ba.

34.To mun dasa aya yau, kuma mu hana maku morewa,
In har ku ka ce lallai sai, kun bi ta kanmu a zarcewa,
Komai ya biyo baya, ku ne asalinsa a somawa,
In kun gaza jurewa, oho ba mu damu ku jure ba.

38. Ki ja ni mu je ganga haru, in rabarbaza baitina,
In biyo ta kasan nan kaf, domin in gwada musu ‘yancina,
Duk wanda ya tanka min, in bangare kansa da dutse na,
Ku biyo ni mu ce Olu, mu kam ba mu yarda ta zarce ba.

39.In ka cire gwamna don ya ce, ba su yarda ta zarce ba,
Ka kwace mukaminsa, amma ka sani ba ka zarce ba,
Ko ka baza tsari NASS, ba za ya saka ku, ku zarce ba,
In su suka kyale ku, mu kam ba mu yarda mu kyale ba
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A kokarinsa na jaddada goyon bayansa da rashin son shugabannin wancan lokacin su yi tazarce a kan mulki, mawakin ya ce, ba su yarda a zarce a kan mulki ba, idan kuwa aka ce za a yi to duk Abin da suka yi sai a zargi masu son ta zarce. Ya kara da cewa a shirye suke su yi fito-na-fito da kowane ne a kan manufar ta zarce,

domin ba su yarda ba. A karshe ya yi kashedi da cewa, duk wanda ya kyale ta zarce ya yi ne don a kan kansa, amma su ba su yarda tazarce ba kamar yadda ya kawo a cikin baitoci na sama.

### 4.3.1 Rashin Kishin Kasa

Rashin kishin kasa akida ce ta rashin son kasa, rashin kishin kasa ya hada da mabambantan manufofi na kin nuna sha'awa wajen ci gaban kasa. Rashin kishin kasa ya samo asali tun lokacin da mutane suka ce, ma damar mutum an haifi shi a cikin kasa ba dole ba ne sai ya zama mai kishin kasa ba (www.answers.com) .

Rashin kishin kasa matsala ce da take yi wa kasa illa sosai. A duk lokacin da aka ce son rai shi ne a gaba idan aka kwatanta da son da ake yi wa kasa an sami matsala. Abin da ya fi kyau shi ne, a kowane lokaci, shugabanni da mabiya ya kasance suna son kasarsu ta haihuwa wannan zai sa su yaki duk wani mutum ko wani abu da zai iya kawo wa wannan kasa tasu matsala. Da alama irin wannan rashin kishin kasa ne ya sanya wasu daga cikin shugabanninmu suke yi wa kasar zagon kasa da yake barazana ga dorewarta.

Hakan ta sa wasu mawaka suka fahimci cewa bari a yi amfani da wannan rashin kishin kasa da yake damun wasu shugabanni a fadakar da talakawa, domin a nuna musu cewa ba za a aminta da irin wannan hali nasu ba, domin haka a bijire musu.

Da farko an ci karo da wakar Mafarkin Mulki ta I ta Jibirin Jalatu a inda yake cewa;

6.Tsaro a zamani na a kashe kowa a kan abin shi,
Ni na ci, na yi dadin, na kwanta ina ta nishi,

Saboda takama, ba mai cewa da ni ka tashi,
Ka ji wahalalli, wai in wa kasarmu kishi,
Wata karuwa ta ce ban kurdi in gyara gashi,
Ko dan ten milyan of dolas, ko kuma ukuba.

11.A da muna da noma na auduga, an san da mu a duniya,
Kasarmu na da noman gyada, an san da mu a duniya,
Ga uwa uba noma, kiwo, an san da mu a duniya,
Kasuwanci ma kasa-kasa, sun san da mu a duniya,
Da dai na fara mulki, komai sai ya sauya,
Na durkusar da gaskiya, ta rusuna wa karya,
Wanda ke da gaskiya, yanzu shi za ya sha azaba.
(Wakar Mafarkin Mulki ta I ta Jibrin Jalatu)

Kamar yadda baitoci na sama suka daukko bayani, sun bayyana cewa a lokacin mulkin wadansu shugabannin babu tsaro a cikin kasa, babu Abin da suka saka a gaba sai hadama da gadara da kuma shashanci da warwason dukiyar mutane, domin babu ruwansu da kasarsu ko ta ci gaba ko kuma ta mutu. Ya kara da cewa sun rugurguza tattalin arzikin kasa gaba daya sun daukko karya sun aza bisa gaskiya, mai gaskiya shi yake shan wahala.

Aliyu Ningi kuwa waiwaye adon tafiya ya yi a kan Abin da yake faruwa a kasar Nijeriya ya ce, kasashe da yawa a cikin duniya sun ci gaba sun bar Nijeriya a baya. Ya yi bayanin cewa, wadansu kasashen suna fama da yaki, wadansu kuwa takunkumi na karya tattalin arziki aka kakaba musu, amma duk da wadannan matsaloli tattare da su, sun ci gaba sun bar Nijeriya a baya wannan ta sa ya yi tambaya cewa, shin wai me ke faruwa ga Nijeriya ne? Bisa fahimta amsar da Ningi zai sami a nan ba ta wuce ta cewa, rashin kishin Nijeriya da 'yan Nijeriya suke yi ne ya kai ta ga halin da ta sami kai a ciki a halin yanzu. ga dai Abin da ya ce;

12.Wasu sun yi nisa duk sun wuce mu,
Wasu na ta yaki, amma har sun dara mu,
Wasu har da takunkumin ma sun wuce mu,
Shin me yake faruwa Nijeriyata, iye,
Shin me yake faruwa Nijeriyata, iye.
(Wakar Hawaye ta Haruna ta Aliyu Ningi)

A cikin baiti na 6, da na 29 na cikin *Wak*ar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi  ya kara fito da rashin kishin kasa da shugabanni suke nuna wa musamman a kokarinsu na raba kawunan talakawan Nijeriya wanda haka ta sa ya yi bayani da a finjire musu. Ya nuna cewa, shi a kan kansa ba zai guje wa 'yan uwansa 'yan Nijeriya ba yana nan tare da su duk dadi duk wahala kamar yadda ya ce ba zai taba bin masu tazarce ba. A ta sa fadar, bin masu tazarce a wurinsa daidai yake da cin amana, hakan ta sa ya ce;

6. Allah da ya tara mu, ya bar mu kasarmu guda tare,
Ya bar mu da jinsi dai, amma ya raba mu a kan yare,
Duk wanda ya daddage, sai ya raba kanmu zaman tare,
Ba zai wuce makonni kadan, bai tadda jafa'i ba.

29. In zan yi Gadara ta, ai dole in yi da kasar nan ne,
In zan gwada kishina, to za ni gwada wa kasar nan ne,
Har ban taba mulki ba, in kare kasarmu farilla ne,
Ba zan ci amana ba, ba zan biye masu ta zarce ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

Kamar yadda aka bayyana a baya, da yawa daga cikin shugabannin wannan kasa a halin yanzu, ba sa son kasar su kansu suke so. Wannan ta sa suke yin kunnen shegu da duk wani abu da yake faruwa tunda ba taba su yake yi ba. Irin wannan manufa ta sami tsokaci a cikin wakokin siyasa na wannan zamani. misali;

5.Da shi da tsohon kwano na unguwar Yakasai bula,
Ba ya gane kamshin abinci amma ya san dala,
Ana ba shi kudi ya jefa yankin shi a matsala,.
Mai bleaching Sanata ta gwangwani an shiga matsala.

(Wakar APC Zuwan Mai Malafa Kano ta Dauda Kahutu Rarara)

Dubi dai Abin da wannan mawaki yake zargin an yi, ana cikin wannan hali na neman mafita amma a daukko wadansu mutane ana ba su mukami suna karba alhali yankunan da suka fito suna cikin wani hali na rashin tabbas.

A gaba kuma wakar APP ce kamar haka;

8.APP jam'iyyar masu fahimta,
Ba ta bidar munafukai sam a cikinta,
Don ita tsai da gaskiya ne manufarta,
Don haka ne ta tsere dukkan sa'anninta,
Da ba sa kishin kasarsu wato Nijeriya.
(Wakar APP Kishin Kasa ta Bashir Sani Ringim)

Shi kuwa wannan mawaki yana bayyana cewa, 'yan jam'iyyarsa masu kishin kasa ne, ba kamar sauran jam'iyyu ba da suke da munafukai da marasa gaskiya a cikinsu wadanda ba sa kishin kasarsu. Kamar yadda ya bayyana 'yan APP masu kishin kasa ne don haka yake nema a bijire wa sauran jam'iyyu wadanda ba sa kishin kasa.

Har yanzu dai a game da zuwan mai malafa kano, ga Dauda Kahutu Rarara;

5.Don ana gobe zuwan shi ma a 'Yanya kuka ake,
An karkashe rayuka su solo ko rawa yake,
A rannan jama'a ta Barno jajen 'ya'ya suke,
An sace 'ya'yansu shi ko yawon kamfen yake,
(Wakar APC Zuwan Mai Malafa Kano ta Dauda Kahutu Rarara)

A nan kuwa, duk da cewa a cikin waka ne amm mawakin ya nuna kininsa da hushinsa a kan abin da aka yi, ya ce shugaban Nijeriya yana yawon kamfe a cikin Nijeriya bayan ga wani bom ya tashi a wani yanki, yankin kasarsa amma sai ga shi yana rawa wai su kamfe suke yi. Da alama irin wannan ne ta sa wannan

mawaki yake kokarin fadakar da mutane da a bijire wa irin wadannan mutane domin ba sa tausayin na kasa, kansu kawai suka sani.

A game da 'yan yankin Arewa kuwa da suke nuna rashin kishin kansu kuwa, ga abin da aka sami. Wannan ya hada da yadda mutanen yankin Arewa a cikin tarayyar Nijeriya suka nemi su mayar da kansu 'Kudi ya fi Mutunci.' ana iya gane wa haka idan aka yi la'akari da cewa, yankin Arewa da yake da yawan al'umma da fadin kasa fiye da sauran yankuman Nijeriya amma duk da haka an wayi gari ba mu da wani tasiri na a zo a gani a game da yadda ake tafiyar da mulkin yankin tun lokacin da aka dawo mulkin dimokiradiyya har ya zuwa yau.

Irin wannan rashin kishi na mutanen Arewa mawakan siyasa suka saka a faifai suna bayyana ra'ayoyinsu domin mutane su fahimta, a taru a bijire wa ire-iren wannan rashin sanin kai da wasunmu da ake ganin su ne shugabannin mu suke yi.

31. Duk wahalar da muke ciki yau to dan Minna ya saka mu fama,
Wai burinsa ya wanke laifi na jun tuweb a wurin na yamma,
Yau san kanka ya sami halin da za a dade babu warwArewa.

32. Dubi halin da ya sa Arewa ya mance takara zai yowa,
Wai Baba me ka bari hakika da za mu bari har kayo wucewa,
Koma ka kare yakin gidanka gwamnanka zai kai ka kushewa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dankaduna)

Lokacin da Nijeriya ta dawo mulkin Dimokiradiyya, yankin Arewa ya sami dama babba wanda ya kamata ya shugabanci kasar nan, a kokarin wanke kai da shugabaninmu na Arewa suke kokarin yi a wurin takwarorinmu na sauran yankunan Nijeriya, saboda laifin da suke ganin sun yi musu. Sai son zuciyarsu ya rinjaye su ba tare da tsinkayen irin Abin da zai kai ya koma ba, suka dakko wani

mutum daga kudu suka nuna a matsayin dan takara kuma Allah ya nufa aka zabe shi, yau ga halin da muka sami kanmu a ciki.

A cikin wakar *CPC Chanji* mawakin ya bayyana ra'ayinsa a game da yadda yake ganin shi ne ummul haba'isun wannan hali na nadama da aka shiga a siyasance. Da yake bayyana ra'ayinsa mawakin ya yi nuni da cewa wannan mutumi da ya saka mu cikin wannan hali da muke ciki a yanzu ba za mu taba amince masa ba nan gaba. Ya fadakar da mutane kan a bijire masa da kuma duk wani abu da zai sake kawowa nan gaba. Ya ce duk da cewa ba a taru aka zama daya ba, akwai wasu sarakuna da ya ce ba zai fadi sunansu ba wadanda suka so a sami canji a Arewa, a karshe ya ce, burin 'yan Arewa ya cika tun da an kashe Arewa murus. a saboda haka sai ya ce;

33. Ku dubi wadanda muke tunanin su ne manyanmu a nan Arewa,
Wanda Sardauna yai musu gata don tsabar kishin 'yan Arewa,
Irin su Baba da shi da Tanko sarakuna har da ku Nufawa.

34. Kun ga abin da kukkai gare mu girmanku kuma yai zubewa,
Akwai wadanda cikin sarakai girmansu kuma yai dagawa,
Su gurinsu a sami canji sunan ne Yale ban fadowa.

29. Burinshi ya cika ku duba ya kashe duk jama'ar Arewa,
Yau Jonathan shi ya haye mulki me za ku ce manyan 'yan arrewa,
Ummaru ko Allah ya ji kanshi kun karasa shi zuwa kushewa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dankaduna)

### 4.3.2 Rashin Adalci

Rashin adalci siffa ce ta rashin gaskiya, a kan danganta rashin adalci da wani abu da ya faru ko kuma wani yanayi da aka sami kai a ciki. Rashin adalci batu ne da yake tasowa lokaci-lokaci cikin mas'alolin masana falsafa da maluma inda suka bayyana da cewa, rashin daidaito wanda yake kishiyar daidaito ne

(www.changingminds.org). Rashin adalci ya danganta daga al'ada zuwa al'ada, ana danganta shi da Abin da mutane suka yi kamar, rashin adana wani abu ku wulakantar da shi ko kuma amfani da abu fiye da kima.

Dangane da rashin adalci, akwai wasu mawaka da suka tsara baitoci suna bayyana rashin gamsuwa da yadda ake amfani da wannan hanya ana tauye wa talakawa hakkokinsu A karshe, sun bayyana cewa yakamata mutane suke nuna rashin amincewa da ire-iren wadannan jagogrori  Misali;

8.Ina mahukunta su ma sun biye halina,
A gama murdiyar zabe da kai, ina gida abu na,
A gama kai kara a kotuna, ni za a ban abu na,
Ka daina gaskiya a zahiri sai ka zo mu zauna,
In ka ki ko, kullum kai kake a rana,
Domin a zahiri babu gaskiya kaf, al'amarina,
Gara ka zo mu zauna, in kuma kai, ka sha azaba.

9.Na zamo kamar dakin kura, sai dai na jikina,
Ministan tsaro, ni za nada da kaina,
Ministan ilimi da lafiya, zan sa na wuri na,
Ministan kudi, ni ne zan nada Abina,
Ministan sufurin jirgin sama, yana wurina,
Ministan ruwa shi ma, ni zan nada da kaina,
Idan na sanya doka, kowannensu kar ya saba.

10.Ministan ma'adannen kasa kwarai, yana wurina,
Ciyaman fetur shi ma, zan san a wurina,
Idan na tara duk gaba dayansu, zan ba su hudu bana,
Arzikin kasar nan gaba daya, mu boye kar mu nuna,
Zan ba ku fasentej mai yawa, in kun bi ra'ayina,
Wanda yak ki bi, zan sanya hukuma, da ra'ayina,
Zan takura shi, gaskiya ta zame musiba.
(Wakar Mafarkin Mulki ta Jibrin Jalatu)

Jibirin Jalatu ya bayyana irin rashin adalcin da yake gudana a cikin kasa musamman idan mutum ya kai ga kujerar mulki. Ya ce, ana rashin adalci a wajen

gudanar da zabe, wanda jama’a suka zaba ba shi ake rantsarwa ba, idan kuma ya kai kara a yi watsi da karar, a takaice murdiya ake yi a danne na kasa wanda bai san kowa ba. Haka kuma idan mutum ya hau karagar mulki sai Abin ya zama “Ramin kura daga ita sai ‘ya’yanta” sai su bi su kankane komai da komai, yin adalci kuwa bai taso ba. Haka za a yi ta tafiya, duk wanda ya nuna adawarsa da yin hakan sai a bullo masa ta hanyar da bai sani ba ya sha wahala a banza.

A gaba kuma Aminu ALA sai ya ce;

8.Sittin a cikin dari, lalura ta sa su bin dare
Ashirin a cikin dari, talauci ya sa su bin dare,
Talatin ta cikin dari, son zuci ya sa su bin dare,
Lidas sun kankane ma ma’adanai, sun dare dare,
Dukiya ta kasa da hakkokinta, sun kanainaye, sun makare,
Ga isa da cikar isa da alfarma, sun tattare,
Shi ya haddasa sace-sace, a ko’ina tamkar ruwa.
(Wakar Bubbukuwa ta Aminu Ala)

A kokarinsa na bayyana bijirewa ga Shugabanni saboda rashin adalci, Aminu ALA ya ce, shugabanni sun kanenaye dukiyar kasa sun tare ta tsab a wurinsu, sun bar talakawa a cikin wahala da rashin abin hannu ga talauci. Sun kame komai sun rike wannan ya jawo mana masifu iri-iri a cikin muhallinmu kama daga sace-sace da banga da sauran munanan abubuwa kamar yadda ya bayyana a cikin baiti na sama.

A gaba kuma an ci karo da Abdullahi Ningi da yake cewa:

Abdullahi Ningi ya ce, tsarin siyasar Nijeriya a halin yanzu ya zama nadi ba zabe ba, don haka za su yi duk mai yiwuwa ganin an sami sauyin wannan al’ada, ba za su kara yarda da duk wani nau’i na rashin shugabanci marar tsari ba. Ya ce komai

yana da lokaci, ya kamata shugabanni su fahimta cewa idan yau su ne gobe wadansu ne, babu wanda zai dauwama a kan mulki duk tsawon lokaci sai mutum ya sauka a ba wa wani kamar yadda yake cewa:

3.Wannan dimokiradiyyar hanyar akwai kurdiya,
Da'awarsu kullum nadi an tara 'yan danniya,
Kuma babu mai dawwama ko kara kwana daya,
Na tabbata ba dole ne gun mai rashin gaskiya,
Za mu wanke Jumhuriya bana lokaci ya yi.

4.Ra'ayinka kaunar mutum damar ka ce dan uwa,
Shin wane ne zai mana, ko zai idan yawa,
Ku zubar batun jam'iya ba ma kawancen kawa,
Kun daina bautar gumakai ba mu bin wawa,
Sai wanda zai taimaka wa kasarmu in ya yi.
(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdu'aziz Abdullahi Ningi)

A cikin wakar *Siyasa Rigar 'Yanci* mawakin ya bayyana yadda za su yi maganin wa-ka-ci-ka tashin da ake musu a tsarin gudanar da mulkin siyasa a Nijeriya. Ya bayyana cewa duk wanda ya ce musu "kule za su ce cas," domin ya ce, sun fahimta tsarin kamar kungiya ce da zarar ba ka ciki to taskun duniya ya kare a kanka. Ya ce a wannan lokacin babu zancen jam'iyya sai dai mutum domin haka a shirye suke su kawar da zaluncin da ake yi musu hakan ta sa ya ce;

3.Sha'anin dimukradiyyar an mai da shi cudi,
Fasalin a Nijeriya ya zam kamar shinge,
Wadda bai cikin kewayen sai dai a mar kage,
Motar dimukuradiyya tayarta na goge,
Tibidnta zai bindiga wasu wa'adi ya yi.

22.Ba yadda za ai kashi bai zam kamar gyara,
Wadda an yi mar zalu kam, tilas ya kai kara,
Duk wadda yai kuskure tilas a mar gyara,
An daura aure waliyyai na jiran gara,

Wasu sun tsaye kan kwana an toshe hanyoyi
(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdul'Aziz Abdullahi Ningi)

Haurna Aliyu Ningi kuwa a cikin tasa wakar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* hannunka mai sanda ya yi wa shugabanni da cewa su tuna wasu ne suka sauka suka ba su mulkin kamar suma yadda za su ba wa wasu. Ya ce idan suna kan mulki ba ruwansu da kowa babu taimako ba adalci babu sauki, sai maganar zabe ta taso su zo suna yi wa mutane ladabi a sake zabar su. Yana fadar haka domin fadakar da mutane da su bijire wa ire-iren wadannan mutane a duk lokacin da suka nemi komawa kan mulki sai ya ce;

23.To in ban da ana sauka, a bai wa wadansu su dana su,
Ba za ku yi mulkin ba, bare ku mayar mu kamar kumba,
To, babu ta zarcewa, idan ba dai a kiyoma ba,
Ba ku tsai da amana ba, mu ko ba za mu ji kunya ba.

39.Son kanku kuke sosai, ba kwa kula da wanda kuke mulka,
Sai kun ji dirin ganga, a na ce kun yi kusan sauka,
Duk sai ku dubulbulce, ku fara abinku kamar hauka,
Ya za a yi ne nema, a ce ba za ku ji kunya ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A cikin wakar da ya yi, ya yi tofin Allah tsine ga wadanda suka amince da wannan shiri na tazarce, ya ce ba za su ji kunyar fallasa duk wani shugaba da ya shiga cikin wannan tsari komai girman mukaminsa. A karshe ya yi Allah wadai da 'yan sanda, ya ce suna cikin hali na kunci dangane da yanayin aikinsu, amma ba su farga ba, su ake sakawa suna harbin mutane domin su kare azzaluman shugabanni, dangane da haka sai ya ce;

44.To ku kyale ta zarce, tun manya ba su fara kashedi ba,
To idan suka fara, mu yaransu ba za mu ji shakka ba,
Mu rugurguza ko waye, bai amsa abin da ya dace ba,
Harka ta butulci ce, mu ko ba mu gaji butulci ba.

45.Sai soja da 'yan sanda, su ne suka yarda ku kare su,
Sun bata kasan nan kaf, kuna kallo kuka kyale su,
In za mu fito mu fada, su sa ku kashe mu ku kare su,
Ku gama ku ritaya, ba za su biya ku na fansho ba
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

### 4.3.3 Yin Mulki

Tsarin mulki a cikin kowace al'umma wajibi ne. Mulki ne kadai zai tabbatar da zaman lafiya yadda kowa zai sami damar yin harkokinsa na yau da kullum, domin neman abinci da arzikin duniya. Wato idan babu mulki a al'umma, to rudani da yamutsi da hargitsi da cutar juna ne za su tabbata. Idan haka ya afku, sai al'umma ta kai ga halaka don babu wanda zai sami sukunin neman abinci ballantana arzikin kasa Yakasai (2012:51).

Domin a sami cikakkiyar lumana da tabbatar zaman lafiya, ya wajaba a sami fahimtar juna a tsakanin masu mulki da wadanda ake mulka. A duk lokacin da aka ce an rasa fahimta musamman daga bangaren masu mulki a kan wadanda ake mulka, abu na gaba da za a sami daga bangaren talakawa wadanda ake mulka shi ne, kin daukar umarni da masu mulki za su bayar, sakamakon haka sai su bijire wa hanyoyin da ake bi ana gudanar da mulkin. A kan haka ne aka hangi wadansu baitoci cikin wakokin jam'iyyun siyasa na Jumhuriya ta hudu an bayyana yadda mawaka suke bayyana halin da ake ciki wanda hakan ta sa suke kiran mabiya da su bijire wa mulkin da bai gamshe su ba. misali;

A cikin wakar Haruna Aliyu Ningi ta Shegiyar Uwa PDP yana cewa;

15.Yanzu jam'iyyar an kashe tushiyarta,
Ta balangwaje an rasa hankalinta,

Kan ta karkashe mu gara mu karta,
Tun da mun farga!

20.Jam'iyyar ta zarce bana babu kanta,
Ga shi nan gaban za mu fatattake ta,
Kan ta kar kasar gara kasarmu ta kar ta,
Mun kashe maciji ba mu sare kansa ba kun ga.

39.Mai kiran dadi kar mu sake mu ba shi,
Ko ku shirya zabe badi ko ku bar shi,
Dole-dole sai kun tafi babu fashi,
'Yan kasarmu mun hallara za mu kau da ke kurga.
(Wakar PDP Shegiyar Uwa ta Haruna Aliyu Ningi)

A game da yadda zababbun shugabanni suke gudanar da mulkin talakawa ya nuna tamkar suna yi ne ba bisa manufofin siyasar da aka zabe su a kai ba, suna aiwatar da nasu manufofin ne na kashin kansu, domin haka abin ya zama kama-karya. Irin wannan manufofi nasu, su suke karya jam'iyyar su kuma kashe sauran 'yan jam'iyya ta hanyar mayar da su ba komai ba. Haka kuma, su kashe kasar saboda son zuciyarsu yana gaba da kishin kasar. Wannan ta sa Haruna Aliyu Ningi yake fadakar da mutane da su yi watsi da irin wannan tsari kuma a taru a kawar da shi domin ci gaban kasa.

A cikin wakar APC maganin PDP ga abin da aka sami:

3. Ga sabuwar jam'iyyar gaskiya,
Mai kwato 'yancin 'yan Nijeriya,
Mai maganin 'ya'yayen bushiya,
Mai kau da berayen Nijeriya,
Ta kau da 'ya'yan sharri,
APC kin hade kan Nijeriya.

9. Sai dadin baki ba gaskiya,
Ba sa bida gun Allah ko daya,
Gurinsu kwashe kudin Nijeriya,
Su kai su can waje mu kau ko daya,

Talakka ba mu fahimta mun tabbata fa ba sa kishin mu ko daya.

10. Yau rana tai tsayuwa kan gaskiya,
Allahu ya kama ku da daidaya,
Duk wanda yac ci amanan Nijeriya
Wallahi ko ta ina zai sha wuya,
To ba batu na mu yafe ai ko'ina fa ba ku da kishin gaskiya.
(Wakar APC Maganin P.D.P. ta Funtua)

A cikin wannan waka an bayyana irin bijirewar da ake son a yi wa masu mulki a wannan kasa musamman talakawan kasa. Jam'iyyar adawa ta bayyana cewa, za ta kwato 'yancin talakawa daga wurin masu mulki wadanda ta bayyana da cewa azzalumai ne kuma 'ya'yan tsiya barayi masu sace dukiyar talakawan Nijeriya. Sun kuma ce za su kawar da shugabannin jam'iyyar masu mulki a duk lokacin da aka sake zabe domin an bayyana su da cewa, 'yan sharri ne marasa son dorewar Nijeriya. Haka kuma, sun ce, 'yan jam'iyyar da take mulki ba su da gaskiys ga rashin tauwakali ba su san komai ba sai satar kudaden kasa sun bar 'yan kasa cikin talauci, kuma ba su kishin gaskiya, kamar yadda bayani ya fito cikin baitocin da suke sama.

A cikin wakar jam'iyyar ACN da aka yi wa Dalhatu Bafarawa an bayyana bijire wa masu mulki ta hanyar yin addu'ar Allah ya wargaza su, ga dai Abin da aka fada;

12. Allah muna addu'a tarwatsa mulkin ja'irin nan,
Ka karya dukkan shirin da suke yi a cikin kasar nan,
Ka sa masu damuwa sa su fada da junansu sannan,
Wanda ke handama zalunci bakin ciki yai ta yowa.
(Wakar ACN ta Bafarawa)

A cikin wannan baiti an yi addu'ar tarwatse mulkin 'yan jam'iyyar da take kan mulki, kuma an bayyana bukatar lalacewar duk wani shiri na sharri da suke kawo

wa cikin kasar nan. Haka kuma an yi addu'a Allah ya saka musu damuwa a cikin harkokinsu, su kuma hadu da bakin cikin tun da zaluntar talakawa suke yi.

A gaba kuma jam'iyyar PDP ce ta yunkuro da bayyana tata bijirewar ga 'yan adawa kamar yadda ta ce suna son bata kasar nan. Mawakin ya bayyana cewa, saura kadan 'yan adawa su sami ikon tafiyar da harkokin mulkin kasar nan sai tasu jam'iyyar ta sami dama wanda hakan ya sa ta ceto wannan kasa kamar yadda ya fada a kasa inda ya ce;

34.Tsuntsaye suna kuka jama'a sun kasa ganewa,
Jemage ya zo yai nasa mutane na ta tafawa,
Wai shi ne cikakken tsuntsu assha in ji Hausawa,
Saura kis ya bata kasar sai ga canji ya shiga kasa ta.
(Wakar PDP Bakandamiya ta Shu'ibu 'Yanmedi)

Haka kuma a cikin wata waka ta PDP mai suna *Bulaliya* marubucin wakar Bala Ibrahim Ringim, ya bayyana rashin yardarsu da abokan adawa inda ya kira su miyagu. Ya ce su ne a matsayin dutsi 'yan adawa kuwa su ne kwai, don haka, ya ce a buga su ga wanda zai ja da baya, wannan yana nuna raunin 'yan adawa ne ta yadda ba za su iya gudanar da mulkin kasa ba, domin haka, a yi hattara, kamar yadda ya kawo a cikin baiti na kasa:

3.A kanku miyagun kasa tsiya ce zan zazzaga,
Kun riki kwai mu muna da dutsi a buga mu ga,
Za mu ga mai ja da baya in wahala ta shiga,
Yau ba ku gaskiya ba za ku ji dadinmu ba.
(Wakar PDP Bulaliya ta Bala Ibrahim Ringim)

Jam'iyyar CPC kai tsaye ta bayyana bijirewarta ga jam'iyyar PDP wadda ita take kan mulki. Ta bayyana wa duniya cewa, za su shimfida adalci a cikin kasa, kuma za su kawar da duk wata barna da suke zargin jam'iyya mai mulki ta kawo wanda

ya hada da shan-jinin talakawa da kuma satar mutane kamar yadda Yala Dan Kaduna ya fada a cikin baiti na kasa:

41. In muka kau da mulkin PDP adalci za mu shinfidawa,
Mu CPC ba ta shan jini ba, jam'iyyar taimako ga kowa,
Ba mai kara satar 'ya'yanku duk fa gaba za kuyo gujewa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dankaduna)

A gaba kuwa wata jam'iyyar adawa ce ta nuna rashin yardar ta da manufofi na shugabancin jam'iyyar da take kan mulki. hakan ce ta faru a nan, jam'iyyar AC ce take bayyana irin bi-ta-da-kulli da ake yi wa 'yan kasa musamman wadanda suka ki amincewa jam'iyyar PDP ta zarce a kan mulki. Ya kalubalanci masu yin mulkin da cewa, ba sa yi wa 'yan kasa aikin komai duk ayyukan da suke ikararin sun yi a kan takarda suke babu komai a kasa. Ya kara da cewa, sun daura aniya za su kawar da masu zaluntar talakawa ko a sami a zauna lafiya cikin kasa. Wannan bayanai ya zo a cikin baitoci na kasa kamar haka;

35.Third-Term ta mutu ka kasa barin wannan shiri,
Bita-da-kulli yanzu ka samo ga mugun sharri,
Komai za ka yi wa kasan nan gobe kana bari,
Zabe na zuwa sai mun yi ko ba ka kiran talakawa.

40.Wannan gwamnatin aikinta cikin paper yake,
Komai za ta yi mana sai da mutanen tsallake,
Masu zuga shi ne ya saka mu a halin ya take,
Sai mu yi hattara mu kawar su mu zauna lafiyarmu da kowa.
(Wakar AC Jam'iyyar Talakawa ta Haruna Aliyu Ningi)

### 4.3.4 Yaudara

Yaudara tana nufin hali na boye gaskiya da niyyar cuta ko zambatar wani (Kamusun Hausa 2006:480). Mawaka na ganin dacin duniya yaudara ne. Dalilinsu kuwa shi ne, ba ta nuna wa masoyinta akwai dadi da daci, dadi kawai za ta ba shi. Ba ta shawartarsa lokacin da za ta ajiye dadi balle ya shirya shan daci.

Don haka, akwai yaudara sosai a ciki. Da masoyanta sun yarda da tana yaudara, da ba za ta yaudare su ba ta raba su da ‘yan uwansu da abokansu da masoyansu idan ta waiwayo su, su waigo su ga ba kowa tare da su Bunza (2012:131-132). A cikin wakokin siyasa an lalubo inda mawaka suka yi tsokaci a kan yaudara a matsayin halin da wadansu ‘yan siyasa da ma suyasun kansu suka sami kansu a ciki, wannan ta sa suke kira da a bijire musu ko za su hankalta su gyara. A wannan gaba za a kawo abubuwan da hannu ya kai kansu;

Ba duniya ce kawai take yaudarar mutane ba, su kansu mutane suna yaudarar kansu da kansu a wadansu lokuta musamman ‘yan siyasa. Dubi dai yadda aka kawo a cikin wannan waka ta *APC maganin PDP* yadda aka ce wani ya bayyana wa duniya cewa shi Malami ne, amma, sai ga shi yana keta shari’ar Musulunci ta cin kudin marayu da satar kudin kasa yana kuma tare da ‘yan iska a kowane lokaci. A nan, wannan waka tana yin ishara ne da cewa duk mai irin wannan hali na yaudara, musamman, a fagen siyasa ba abin yarda ba ne bare a amince masa, misali a cikin wakar APC mawakin yana cewa:

> 5.Su wane an ce Malam amma zuciyarsu ba ta da kishin,
> Sai dai su tone kudin Nijeriya,
> Sun kai su can waje don kin gaskiya,
> Hakkin marayu sun ci gaba daya,
> Sun tattara sun kwashe gaba daya,
> Mai tattaro 'yan iska ta dan iso ta tsittsince su gaba daya.
> (Wakar APC Maganin P.D.P. ta Funtua)

Baya ga yaudarar kai da ‘yan siyasa suke yi, a junansu ma yaudarar tana taka muhimmiyar rawa kamar dai yadda aka nazarta a cikin wakar *Zuwan Mai Malafa Kano* ‘yan siyasar PDP sun gayyato shugaban kasa wanda dan jam’iyyar ne,

amma, kuma abin ya zama yaudara. Kamar yadda mawakin ya ce, dalilin da ya sa ake ganin an yaudare shi, a kusa da filin da yake lacca sai ga wasu suna yin wasan kwallo wasu kuwa ma sukuwar dawaki suke yi, wannan ya nuna ba a fadakar da mutane a game da zuwan shugabansu ba tun da shi ne shugaban Nijeriya kowa da komai a cikin kasa karkashin shugabancinsa yake. Ga abin da Rarara ya ce:

8.Don ko mu mun san shafe-shafe mu kuma mun san kala,
'Yar tiredar din ta yi caca ta tafi neman dala,
Allah sa ki yi biyu babu karuwancin yai matsala,
Zuwan mai malfa Kano ya gane ya kai kasa,
Ya waiga ya ga babu 'yan Kano a gurin ya rasa,
Suna taro ga wadansu na sukuwa a kusa,
(Wakar APC Zuwan Mai Malafa Kano ta Dauda Kahutu Rarara)

A nan kuwa 'yan siyasar adawa mawakin ya kira kai tsaye mayaudara. Ya bayyana cewa, a cikin sauran jam'iyyu ana yaudara da rashin adalci sabanin ta sa jam'iyyar ta ACN mai son ci gaba ce kuma za ta wanzar da adalci idan jama'a suka zabe ta. Wannan ta sa ya ce:

1.Talakawa a sannan mun riga mun gane mayaudara,
Mu hade mu bi tsintsiya don mu share mai yin yaudara,
A C N garkuwa ce ta kare dukkan lalura,
Don zaben ci gaba za mu zabi jam'iyya mai adalci.
(Wakar ACN Jama'ar Nijeriya ta Kabir)

Ga abin da aka sami dangane da jam'iyyar DPP:

A nan ma, abin haka yake, jam'iyyar DPP aka bayyana a matsayin jam'iyyar da babu mayaudara a cikinta kuma ba ta san yaudara ba ta kuma iya yin yaudara ba. Ya kara da cewa, duk sirrin sauran jam'iyyu ba wanda bai sani ba domin haka yana kira ga talakawa da su zo su shiga DPP domin tafiya ta gaskiya kamar yadda ya ce:

1.E! har yau Sakkwatawa ba ku gane mayaudara ba,
Mugun halinsu dangi ba ku ankare ba,
Amma ku biyo ni sannu ku raka da duba,
Duk kwansu wallah ba wanda ban kyakyashe ba.
(Wakar DPP, DPP a Kasa a Tsare ta Auwwal Mujaddadi)

A cikin wakar jam'iyyar CPC kuwa sai aka ce;

7. Jam'iyyar da muke ciki da mun dauka masu tallafa ne,
Mai masara jam'iyyar butulci ashe masarar duk na yaudara ne,
Sun sa Janar ya shigar da kara ashe da baya za su gujewa.

8. Sukai ta sa mu muna ta fama gurinmu mu hayar da kowa,
Ashe manufarsu su sami mulki sai su guje ba su waiwayawa,
Abin takaici da za ku duba har Indiya duk mukai rakawa.

11.Duk murdiyar da akai gare mu da sa hannun masarar barayi,
Su suka sai da zaben Buhari duk suka bar mu muna bulayi,
Gwamnoninn da mukai azawa su suka kai mu mukai rasawa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dankaduna)

A cikin (baiti na 7, da 8, da kuma na 11) na wakar CPC Chanji ta Yala Dan Kaduna ya bayyana yadda jam'iyyar ANPP ta yaudare su wanda hakan ta sa suke bijire suka kafa tasu siyasar wato CPC. Ya yi nuni da cewa, masu son mulki ne a cikin ANPP ba masu kishin talakawa ba, ya bayyana cewa, zaben baya da aka yi wanda aka ce dan takarar shugaban kasa Muhammadu Buhari ya fadi duk hadin baki ne na mayaudara da suke cikin jam'iyyar. Ya kara da cewa, hatta gwamnonin da aka zabe su a karkashin tutar wannan jam'iyya cikin rigar Buhari suka shiga ashe duk yaudara ce ba a gane ba sai yanzu.

A nan kuma an zargi jam'iyyar PDP da azabtar da mutane domin sun ce za su kawo wa mutane yalwa ta hanyar lema sai ga shi sun bar mutane a cikin wahala, mutane suna cikin rana. Sai ya kara da cewa a yanzu kansu ya waye ba za a sake

yaudararsu ba, a karshe ya kira 'yan PDP da cewa mayaudara ne, kamar yadda ya fada;

5. Karya fure take ba ta 'ya'ya kun ji batu na,
Sun ce maku lema sannan sun bar mu a rana,
Yanzu kai ya waye mu mun canza maku suna,
Sunanku mayaudara mun gane ba ku nufin adalci.
(Wakar ACN Jama'ar Nijeriya ta Kabir)

### 4.4 Bijire Wa Rusa Tattalin Arzikin Kasa

Talauci ya sami gindin zama a tsakanin mutanen Nijeriya saboda rashin gudanar da mulki da ake ganin ya faru ne sakamakon rashin shugabanci nagari. Mutane da yawa suna cikin matsi na rashin samin kudin shiga da rashin aikin yi da jahilci da sauransu. Hakan ta sa wadansu mawaka suka bayyana rashin gamsuwarsu dangane da yadda ake samin irin wannan yanayi a cikin sha'anin mulkin kasa. ga misalai daga cikin wadansu wakoki, da farko ga wakar "Gadar Zare"

Wannan waka mai suna "Rasha Abokan Fita Kunya" ta Malam Mudi ta jawo masa dauri a gidan yari. A fahimtar Turawan mulkin mallalaka wannan sako ne da kan iya tunzura talakawa su yi bore, kuma kan iya jefa kasa cikin juyin-juya hali irin na Kwaminisanci. Mudi Spikin ya rubuta wannan waka a 1948.

A cikin wasu baitocin wannan waka za a lura cewa mawakin ya bayyana bijirewarsa ga tsarin rusa tattalin arzikin Nijeriya, musamman ire-iren tsare-tsaren da kasar Ingila ta kawo wanda ya kaimu ga rushewar arzikin kasar mu. Ya bayyana cewa, kasar Nigeriya za ta daina da hulda da kasar Ingila domin bayyanar rashin adalci daga wurinsu da rashin rikon gaskiya. Ya kara da cewa,

kasar Ingila ta bar mutanen Nigeriya babu gonakin nomawa babu kudin shiga. Kamar yadda bayanai suka nuna, a da hanyar samin kudin shiga na Nigeriya daga noma da kiwo ne, sai ga shi an wayi gari babu komia a hannun mutane an bar su cikin talauci. A gaba kuma ya ce, duk tsawon lokacin da Turawan Ingila suka yi a cikin kasar Nijeriya ba su dadi mutane da komai ba. Ga abin da ya ce a cikin waka:

19. Mu zam mun fice daga gun Ingilishi,
Mutanen da ba sa rikon gaskiya.

20. Sun bar mu babu kudi babu gona,
Babu abin yi cikin gaskiya.

21. Sun shekaru yanzu hamsin kasarmu,
Ba taimako babu son gaskiya.
(Wakar Mudi Sipikin ta Rasha Abokan Fita Kunya)

Aminu ALA a cikin *Wakar Baubawan Burmi,* ya bayyana yadda mugun mulkin da shugabanni suke yi ya mayar da talakawa suka kasance cikin talauci mai tsanani har ya zame wa mutane kamar abin gado. Ya ce, an bar talakawa cikin rashin aikin yi, mutane sun zama 'yan raraka, maganar a ce an sami wani ya hau mulki sabanin wadanda suke kai kuwa wannan ya zama tarihi, wadanda suke kai sun mayar da shi gado sai su sai na kusa da su, sakamakon wannan sai mawakin ya ce ba za a taba amincewa da haka ba. Za su fito fili su nuna rashin yardarsu da amincewarsu da irin wannan tsari haka ta sa ya ce;

14.Talauci shi muka gado,
Jahilci ko ya zamo rigarmu,
Ba mu da ikon yin mulki.

16.Balle mu ciro masharin kukunmu,
Mu dore da tumasanci,
Mabarata muke a hannun jagora.

(Wakar Baubawan Burmi ta Aminu Ala)

Aminu Ala kuwa da ya kalli irin salon mulki da ake gudanarwa a kasar nan ya dubi irin ta'annatin da ake yi da dukiyar jama'a sai ya ce, a yanzu shugabanni sun nuna ba sa kishin kasarsu, sata ta ko yaya yin ta ake a Nijeriya ga zamba cikin aminci, ga rashin tsaro, sai kashe mutane ake yi ba kakkautawa, duk wadannan matsaloli suna faruwa ne saboda ba a son kasar kuma ba a so ta ci gaba domin haka ya kawo baitocin da suke nuna bijrewa ga irin wadannan shugabanni kamar yadda ya ce;

5.barayinmu a ban kasa, atifishiyal muka kirkiro,
'Yan dabaru a ko'ina, atifishiyal muka kirkiro,
Masu 419 Arewa na kirkira, aka kirkiro,
Wahalar da muke ciki, ita tas saka suka bijjiro,
Na rashin shuwagabanni adalai, da rashin tsaro,
Rayukanmu kamar kiyashi, fagen kulawa ba tsaro,
Rabbi kai ne Rahimi, tsare kasar Nijeriya.
(Wakar Bubbukuwa ta Aminu Ala)

A gaba kuma, an sami wani mawakin da ya bayyana halin da talakawa suka sami kansu a ciki sakamakon wargaza kyakkyawar manufar gudanar da mulki da tattalin arzikin kasa da shugabanninmu suke yi. Ya bayyana yadda 'yan kasa suka zama tamkar masu bara, ga kuma tsananin wahalar rayuwa da mutanen kasa suke ciki. Ya fada cewa, saboda rashin sakuni na rayuwa, talaka ko barci ba ya iya yi ga kuma rashin aikin yi wanda yana daga cikin ummul haba'isun shaye-shaye da yara suke yi suna haukacewa. Mawakin ya kawo wadannan baitoci ne saboda ya fadakar da mutane da su yi Allah wadai da irin da irin wadannan azzaluman shugabanni. Ga Abin da ya ce;

14.An mai da mu sai bara wasu na bidar kanzo,
Ba a kusantarmu ma sai in wuya ta zo,

Kuma ba mutum dan adam mai maganin dozo,
Bana ba mu bin mai abawa, mai zare ya zo,
‘Yancinmu rigarmu ce, bana lokaci ya yi.

44. An sha da mu manguna bakin mu na daci,
Matar da ke nakuda ai ba ta ma barci,
Duk wadda ke yin fito gurinsa ya kai gacci,
Yau ga shi Nijeriya marashi ba ya bacci,
Tsananin rashin babu, kansa tauna kwayoyi.
(Wakar Siyasa Rigar ‘Yanci ta Abdul’Aziz Abdullahi Ningi)

A gaba kuma Haruna Aliyu Ningi ne yake cewa:

7. Kun boye kudi, kun ce ba za ku fitar su mu sami ba,
Don ku yi mana talala, a kan ba mu yarda ta zarce ba,
Mu mun gama konewa, tokarku ba za ta yi illa ba,
Mun yarda ku more ku, kune ba ku yarda mu more ba.

41. Ya rurrufe boda kaf, don kar jama’a su sayo sifiri,
Don kar mu ci shinkafa, sai dai mu tsaya a tikar gari,
Ya daddaga mayin ma ya sanya kasar mu cikin bori,
Maganarmu ta fetur ma, a yau ba mu gane ministan ba
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A kokarinsa na finjire wa halin da shugabanni suka saka talakawa a ciki da ukubar talauci da suka kakaba wa mutane, Haruna Aliyu Ningi a cikin *Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* ya soki manufofin gwamnati ta wancan lokacin dangane da yadda suka kawo wa ‘yan kasa talauci. Ya ce sun boye kudade sai zabe ya zo ko wata bukatar kansu su fitar da su domin su yi wa mutane talala. Haka kuma ya ce, sun toshe iyakokin kasashen masu makwabtaka da Nijeriya domin kada a yi kasuwanci mutane su ji dadi. Bukatarsu mutane su zauna cikin talauci da rashin walwala kamar dai yadda ya kawo a cikin baitocin da suke sama.

### 4.4.1 Cin Hanci

Ma’anar cin hanci ta rabu ya zuwa rukuni-rukuni musamman a cikin kasashe masu tasowa irin su Nijeriya, wannan ba zai rasa nasaba da irin rawar da masana

suke takawa a kansa ba musamman ta yin tsokaci a game da batun. A takaice cin-hanci yana nufin karya dokoki domin amfanin kai da samin moriya (Sen 1999:275).

Haka kuma ana iya bayyana cin-hanci da cewa, mallakar dukiya ko karfin fada-a-ji daga cikin arzikin kasa, ko kuma amfani da doka a wurin da ba ta dace ba domin wani ya amfana (Lipset at el 2000:112).

Bankin Duniya ya bayyana cin-hanci a matsayin, karya dokar aiki domin wani ya amfana kuma hanya ce da take kawo talauci ta kuma rufe hanyar kawar da shi (Babalobi 2008:11-12).

A cikin kasashe masu tasowa ciki har da Nijeriya, ana samin cin-hanci daban-daban da suka hada da bangaren siyasa da tsarin gudanarwa da harkar zabe da rashawa da ha'inci da almubazzaranci da zalunci da alfarma da kuma nuna 'yangaranci (Sondhi 2000:1-2).

Duk da cewa kasar Nijeriya ita ce kasa mafi girma a cikin duniya ta bakar fata, da yawa daga cikin mutanenta suna cikin kangin talauci da jahilci da rashin wadatar harkokin lafiya wadanda ababe ne da cin-hanci da rashin adalci suka haifar da su.

Cin-hanci a cikin kasa kamar cutar daji ce, idan ba a farga da ita ba a kan lokaci sai ta hallaka dukkan kasa abin da zai janyo bala'li da wahalhalu. Cin-hanci kamar cuta yake mai yaduwa ta yadda idan ba a magance shi ba yana iya zama kamar wuta a cikin daji mai surkukin bishiyoyi. Kamar kwayar cutar sida ce mai kawo cutar kanjamau da ba ta da magani (Sondhi 2000:1-2).

Wannan bayanin da Sondhi ya kawo yana bayyana yadda cin-hanci yake shafar al'ummu wadanda kasar Nijeriya tana daga cikinsu. Yanayi ne da yake yaki da duk wani irin ci gaba da kuma kyakkyawan tsari da ciyar da kasa gaba. Abu ne da yake shafar harkokin siyasa da tattalin arzikin kasa yana kuma lalata kyawawan al'adun da al'ummu suka gada iyaye da kakanni.

A ranar 1 ga watan Oktoba shekarar 1960 lokacin da Nijeriya ta sami 'yancin kai, tun daga wannan lokaci duk gwamnatocin da aka kafa na farar hula da na soja, sun yi da'awar yaki da cin-hanci, amma babu wani sauyi na a-zo-a-gani. Fitattu daga cikin gwamnatocin da suka yaki cin-hanci a kasar nan sun hada da lokacin mulkin Murtala da Obasanjo a shekarar (1975-1979), sai kuma lokacin mulkin Buhari da Idiagbon a shekarar (1983-1985). Haka kuma a shekarar 1999 lokacin da Nijeriya ta dawo tafarkin mulkin dimokiradiyya ta yi alkawarin yaki da cin-hanci wanda shi ne ummul haba'isun lalacewar al'amura a kasar nan. Gwamnatin ta bayyana cin-hanci a matsayin abin kunya musamman ga jami'an Nijeriya musamman a kokarinta na daidaita kasar da sauran kasashe saboda da irin wariyar da kasar ta sha a tsakaninta da wasu kasashe ta fuskar difilomasiya. Haka kuma abin ya zame wa Nijeriya wani kandagarke na neman yafiyar bashi da kuma samin karuwar saka hannayen jari daga kasashen waje (Abubakar 2012:3).

Yau, wannan kasa tamu tana tsakiyar neman duk wani shirin da zai kyautata mata tarbiya da cusa wa 'yan kasa kishin kasarsu. Idan muka kalli ire-iren miyagun dabi'u na rashin da'a da zalunci da ke gudana a al'ummarmu a yau, abin zai ba mai hankali tsoro sosai. Yau, kusan babu fannin rayuwar dan Nijeriya da bai

bukatar garambawul sosai Bunza (1994:12). Cin hanci ya yi katutu a cikn rayuwar 'yan Nijeriya misali; ta fannin ma'ikata, abin ya wuce misali idan aka yi la'akari da yadda mutane suke tara dukiyar haramun da handama da babakere da rub-da-ciki da dukiyar jama'a. A fagen siyasa mai kudi shi ne mai kuri'a, in ba ka da kudi, komai adalcinka da rikon amanarka, ba ka cin zabe ko a unguwarku. Idan ka ji 'yan Nijeriya sun cika zargin wani ma'ikacin hukuma, ka matsa ka bincika sosai, za ka tarar yana son ya auna gaskiya ne. Haka da za a kalli hoton kasuwancinmu kawai ya isa a rike baki, don mamakin irin abubuwan da jama'a suka kirkiro wa kansu don zalunci da rashin sanin ya kamata. Saboda wannan matsala ta cin hanci mawaka wakokin siyasa suka kalli matsalar suka yi Allah wadai da mutanen da suka fado karkashhin wannan cuta. Misali:

7. Abin da ya sa ni tunzuri, na dora tsuwa cikin dare,
Na kasa bacci cikin dare, ina wasi-wasi na fandare,
Batun hukunci nai nazari, da shi ya ka kagi falken dare,
Masu mulki daga kansila, 'yan majalisa sun fandare,
Kwamashinoni, Ciyamomi, ga Gwamnoni sun Fandare,
In suka saci hakkin jama'a, babu hukunci gare-gare,
Lallai barayi suna suka tara, an yi gudu da ba wurin zuwa.
(Wakar Bubbukuwa ta Aminu Ala)

Satar da Aminu ALA yake magana a nan sata ce ta cin hanci, hadin baki shugabanni suke yi da wasu ma'ikatan gwamnati ana kara kudaden yin ayyuka ko kuma a kirkira ayyukan karya ana fitar da kudinsu. Abin ya zama kamar doka a Nijeriya cewa, idan ka rika mukami sai ka zama mai arziki. A nan, mawakin yana tunasar da talakawa a game da ire-iren wadannan shugabanni saboda a guje musu a kuma hani gaba.

16.Rashawa tana nan, da cin hanci yana nan,
Rikicin kabila da addini yana nan,
Ga cin amana da son kayi yana nan,
Ga karya dokar kasa, gun masu doka, iye.
(Wakar Hawaye ta Haruna Aliyu Ningi)

A nan kuma, fadakarwa ce ta kai tsaye ake yi wa zababbun wakilai a kan cin hanci da rashawa da cin amana da karya dokar kasa. Saboda cin hanci an wayi gari a Nijeriya shugaba ba ya yin laifi. Idan ka ga an hukunta mutum talaka ne wanda bai san kowa ba. Wadannan mawaka suna fadakarwa ne domin mu fahimta mu bijire wa ire-iren wadannan kama-karya da ake yi mana saboda kasar ta ci gaba da dorewa.

Da zarar an nada mutum wani mukami cikin lokaci kankani sai ya zama mai kudi, kasa ta zama babu mai son ta kowa kansa yake so. A fili ake ba wa shugabanni toshiyar baki su kuma su karba daga baya su saka wa wanda ya bayar da wani abu, mukami ko kuma kwangila.

Dubi dai Abin da Dauda Kahutu Rarara yake cewa;

5.A ranar muka tabbatar da malfa ta ja dala,
Dalolin da Sunusi yaf fada ya zamo matsala,
Domin ya fadi yadda dukka satarsu ta kammala,
Su Duna ana can ana ta faman neman dala,
Ya aje rawaninsa yai Abuja neman dala,
Har farin doki yas saya kafin alkalamin dala.
(Wakar APC Zuwan Mai Malafa Kano ta Dauda Kahutu Rarara)

Mawakin yana magana ne a kan Abin da ya faru a Kano lokacin da shugaban Nijeriya ya je can. Da alama takaici ne ya kama mawakin a kan Abin da ya faru. Ya duba ya ga halin da yankin Arewa yake ciki amma sai ga shi shugabanni sun taru suna rawa a fili wai siyasa suke alhali a wannan lokaci ga wasu yara can an

sace an kuma kai wa wani yanki farmaki da bom har mutane da yawa sun mutu baya ga asarar dukiya. A cikin wannan hali sai ga ‘yan Arewa suna cewa su sun ji sun gani wannan shugaba yana da tsari kuma yana aiki don haka sun koma PDP.

A cikin wakar AC kuwa:

12.Mu ba jam’iyyar rashawa ko cin hanci ba ce,
Ba wai jam’iyyar da ake fada a ciki ba ce,
Ba fatin da ke hada tsofin ‘yan gunda ba ce,
Ba kuma jam’iyyar da take kashe ‘ya’yanta ba ce ‘yar yawa.
(Wakar AC Jam’iyyar Talakawa ta Haruna Aliyu Ningi)

A nan kuma Haruna Aliyu Ningi ne yake gega ta sa jam’iyyar da cewa ba ta masu cin hanci ba ce ba kuma jam’iyyar fada ba ce haka kuma ba jam’iyyar da take kashe ‘ya’yanta ba ce. Idan aka yi la’akari da Abin da mawakin ya fada, shagube ne ga sauran jam’iyyu musamman wadanda ake zargi da irin wadancan manufofi da ya lasafta. A takaice yana fadakar da mutane da su ki yarda da jam’iyya mai manufofi irin wadancan su kuma shiga tsarkakkiyar jam’iyya.

A gaba kuma an tsinkayi abin da mai wakar masu gudu su gudu inda yake cewa:

1.Ku gaya musu masu gudu su gudu,
Kai! In kasan kai sata ka gudu,
Hai! Ku gaya ma barayin can su matsa,
Ko way yi sake Janaral ya ritsa,
Ga baba Buhari janar a sama, hayya!
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Da alama ya gama yanke hukunci a kan mukarraban gwamnatin da ta shude cewa sun yi wa-ka-ci-wa-tashi da dukiyar mutanen Nijeriya. Wasu sun yi sata wasu kuwa rashawa aka yi ta karba wadansu kuma cin hanci wasu kuwa har halasta kudin haram suka yi. Idan ba haka ba babu dalilin da mawakin zai ce wai in ka san ka yi sata ka gudu! ya kara da cewa a gaya wa barayi su gudu, wannan duk

alamu ne na kin yarda da abubuwan da waccan gwamnati da mutanenta suka tafka na bangaren cin hanci

Sai ya kara da cewa:

9.Ya al'umma na kasa ku taho ku ji labarin da ake,
Janaral ya amshi kasa amma fa kusan halin da take,
Farko ga cin hanci ya yadu a kan layin da muke,
Kuma ba shi ya yi yawa su dan baki bankaurar su suke,
Kasa ga shi babu tsaro kullum ibar rayinmu ake,
Tattalin arziki na kasa duk ya rushe maganar da ake,
Harkar noma ziro wuta da ruwa hanya a hade,
Harkar ilimi ziro kullum yajin aikinsu suke,
Kuma fanni na lafiya likitoci zaluntarsu ake,
Ana ta bukin murna amma fa kusan halin da muke,
Janaral ya karbi kasa shi dai burin gyarata yake,
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

A cikin wannan layukan waka a fili mawakin ya bayyana cewa akwai cin hanci a cikin wannan kasa. wannan kuwa ba zai rasa nasaba da halin da gwamnatin da ta zo ta sami kasar a ciki ba. Abu ne sananne cewa, a lokacin gwamnatin da ta shude yajin aikin ma'ikata ya yawaita kwarai da gaske, kama daga ma'ikatar ilimi da ta lafiya da ta jiragen sama, ta kai ta kawo har 'yan sanda said a suka yi barazanar shiga yajin aiki. Yawaitar cin-hanci a tsakanin jami'an gwamnati ake zargi ya kazantar da kuma dagulewar al'amuran kasar baki daya.

A gaba kuma sai ya ce:

15.Kai masu gudu su gudu bana GMB shi ne da kasa,
In ka ji ana a gudu watakila barayi ne mu tasa,
Mai tsoron GMB idan ka tara ka cuci kasa,
Duk mai zagin Janaral watakila munafinci ya dasa,
Ga janar ya karbi sama ku masu munafunci ku gusa,
Don shi mulkin Janaral baya ra'ayin danne na kasa,
Sai baba Buhari Janar don shi dai alkairi ya tasa,
Masu kin ka barayi ne sun san da akwai kulli a kasa,
A kasa sai mui murna don mun harbo kusu na bisa,

Janaral kai ne da bisa Allah ya taya ka riko janaral dan baiwa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Mawakin ya fito fili yana fadakar da mutane inda aka fito daga wajen gwamnatin da ta wuce, ya bayyana cewa kusan komai na ayyukan raya kasa sun rushe wadanda ake tafiyar da su kuma sun tsaya cak. Yana jan hankalin mutane da a yi a sannu tunda maganar gyara ake yi, masu iya magana suna cewa "barnar kwana guda, wata guda ba zai isa a gyara ta ba" wannan ta sa mawakin yake kiran mutane da su yi hakuri da wannan gwamnatin.

A gaba kuma duk dai a game da cin hanci, a cikin wakar Lema ta Yage ta Dauda Kafutu da Wasu suna cewa:

Hana cin hancisai Baba Buhari,
Korar rashawa sai Baba Buhari.
Zai gyara kasarmu an kau da mazambata,
Yau Nijeriya tana hannun gaskiya.
Tafiya ta tafi yau mun buge gwada babu ji,
Mun dauko Janar Buhari yai agaji,
Tattalin arzikinmu zai dawo babu ji,
(Wakar Lema ta Yage ta Dauda Kahutu da Wasu)

Wannan baiti na sama da ya fito daga cikin wakar Lema ta Yage yana bushara ne ga mutane a kan halin rusa tattalin arzikin kasa da gwamnatin da ta wuce suka yi, da ya hada da cin hanci. Ba komai ta sa mawakin ya kawo wannan baiti ba, sai don kurun ya nuna gazawar gwamnatin da ta wuce, ya kuma nuna wa talakawa fa'idar gwamnatin da ta zo. Yana fada cewa, wannan gwamnati za ta hana cin hanci da rashawa kuma tattalin arzikin Nijeriya zai bunkasa. Da alama ya fadi haka ne domin a guje jam'iyyar da tasu jam'iyyar ta karbi mulki a hannunta.

### 4.5 Bijirewa Ta Hanyar Farfaganda

Farfaganda wata hanya ce da ake amfani da ita domin a cusa ra'ayi don a jawo hankalin jama'a ga wani al'amari ya alla sabo ne ko tsoho don Abin ya sami karbuwa sosai da sosai. ana yin farfaganda don a nuna kyama ko adawa ga wani abu, don a muzanta ko tallata Abin Isah (2012:87).

A takaice farfaganda hanya ce ta baza ra'ayi domin lallashi da jawo hankalin jama'a domin isar da wani sabon tunani zuwa na wani ra'ayi ko tunani, da a da ta riga ta runguma, kuma ake son yanzu a karbi sabon abin da aka zo da shi.

Abin. Irin wannan tsari ne wasu marubuta wakokin Hausa ke bi suna ilimantar da mutane kan wani shiri da su marubutan ke ganin bai da tasiri ga rayuwar mutane, watakila abu ne mai amfani ko maras shi ga al'umma. A kan yada farfaganda a gidajen rediyo da talabijin, a jaridu da mujallu, da fina-finai da wakoki kamar yadda aka yi kokarin kawowa a nan kasa.

An kasa farfaganda ya zuwa;

Kyakkyawar farfadanda

Mummunar farfaganda da kuma

Jirwaye ko wake-waken farfaganda.

Kyakkyawar farfaganda

Farfaganda ce wadda aka fi sani kuma mai tsafta mai kyau, ta kowace fuska ba karya ko yaudara a cikinta wacce akasari takan bi ayyanannun hanyoyi na

mu’amula tare da fuskantar lamari kai tsaye (Jumare 2007 da Mannura 2008 da kuma Hassan 2010).

Mummunar Farfaganda

Farfaganda ce da ake yi domin muzanta wani abu, a kunyata shi, ana amfani da karya ko yaudara da cin fuska da duk wata hanya ta kaskantar da mutum da mutane za su kasa gane daga inda take fitowa (Jumare 2007 da Mannura 2008 da kuma Hassan 2010).

Jirwayayyar ko wake-waken Farfaganda

Farfaganda ce da ba a gane daga inda ta fito ko su wa ke yin ta ba, irin wannan ruwa biyu gare ta hadakar gaskiya da karya ko gaskiya da yaudara, domin su kara wa abin da suke yi wa farfaganda armashi da yakan jefa jama’a cikin rudu da kasa rarrabewa da gaskiyar lamari.

Wasu daga cikin rubutattun wakokin siyasa na Hausa, wakoki ne na farfaganda da ke kokarin bijire wa wani tsari da ake aiwatarwa a gwamnatance ko kuma wanda bai yi daidai da tsarin harkokin siyasa ko manufofinta ba. ‘Yan siyasa kan yi amfani da farfaganda su bijire a kokarinsu na yada manufofinsu domin su yi tasiri a tunanin jama’a, da kuma jawo hankali da lallashi domin haka ta cim ma ruwa.

Ga abin da aka sami na nuna bijirewa ta hanyar farfaganda a cikin wakokin siyasa;

3.Sun ce kasa musiba, ni ko, musiba ba ta gabana,
Sun ce kasa bala’i, ni ko bala’i ba ya gidana,

Sun ce a kama gaskiya, ni kuma gaskiya ba ta gabana,
Sun ce a daina cin hanci, cin hanci ya zama jinin jikina,
Sun ce a daina murdiya, ni kuma murdiya na hau Abina,
Sun ce da ni tsaro, ni ko tsaro ba ya gabana,
Ban bi gaskiya ba, mutan kasata ku shiga azaba.

4 .Manya iyayen kasa, su ma na bata lamarinsu,
Su za su zo gabana, a da fa ni zan je gabansu,
In fadi, in tashi, har in Allah ya taimake su,
Sai na sakwarkwata su, na karya kwarin da ke gurinsu,
Idan na zo da tsari suka ki bi, zan gina asusu,
Baho-bahom kudi zan tattara in kai gabansu,
Wallahi za su bi ni, daga karshe su shiga ukuba.
(Wakar Mafarkin Mulki ta I ta Jibrin Jalatu)

A kokarinsa na fadakar da mutane su lura da ire-iren mutanen da suke zaba domin su wakilce su a matakan mukamai daban-daban, Jibrin Jalatu ya ce, mutanen da ake zaba ba sa yi wa mutane wakilci na kwarai, ba ruwansu da duk wani hali na musiba da bala'i da rashin gaskiya da cin hanci da murdiya da rashin tsaro da talakawa suke samin kansu ciki. Haka kuma ya kara da cewa, 'yan siyasa suna amfani da halin talauci da kwadayi da kuma handama da wasu mutane suke da shi musamman wadanda suke kusa da 'yan siyasar ta yadda za a saye su da abin duniya kalilan a karshe kuma a yi musu wulakanci. Wannan ta sa mawakin yake fadakar da mutane domin a bijire wa irin wadannan wakilai.

Duk dai a game da farfaganda, sai aka ce;

9.Tafiya muke yi a kurmi mai itace,
Kuma ga dare, ga ruwa makil a kwance,
Kuma ga macizan ruwa da na kan itace,
Ga babu mai toci ko sandar rikewa.

14.Amsarki na san ta ba sai kin fada ba,
Ciwon da ke cin ki ba karami ba ne ba,
Ranar da zai so ki ban ga tana zuwa ba,
Ni kam ina jin da kyar in za ki rayu, iye.

15. Mamarmu Nijeriya, ciwo take yi,
Shin foliyo ko kanjamau take yi,
Sida take, koko dai kwalara take yi,
Ai fa kwarafshan ina jin shi take yi.

17. Kuma ga siyasar ta'addanci tana nan,
Ga sace-sacen mutane ba a bari ba,
Cututtuka barkatai kuma ba a kula ba,
Murna kike mama, ko kuka kike yi, iye.
(Wakar Hawaye ta Haruna Aliyu Ningi)

Haruna Aliyu Ningi ya tunasar cewa, talakawa suna cikin wani hali na rashin tabbas game da dorewar kasarsu Nijeriya saboda rashin iya gudanar da mulki daga wajen shugabanni. Kasar tana cikin wani hali na kunci tamkar a ce mutum yana cikin daji da daddare kuma ana ruwa kums babu cocilan a hannunsa ga macizai a hanya. Wannan ta sa ya yi tambaya cewa "wai me yake damun Nijeriya?" Foliyo ne yake damunta ko ciwon sida ko kuma cin hanci. Abubuwan rashi a cikin Nijeriya sun yi yawa in ji shi, ga ta'addanci ga sace-sacen mutane ga kuma cututtuka. Wadannan abubuwa suka sa yake fadakar da mutane su zabi nagari nan gaba a wajen wakilci ba irin wadannan da suke kai ba yanzu, da suke neman hallaka mutane tun kwanakinsu ba su kare ba.

A gaba kuma Alan waka ne yake cewa;

22.Su yi oda ta atamfar nan sosa,
Sun mammanna gumakansu,
Su rarraba mu dauke mu daura.

35.Allah kai kab ban iko,
In ki abin gudu da fatar bakina,
Allah kab ban hikima,
In yi ragargaza da harshen bakina,
In fadakar gun al'umma,
Don su yi kyama ga mulki na gadara.

(Wakar Baubawan Burmi ta Aminu Ala)

A nan kuwa karin haske aka sami a game da ire-iren fadakarwar da ake yi wa mutane musamman a game da irin halin da ake ciki a wannan kasa. Ya nuna cewa, masu mulki suna yaudarar mutane suna ba su abin da bai kai ya kawo ba domin su nuna amincewar su a kansu domin su wakilce su. Ya ce yana addu'a Allah ya ba shi ikon fahimtar irin wannan wayo da ake musu don haka yana fadakar da mutane su tashi a tsaye kar su yarda da sakiyar da babu ruwa a cikinta.

A cikin Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba an sami farfaganda ta fadakar da mutane da su nuna rashin yardar su da shirin zarcewa a kan mulki da wasu suke son yi kamar haka;

6. Maganar na biyun Ojo, dama bai zo shi da hujja ba,
In ban da rashin kumya ta Ojo da raina karama ba,
Ya za a yi alhanzir, ba za mu kira shi haramun ba,
To, ku je ku ci ba ma ci, ba za a ciyar mu masifa ba.

42. Tsoho hakuri ne dai, sai ka yi ka daina bakar gaba,
To abin da ka kukkulla, ba zai tafi yanda ka shirya ba,
To mutan kudu ba sa so, Arewa kakaf ba mu yarje ba,
Ai hannu daya ba zai dau, abin da yake rufe daki.

(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

Yana daga cikin manufar farfaganda jiyar da labari mai kyau ko marar kyau, a nan bayani ne mai kyau wanda ake fadakar da talakawa a kansa da su farka su fahimci abin da ake magana a kansa. Zarcewa a kan mulki abu ne da ba ya kan tsarin dokar kasa, kuma a ce ana so a yi shi domin kawai zababbun wakilai suna da madafun iko a hannunsu. Wannan ta sa ya ce talakawan kudancin kasa har zuwa na Arewa su ce ba sa so kuma ba su aminta da a yi hakan ba.

A cikin wakar APP da aka yi wa Jimmai Wakili a jahar Zamfara, mawakin ya fito fili ya bayana munin jam'iyyar PDP ta yadda jama'a za su guje ta. Da farko ya bayyana cewa za su yi addu'a Allah ya sa a daina son 'yan PDP gaba dayansu, ya kuma ce duk masu son two time a kan mulkin kasar nan azzalumai ne 'yan bakin ciki marasa son talakawa ga kuma keta da bakar rowa. Ya bayyana wadannan abubuwa ne domin a guje wa PDP duk da cewa wadansu daga cikin halayen da ya bayyana bai zama lalle a ce sun kebanta ga su 'yan PDP din ba. Ga Abin da ya ce;

.

6.Kuma ga shi mulkin mai kunne ana ta yin Allah waddai,
Duk wanda yas shiga PDP an daina son shi ga baki dai,
Ko ma su son a yi tu tayims jahar mu yau sun zam dai-dai,
Wadanda ke son zalunci da kuntata wa talakkawa.

23.Ni na sani 'yan PDP bakin ciki da bakar keta,
Da kuntatawa tsakanin su da yi wa kan su bakar fata,
Da hassada a cikin lamarinsu a ko da yaushe cikin keta,
Kuma sun kware a wajenn rowa da kuntata wa talakkawa.
(Wakar Jimmai Wakili APP ta M. Ali)

A nan kuwa Garba Gashua ne ya watsa dafin farfaganda ga 'yan jam'iyyar da suke adawa da wadda ya yi wa waka wato APP saboda rashin yarda da ya yi da su. Ya bayyana siyasar 'yan adawa da cewa ta 'yan ta'adda ce masu amfani da makamai suna cutar da mutane ba dalilin tsaye ba na zaune, haka ta sa ya ce;

24.Kin gaji siyasar 'yan ta'adda,
Ki ziga su su koma mu dauki sanda,
Da wuka da takubba sui ta'adda,
Da wuyanki kamar an bi da randa,
Tafi ba ki da kima gun mutane.
(Wakar Ke 'Yar Fakara APP ta Garba Gashuwa)

Wakar APP ta Bashir Sani Ringim ta taho da salon bayyana farfaganda iri biyu a lokaci guda. A bangare na farko ta bayyana bakar farfaganda a kan jam'iyyar

adawa inda ta bayyana ta a matsayin jam'iyya mai halin bera wato ta barayi ke nan, ya kuma ce ba su da halin yin gaskiya ko kadan. Ta bangaren farar farfaganda kuwa, mawakin sai ya yabi jam'iyyarsa ta yadda mutane za su so ta kamar yadda ya nema da a kyamaci jam'iyyar adawa. Ya ce jam'iyyarsa babu azzalumi a cikinta kuma babu Abin da zai saka mutum ya yi tagumi a cikinta, wato babu halin kaico a cikin tasu jam'iyyar. Hakan ta sa ya ce;

35.APP cikin kasa ita tai zarra,
Don lamarinta dukka babu shirin kwara,
'Ya'yan jam'iyoyin masu halin bera,
Ba komai da mu da su sai fa harara,
Domin babu su a kan lamarin gaskiya.

37.APP cikin kasa ba ta da zullumi,
Babu abin da zai sa ka har kai tagumi,
Ga ta da kyan idon da ba ya dundumi,
'Yan lema a yau kuke bin ta da lallami,
Ku lalubi inuwarta don ku bi ta ga baki daya.
(Wakar APP Kishin Kasa Bashir Sani Ringim)

A nan kuwa jam'iyyar ACN ce take caccakar jam'iyyun adawa ta fuskar farfaganda ta yadda mutane za su amince mata su kuma guje wa jam'iyyun adawa. Mawakin ya ce, sauran jam'iyyu sun fake da addini suna cutar talakawa. Ba komai suka saka a gaba ba, sai son ransu da zuciyarsu ba ruwansu da batun talakawa kamar yadda ya kawo a cikin (baiti na 37).

A gaba kuma ga abin da aka sami;

12.Su sun fake da addini ne ina son kui hattara talakawa,
Domin biyan bukatar kansu ba dan ku ba suke talakawa,
Su ayyukanku ne ba sa so da A C N ke wa talakawa,
Ku kara nazarin kan kowa Na Mama yau ya fashe maku komai.
(Wakar ACN ta Hassan Na Mama)

Wani aiki sai farfaganda, in ba farfaganda ba a ce mutum ba ya tsoron Allah Mahalicci da ya yi shi sai abokin adawar siyasa. An kawo wannan domin a dauke hankalin mutane su bijire wa wancan mutumin da jam'iyyarsa duk da cewa ita ce take kan mulki ta yadda mutane za su dawo da ra'ayinsu wurin adawa. wannan farfaganda ta fito a cikin wakar "Kama shi Lado" ta Ibrahim Katsina (baiti na 6) kamar haka;

5.Kama shi Lado, kai kama shi Lado,
Damko shi Lado, kai damko shi Lado,
Ba ya tsoron Allah Ubangijinai sai Lado,
To kama shi Lado tun da bai san Allah ba.
(Wakar CPC Kama Shi Lado ta Ibrahim Katsina)

Wakar CPC Chanji;

6.Farko dai ku sani mutane mun fita mai masarar barayi,
Mun banbare masarar cikinta sai totuwa muka bar wa bayi,
Mayaudara maciya amana mun bar ku kowa da kowa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dankaduna)

A cikin (baiti na 6) na wakar CPC da take sama an takalo batun wata jam'iyya ne, a inda aka nuna ta barayi ce domin haka sun guje mata kamar yadda yake jan hankalin mutane su ma da su yi hakan. Ya bayyana jam'iyyar da cewa ta mayaudara ce da maciya amana domin haka talakawa su yi hattara.

A nan Dauda Kafutu yana yin tambihi ne ga mutanen Arewa da suka nuna rashin yardarsu da jam'iyyar adawa wadda kuma it ace ta lashe zabe. Yana bayyana musu cewa, tun da gwaninsu ya fadi sai su je su raka shi har garinsu tunda yanzu sai a koma gidan gado, fita daga fadar shugaban kasa ya zama dole. A cikin wakar ya zayyano wadanda suka nuna butulcinsu ga wannan yanki na Arewa a saboda

da gwaninsu wanda ba yanki daya suka fito ba. Ya jero su inda ya bawa kowa suna daidai matsayinsa ko siffarsa ko kuma yanayinsa ko wani abu da ya yi ya zame masa sheda. ire-iren wadannan sunaye da ya kawo sun hada da Duna da ministan hayaniya da ya kira stufid da mai rodi da mai bilicin da sauransu, wannan ta sa ya ce:

16. Su Duna ana ta shiri bana za a Otoke zuwa rakiya,
Tilas na kira Anti mai bilicin dawo ki yi rakiya,
Wai ina Kauran mata da kai a cikin wannan rakiya,
Da na Sakkwato ba sauki tilas ka shigo wannan rakiya,
A rufe ma da fatiya Malam Namadi na waya tu waya?
Ku kira mani Mai Rodi shi ma zai je wannan rakiya,
Tsohon gwamnan Barno da ya sa malfa mun kori kaya,
A Kano tsohon kwano yana ciki duk za sui rakiya,
A ministan hayaniya ku kira shi sutufid of za yiya,
Ku tunawa fes ledi ta Otoke bataun magana ta jiya,
An gyara gidan gado a Otoke ana ta shirin tafiya,
Ga Buhari cikin bila haihuwatai na yaye gajiya,
Ga shi albarkar 'ya'ya ita ce sanadi mun kori kaya,
Allah raka taki gona can a Otoke mu kori kaya,
Janar ya amsa janar bana dai bila kaine da rikon talakawa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

A kokarinsa na nuna kin yarda da PDP mawakin jam’iyyar adawa da ta yi nasara a zaben da aka gudanar a wannan lokaci, Dauda Kahutu Rarara ya bayyana cewa, sun gama da PDP manufa ta fadi zabe domin haka an hallakata ta mutu. Sakamakon haka, mawakin yana fada wa shugaban da ya sha kaye a zabe cewa, ya yi maza ya hada kayansa ya bar musu gidan gwamnati saboda nasu gwanin da aka zaba ya shiga.

1.A'a masu gudu su gudu, bana dai Janaral ya karbi sama,
Mun hallaka PDP bana APC ita ce da kasa,
Mai malfa fara shiri bana za ka fice bila da gudu gaggawa.
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

Mawakin ya kara da cewa, jam'iyyar da suka kayar a zabe tumbir suka yi mata, wato sun kwace mukamin da aka zabi danta a kai. Manufar mawakin a nan ita ce a yanzu su ke da rinjaye a zabe tun da su suka sami shugaban kasa, jam'iyyar adawa kuwa ta tashi da kusan a ce babu komai, kamar mutum ne a cikin sutura sai a yaye suturar a bar shi tumbur. wannan ta sa ya ce:

> 3. Ita PDP tumbur muka ce za ai kuma an yi haka,
> Mun hallaka PDP a saman da kasan mu ne da duka,
> A kasa a tsaya a raka in ji Baba janar shi ne waraka,
> Yau ga canji ya zo APC kullum na habaka.
> (Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

A nan kuma, mawakin yana jan hankalin talakawa a game da irin shigo shigo ba zurfi da 'yan PDP suka yi wa Shugaban kasar da ya fadi a zabe suka yi masa a garin Kano. Sun nuna masa cewa, su ne da garin Kano, kuma jam'iyyarsu ita talakawa suke yi kuma ita za su zaba. Abin har ya kai da an basu mukamai a gwamnatin tarayya, amma da zabe ya zo sai 'yar manuniya ta nuna. Ya bawa wadancan mutane suna na banza inda ya kira daya da tsohon kwano, wato ya lalace ba shi da amfani kenan. Dayar kuma sai y ace kira tad a kilaki wato matar banza kenan da ba ta da aure.

> 10. Ga ministan nan na wata shidda kalllo ya koma a sama,
> Mundubawa zan koma ranar handin oba rigima,
> Maganar tsohon kwano an kwashi dala fansho na kuma,
> Kun yaudari mai malfa kun ce a kano kune a sama,
> Da kilaki taje zabe a sauna kawaji akai rigima,
> Ita PDP sintir akai mata naga zani a sama.
> (Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

Da ya karkato wajen bangaren mata, mawakin ya bayyana irin katobarar da matar wancan shugaban kasa ta yi na zagin mutane musamman mutanen Arewacin Nijeriya a lokacin da mijinta yake yawon kamfe. Ya fada mata cewa, yanzu maganar zagi ta wuce sai dai ta zagi wani, zabe kuma sun fadi. A kokarin mawakin mawakin na nema mata mafita shi ne ya ce sai ta koma garin mijinta. siyasarsu ta watse ta fatattake don haka kaikayi ya koma kan mashekiya. Ga abin da ya ce a kasa:

30. Bari in gaya wa fes ledi bana Otoke za ki,
Madam kina ta zaginmu kina yabon mijinki,
A yanzu ba musu sai kin gane kuskurenki,
Otoke za ki koma Abuja ta yi tsada.
Lema ta yage ta fatattake nace ta yage,
'Yan malfa mun maku gwalo,
Rarara ya ce ai zigidir,
Ai wanwar,
Ai tumburrrr,
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

A nan kuma Rarara ya kore maganar jam'iyyar PDP ya ce, jam'iyyar APC ta hadiye ta gaba daya, domin haka maganarta ta riga ta wuce. Ya ce jam'iyyarsa ta cinye komai a zabe ta bar jam'iyyar PDP domin makaryata ne, kuma karyar ta kare kamar yadda yake cewa:

Karyar wasu ta gama kArewa APC ta hadiye malfa ashe,
Baba ya ce mui APC sak ashe,
Da saman da kasan tsakiyar mun lashe,
Mun bar wasu sun zama 'ya'yan fashe,
Alo a buga masu taken tashe,
Domin karyar wasu ta zo karshe.
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Lema ta Yage)

A nan kuma ya bayyana cewa, sun gama da ‘yan PDP. Ya jaddada wa talakawa domin su fahimta cewa, a baya wuya suke sha domin komai nasu yana da bambanci da na shugabanni, hatta da ruwan sha ba sa shan irin wanda talakawa suke sha, haka ta bangaren sutura, abin da matansu suke amfani da shi, ko kusa ba a hada shi da na sauran matan talakawa, ga dai abin da ya fada:

Tunkwal uwar daka mun ci uban na masu malfa.
Jama'ar kasa mu gane da can wuya muke sha,
Su su sha ruwa na roba na kududdufi muke sha,
Matansu na da leshi na mu su sa ajaja,
Mun ce ai masu zindir an masu babu mai ja.
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Lema ta Yage)

A gaba kuma an ci karo da wakar Lema ta Yage inda yake cewa:

A kokarinsa na fadakar da mutane su fahimta cewa, a halin yanzu kowa ya dawo daga rakiyar jam’iyyar PDP a cikin Nijeriya, kowa ba ya sonta. A halin yanzu kowa jam’iyyar APC yake a ko ina tun daga mutanen kudu har zuwa Arewa, tun daga Turawa har zuwa Hausawa da Yarabawa da Inyamurai da sojoji da ‘yansanda da kowa da kowa. Wannan ya haifar da baitin da ke biye da wannan bayani da ke kasa.

| | |
|---|---|
| Talakkawa | sai baba Buhari, |
| Masu kudi | sai baba Buhari, |
| Sojoji | sai baba Buhari, |
| Ga 'yan sanda | sai baba Buhari, |
| Jama'ar yaroba | sai baba Buhari, |
| Ga hausawa | sai baba Buhari, |
| Har ma da Ibo | sai baba Buhari, |
| Ga Turawa | sai baba Buhari, |

(Wakar Lema Ta Yage ta Dauda Kahutu Rarara)

A nan kuma mawakin yana fadakar da talakawa a game da halin butulci na daya jam’iyyar, ya kuma kara da cewa, ya fada tun da farko cewa, jama’a za su fice

daga cikinta saboda rashin ingancin shugaban da ya ci zabe a karkashinta. Ta daya hannun kuma ya nuna cewa, shugaban da aka sami yanzu ‘yan mazan jiya ne kuma mangarci mai sanin yakamata. Ga abin day a fada:

Kin dana butulci karshe jama'a sun barki,
Na barki da yara za ni gangara kan aiki.
A yau muka san mun sami shugaba managarci,
Mazan jiya kai ke sa munafukai sui barci,
Dan Nijeriya sai yanzu ne yazam mai 'yanci,
A da bai san ma me ake nufi ba da 'yanci.
(Wakar Lema Ta Yage ta Dauda Kahutu Rarara)

### 4.5.1 Zalunci

Kwara ko tauye hakki ko yin ha’inci ga wani don a cuce shi, shi ake nufi da zalunci (Kamusun Hausa 2006:488). Ta la’akari da wannan ma’ana an fahimta cewa, mawakan siyasa sukan tsarma baitoci a cikin wakokinsu suna bayyana korafin talakawa a kan yadda aka danne su. suna yin haka ne domin talakawa su bijire wa jam’iyya mai mulki wadda ita ce take tauye su, su dawo ga bangaren adawa domin samin canji. Ga misali daga cikin wadansu wakoki da hannu yakai kansu.

Alafazazi yana cewa a cikin waka, zaluncin da ake yi wa mutane a kasar nan ya yi tsanani ta yadda komai ya tabarbare, talauci ya kama mutane an bar yara babu karatu, makarantu babu kayan aiki, yara sai talla suke yi a kan tituna ko’ina a cikin kasa. Ya kara da cewa, shugabanni sun kama arzikin kasa sun rike sun saka mutane cikin kunci, sai rikici da fadace-fadace ko’ina musamman a yankin Arewa sai tashin hankali ake yi. Mutanen Nijeriya ba su san wani abu gudun hijira ba sai ga shi yanzu an mayar da ‘yan Nijeriya gudun hijira zuwa wadansu kasashe, kasarsu ta haihuwa ta gagare su zama. A karshe sai mawakin ya ce, yana kira ga

‘yan Nijeriya su fito a yi gangami domin a kawo gyara da canji a cikin wannan kasa. wannan ta sa ya ce;

6. Ga misali zan maka dan uwa talakawa na a cikin wuya,
Bi gefen titi za ka ga 'yan tallarmu suna ta dawainiya,
Mabarata birni da karkara ko'ina a kasar Nijeriya,
Ba karatu babu sana'a ta ya kasar nan za tai lafiya.

8. Jam'iyyar da take mulkin kasar ta zame mana tarkon dattsiya,
In ta sami na kirki sai ta janye shi sai ta sa ya sha wuya,
Ta kama kasar ta makure za ta sami mu fada rijiya,
Jama'a ku fito mui gangami don mu ceci kasar Nijeriya.

9. Da in aka ce mana 'yan gudun hijira to sai mui dariya,
Yanzu ga talakawa 'yan uwanmu suna ta barin Nijeriya,
'Yan gudun hijirar Maiduguri sai shiga Nijar ba sa waiwaya,
Rana zafi inuwa ko kuna take masu nan Nijeriya.
(Wakar A.P.C. ta Alfazaze)

A gaba kuma wakar DPP ce aka sami;

A cikin wakar DPP ta “DPP a kasa a raka a tsare” ta Auwwal Mujaddadi cewa ya yi zalunci ba ya dorewa, duk wanda aka zalunta idan ya yi hakuri wata rana sai labari. Wannan ya nuna cewa jam’iyyar DPP ta yadda ana zaluntar talakawa a Nijeriya ke nan. Ya bayyana haka ne a cikin (baiti na 4) na wakarsa kamar haka;

3.E! alzulmu la ya dumu inji shugabana,
Zalunci ba ya dorewa a dare da rana,
Ni Awwal Mujaddadi ne ya ‘yan uwana,
Annabi ne ya ce su ba su gasgata ba.
(Wakar DPP, DPP a Kasa a Raka a Tsare ta Auwwal Mujaddadi)

Abokin tafiyar zalunci ita ce haramun, wannan mawaki na jam’iyyar CPC ya yi zargin cewa wadanda suke kan mulkin Nijeriya da cewa haramun suke ci domin zalunci suke yi suna samin abubuwan da suke tarawa. Ya ce ba su tsaya wajen yin zalunci da tara haramun ba, sai da ta kai su ga son zarcewa a kan mulki domin su

halaka Arewa kamar yadda ya ce. Ya ce, da tazarce ba ta karbu ba sai kuma suka fito da wani salo na kama mai gaskiya da kuma mai yin gaskiya. misali;

27. Kun ji wadanda haram ta kai su kan mulki har sukai gamawa,
Da ya gama ya izo tazarce burinsa ya kashe Arewa,
Ga shi tazarcen ta gagare shi wani tarkon shi ya yo danawa.
(Wakar CPC, CPC Chanji ta Yala Dan Kaduna)

A gaba kuma sai aka ci karo da;

1.Talakawa yau muna ta bulayi,
Albarkacin Manzonmu masoyi,
Manyan zaluntar mu suke yi,
PDP ba za ta iya ba, sun sanya muna ta bulayi.

2. Siyasa an kira ta da 'yanci,
Mu kam tamu ba adalci,
Riga ce ta masu mutunci,
Buhari Tinubu za mu taya ku,
Nijeriyarmu baya take yi.
(Wakar APC ta PDP Ba Za Ta Iya ba)

A cikin baitocin wakar da ta zo a sama, wani karin haske ne a game da zaluncin da ake zargin shugabanni suna yi. Haka ta sa mawakin ya tsara wannan waka kuma ya bata suna "PDP Ba Za Ta Iya Ba." Ya ce an saka talakawa sai bulayi suke yi manufa ba su san Abin da zai kai ya komo ba domin manyan kasa zalunci kawai suke yi, kasa ta lalace babu adalci ko kadan.

A gaba kuma Dauda Kahutu Rarara aka sami yana bayyana irin rashin adalcin gwamnatin da ta fadi daga kan mulkin Nijeriya ta yi wanda abin har ya gama da shi. Ga abin da ya fada:

4. Inji masu karin magana wasu sun kare wasu na tafiya,
Wasu sun yi abin kunya su dan baki an fada ma kaya,
Wasu na ta shirin hijira muka ce masu don Allah ku tsaya,
Ka san a karin magana wani zai magana ya tuna da jiya,

Cikin a saya a biya in an mana adalci mu taya,
Ni nasan iya tsawo baya wuce dai kayi da wuya,
Ga shi karshen PDP ya zo jama'a murna mu taya,
A garinmu mahaifata sun barni ina daki na haya,
Yanzu gamu da APC jirgin maja Allah ka taya,
Allah ka taya mu riko Buhari ka je bila ka rike talakawa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

**4.5.2 Tonon Slili**

Hanya ce ta bayyana Abin da ba a son bayyanawa ko tozarta halayen da suke tattare da mutum da ba a son a sani, da fito da abubuwan karara wadanda za su muzanta mutum ko su ci mutuncinsa, domin wasu su ji su guje shi, wata sa'a domin samin galaba wata sa'a domin mutum ya ji dadi, wata sa'a kuma domin ya kawo gyara cikin al'umma Yakasai (2012:169).

Kamar jan ra'ayi, ana samin wannan salo ne a cikin jawabi ko kuma wakokin siyasa. Akwai hanyoyi da dama da masu wakokin siyasa suke amfani da su wajen yin tonon silili, wadannan hanyoyi sun hada da suka da habaici da kushewa da kuma zambo ga wanda ba a so.

A cikin wata waka 'Zuwan Mai Malafa Kano' da Dauda Kahutu Rarara ya yi lokacin da shugaban kasa wanda dan jam'iyyar PDP ya je garin Kano. A cikin wakar ya bayyana wadansu abubuwa da 'yan jam'iyyar ba za su so mutane su sani ba, a kokarinsa na kawar da hankulan mutane a kan waccan jam'iyya.

A cikin (baiti na 63, da baiti na 64, da kuma baiti na 65.) ya ce a wannan taro da suka yi 'yan PDP sun bayyana da kansu cewa sun yi kuskure, domin kuwa sai ga shi manyan mutane da ake ganin su ne shugabannin al'umma suna yin rawa. shugaban kasa kuwa da kansa ya fada cewa a lokacin zaben da ya wuce na

shekara ta 2009 sun ba wa gwamnan Kano kudi domin a raba a zabi PDP amma ya hana. Shi kuwa shugaban jam'iyyar PDP wanda Musulmi sai ya ce duk wanda ya shiga Jam'iyyar PDP a wannan rana kamar ya shiga Musulunci ne. misali;

62.Tabargazar zuwan mai malfa,
A ranar muka tabbatar da PDP ta bare,
A ranar suka tona kansu sun shimfida kuskure,
A rannan muka ware kulba mun gane kadangare,
A ranar suka tona kansu yau karya ta kure,
A ranar muka san na kan tudu muka san gangare.

63.Don a rannan o'eyai rawa da alkyabba kuskure,
Don a rannan muka gane ginshikin malfa mamure,
A rannan muka gane matsayin kowane bangare,
Shugaban jam'iyyarsu ga shi ya tabka uban kure,
Yanzu komai ya tonu tallakawa sun ankare.

64.A ranar muka gane masu malfa karya suke,
Ana coge ana rage mu kullum kasuwa muke,
A rannan muka gane shi siyasar koyo yake,
Sai a rannan muka gane kurri'u dukka saye yake.
A gurin ne ya fada da kanshi al'umma sun rike.
(Wakar APC Zuwan Mai Malafa Kano ta Dauda Kahutu Rarara)

A nan kuma mawakin APC ne ya zargi jam'iyyar PDP da mulkin kama-karya da kuma yi wa kasar Nijeriya zagon kasa. Ya fada cewa duk da irin wadannan munanan manufofi nasu ba zai hana su bin ra'ayinsu ba da kuma fadar gaskiya ba. Ya ce a baya sun yi Abin da ya yi kama da bauta amma a yanzu an sha su sun warke, kuma ba za su bi wanda ba nasu ba, ya ce a kan haka sai dai a yi duk abin da za a yi da su. Kamar yadda aka bayyana a kasa, mawakin da ya yi wannan zargi babu ruwansa da kowane irin aiki jam'iyyar PDP ta yi, shi dai tunda ba jam'iyyarsa ba ce yana iya yin suka. misali;

5. Hakika ku ji ka da mage bai zama yankata ba,
Kama-karya ba za ta sa mu ki sukan ku ba,
Wannan tsarin ba za ya sa mu ki ra'ayinmu ba,
Zagon kasa da kuke kasarmu ba zai karya mu ba,
Mun san damarar da za mu sake Nijeriya.

78. Tallan turmi akwai wuya bana ba zan yi ba,
Ba zan bi abin da zuciyata ba ta gamsu ba,
Cutar da kare ya tashi zancen ku biyo ba,
Akuya in tai ku tabbata ba ta tashi ba,
Ko za a dafa mu ba mu bin dan baubauniya..
(Sungumin Bugun Lema APC ta Aminu Ibrahim Dandago)

**4.5.3 Zambo**

Zambo kwatance ne da ake yi da nufin muzantawa ko kuma nishadantarwa ko neman abin masarufi daga wanda aka yi wa zambon. Haka kuma kai tsaye zambo shi ne kwatanta mutum da wata dabba ko wani abu maras kyau ko a fadi halinsa mummuna yadda wanda duk ya san da wanda ake, zai fahimta da shi ake (Dangambo 1984:42). Zambo na iya kasancewa na daya daga cikin wadannan nau'uka: zambon halitta, ko zambon dabi'a da zambon mukami ko matsayi da zambon habaici da zambon kwatanci da kuma zambon gama-gari (Garba 1998:38-47).

A takaice zambo magana ce da akan shirya domin a muzanta wani mutum. Haka kuma zambo yana iya zama wasu lafuzza ne da ake shiryawa domin a danganta su ga wani mutum da nufin muzanta halayensa a cikin al'ummar da yake rayuwa.

Mawaka da sha'irai sun yi amfani da zambo a matsayin siga ta nuna kin aminci a tsakannin 'yan siyasa ko kuma a tsakanin jam'iyyun siyasa. misali;

Da farko an ci karo da wakar jam'iyyar APP inda mawakin yake cewa;

4. Ni na ga wancan mai gashi bakinsa ya yi kamar jaba,

Ya kwankwashe da gidadanci ya jefa kan shi cikin kwaba,
Azuraki mai tu tayims to ga shi yanzu cikin wahala,
Wallahi ran handin oba ba zai ki cimma na jaki ba.

10.Shi wanga mai gashin baki bai tausaya wa talakkawa,
Bakin kare mai dan gashi yau ya zamo kasarin kalwa,
Shi babu mai amfanin shi ya zam disho a wurin kowa,
Jahar mu bai da muhimmanci ko da zuwa ga talakkawa.
(Wakar Jimmai Wakili APP ta M. Ali)

Kamar yadda bayani ya gabata a sama, akwai zambo iri-iri da ya hada da na halitta ko na waka ko magana, a nan zambo ne na halitta aka yi wa an jam'iyyar adawa a inda aka yi amfani da halittar jikinsa aka masa zambo. Ba komai ya kawo wannan zambo ba, sai don kawai jam'iyyar ANPP ta nuna ba ta yarda da manufofin jam'iyyar PDP ba. A sakamakon haka aka yi wa dan adawa zambo da cewa gashin bakinsa kamar na jaba, bakinsa kuma kamar na kare, a karshe aka kassara shi aka nuna ba shi da amfani a gun talakawan jaharsu gaba daya. wannan bayani ya fito a cikin wakar ANPP mai suna Wakar ANPP ta Jimmai Wakili kamar yadda aka kawo a sama.

Waka ta gaba da take dauke da zambo wakar APP ce mai suna "Bindiga Maganin Mai Keta" Masu iya magana suna cewa, "Mayar da ruwa rijiya ba barna ba ne" Abin da ya faru a nan kenan. An fahimta dan jam'iyyar APP aka yi wa zambo a cikin wakar jam'iyyarsu domin a nuna rashin amincewa da irin halayyar butulci da ya nuna, a lokacin da jam'iyya mai mulki ta nada shi minista a matsayinsa na dan adawa. Wannan ta sa mawakin ya ce;

16.Wayyo jan biri na gane nufinka,
Da ca nake masoyin jama'a ne,
Ashe kiran ka kisan jama'a ne,

Ja'irin aka ba ka minister sai ka karba.
Ka manta na baya.
(Wakar APP Bindiga Maganin Mai Keta ta Isma'ila Abdullahi Sha Bege)

A cikin wakar APC mai suna "Sungumin Bugun Lema" wadda Aminu Dandago ya yi, ya bayyana zambo na halayya ga abokan adawa. A cikin wakar an muzanta 'yan adawa da cewa shashashu ne kuma 'yan iska. ya kara da cewa, mahaukata ne kuma katabarbaru, manufa wadanda ba su da siffa mai kyau da tsari. ya bayyana haka ne a cikin (baiti na 80, da kuma na85).

78.Mai taya kishi ga kishiya shashashan gari,
Mai ba da gudunmuwa ga 'yan iska shagiri,
An yi butulci a bara aka dau makatartari,
Shashashan babu wanda yat tsira da ko dari,
Bana ai hatara a duba masa toyayyiya.

85.Bakar motar can ku duba an tara mahaukata,
Sun lamunce da wanda zai ja ta ya sa wuta,
Suna ta fada wa direba ka da ma fa ya dakata,
Har ma da wadanda ke fadi sun shiga ba fita,
Jalla ka kare mu don saninmu ga baki daya.
(Sungumin Bugun Lema APC ta Aminu Ibrahim Dandago)

Ta la'akari da irin kalmomi na batanci da suka fito a cikin wannan waka, ana iya fahimta cewa duk wanda yake hankoran neman mulki watau dan adawa yana da kaifin baki a wajen mayar da martani. Haka kuma duk lokacin da aka ce wanda ake mulka zai mayar da martani ga wanda yake mulki lalle babu shakka za a sami kalmomi masu nauyi na zambo da makamantan haka. A cikin wakar "Kama shi Lado" ta Ibrahim Katsina, an sami fitowar kalmomi masu nauyi na muzantawa a kan 'yan adawa. An zambaci 'yan adawa aka ce sun zama tukwane kuma sun zama taurarruwa mai wutsiya, manufa abin da babu alheria a cikinsa. Mawakin bai tsaya a nan ba sai da ya kassara 'yan adawa da cewa jemagu ne masu kashin

kwance. Duk wanda aka ce masa jemage ana nufin ya zama abin da ba shi da jinsi, shi ba tsuntsu ba shi kuma ba a ce dabba ba, haka kuma ya ce sun zama dabbobi. A cikin wani dangon kuma ya ce sun zama alade ga kuma katon baki. Duk wanda aka ce ya zama alade an muzanta shi iyakar muzantawa saboda babu dabbar da addinin Musulunci ya tsine wa kamar alade wanda shi ake kira da suna (Alhanzir). Ga Abin da ya fada nan a kasa;

2.Du tukunya ta garinmu mun ga ba ta iya sanwa ba,
Tauraruwa mai wutsiya ganinki ba alkhairi ba,
Kun ga mai tubar da ba ta domin Allah ba,
Jemage yatsunka yau ba sa rike reshe ba.

9.Kai Allah wadan katon garinmu mai kashin kwance,
Ga mutum mai huskar mutum, mai siga ta bisashe,
Kwandareren bakin shi ma kamar ya sha taushe,
Gahiya gashin bakinki ba na mutumci ba.

15.Lallai aladen garinmu yau ya dimauce,
Giyar mulki ce ta sa ido nai ya makance,
Birni, kauye yau ana fadi ya lalace,
Tun da ba ya kaunar mu yau ba zai kuma mulki ba.
(Wakar CPC Kama Shi Lado ta Ibrahim Katsina)

**4.6 Bijire Wa Tsarin Tafiyar Da Gwamnati**

Mutanen kasa musamman talakawa sun bayyana rashin yardarsu a game da yadda ake tafiyar da lamuran harkokin mulkin kasar nan, musamman ta fuskar tsari da tanade-tanaden addinin musulunci, addinin da mafiya yawan masu yin sa Hausawa ne. Wannan ya taso sabili da tasirin addinin a cikin rayuwar Hausawa wadanda mafiya yawansu Musulmi ne. Sun nuna kokensu musamman a cikin wakokin masu tasirin addinin musamman na masu akidar shi'a da 'yan tajdidi da kuma wasu na siyasa. Sun bayyana cewa ba za su amince da tsarin da gwamnatoci

suke bi ba a yanzu domin tsari ne na kafirci da Yahudawa suka kawo, suna kira da a koma tsarin Kur'ani da sunnah kamar yadda addinin Musulunci ya kawo. Sun kara jaddawa cewa, duk wani abu sabanin wannan za su bijire masa. Sun bayyana manufarsu ta bijirewa a cikin wadansu hanyoyi da suka hada da:

### 4.6.1 Fito-Na-Fito

A cikin "The Free Dictionary" an bayyana fito-na-fito da cewa, yin gaba da gaba da gwamnati.

A cikin "Wikidictionary" kuwa sai aka ce, kalubalantar gwamnati musamman a yi gaba-da-gaba.

A cikin Kamusun Hausa (2006:477) kuwa ga abin da aka sami a game da hakan, farwa wasu mutane da fada domin a mulke su.

A takaice ana iya cewa, yin gaba-da-gaba tsakanin gwamnati da masu bore, shi ake nufi da fito-na-fito.

Bayyana yin fito-na-fito cikin wakokin siyasa ba sabon abu ba ne, a lokacin da 'tura ta kai bango' za a tarar mutane a shirye suke ko a mutu ko a rayu, amma ba za su yarda a tursasa musu ba ko kuma a kawo musu Abin da ba zabinsu ba.

A cikin Wakar *Siyasa Rigar 'Yanci* ta Abdul'Aziz Abdullahi Ningi ya bayyana cewa su ba sa tsoro, musamman su 'yan Arewa domin an yi dabara an kawar da su daga cikin mulki, ya ce ko bore suna iya yi muddin za a sami gyara a tsarin tafiyar da siyasar Nijeriya. Ya kara da cewa, lokaci ya wuce na yin magudin zabe, sun sadaukar da rayuwarsu a shirye suke su mutu. Ya bayyana cewa, masu

zalunci su ne suke tsoron mutuwa, su babu gudu babu ja da baya kamar yadda ya fada a cikin baitocin da suke tafe;

12. In ba butulci ba kai, ko nuna wauta ba,
Ya zan ci naman kare kuma ga na rago ba,
Ya mai ido zai shige garken makafi ba,
Sauyi muke so mata sa ban da tsoro ba,
Na Arewa an kakkabe mu cikin ruwan sanyi.

13.In ba da wauta ba, shirme ko rashin kai ba,
Ya zan ta bin wadda bai so na da hutu ba,
Kuma ba ya kaunar a ce na canza riga ba,
Mu fito da kwai, kwarkwatarmu zuwa ga bore ba,
Zabe a Nijeriya bana babu mai sanyi.

18.Mu ba wakilai ba ne, mu ba jakadu ba,
Ba shugabanni ba ne, mu ba sarakai ba,
Mutuwarmu ko yau ta zo, mu ba mu tsoro ba,
Su ne suke kinta don sun san da horo ba,
Amma suke cin hakkinmu da dukiya nauyi.
(Wakar Siyasa Rigar 'Yanci ta Abdu'aziz Abdullahi Ningi)

A gaba kuma sai ya ce maganar tsoro fa babu ita, babu gudu ba ja da baya gyara sai an yi shi musamman na zabe da tsarin mulki idan kuwa an ki yi, za su yi zanga-zanga su kona tayoyi domin nuna fushinsu da kuma bijire wa duk wata danniya da aka tsara aiwatarwa, sai ya ce;

18. Bai dan adam martaba bai zam da laifi ba,
Amma ka bauta masa ba a ba ka dama ba,
Tsoronsa tamkar Makagi bai da rana ba,
Bai bar abin duk da bai, ya halarta kai mar ba,
Don son abin duniya ka kauce ayoyi

21. Jama'a ku zo nai kira, ra'ayinmu sai mun yi,
Don me a Nijeriya za a mai da mu bayi,
Bana ba mu kaunar nadi, kuma lokaci ya yi,
Duk wanda zai murda zabe mu kona tayoyi,
Shi ne dimokiradiyyar, damarmu sai mun yi.

23. Yanayin dimokiradiyyar ya canza ‘yar lale,
Duk wadda zai, yai shirin zai zo da dan falle,
Ko da kamar hankicif, zai zo da dan kyalle,
Don goge dattin da za mu zuba cikin talle,
Don gyara Nijeriya bana lokaci ya yi.
(Wakar Siyasa Rigar ‘Yanci ta Abdul’Aziz Abdullahi Ningi)

A nan kuma an kalato abubuwan da aka yi amfani da su wajen nuna rashin amincewa da ci gaba a kan mulki da shugaba Obasanjo ya ce zai yi. Wakar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi ta bayyana kanta sosai domn ta yi suka na zahiri ga manufofin shugabanni na wancan lokaci har haka ta cim ma ruwa.

A cikin baitoci uku na wakar baiti na 12, 14, da 16. Mawakin ya bayyana irin mulkin kama karya da ake yi ta yadda duk wanda ya soki ra’ayinsu sai a ce hukumar yaki da hana zamba da halasta kudin haram karkashin shugabancin Ribadu (EFCC) ta kama mutum ma damar yana cikin gwamnati, idan kuma ba a dama wa da shi sai a tura ‘yan ina da kisa su kashe mutum. Sakamakon haka sai mawakin ya ce ko za a ci namansa ba zai fasa fadar ra’ayinsa ba na ba su yarda a zarce a kan mulki ba, kuma harkar zabe dole sai an gyara wanda ya ci a ba shi wanda bai ci ba ya yi hakuri. A gaba kuma ya ce duk wanda bai yadda da ra’ayinsu na a hana zarcewa kan mulki ba, idan Musulmi ne to ba na kwarai ba ne idan kuwa kirista ne bai san dalilin gina coci ba ga dai Abin da ya fada;

12. Wai wanda ya ce a’a, a kan ce Ribadu ya kama shi,
In ba ya cikin gammen, ka sa makasanka su harbe shi,
Karshe ko idan ya zo, mutum ba ya iya canza shi
Ko za ka ci namana, zan ce ba mu yarda ta zarce ba.

14. To, ko kau da batun zabe, in dai ba a kyautata tsarin ba,
Sai mun yi su caccanza, sannan ba su ba mu dalili ba,
In dai muka sa tsoro, ba za mu rufe su da duka ba,
To, masu ta zarcen nan, ba za mu hana su, su zarce ba.

16.Duk wanda ya ce ta wuce, ku ce bai yarda da Allah ba,
To, idan a Musulmi ne, bai gane dalilin sallah ba,
To, idan a kirista ne, bai san ma'anar gina coci ba,
Ai ni a mutuncina, gare su da bai wuce zagi ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A gaba kuma ya ce, duk wanda ya karya fadar Allah su za su masa horo, saboda ya fahimta cewa, 'yan siyasar Nijeriya ba tsoron Allah suke yi ba wannan ta sa sun yi miyagun tsare-tsare sun bata siyasar sun kashe ta. Sakamakon haka mawakin ya ce, sun sadaukar da rayinsu kuma a shirye suke su yi bore. Mawakin yana fadar ire-iren wadannan maganganu ne domin ya tabbatarwa da mutane cewa, nuna bijirewa da rashin amincewa ga masu mulki a wancan lokacin ta kai duk inda ta kai, an je makura wannan ta sa ya ce;

18.Duk wanda ya bar Allah, mu bar shi da wanda yake tsoro,
Amma mu sani duk ran da za ya kira mu wurin taro,
A cikin izinin Allah, mu taru da kanmu mu mar horo,
Mu gwada musu fau-fau cewa ba mu yarda ta zarce ba.

40.To ki ja mu mu je ganga, domin mu kawar da Obasanjo,
Ko za a yi girki na, ai dole mu rusa fadar Ojo,
Ba su bar jam'iyya ba, sun sa ta kilu da rawar banjo,
Maganar da nake yanzu, har yau ba su rarraba kayi ba.

49. Ku fada wa Obasanjo, in ji ni Haruna ya bar ture,
Na saddaka rayina, in jagoranci a mar bare,
Zan ce wa kasan nan kaf, cikin kowanne irin yare,
Ku fito mu jajirce, a kan ba mu yarda ta zarce ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

A gaba kuma, umarni mawakin ya ba wa talakawa cewa duk wanda ya yarda da zarcewa a kan mulki kamar yadda suka tsara a wancan lokacin idan ya je garinsu su jefe shi. Idan kuma hakan ta ci tura to a fito a yi bore kamar yadda (baiti na 50, da na 51) suka dakko.

50. Duk wanda ya zo zance ta zarce garinku ku jefe shi,
In ya ki ya tsere ma, dama aka ba ku ku jefe shi,
In ya mutu shi kenan, ai ya tafi ya yi asara shi,
Domin ba mu fara ba, sannan ba mu yarda ta zarce ba.

51. In ban da mutanen nan rikici suka shirya su kulla ba,
In dai iya aiki ne, sun san ba su kai ya Amerika ba,
Ba su nemi ta zarce ba, sai ku da ba kui mana aiki ba,
Ai dole mu ma bore, domin ba ka kai ya kasan nan ba.
(Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta Haruna Aliyu Ningi)

### 4.6.2 Bijirewa Ta Siyasa Mai Jibi da Addini

Siyasa da addini abubuwa ne da suka jibanci rayuwar al'umma ta duniya da lahira, kuma su na da tasirin gaske cikin jininsu. Don haka ne wadansu lokuta mawaka suke amfani da waka wajen cim ma burinsu na siyasa da addini. Akan haka ne aka sami wakoki na adini da suke nuna kin yarda da ire-iren sauyin da ake sami musamman abin da ya shafi addini.

A kokarinsa na bayyana bijirewarsu ga tsarin da ake gudanarwa lokacin gwamnatin da ta wuce ta wancan lokacin, sha'irin ya fito fili ya nuna rashin yardarsu da tsarin da gwamnain ta kawo a wancan lokaci. Bijrewar ta su, kamar yadda ya nuna ta faro tun daga kan shugaban kasa zuwan gwamna har zuwa kan maiunguwa duk ya nuna ba za su amince da mulkinsu ba. Ya kara da cewa dukkan shugabanni sun kauce daga kan tsarin da Allah ya kawo sun koma kan na Turawa. Kamar yadda ya kawo a cikin wakar ya ce, mutum da yake kashi da tusa wai a ce shi ne zai kirkira doka a bi shi bayan ga dokar Allah subahanahu wata'ala. Ya fada ya kuma ce tun dadewa yake fada ba za su bi gwamnatin da ke kan mulki ba domin tsari ne na son zuciya. Ga abin da ya fada a kasa:

4. Mu ba mu bin wani duk shakiyyin gari,
Mai kashi da tusa sai kace bodari,
Komai azabarsa a gidan kiri-kiri,
Fankam-fayau ne bai kashewa da rayawa.

5. Tun kan Presdent har da Gwamna kuwa,
Ministas, Ciyamomi mai unguwa,
Duk ba ku bin Allah mun gane kuwa,
Mu babu mu ba ku ku gane da gaggawa.

18. Ai tun-tuni abu daya ne muka fada,
Har yau da gobe da jibi shi ne dada,
Ba ma biyar su Abacha ba ma rada,
Sun bar shari'ar Rabbi sun dau ta Turawa.
(Wakar Fito-na-Fito ta Mustapha Umar Baba)

A gaba kuma, duk dai a cikin wakar ta fito-na-fito, sha'irin ya bayyana cewa, sam-sam ba su yarda da wannan gwamnatin kuma suna yin addu'a Allah ya tsine mata ya lalata ta. Abin da wannan sha'iri ya kawo iyakar nuna bujirewa kenan abu ya hada da cin mutunci ya zama bijirewa zazzafa ken an. Ga baitin nan a kasa:

20. Musulmin cikin Katsina duka mun fita,
Muna gwamnatin nan Allah tsine mata,
Allah ya tarwatsa wanda ke ja nata,
Ya tsine masa, shege wakilin Yahudawa.
(Wakar Fito-na-Fito ta Mustapha Umar Baba)

A kokarin fahimtar ire-iren wakokin da aka sami masu dauke da bayanai a kan yadda akae bijre wa tsarin tafiyar da mulkin kasa an ci karo da wakar Ba za mu bi kwansitushin ba:

9.Ba za mu bi kwanstitution ba.

17. Allah yai gargadn cewa,
Kar mu yarda da wanda bai bi shi ba.

18. Kun ga sai mu sani kwarai cewa,
Bin gwamnati bai kamace mu ba.

21.Jahiliyya mun fada cewa,
Ba za mu bi dukka dokar ku ba.

22.Ciyamomi zuwa gwamna,
Ba za mu bi dukka dokar ku ba.
(Wakar Ba Za Mu Bi Kwansitushin Ba ta Aliyu Rabi'u Kurna Kano)

Ta la'akari da kunshiyar baitocin da suke sama, za a fahimta cewa, lalle an kai makura tunda sha'irin ya ce ba za su bi duk wata doka da aka saka musu wajen tafiyar da harkokin kasa ba ma damar dokar ba ta Allah ba ce. A takaice sha'irin yana kokarin bayyana manufa ce ta a koma ga kur'ani da sunnah wajen tafiyar da tsarin mulkin kasa, idan kuwa ba haka ba za su bijire wa duk wani shugaba tun daga shugaban kasa har zuwa ciyaman tunda ba bisa tsarin dokokin da Allah ya tsara suke a kai ba.

A gaba kuma sai ya ce:

23.Sarkin Gargajiya shima,
Ba za mu bi dukka dokarsa ba.

24.Balle dagutu babban naku,
Ba zai doka mu amsa ba.

32.Balle wai don sun mana tsawa,
Sam ba za mu firgita ba.
(Wakar Ba Za Mu Bi Kwansitushin Ba ta Aliyu Rabi'u Kurna Kano)

Kamar yadda sha'irin ya bayyana a nan bijirewarsu ba ta tsaya a kan zababbun shugabanni ko wadanda aka nada ba, abin ya kai har ga kan sarakuna wadanda su gado suka yi kuma ake ganin shugabannin Musulunci ne. Ya ce, su ma sun zama 'yan koren Yahudu da Dagutu domin haka ba za a bi su ba.

A nan kuma sai ya ce:

37. Kuma dai sai mun fada cewa,

Ba za mu bi dukka dokarku ba.

38. Mun yi tawaye muna cewa,
    Ba za mu bi wagga gwamnati ba.
39. Bara'a ce muke nunawa,
    Mu ba ma bi gwamnatai ba.

(Wakar Ba Za Mu Bi Kwansitushin Ba ta Aliyu Rabi'u Kurna Kano)

A nan kara jaddada manufa ce da karfafawa sha'irin ya yi a kan manufarsa ta kin aminta da tsarin mulkin kwansitushin wanda a kansa ne ake tafiyar da harkokin kasar nan. Ya kara da cewa, sun yi tawaye da wannan tsari kuma ba za su bi tsarin ba.

Duk dai a cikin wannan waka ta ba za mu bi kwansitushin ba, an sami sha'irin yana cewa:

54. Ko da za a harba nukiliya,
    A cikinmu ba za mu fasa ba.
69. Domin haka ne muke cewa,
    Ba za mu ma siyasa ba.
70. Tsari na Amerika ne aka dauko,
    Ba tsari na Allah ba.
71. Kuma tsarin mun yi mai tawaye,
    Tun bai tsai da tsari ba.

(Wakar Ba Za Mu Bi Kwansitushin Ba ta Aliyu Rabi'u Kurna Kano)

Ta faru ta kare in ji masu iya magana wai "an yi mai dame daya sata" Da alama sha'irin ya kule bisa bin wannan tsari na kwansitushin. Ya fito ya bayyana cewa, ko za harba musu nukiliya ba za su bi wannan tsari ba. Kamar yadda aka sani nukiliya shi ne kololuwar makami da kowace kasa take so ta mallaka saboda da tasirinsa, hasali ma duk kasar da ta ke da shi ana mata daukar kasar da ta ci gaba kuma ta zama gagara dangi. Kuma makami da ake amfani da shi wajen aiwatar da kololuwar mugunta To shi ne sha'irin ya ce ko wannan aka harba musu ba za su bi wannan tsari ba.

A gaba kuma an kyallaro wani abu daga cikin waken bara'a ta Abdulmumini Abubakar Bauchi inda yake cewa:

1.Waken bara'a dai dole ne,
Don mu nuna rashin yardanmu ne,
Da tsiyansu da zalincinsu ne.
(Waken Bara'a ta Malam Abdulmumini Abubakar Bauchi)

A cikin wannan waka ta Bara'a 'yar uwar dayar ce wakar ba za mu bi kwansitushin ba. Ita ma ta yi nuni da manufa ta kin yarda da tsarin da ake amfani das hi wajen tafiyar da harkokin mulki. Ya bayyana cewa, ba za su yarda ba domin babu komai a cikin tsarin sai zalunci.

Haka kuma an tsinci wani abu daga cikin wakar Tawaye ga shugabanni ta Malam?

10 To ku sani mahukuntan zamani,
Mun yi muku tawaye tuni,
Komi za ku yi mana mun sani,
An yi wa Muhammadu Mujitaba.

15 To muma ba za mu bi su ba,
Ba za mu bi tsarin nasu ba,
Ku Turawa kuka sa gaba,
Ba ku dau Allah da Rasulu ba.

20 Mazon Allah ya sanar da mu,
Muhukuntannan kuma mun gamu,
Jama'a kuma tashi mu gangamu,
Mu yi tawaye ba fargaba.
(Wakar Tawaye ga Shugabanni ta Malam)

A cikin wannan waka ta "Tawaye" ta yi Allah wadai da tsarin da ake kansa na kwansitushin, ya ce za su yi tawaye ga wannan tsari ba tare da jin tsoro ko yin wata fargaba ba. Ya ce duk abin da za a musu sai a musu, babu irin abin da ba a yi wa Mazon Allah Annabi Muhammadu ba  Tsira da Amincin Allah su kara tabbata

a gare shi a lokacin da ya kawo Musulunci ya kuma bijire wa addinin jahilliya. Ya kara da cewa, tun da dokar da suka kawo ba ta Allah ba ce, ba za su karba kuma ba za su bi ba.

## 4.7 BIJIREWA A WAKAR JAM'IYYAR APC "MASU GUDU SU GUDU" TA DAUDA KAHUTU RARARA

Asalin wannan waka shi ne fitowar Janar Muhammadu Buhari takarar zaben shugaban kasa ne 2015 wanda aka yi ranar 28/03/2015, a inda kuma Buharin ya yi nasara. Buhari ya yi farin jini kwarai da gaske musamman ma a wurin talakawa wadanda suke ganin waccan gwamnatin da ta shude ta sa su cikin kuncin rayuwa; ana ganin da an sarrafa arzikin da kasar nan take da shi da wasu ba su zama biliniyoyi ba, alhali wadansu suna cikin halin kaka-nika-yi.

Mawakin ya tsara wakar ne bayan Buhari ya yi nasara a zaben da aka yi. Ga wasu baitoci wadanda a cikinsu mawakin yake bayyana ra'ayinsa na kin yarda da kuma amincewa da daya jam'iyyar. Ya yi suka kwarai da gaske a kan manufofin waccan jam'iyyar musammam abin da ya shafi sarrafa tattalin arzikin kasa, wanda shi ne kanwa uwar gami na tafiyar da duk wasu tsare-tsare da za su inganta rayuwar 'yan kasa da ma ita kanta kasar. Misali:

A kokarinsa na nuna kin yarda da PDP mawakin jam'iyyar adawa da ta yi nasara a zaben da aka gudanar a wannan lokaci, Dauda Kahutu Rarara ya bayyana cewa, sun gama da PDP manufa ta fadi zabe domin haka an hallakata ta mutu. Sakamakon haka, mawakin yana fada wa shugaban da ya sha kaye a zabe cewa, ya yi maza ya hada kayansa ya bar musu gidan gwamnati saboda nasu gwanin da aka zaba ya shiga.

1.A'a masu gudu su gudu, bana dai Janaral ya karbi sama,
Mun hallaka PDP bana APC ita ce da kasa,
Mai malfa fara shiri bana za ka fice bila da gudu gaggawa.
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

A gaba kuma ga abin da yake cewa;

Ku gaya musu ma su gudu su gudu,
Kai! In kasan kai sata ka gudu,
Hai! Ku gaya ma barayin can su matsa,
Ko way yi sake Janaral ya ritsa,
Ga baba Buhari janar a sama, hayya!
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Da alama ya gama yanke hukunci a kan mukarraban gwamnatin da ta shude cewa sun yi wa-ka-ci-wa-tashi da dukiyar mutanen Nijeriya. Wasu sun yi sata wasu kuwa rashawa aka yi ta karba wadansu kuma cin hanci wasu kuwa har halasta kudin haram suka yi. Idan ba haka ba babu dalilin da mawakin zai ce wai in ka san ka yi sata ka gudu! ya kara da cewa a gaya wa barayi su gudu, wannan duk alamu ne na kin yarda da abubuwan da waccan gwamnati da mutanenta suka tafka na bangaren cin hanci

Mawakin ya kara da cewa, jam'iyyar da suka kayar a zabe tumbir suka yi mata, wato sun kwace mukamin da aka zabi danta a kai. Manufar mawakin a nan ita ce a yanzu suke da rinjaye a zabe tun da su suka sami shugaban kasa, jam'iyyar adawa kuwa ta tashi da kusan a ce babu komai, kamar mutum ne a cikin sutura sai a yaye suturar a bar shi tumbur. wannan ta sa ya ce:

3. Ita PDP tumbur muka ce za ai kuma an yi haka,
Mun hallaka PDP a saman da kasan mu ne da duka,
A kasa a tsaya a raka in ji Baba janar shi ne waraka,
Yau ga canji ya zo APC kullum na habaka.

(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

A gaba kuma Dauda Kahutu Rarara ya kara da bayyana irin rashin adalcin gwamnatin da ta fadi daga kan mulkin Nijeriya ta yi wanda abin har ya gama da shi. Ga abin da ya fada:

4. Inji masu karin magana wasu sun kare wasu na tafiya,
Wasu sun yi abin kunya su dan baki an fada ma kaya,
Wasu na ta shirin hijira muka ce masu don Allah ku tsaya,
Ka san a karin magana wani zai magana ya tuna da jiya,
Cikin a saya a biya in an mana adalci mu taya,
Ni nasan iya tsawo baya wuce dai kayi da wuya,
Ga shi karshen PDP ya zo jama'a murna mu taya,
A garinmu mahaifata sun barni ina daki na haya,
Yanzu gamu da APC jirgin maja Allah ka taya,
Allah ka taya mu riko Buhari ka je bila ka rike talakawa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Sai ya kara da cewa:

9. Ya al'umma na kasa ku taho ku ji labarin da ake,
Janaral ya amshi kasa amma fa kusan halin da take,
Farko ga cin hanci ya yadu a kan layin da muke,
Kuma bashi ya yi yawa su dan baki bankaurar su suke,
Kasa ga shi babu tsaro kullum ibar rayinmu ake,
Tattalin arziki na kasa duk ya rushe maganar da ake,
Harkar noma ziro wuta da ruwa hanya a hade,
Harkar ilimi ziro kullum yajin aikinsu suke,
Kuma fanni na lafiya likitoci zaluntarsu ake,
Ana ta bukin murna amma fa kusan halin da muke,
Janaral ya karbi kasa shi dai burin gyarata yake,
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

A cikin wannan layukan waka a fili mawakin ya bayyana cewa akwai cin hanci a cikin wannan kasa, wannan kuwa ba zai rasa nasaba da halin da gwamnatin da ta zo ta sami kasar a ciki ba. Abu ne sananne cewa, a lokacin gwamnatin da ta shude yajin aikin ma’ikata ya yawaita kwarai da gaske, kama daga ma’ikatar ilimi da ta

lafiya da ta jiragen sama, ta kai ta kawo har ‘yan sanda sai da suka yi barazanar shiga yajin aiki. Yawaitar cin-hanci a tsakanin jami’an gwamnati ake zargi ya kazanta da kuma kawo dagulewar al’amuran kasar baki daya.

A nan kuma, mawakin yana jan hankalin talakawa a game da irin shigo shigo ba zurfi da ‘yan PDP suka yi wa shugaban kasar da ya fadi a zabe suka yi masa a garin Kano. Sun nuna masa cewa, su ne da garin Kano, kuma jam’iyyarsu ita talakawa suke yi kuma ita za su zaba. Abin har ya kai da an basu mukamai a gwamnatin tarayya, amma da zabe ya zo sai ‘yar manuniya ta nuna. Ya ba wa wadancan mutane suna na banza inda ya kira daya da tsohon kwano, wato ya lalace ba shi da amfani kenan. Dayar kuma sai ya ce kira ta da suna kilaki wato matar banza kenan da ba ta da aure.

10. Ga ministan nan na wata shida kalllo ya koma a sama,
Mundubawa zan koma ranar handin oba rigima,
Maganar tsohon kwano an kwashi dala fansho na kuma,
Kun yaudari mai malfa kun ce a Kano ku ne a sama,
Da kilaki ta je zabe a Sauna Kawaji a kai rigima,
Ita PDP sintir akai mata naga zani a sama.
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

A gaba kuma sai ya ce:

15.Kai masu gudu su gudu bana GMB shi ne da kasa,
In kaji ana a gudu watakila barayi ne mu tasa,
Mai tsoron GMB idan ka tara ka cuci kasa,
Duk mai zagin Janaral watakila munafinci ya dasa,
Ga janar ya karbi sama ku masu munafunci ku gusa,
Don shi mulkin janaral baya ra'ayin danne na kasa,
Sai baba Buhari janar don shi dai alkairi ya tasa,
Masu kin ka barayi ne sun san da akwai kulli a kasa,
A kasa sai mui murna don mun harbo kusu na bisa,
Janaral kai ne da bisa Allah ya taya ka riko Janaral dan baiwa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Mawakin ya fito fili yana fadakar da mutane inda aka fito daga wajen gwamnatin da ta wuce, ya bayyana cewa kusan komai na ayyukan raya kasa sun rushe wadanda ake tafiyar da su kuma sun tsaya cak. Yana jan hankalin mutane da a yi a sannu tunda maganar gyara ake yi, masu iya magana suna cewa “barnar kwana guda, wata guda ba zai isa a gyara ta ba” wannan ta sa mawakin yake kiran mutane da su yi hakuri da wannan gwamnatin.

A nan Dauda Kafutu yana yin fadakarwa ce ga mutanen Arewa da suka nuna rashin yardarsu da jam’iyyar adawa wadda kuma ita ce ta lashe zabe. Yana bayyana musu cewa, tun da gwaninsu ya fadi sai su je su raka shi har garinsu tunda yanzu sai a koma gidan gado, fita daga fadar shugaban kasa ya zama dole. A cikin wakar ya zayyano wadanda suka nuna butulcinsu ga wannan yanki na Arewa a saboda da gwaninsu wanda ba yanki daya suka fito ba. Ya jero su inda ya bawa kowa suna daidai matsayinsa ko siffarsa ko kuma yanayinsa ko wani abu da ya yi ya zame masa sheda. ire-iren wadannan sunaye da ya kawo sun hada da Duna da ministan hayaniya da ya kira stufid da mai rodi da mai bilicin da sauransu, wannan ta sa ya ce:

16. Su Duna ana ta shiri bana za a Otoke zuwa rakiya,
Tilas na kira anti mai bilicin dawo kiy rakiya,
Wai ina kauran mata da kai a cikin wannan rakiya,
Da na sakkwato ba sauki tilas ka shigo wannan rakiya,
A rufe ma da fatiya Malam Namadi na waya tu waya?
Ku kira mani mai rodi shi ma zai je wannan rakiya,
Tsohon gwamnan Barno da yasa malfa mun kori kaya,
A Kano tsohon kwano yana ciki duk za sui rakiya,
A ministan hayaniya ku kira shi sutufid of za yiya,
Ku tunawa fes ledi ta Otoke bataun magana ta jiya,
An gyara gidan gado a Otoke ana ta shirin tafiya,
Ga Buhari cikin bila haihuwatai na yaye gajiya,

Ga shi albarkar 'ya'ya ita ce sanadi mun kori kaya,
Allah raka taki gona can a Otoke mu kori kaya,
Janar ya amsa janar bana dai bila kaine da rikon talakawa.
(Wakar Masu Gudu Su Gudu ta Dauda Kahutu Rarara)

Da ya karkato wajen bangaren mata, mawakin ya bayyana irin katobarar da matar wancan shugaban kasa ta yi na zagin mutane musamman mutanen Arewacin Nijeriya a lokacin da mijinta yake yawon kamfe. Ya fada mata cewa, yanzu maganar zagi ta wuce sai dai ta zagi wani, zabe kuma sun fadi. A kokarin mawakin na nema mata mafita shi ne ya ce sai ta koma garin mijinta. Siyasarsu ta watse ta fatattake don haka kaikayi ya koma kan mashekiya. Ga abin da ya ce a kasa:

30. Bari in gaya wa fes ledi bana Otoke za ki,
Madam kina ta zaginmu kina yabon mijinki,
A yanzu ba musu sai kin gane kuskurenki,
Otoke za ki koma Abuja ta yi tsada.
Lema ta yage ta fatattake nace ta yage,
'Yan malfa mun maku gwalo,
Rarara ya ce ai zigidir,
Ai wanwar,
Ai tumburrrr,
(Wakar Dauda Kahutu Rarara ta Masu Gudu Su Gudu)

**4.8 Kammalawa**

Wannan babi ya tattaro abubuwa muhimmai da suka faru sakamakon wakokin masu dauke da bijirewa da aka sami bayan kafuwar mulkin domokuradiyya. Sakamakon wakokin da aka nazarta, ya samar da batutuwa biyar manya da a kansu ire-iren bijirewar da aka sami ta ginu. Da farko an sami bijirewa tsakanin jam'iyyun siyasa, a karkashin wannan an fuskanci abin da ya shafi abokan adawa, da kuma gamayyar jam'iyyu. Batu na biyu da bijirewa ta ginu a kansa a wannan

babi shi ne, bijirewa shugabannin mulkin siyasa. A karkashin wannan an dubi rashin adalci da yin mulki da yaudara. Batu na gaba shi ne, bijire wa rusa tattalin arzikin kasa, a nan an fuskanci cin hanci ne kawai, wato yadda shugabanni suka rika wawashe dukiyar kasa suka lalata tsarin inganta rayuwar ‘yan kasa ta hanyar rashawa da ha’inci. Batu na gaba wanda kusan shi ne kandami a cikin saura shi ne na farfaganda. A karkashin farfaganda an dubi abubuwa da dama da suka hada da; zalunci, da tonon silili da kuma zambo. Batu na karshe shi ne wanda ya shafi, bijire wa tsarin tafiyar da gwamnati, a karkashin wannan batu an mayar da hankali a kana bin da ya shafi yadda ‘yan kasa suka rika yin kalamai a cikin wakoki da yake nuna rashin yardarsu da tsarin da ake tafiyar da gwamnati a kansa.

## BABI NA BIYAR
## NADEWA

### 5.1 Kammalawa

Kamar yadda aka gani, sunan wannan aiki “ Bijirewa A Wakokin Siyasa: Bincike Kan Wakokin 1903-2015.” A kokarin gabatar da aikin, a cikin babi na farko an kawo bayani a kan dalilin bincike, da manufar bincike, sai kuma Muradin bincike wato muradin da aka hango, kuma ake son cim mawa da wannan nazari. Wannan shi ya kaimu ga hasashen da aka yi a idan aka gudanar da wannan aiki. Daga hasashe kuma, sai aka yi tsokaci kan Farfajiyar bincike da kuma hujjojin da aka dogara da su don gudanar da wannan bincike. Hanyoyin tattara bayanan binciken sun fada karkashin wannan babi, inda aka fayyace, dalla-dalla, duk wata hanya da aka a bi domin ganin cewa haka ta cim ma ruwa. Haka kuma duk dai a karkashin hanyoyin tattara bayanai, an dubi dalilin da yasa aka zabi wakokin da aka yi amfani da su, da kuma yankunan da wakokin suka fito. A karshe an kawo bayani a kan ra’in bincike, wato ra’in da aka dora wannan aiki a kansa.

A cikin babi na biyu, an nazarci abubuwan da masana da manazarta suka kawo wadanda suke da nasaba da wannan bincike, da kuma ma’anonin wadansu muhimman batutuwa, domin fayyacewa. An kawo bayanin masana a kan kasar Hausa, a gaba an kawo bayani a kan ginuwar mulki a kasar Hausa, da tarihin wakokin bijirewa a kasar Hausa. Sai kuma ma’anar siyasa da ginuwar siyasar zamani, haka kuma an kawo abin dam asana suka fada a kan Dimukiradiyya da kuma akidar neman sauyi a siysar kasar Hausa. A gaba, an sami abubuwan dam asana suka fada a a kan ire-iren gwagwarmayar da ‘yan kasa suka yi da Turawan

Mulkin Mallaka, a gaba an kawo bayanin da aka sami a kan bore musamman wanda aka taba yi a cikin Daular Usumaniya.

Babi na uku kuwa, ya tattaro abubuwa muhimmai masu dama a tarihin wakokin siyasa a kasar Hausa. Ya tabo zamunna da suka hada da zuwan Turawan Mulkin Mallaka kasar Hausa, irin yadda aka yi gwagwarmaya da su ta yadda har wakoki aka rinka rubutawa ana karantawa a game da nuna rashin yarda da zuwan nasu. Haka kuma an nazarci wakokin da aka yi wa siyasun Jumhuriya ta farko, wadannan siyasu sun hada da NEPU da NPC wadanda su ne manyan siyasu a nan yankin Arewa wadanda aka yi musu wakoki cikin harshen Hausa. A gaba kuma an dubi wakokin da aka sami a cikin Jumhuriya ta biyu, kamar ‘yar uwarta Jumhuriya ta farko, a nan ma jam’iyu biyu ne suka yi fice a yankin Arewa duk da cewa ba su kenan ba. Wakokin  jam’iyyun siyasar da aka kalla a wannan Jumhuriya sun hada da NPN da kuma PRP. A cikin Jumhuriya ta uku an nazarci bijirewa a cikin wasu wakokin jam’iyyun siyasar da suka sami. An nazarci wakokin jam’iyyar SDP da NRC haka kuma an zakulo wadansu abubuwa a cikin wakokin jam’iyyar UNCP da kuma ta NCPN. A karshen wannan babi an nazarci bijirewa a cikin wakokin da aka yi sakamakon irin mulkin da Sarakuna suke shimfidawa a kasar Hausa, wanda yake cike da rashin adalci da kuma da kin bin doka, abin da ya kai har wakoki aka sami sha’irai sun rubuta domin fadakar da talakawa.

Babi na hudu ya tattaro abubuwa muhimmai da suka faru sakamakon wakokin masu dauke da bijirewa da aka sami lokacin mulkin Domokiradiyya. Sakamakon

wakokin da aka nazarta, aa sami da batutuwa biyar manya da a kansu ne ire-iren bijirewar da aka sami ta ginu. Da farko an sami bijirewa tsakanin jam'iyyun siyasa, a karkashin wannan an fuskanci abin da ya shafi abokan adawa, da kuma gamayyar jam'iyyu. Batu na biyu da bijirewa ta ginu a kansa a wannan babi shi ne, bijirewa shugabannin mulkin siyasa. A karkashin wannan an dubi rashin adalci da yin mulki da yaudara. Batu na gaba shi ne, bijire wa rusa tattalin arzikin kasa, a nan an fuskanci cin hanci ne kawai, wato yadda shugabanni suka rika wawashe dukiyar kasa suka lalata tsarin inganta rayuwar 'yan kasa ta hanyar rashawa da ha'inci. Batu na gaba wanda kusan shi ne kandami a cikin saura shi ne na farfaganda. A karkashin farfaganda an dubi abubuwa da dama da suka hada da; zalunci, da tonon silili da kuma zambo. Batu na karshe shi ne wanda ya shafi, bijire wa tsarin tafiyar da gwamnati, a karkashin wannan batu an mayar da hankali a kana bin da ya shafi yadda 'yan kasa suka rika yin kalamai a cikin wakoki da yake nuna rashin yardarsu da tsarin da ake tafiyar da gwamnati a kansa.

**Sakamakon Bincike**

Nazari a kan wakokin siyasa, wani fage ne mai bukatar zuzzurfan bincike mutuka musamman ma ga mai karatun digiri na uku. Wakokin siyasa, wakoki ne masu kunshe da hikimomi da kuma dabaru na jawo hankali domin samin isar da sakon da suke son isarwa ga jama'a. A cikin ire-iren sakonnin da suke isarwa har da bijirewa, manufa bayyana ra'ayin rashin amincewa ko kin yarda da ra'ayin wani ko wasu. Sukan yi amfani da hanyoyi ko hikimomi iri-iri wajen cim ma wannan manufa..

An fahimci cewa, har ya zuwa wannan lokaci da ake ciki ana jin duriyar wakoki na Hausa da wakokin siyasa masu dauke da bijirewa, duk da cewa a halin yanzu da yawa daga cikin sha'irai ba sa dora wakokinsu a kan kishin kasa da akida, da yawansu sun zama 'yan neman kudi, sababin na dauri da suke yin wakokin domin ra'ayi.

An nazarci wakokin bijirewa a kasar Hausa, amma, an fahimci cewa da yawa daga cikin wakokin ratsin bijirewa ce a cikinsu. Kusan kashi tamanin na yawan wakoki (67) da aka kebance aka nazarta a kan wanna siga suke. Kashi ashirin ne daga cikinsu za a iya bugun kirji a ce na bijirewa ne muraran

Har ya zuwa wannan lokaci da ake ciki a yanzu wato karni na ashirin da daya ana samin wakoki masu dauke da bijirewa da kuma wadanda suke dauke da ratsin bijirewa, musamman a fagen siyasa da addini da Al'adu da kuma abin da ya shafi tattalin arzikin kasa.

Da tafiya ta yi tafiya, kishin kasa ya yi karanci daga zukatan marubuta da mawakan siyasa, sai ya kasance akan sami mawaki ya yi wa fiye da jam'iyya daya waka. haka kuma akan sami mawakan suna yawo, ko kuma ana dauko su haya jiha-jiha ana neman su yi waka ga dan siyasa a biya su.

Wakokin siyasa na lokacin zuwan Turawa sun fi daukar kalmomi masu nauyi wadanda suke fasalta sosuwar da zuciya ta yi domin furta sako. Haka abin ya ci gaba, na Jumhuriya ta farko sun fi na Jumhuriya ta biyu daukko irin wadancan kalmomi da aka yi amfani da cikin waka a Jumhuriya ta biyu sun fi na Jumhuriya

ta uku, na Jumhuriya ta uku sun fi na Jumhuriya ta hudu. A cikin Jumhuriya ta hudu kuma wakokin siyasa sun fi na jam'iyyun siyasa.

A wannan zamani an fi samin mawaka da yawa amma wakokin ba su da afki sai ka ga mawaki ya yi wa jam'iyyar adawa waka, can kuma ka ga ya yi wa jam'iyya mai mulki waka lokaci guda kuma cikin jiha guda ko makwabtan jihohi. (Misali Auwwalu Ibrahim Gwammaja, ya yi wa katukan Sakkwato Alhaji Maigari Dingyadi dan takarar gwamna a jihar Sakkwato karkashin jam'iyyar D.P.P. mai suna *Dan Halak*, sai ga shi wannan mawaki ya fito ya bugi kirji da cewa shi ne ya rera wakar Abubakar Gada mai neman tikitin takarar gwamna a jahar Sakkwato karkashin jam'iyyar P.D.P. mai suna *Ta bare Ta Ragargaje*. haka abin ya kasance a kan Garba Gashua, ya yi wa jam'iyyar NRC waka, sannan ya yi wa SDP waka. Shi kuwa Aminu Ibrahim Dandago kusan kunshiyar waka daya ya yi wa jam'iyyun siyasa har uku waka da ita, jam'iyyun sun hada da NCPN, da APP, da kuma jam'iyyar APC).

Manazarta adabi, su ma za su ci gajiyar wannan aiki, don aikin ya tabo wani ginshikin sashe na adabi, wato waka. Ko a cikin rabe-raben adabi, manazartan suna ji da waka, domin a iya cewa, an fi yi mata hidima fiye da sauran dangoginta. Sannan kuma, yadda aka sami cakuduwar nau'o'in wakokin Hausa a wuri daya, shi ma wani ci gaban adabi ne.

Bahaushe kan bijire ne idan ya fahimci cewa ana so a tilasata masa ya yi, ko ya bi wani abu da ba ya so, ko bai gamsu da shi ba. Haka kuma, yakan bijire idan yana

cikin yin abu sai ya fahimci cewa ci gaba da aikata, ko bin abin zai cutar da shi ko ya cutar da sauran jama'a.

Da yawa daga cikin wakokin da aka nazarta suna dauke da jigo na siyasa da ya kama daga kamfe zuwa zabe da kuma shari'ar zabe. Akwai wakokin da suke dauke da jigon bijirewa al'adu da addini da kuma wadanda suke da dangantaka da tattalin arzikin kasa.

A kasar Hausa, waka wata hanya ce ta isar da sako, don Hausawa sun rike ta tun zamani mai tsawo, suna amfani da ita, suna isar da manufofinsu da sakonninsu ga jama'a

Bijirewa tana da sigogi da ake amfani da su wajen bayyana ta, irin sigogin da ake bayyana ta da su sun hada da hijira da shahada da kamfe da zabe da shari'ar zabe da salon magana, da zambo da zagi da tonon silili da addu'a da habaici da sauransu.

Haka kuma, an fahimci cewa, harshen 'yan adawa ya fi zafi da kaifi, kuma kalamansu kowane lokaci a cike suke da kalmomi masu nauyi na muzantawa.

## MANAZARTA


Abbinket, J. et al (2003). *Rethinking Resistance, Revolt and Violence in African History*. Leiden.

Abdulkadir, D. (1974).*Poetry, Life and Opinions of Sa'adu Zungur*. Zaria:Northern Nigeria Publishing Company.

Abdulkadir, D. (1979). *Zababbun Wakokin Da da na Yanzu*. Lagos:Thomas Nelson (Nigeria) Ltd 8 Ilupeju Bye-Pass P. M. B. 21303 Ikeja.

Abdullahi, B. (2013). Markisanci a Wakokin Fiyano: Misalai Daga Wakar Siyasa Ta Baubawan Burmi *Zauren Waka*. Journal of Hausa Poetry Studies. Department of Nigerian Languages, Sokoto:Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Abdullahi, I. S. S. (2008). Jiya ba Yau ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Karatun Digiri na Uku, Sashen Harsunan Nijeriya. Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Abdullahi, I. S. S. (2013) Dimokiradiyya A Bamagujen Ma'auni. 1st National Conference in Language, Lterature and Culture.Center for the Study of Nigerian Languages Kano: Bayero University, Nigeria.

Abdullahi, N. (1998). Poetry as a Weapon of Sruggle for Liberation : A Study of Some Selected Poems of Dennis Brutus and Oswald Mtshali M. A. Dissertation Department of Modern European Language and Linguistics. Sokoto :Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Abubakar, at el. (2013). A Critical Assesement of Anti-Corruption Crusade in Nigeria, 1999- 2010. A Paper Presented at 57th Congress of the Historical Society of Nigeria, Lapai:Niger State.

Abbraham, R. C. (1962.) *Dictionary of Hausa Language*. London: Hodder and Soughton.

Adamu, M. (2010). *The Major Landmarks in in the History of Hausaland*. The Eleventh Inuagural Lecture. Sokoto:Trans-Akab Printing and Publishing.

Adamu, M. T, (2003). *Asalin Hausawa da Harshensu*. Kano:Dan Sarkin Kura Publishers.

Adeleye, R. A. (1971). *Power and Diplomacy in Northern Nigeria 1804-1906.*

The Sokoto Caliphate and its Enemies. Longman.

Ahmad, M.S. (1900). Almuyassar Ulumul Fikira Wat Tafkir. Darussadafa, Alkahira.

Ahmad, A. (Mrs), (1981). An Anthology of the Verse of Nana Asma'u. M. A. Hausa. London: SOAS, University London.

Ahmed, A. (1981). Matsayin Kirari a Adabin Baka na Hausa. Kundin Kammala Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Bayero University, Nigeria.

Ahmad, A. A. (2003). Nzarin Zambo-Zagi a Adabin Hausa:Tsokaci kan Siyasar Arewacin Nijeriya (1950-1960) Kundin Kammala Karatun Digiri na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto:Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Ainu, H. A. (1984). Rayuwar Malam Ibrahim Khalil da Wakokinsa. Kundin Karatun Digiri na Farko. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Ainu, H. A. (2007). Rubutattun Wakokin Addu'a na Hausa: Nazarin Jigonsu da Salonsu. Kundin Digiri na Uku. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Al-Hajj, A. M. (1973). The Mahdist Tradition in Northern Nigeria. Ph, D Thesis Department of History. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Al-Maududi, A. A. (1963). *A Short History of the Revivalist Movement in Islam*. Lahore: Islamic Publication.

Ajayi, A. (1983). Women in Transition in Zulu Sofola's Play's in *Nigerian Theatre Journal* vol 1 No 1.

Amin, M. L. (1997). Ra'ayin Sauyi a Wakokin Sa'adu Zungur. Takarda da aka Gabatar a Taron Kungiyar Marubuta da ManazartaWakokin Hausa, Dandalin Hikima.

Amin, M. L. (2000). Wakokin Jihadi Goshin Karni na 21 Mujjallar *Hausa Studies*. Department of Nigerian Languages, Sokoto:Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Amin, M.L. (2004). Radicalism in the Poetry of Sa'adu Zungur: *Journal of Arts*

*and Humanities* vol 1 No 2. International Reserch Development Institute.

Amin, M. L. (2006). Reformism As The Theme In The Hausa Religio- Political Poetry, *African Cultural Studies.* Vol. 18, No Tylor and Francis Grovis.

Amfani, A. H. (1996). Aspect of Agreement Reletions in Hausa Clause Structure. Ph, D Thesis. Ibadan: University of Ibadan.

Amfani, A. H. (2011). Hausa da Hausawa: Jiya da Yau da Gobe. A Paper Presented at a One Day Symposium. Department of African Languages and Cultures. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Amfani, A. H. (2012). Hausa da Hausawa: Jiya da Yau da Gobe. *Festchscript in Honour of Prof. Dalhatu Muhammad.* Department of African Languages and Cultures. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Anis, I. et al (1934). *Almunjidul Wasid*. Darul jeel Beirout:Lebanon.

Ashiru, D. (2009).The Judiciary and the Democratisation Process in Nigeria. In I S.

Asirvatham, E. et al. *Political Theory* Ram Nagar, New Delhi-110055. S Chand and Comppany Ltd.

Babalobi, B. (2008). Corruption In Nigeria: Its Causes and Solutions A Report of a Workshop for Civil Society Organisation in The Fight Against Corruption Organised by Zero Corruption Coalition (ZCC), Lagos.

Bako, A. et al (2014). *Tradionalist and Nationalist Values in Politucal Practices: A Biography of Malam Lawan Danbazau (Ki-Kasala)* 1922-2000. Sokoto:Usmanu Danfodiyo University Press.

Barry, P. (1995). eds. *Beginning The Theory: An Introduction to Literary And Cultural Theory*. New York:Manchaster University Press.

Beargery, G. P. (1934). *Hausa-English and English-Hausa Vocabulary.* London:Oxford University Press.

Birnin-Tudu, S. Y. (2007). Jigo da Salon Rubutattun Wakokin Furu'a na Karni na Ashirin. Kundin Digiri na Uku. Sahen Nazarin Harsuna Nijeriya. Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Birniwa, H.A. (1981). The Infraji i and iv of Aliyu Namangi. MA Thesis. London: SOAS, University of London.

Birniwa, H. A. (1987) Conservatism and Dissent: A Comparative Study on NPC/NPN and NEPU/PRP Hausa Political Verse From Circa 1946-1984. Ph, D Thesis Department of Nigerian Languages. Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Birniwa, H. A. (2006). Shahada Zahira: An Analysis of Imamu Muhammadu's Verse on the 1906 Hadejia Revolt. A Pper Presented at the Conference on the British Conquest of Hadejia Emirate and its Aftermath to Mark a Centenery of Hadejia Emirate's Resistance to British Colonial Invasion, April 1906 – April 2006.

Birniwa, H. A. (2015). Gudummuwar Wakokin Hausa Ga Dorewar Dimokiradiyya: Misali Daga Wakokin Dauda Kahutu (Rarara). Takarda Da Aka Gabatar a Taron Bita Na Kwana Guda A Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Barnhart, W. et al (1977). *State Intervention and Rural Resistance*: The Transkei 1900 – 1965. In Martinda A. Klein (ed) *Peasants in Africa* London: Sage.

Bunza, A. M. (2001). A Dade Ana Yi Sai Gaskiya. Laluban Gurbin Gaskiya Cikin Adabin Hausa. Mukala da Aka Gabatar A Taron Kara wa Juna Sani, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Bunza, A. M. (2002). Gwagwarmayar Malaman Sakkwato da Dasisar Nasara. Yunkurin bi-ta-da-kullin Akirka Cikin Wakar Osho ta Malam Muhammadu Huci, Tahamisin Malam Mahrazu Barmu Kwasare cikn Juyayin Masana:Mukalun Binciken Adabi da Harshe da Al'adun Hausawa don Juyayin Malam Habibu Alhassan (1935-1995). Huhkumar Fassara, Ofishin Fassara Jakadiyar UNESCO.

Bunaza, A. M. (2006). *Gadon Fede Al'ada*. Lagos:Tiwal Nigeria Ltd.

Bunza, A. M. (2012). Duniya a Ma'aunin Bahaushe *Harshe 6* Journal of African Languages. Department of African Languages and Cultures. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Bunza, A. M. (2013). Makamin Dimokiradiyya A Falsafar Al'ada. 1st National Conference in Language, Lterature and Culture. Center for the Study of Nigerian Languages, Kano: Bayero University, Nigeria.

Bunza, M. U. (2005). The Iraninan Model of Political Islamic Movement in Nigeria (1979-2002). *L' Islam Politique au Sud du Sahara. Identites, Discours et Enjeux.KARTHALA22-24,* Boulevard Arago 75013 Paris.

Bunza, D. B. (2012). Nazarin Diwanin Malam Maharazu Barmu Kwasare.

Kundin Kammala Karatun Digiri na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Coleman, J. S. (1958). *Background to Nationalism.* Barkelys and Los Angles:University of California Press.

CNHN/BUK (2006) *Kamusun Hausa*. Zaria:Ahmadu Bello University Press Limited.

Danbazau, L. (1981).*Tarihin Gwagwarmayar NEPU da PRP 1950-1981.* Zariya: Gaskiya Corporaion

Danbazau, L. (2001).*Politics and Religion in Nigeria.* Kaduna:Vengurd Printer and Publishers Limited Nigeria.

Dangambo, A. (1980). Hausa Wa'azi Verse from 1800 – 1970: A Critical Study of Form, Content, Language and Style. Kundin Digiri na Uku. London SOAS:University of London.

Dangambo, A. (1981). Rikidar Azanci. Siddabarun Salo da Harshe Cikin Tabarkoko, Tahamisin Aliyu Dansidi Sarkin Zazzau, Kano: Bayero University, Nigeria.

Dangambo, A. (1984). *Rabe-Raben Asabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kano:Triumph Publishing Company. Gidan Sa'adu Zungur.

Dangulbi, R. A. (2008) Siyasa a Nijeriya: Gudummuwar Marubuta Wakokin Siyasa na Hausa ga Kafa Dimokiradiyya a Jumhuriya ta Hudu Zango na Farko. M A Thesis Hausa Studies Dept of Nig Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Sokoto.

Dan'illela, A. (2010). Rubutattun Wakokin Siyasa: Nazari A Kan Jihohin Sakkwato da Kebbi da Zamfara. M A Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Dudley, B. J. (1968) *Parties and Politics in Northern Nigeria*. London:Frank Class and Co, Ltd.

Dunfawa, A.A. (1983). Gudummuwar Masu Darika Wajen Habaka Rubutattun Wakokin Hausa. M. A. Thesis. Department of Nigeria and African Languages. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Dunfawa, A.A. (2003). Waka A Tunanin Yara. Ph, D. Thesis, Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Dunfawa, A. A (2007). Gudummuwar Kano ga Jagorancin Yada Addinin Musulunci a Kasar Hausa Kafin Jihadin Shehu Usmanu Danfodoyo. *Al-Nahda: A Journal of Islamic Heritage vol 5 no 1&2. Center for Islamic Studies,* Sokoto:Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Ekpu, R. (1986). The Amazons are Coming in Newswatch 16th – June.

Eya, N. (2003). *Electoral Processes, Electoral Malpractice and Electoral Violence.* Enugu: Sges Publications Nigeria Ltd.

Funtua, A. I. (2003). Wakokin Siyasa na Hausa a Jumhuriya ta uku: Yanaye-yaneyensu da Sigoginsu .Kundin Kammala Karatun Digiri na Biyu. Kano: Bayero University, Nigeria.

Fodiyo, A. (nd). *Diya'ul Hukkam*. Lebanun:Darul Arabiya.

Furniss, G. L. (1977). Some Aspect of Modern Hausa Poetry:Theme Style and Values with Special Reference to the 'Hikima' Poetry Circle in Kano. Ph, D. Thesis, London: SOAS University of London.

Furniss, G. L.(1995). *Ideology in Practice: Hausa Poetry as Exposition of Values and Viewpionts*. Koln:Rudiger Koppe Verlag.

Furniss, G. L. (1996). *Poetry. Prose and Popular Culture in Hausa.* London: International African Library.

Garba, M. (1998). Azancin Magana a Wakokin Makadan Baka (A Study of Figure of Speech in the Hausa Oral Poetry). M A Dissertation, Department of Nigerian Languages. Kano: Bayero University, Nigeria.

Gobir, A. Y. (2012). Tasirin Iskoki ga Cututtuka da Magungunan Hausawa. Kundin Karartun Digiri na Uku. Sahen Nazarin Harsunan Najeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Gummi, A.M. (Babu Shekarar Bugawa). *Alkur'ani Mai Girma Da Kuma Tarjamar Ma'anoninsa Zuwa Ga Harshen Hausa* Wurin Da Aka Tanada

Musamman Don Buga Alkur'ani Mai Girma, Na Mai Kula Da Masallatai Biyu Masu Tsarki, Fahad: Madina.

Gusau, U. G. (2007). Tasirun Al'adun Hausawa a kan Makarantun Allo a Zamfara: Nazari a kan Wasu Al'adu da Suka Danganci Karatu da Mu'amula da Harshe. Kundin Karatun Digiri na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Gusau, S. M. (1983). Kirari da Aiwatar da shi a Wakokin Noma na Baka. Makalar da aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sani. Center for Hausa Studies. Kano: Bayero University, Nigeria.

Gusau, S. M. (1984). Wakoin Noma na Baka: Yanaye-yaneyansu da Sigoginsu, Musamman a Sakkwato. Juzu'i na Daya. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Bayero University, Nigeria.

Gusau, S. M. (1995).*Dabarun Nazarin Wakar Baka*. Kaduna: Fisbas Media Service.

Gusau, S. M. (2002). *Salihu Jankidi*, Sarkin Taushi. Kaduna:Baraka Press and Publishers Ltd.

Gusau, S. M. (2008). Wakokin Makadan Fada: Jigoginsu da Yanaye-yanayensu Musamman a Kasar Sakkwato. Kundin Karatun Digiri na Uku. Sahen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Bayero University, Nigeria.

Gusau,S.M.(2008).*Dabarun Nazarin Adabin Hausa*.Zaria:Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2014). Wakar Baka Bahaushiya (The Hausa Oral Songs). Bieng a Professorial Inaugural Lecture No14. Sashen Koyar da Harsunan Nigeriya. Kano: Bayero Uiniversity, Nijeriya.

Gwinn, R. et al (1992). *The New Encyclopedia Briticana*. Chicago:University of Chicago Press.

Greenberg, J. H. (1946). *The Influence of Islam on Sudanes Religion*. J J Augustine N Y.

Habib, A. (1988). " Rashin Jituwa Tsakanin Malaman Satiru da Turawan Mulkin Mallaka (1906)". Takarda da aka Gabatar a Taron Kasa a kan Tasirin

Mulkin Mallaka a kan Ilmi da Cibiyoyin Addinin Musulunci daga Shekarar 1903 zuwa 1960. Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Hassan, B. M. (2010). Hausa Political Verse as an Effective Tool for Mobilisation. *Dagel, Journal of Faculty of Arts and Islamic Studies*. Vol ix, Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Hassan, B. M. (2010). Short Biographies of Selected Hausa Political Poet. *Journal of Humanities.* Faculty of Arts and Islamic Studies Kano: Bayero University, Nigeria.

Hassan, S. (2013). Kyautata Dimokiradiyya Ta Fuskar Adabi : Tsokaci A Kan Wakar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* Ta Haruna Aliyu Ningi. 1st National Conference in Language, Literature and Culture. Center for the Study of Nigerian Languages Kano: Bayero University, Nigeria.

Harlow, B. (1987). *Resistance Literature*. Newyork:Methuen inc 29 West 35th Street, NY 10001.

Hawkins, J. M. (1981). *The Oxford Mini Dictionary*. New York: Oxford University Press.

Herskovits, J. (1979). Democracy in Nigeria. Foreign Affairs, Council on Foreign Reletion.

Hiskett, M. (1975). *A History of Hausa Islamic Verse*. SOAS London:Malet Street, WCIE 7HP.

Hiskeet, M. (1977). *An Anthology of Hausa Political Verse*. London.

Ibn Khaldun (1920). *Ad- Dorar Al Kaminah Fi Ayan Al Miah Al Thamina*, Beirut: Dar Ihya Al Torath Al –Araby.

Ibrahim, F. O. (2002). *Prince of the Times: Ado Bayero and the Transformation of Emiral Authority in Kano.* Africa World Press, inc Trenton.

Idris, Y. (2010). Wakokin Addini na Siyasa: Nazarin Wakokin Emmanuel Wise mai Molo. Kundin Kammala Karatun Digiri na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka. Zariya: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Idris, Y. (2012). Turken Yunwa a Wakokin Noma. *Dundaye Journal of Hausa Studies* vol 1 no 4. Sashen Nazarin Harsunan Nageriya, Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Imam, A. H. (2002). Wakokin Bijirewa na Tajadidi. Kundin Neman Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka. Zaria Ahmadu Bello University, Nigeria.

Isah, Z. (Miss) (2012). Farfaganda a Wasu Wakokin Siyasa na Zamani. Kundin Digiri na Biyu, Sahen Harsunan Afirka da Al'adu. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Isa, Z. (Miss) (2013). Gudummuwar Mawakan Hausa ga Ci Gaban Arewacin Nijeriya:Nazarin Wakar "Ajanda" ta Haruna Aliyu Ningi. 1st National Conference in Language, Lterature and Culture. Center for Study of the Nigerian Languages, Kano: Bayero University, Nigeria.

Jackson, S. (1978) Hausa Women on Strike: *Review of African Political Econamy*. Afrografika Publishers P. O. Box 272 Yaba, Lagos:Nigeria.

Jega, A. et al (2003). *The Public Poet*: A Biography of Mudi Sipikin. Set in Georgi Verdena.

Joyce, P. (2003). *Teach Yourself Politics*. London:Hodder Arnold.

Jumare, M. S. (2007). Tasirin Farfaganda a Tallar 'Yan Siyasa. Kundin Digiri na Farko. Sahen Harsunan Nijeriya da Afirka. Zaria:Ahmadu Bello University, Nigeria.

Junaidu, S. W. (1990). Resistance to Western Cultures in the Sakkwato Caliphate: A lesson to Generation Yet Unborn. *State and Society in the Sokoto Caliphate* eds by Kani, M. et al. Zaria: Gaskiya Coporation Limited.

Kirk-Green, A. et al (1981). *Nigeria Since 1970: A Political and Econamic Outline,* London: Hodder and Stoughton.

Kuna, et al (1996). The Politics of Abuse and the Poetics of Violence in Northern Nigeria, 1940- 1966. A paper Presented at a Conference in Memory of Late Malam Aminu Kano. African Center for Political and Social Reserch, Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Kuna, M. J. (2000). Violence and State Formation: the Case: The Case of Northern Nigeria, 1900-1966 Ph, D, Thesis. Department of Political Science. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Khalid, S. eds (2008). Jega:*A social Econamic and Political History*. Kraft Books Limited.

Lawal, B. M. (1983). Wakar Gagara Karya Sadauki ta Buda Dantanoma. Kundin Digiri na Farko. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Lipset, S. M. et al (2000). “Corruption, Culture, and Markets” In E. H. Lawrencr and P. H. Samiel (eds) In Culture Matters. New York: Basic Boks.

Malam, M.T. (2001). Dennis Brutus as a Nationalist: A Study of its Selected Poems in a Simple Lust. Degel: Journal of F.A.I.S. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Malumfashi, A. I. (1984). Wa’azi a Rubutattun Wakokin Karni Na Ashirin. Takarda da Aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sani A Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Malumfashi, A. I. (1985). Bori Addini Ko Wasa? Takarda da Aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sani A Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Malumfashi, A. I. (1988). Resistance in Hausa Written Poetry 1900-1960. A Seminar Paper Presented at Faculty of Arts and Social Science. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria. .

Mani, A. (1956). *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa*. Zaria:Northern Nigeria Publishing Company.

Miles, W. F S. (2003). *Hausa Land Divided*: Clonialism and Independence In Nigeria and Niger. N Y Cornell University Press.

Mohammed, A. S. (2008). The Songs and Poems of the Satiru Revolt c. 1894-1906 in *Radical Eassys in Nigerian Literature*. Darah, G. G. eds. Maltthouse Press Limited.

Muhammad, D, (1977). Individual Talent in the Poetic Tradition: A Study of Akilu Aliyu and his Art. Ph, D. Thesis SOAS. Lodon: University London.

Mukhtar, I. (1999). The Form and Content of Resistance to European Expansion in the Sokoto Caliphate: A Documented Evidance from Hausa Literary

Poem of Sultan Attahiru Ahmadu (1902-1903). Al-Nahda A Journal of Islamic Heritage vol 2, Center for Islamic Studies: Sokoto, Nigeria.

Mungadi, A.A. (2000). Jigon Suka da Bijire wa Hukuma Cikin Karni na Ashirin (1940- 1999). KundinKammala Karatun Digiri na Biyu. Sashen Nazarin HarsunanNijeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Maishanu, H.M.et al (2004). The Role of 20th Century Ulama in the Spread of Islamic Education: The Case of Malam Ibrahim Halilu Marinar Tsamiya 1920-1977. National Seminar on Muslims and Islamic Schoolarship in Nigeria in the 20th Century. Center for Islamic Studies Series 3. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Nasir, I. (2011). Amfanin Kafofin Sadarwa Wajen Bunkasar Dimokiradiyya. Takarda Da Aka Gabatar A Taron Kara wa Juna Ilimi Na Kasa Karo Na Hudu. Zaria: F.C.E. Nigeria.

Nnadozie, U. (2007). History of Election in Nigeria, in Elections and Future of Democracy in Nigeria edited by Jega et al. Nigeria: A Publication of the Nigerian Political Science Association.

Omar, S. (1983). Style and Theme in the Poems of Mu'azu Hadeja. MA Thesis SOAS. London: University of London.

Omar, S. (2012). Malam Mu'azu Hadejia Fasihin Mazan Jiya:Nazarin Rayuwarsa da Wakokinsa. Ph,D. Hausa Studies, Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Okoth, A. (1979). *History of Africa* 1855-1914.

Orr, C. W. J (1911). *The Making of Northern Nigeria*. London.

Palmer, H. R. (1928). *Sudaness Memoirs*, Lagos.

Paden, J. N. (1973). *Religion and Political Culture in Kano*. Berkely/Los Angles/London: University of California Press

Padden, J, N. (1986). *Ahmadu Bello* Sardauna of Sokoto. Zaria: Huda-Huda Publishing Company. Nigeria.

Patton, A.J. (1975). The Ningi Chiefdon and the African Frontier: Mountaineers and Resistance to the Sokoto Caliphate.C A 1800-1908. Ph, D. Thesis University of Wisconsin-Madison.

Sa'id, B. (1978). Gudummuwar Masu Jihadi Kan Adabin Hausa. Kundin Digiri na Biyu. Kano: ABC/ABU.

Rosendle, L. G. (2013). *College Girl*. Albony State University of New York Press. U.S.A.

Sa'id, B. (1995). The Reaction of Hausa Poets to Western Civilisation. *Harsunan Nijeriya* vol xvii, Center for the Study of the Nigerian Languges. Kano:Bayero University, Nigeria

Sa'id, B. (2002). Rbutattun Wakokin Hausa na Karni na Ashirin a Sakkwato, Kabi da Zamfara. Kundin Digiri na Uku. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Bayero University, Nigeria.

Sarki, H. A. (2000).Tarihin Zuwan Musulunci Afirka da Shigowarsa Kasar Hausa. Babu wurin bugu.

Sifawa, A.A. (2011). Colonial Infrastructure and Social Service in Sokoto Metropolis 1903-1960. M. A Dissertation, Department of History. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Skinner, N. (1965). Kamus Na Hausa Da Turanci. Zaria:Northern Nigeria Publishing Company.

Skinner, N. (1980). *An Anthology of Hausa Literature*. Zaria:Northern Nigeria Publishing Company

Sklar, R. S. (1963). *Nigerian Political Parties*: Power In an Emergent African Nation, Princeton.

Skolnik, J. (1969). *The Politics of Protest*. New York: Bellantine

Sofola, Z. (1977). *The Sweet Trap*. Ibadan: University Press, Nigeria.

Sondhi, S. (2000). "Combating Corruption in India: The Role of Civil Society" A Paper Prepared for the xviii World Congress of International Political Science Association, Quebec City: Canada.

Sokoto, A. M. (1983). A Social Interpretation of the Satiru Revolt of C. 1894-1906. M A Thesis, Department of Sociology. Zaria: Ahmadu Bello University, Nigeria.

Sulaiman, I. (1987). *The Islamic State and the Challenge of History Ideals, Policies and Operation of the Sokoto Caliphate*. East-West University Islamic Studies. London and New-York: Mansell Publishing Limited.

Sulaiman, M. D. (1993). Shia'ism and the Islamic Movement in Nigeria. Islam et Societe all Sud du Sahara.

Talton, B. (2006). African Resistance to Colonial Rule. Schomburg-Mellon Humanities Institute. Schomburg Center for Reserch in Black Culture.

Tamuno, (1972). *The Evolution of the Nigerian State*: The Southern Phase 1898-1914. London: Longman.

Tibenderana, P. K. (1988). *Sokoto Province Under Colonial Rule 1903-1939*. Zaria:A. B. U. Press,

Tsiga, I. A. (2014). One Hundred Years of Karatun Boko: Education Language and Value Change in Hausa Land. A paper Presentation of the Book, *Ruwan Bagaja in Perspectives* Eight Decades of a Hausa Masterpiece in Prose (1933-2013). Katsina: Umaru Musa 'Yaradua University, Nigeria.

Umar, M. B. (1987). *Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya*. Kano:Triumph Publishing Company. Gidan Sa'adu Zungur.

Umar, S. M. (2006). *Islam and Colonialism: Itellectual Responses of Muslims of Northern Nigeria to British Colonial Rule*. Brill Leiden Boston.

Usman, N. A. (2012). Gudummuwar Wakokin Adawar Siyasa Wajen Habaka Adabin Hausa: Nazari Kan Wakokin Haruna Aliyu Ningi. Takarda da aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sanin a Kasa na Farko. C. S. N. L. Kano. Bayero University, Nigeria.

Usman, A. F. (1994). The Development of Colonial Education in Offa With Special Reference to Offa Grammar School (1943-1993). M A History. Department of History. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Usman, B. B. (2008). Hikimar Magabata: Nazari A kan Rayuwar Malam (Dr) Umaru Nasarwa Wazirin Gwandu (1916-2000) Da Wakokinsa.Kundin Neman Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nijeriya.Sokoto Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Usman, M. T. (2000). Another Consideration of the Internal Factors for the Collapse of the Sokoto Caliphate 1804 – 1903. *Dagel Journal of F. A. I. S.* Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Usman, M. T. (2003). Literary Legacy of the Sokoto Caliphate: Commentry on Some Selected Poems From Northern Nigeria. *F. A. I. S Journal of Humanities* vol 2 No 4. Kano: Bayero University, Nigeri.

Wakili, H. (1985). Attempt to Reject the Imposition of Colonial Rule: Hadejia Revolt of 1906 and its Consequences. B A History, Department of History. Kano: Bayero University, Nigeria.

Wakili, H. (2005). *Turawa a Kasar Hadeja: Karon Hadejiyawa da Turawan Mulkin Mallaka*. Kano:Benchmark Publishers Limited.

Yahya, A. B. (1987). The Hausa Verse Category of Madahu With Special Reference to Theme, Style and the Background of Islamic Sources and Belief. Kundin Digiri na Uku. Sahen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto: Usmanu Danfodiyo, Nigeria.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce*: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa. Zaria: Gaskiya coporation.

Yakasai, A. S. (1988). Tarihin Hausawa da Yanayin Kasar Hausa. Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University, Nigeria.

Yakasai, A. S. (2012). *Jagoran Ilimin Walwalar Harshe*. Sokoto:Garkuwa Media Service Ltd Gida Mai Lamba 52 Layin Sarki Yahaya, Nijeriya.

Yakawada, M. T. (1983). Wakekeniya. B. A. Project Department of Nigeria and African Languages. Zaria: Ahmadu Bello, Nigeria.

Yakawada, M. T. (1987). Tarkakken Matanin Wakar Kanzil Azim Ta Aliyu Namangi. M.A. Arts. Department of Nigeria and African Languages. Zaria:Ahmadu Bello, Nigeria.

Yakawada, M. T. (2002). Eulogues,The Building Blocks of Hausa Praise Songs:Thematic and Structural Examination. Ph.D. Thesis. Department of Nigeria and African Languages. Zaria: Ahmadu Bello, Nigeria.

Yakawada, M. T. (2013). Adabi da Harkokin Siyasa: Bijirewa a Wakar "Shegiyar Uwa mai Kashe 'Ya'yanta PDP" ta Haruna Aliyu Ningi. 1st National Conference in Language, Literature and Culture. Center for Study of Nigerian Languages. Kano: Bayero University.

Yakubu, A. M. (1999). *Sa'adu Zungur*: An Anthology of the Social and Political Writings of a Nigerian Nationalist. Kaduna: Nigerian Defence Academy Press.

Yakubu, B. (1972). *The Phenomenon of Kirari in Hausa Society*. Kano: ABC/ABU

Yusuf, A. B. (1975). *Freedom Fighter*: Annoted Memoirs of Malam Ilah Ringim. Sokoto:Sidi Ummaru Printing Press.

Zagga, I. M. B. et al (2004). The Sokoto Response to British Colonial Imposition. *The Sokoto Caliphate: A Legacy of Schoolarship and Good Governce.*

Zarruk, R. M. et al (1976). *Kirarin Duniya*. Zaria:Ganuwa Publishers. Nigeria.

Zarruk, R. M. et al (1982). *Zaman Hausawa*. Zaria:Institute of Education.

**Shafukan Yanar Gizo Da Aka Duba**

WWW. Babylon.Com
ENCYCLOPEDIA (Ask.com)
Answers.com
Changing minds.org
Binnary Qoute Dictionary.com

## RATAYE

Ratayen wasu daga cikin Wakokin da aka yi nazari, an karkasa su ya zuwa Jumhuriya ta farko ya zuwa ta hudu. An zabi wakoki a cikin kowace Jumhuriya daga cikin jam'iyyun da aka fi yi waka cikin harshen Hausa. An yi hakan ne da nufin kawo samfur na ire-iren wakokin da aka nazarta.

## JUMHURIYA TA FARKO

A Jumhuriya ta farko, daga bangaren jam'iyyar N.P.C. an zabi wakar "Siyasa Zamanin Salama" ta Alhaji Bello Gidadawa, ga wakar kamar haka:

### WAKAR SIYASA ZAMANIN SALAMA (N.P.C.)
### ALHAJI BELLO GIDADAWA

1.Salamu alaikumu jama'ar salama,
Alaika salamu ya mai son salama.

2.Jiya ku 'yan uwana mun yi zama,
Da munka zamo jama'ar yin salama.

3.Ina yin assalatu bisa masoyi,
Muhammadu sayyadi wa ma'as salama.

4.Da alayensa na dada nawa bege,
Kaza da sahabbai masu dubun salama

5.Batun kalimar salama zan fada ma,
Ka gane shi ka sa ka zamo da himma.

6.Akwai fatar kwarai ga fadin salama,
Da alfarmar Rasulu muna salama.

7.Cikin tafiya akwai kalimar salama,
Idan ka har dace ta fa ka yi zama.

8.Idan ka yo salati kana gamawa,
Da taslimi gaba dai don salama.

9.Idan sallafa kay yo ka sani kau,
A karshe can akwai kalimar salama.

10.Idan ko ka ki yin ta fa don ka gane,
Cikin aikinka lalle kai zalama.

11.Ga kanka zama fa ka cuce shi dahir,
Hakika ba shi kara fita gumuma.

12.Idan ka je ka Makka ana bukatar,
Shiga Babus Salami ka san salama.

13.A cana Madina har ko na ga kofa,
A masjidu anka ce Babus Salama.

14.Ka duba can ga jefa khalilu naran,
Hakikan ya shiga ta cikin salama.

15Dada ranar shiga Aljanna hakkan,
Muna barka muna ta kiran salama.

16.Zama mun tsira babu taraddudi kau,
Zama sabonmu ya bata sai salama.

17.Idan ka gane wanga irin bayani,
Fa kan sa bin salama as salama.

18.Dada in ka fahimta ina fada ma,
Ka zan yin addu'a ga matan salama.

19.Fa na roka ga Allah don Habibi,
Muhammadu taimaka ga matan salama.

20.Ka sa nasara gare su ga wanga yaki,
Na zabe don mu sami zaman salama.

21.Ka rinjayar da su su fi kulli yaumin,
Ka sa jama'a su karu ga bin salama.

22.Fa don kur'anu Allah don sahabbai,
Ka sa nasara ga jam'iyyar salama.

23.Ka taimaki shugabanmu Firimiyanmu,
Muna son koda yaushe shi san salama.

24.Ahmadu Bello jikan Bello hakkan,
Muna kamnar ka jikan mai karama.

25.Karamar Shehu tas sa kacci girma,
Mutum mai hankali duk ya sakam ma.

26.Zama ya san nufinka ga rain a hairi,
Kana famar shi duma cikin salama.

27.Fa duk mai hankali kuma mai tunani,
Shina yin taimako ga bidar salama.

28.Mutum mai hankali bai said a kainai,
Shina murna, da sannu shina nadama.

29.Fa cin kwakwa da Hausa ka san wuya ta,
Idan ka sha fa ka fita das salama.

30.Ku bar akashin Guruf birnin gururi,
Biyar su shina hana ka zaman salama.

31.Fa 'yan kudinsu lura ka san guba ta,
Idan ka ci su ba ka cikin salama.

32.Hakika zaka abku cikin bala'i,
A karshe al'amar shi zamo takima.

33.Hade loma guda mai kumburaswa,
Akwai hadari ku nemi shiga salama.

34.Ilahi karya Eji sa su rude,
Hana su su tashi sai ran Alkiyama.

35.Ta'ala waste NEPU ka karya yakin,
Munafukkai ka kais u wurin nadama.

36.Abokan NEPU mun san nasu hali,
Baki na bai da haske sai zalama

37.Fa ya kahharu kaddara za su koka,
Su ce 'Wayyo!' su nemi bidar salama.

38.Fa rokona ina fata ga Allah,
Shi karbam min shi taimaki 'yan salama.

39.Fa fatata shi taimaki duk Musulmi,
Su karu da lafiya da zaman salama.

40.Shi sa caffammu ba ta fita ga hannu,
Amirul Muminina cikin salama.

41.Shi kyautata al'amurranai shi tanyai,
Shi taimaki Muslimina zuwa salama.

42.Saraki duk na Islama tsare su,
Ga sharrin fasikai jama'ar zalama.

43.Ka daukaki shugabanmu Firimiyanmu,
Ka kai shi ga martaba tar okon salama.

44.Fa ya Mannanu sa Nijeriya duk,
Ta zam mulkinsa don shi tsare salama.

45.Ministoci da sauran masu tanyo,
Su san nasara su karya maki salama.

46.Dada zance kadan gun masu lura,
Shina sawas su lura su so salama.

47.Mu kuble wagga waka nan mu nace,
Bisa ga du'a'u har mu shigo salama.

48.Salati da sallama su zamo ga Manzo,
Mu san tsira mu sami cikas salama.

49.Muhammadu Bello Alhaji yay yi waka,
Gidadawa gidansu cikin salama.

50.Fa ranar Ahdi niy yo wagga waka,
Takwas ga Nubemba lalle na yi zama.

51.Hijira dubu sannan dari tara an gama,
Hamsin ka sa tara za ka gane salama.

52.Tammat cikawas sallam bisa sallama,
Ranar cika wa duk mu sami salama.

Haka kuma, duk dai a cikin Jumhuriya ta farko. Daga bangaren jam'iyyar N.E.P.U. an zabi wakar " 'Yan Sawaba" ta Malam Gambo Hawaja kamar haka:

**WAKAR 'YAN SAWABA TSARI (N.E.P.U.)**

**M. GAMBO HAWAJA JOS 25/1/1954**

1.Summas Salati Ala Nabiyu Muhammadu,

Alai sahabbai Tabi'ina da Auliya.

2.Allahu Sarki shi kadai yake Wahidu,

Sammai da kassai Jalla bas hi ba kishiya.

3.Shi ba fari shi ba baki ba Ubangiji,

Shidi da kore Jalla bas hi da rawaya.

4.Ba saki-saki ba na kamar yar an ba ne,

Ba ja ba ne shi Jalla ya wuce kwaikwayo.

5.Zatinsa ba ya tattara ba rarraba,

Kawai da motsi Jalla ba yai ko daya.

6.Allahu bai haifaba shi ba a haife shi ba,

Sarki da ba dangi kane balle diya.

7.Sarkin da ba na biyunsa ba na uku nasa,

Mulkinsa ba mai taimaka masa ko daya.

8.Shi yai sama'u da Arli ya yi masharika,

Da magariba da yaminiya da shimaliya.

9.Kiwo na sama'u da Arli daji ko siji,

Haske duhu bay a hana shi zanin daya.

10.Albarkacin manzonka zan yabi jam'iyya,

Kai son ta tunbuke zaluman Nijeriya.

11.Mu ne mutanen nan da munka fito bidar,

Yanci ya sami a tsarkaka Nijeriya.

12.Ita jam'iyyan nan NEPU ta dau aniya,

Sai ta ga bayan zaluman ga masha giya.

13.Ta dau makami sun fi bom har bindiga,

Kun san su ko in fade su sune gaskiya.

14.Iggwa da bam bai magani in ta zaka,

Wa ke da ikon dankofe wa gaskiya.

15.Kai fankashali sha zumami ka dakata,

Kwaron da ba shi da nasa sai kwalamar tsiya.

16.Kai ba ka noma ba fatauci ko kadan,

Kuma ba sana'a sai yawan faharin tsiya.

17.Na tabbata dan NEPU ba zai soka ba,

Tamkar kudan shadda ya sauka a kan miya.

18.Mu NEPU mu ne kainuwa bisa kan ruwa,

Wawa da zai taka mu shi zai dulmiya.

19.Ga NEPU dutse ba a far maka nan da nan,

In munka farwa zalumi zai ka wuya.

20.Mu ne tsakin tsakuwa a gun azzalumi,

Kafin a ci mu a radu bai sai an sha wuya.

21.Kai turdimi jaki dakikin duniya,

Katon cikin wofi na cinye haramiya.

22.Ni zan gayama gaskiya in zaka ji,

Bar sa Wali a batun da ba shi da gaskiya.

23.Don Shehu bai ja kafiri a jikinsa ba,

Shi sai Musulmi wanda ke rike gaskiya.

24.Bai ja cikin hotal ba Shehu Mujaddadi,

Kuma ba shi karya bai zama da masha giya.

25.Har yai wafati Shehu bai cuce mu ba,

Allah ya gafar-ce shi Shehu mazan biya.

26.Ku jakunan shaidan ba zaku ga Shehu ba,

Bar sanya Shehu cikin batunku na jam'iyya.

27.Kaka uba bai fidda dausa ga hallak,

In dan ya ce bai kama hanyar gaskiya.

28.Kuma ga misali Jalla ya saukar mana,

Aya akan kana;ana inda ya dulmiya.

29.Kai mai kirarin martabar kaka tsaya,

Ka tuna Hassan da Hussaini sun riki gaskiya.

30.Bar takamar kakanka banga fitar kaba,

Kakanka baya yin hannu da Baturiya.

31.Kuma ba shi cewa goro ai masa jangali,

Shi bai kawa da Nasara baya shan giya.

32.Gemunka har sajenka ba shi da martaba,

In dai ya zam aikinka babu na gaskiya.

33.Dan wane jikan wane bata isar maka,

Allaahu ya ce sai kana bin gaskiya.

34.Mai daura bante in ya baiyana gaskiya,

Ya zarce mai rawanin da ke son dulmiya.

35.Da martaba kaka ka mulkin duniya,

Awolowo shi wa ya bashi Firimiya?

36.Kai gafara sa ya isheni ku dakata,

Ba na gudu sai na ga gashin saniya.

37.Sun raina hanyar Shehu sun bijire masa,

Basa bukatar lahira sai dukiya.

38.Su dai su hau mota su sauka a hil tasha,

Ran juma’a ran nan suke shagalin giya.

39.Da ya yi imani ya dubi mazan gaba,

Da su kai sarautar duniya baki daya.

40.Ba su shuka sharran dan su cuci waninsu ba,

Su sai shirin da sukai a taimaki gaskiya.

41.Duk Annabawa Mursalai da sukai gaba,

Sun bauta Allah sun tsaya bisa gaskiya.

42.Jikan ma’aiki wanda ankai duniya,

Har lahira dominsa sun rike gaskiya.

43.Kai gaskami mai kasuwa daya dakata,

Ka tuna da Allah gara ka rage ta riya.

44.In ka ki zakai sammakon bubukuwa,

Jama’a mu tsira da Shehu kai ko ka sha wuya.

45.In ban da  jahilcin sa ba shi tunanniya,

Mune muke ci sheshi yamma da safiya.

46.Bana cikin NPC bana son shiga,

Manyansu basa taimakon Nijeriya.

47.Na raina jam’iyyar su masu abin fada.

Ni na tsaya kan NEPU tutar gaskiya.

48.Tutar da ba ta da jahili ba zamili,

Da baki da ja kore ga fatar taurariya.

49.In ban da wawa jahili da rashin shi ne,

Wa zai bi jam’iyyar da bata da gaskiya.

50.Wallahi Allah zan gaya muku ‘yan uwa,

Talakan dake NPC bashi da zuciya.

51.Daga dai kawali sai maroki ke shiga,

Sai wanda zaiki ubansa dan kwadayin miya.

52.Kuma mai kudin da ka ganshi ya shiga tabbata,

Ya raina masa yana bidar na haramiya.

53.Ku ne talakka uba talakka uwa haka,

Wai har da dan sarki kuke gama jam’iyya.

54.Kurdinku ya rude ku kun yi shin fada,

Dan kun ki bin asalinku kun bi masha giya.

55.Komai kudi ko Malamin da ya karkata,

Allahu shawo kansa mui masa fatiya.

56.Asirin cikin riga jama'a na tuna,

Zan bar uba domin diyansa na gaskiya.

57.Na 'yanta randa dan rowan da yake ciki,

Ba don wadansu ba wane da ya sha wuya.

58.Yau ba maki dan NEPU sai azzalimi,

Sai jahilin talakan dake son dulmiya.

59.Sai wanda Allah yai shi ba shi da hankali,

Sai masu neman hallaka don dukiya.

60.Sai tajiran nan masu son bashin tsiya,

Wai za a ba su kudi suna ta dawainiya.

61.Sun manta kyauta wadda Allah yai musu,

Su dai nufunsu a ba su bashi ba biya.

62.Wannan kudi kwa ji su baku gane su ba,

Don Allah Alhaji wane daina dawainiya.

63.Tsuguna ka tashi akwaita an fansar kare,

An sai biri da kudinsa gare gidan jiya.

64.A cikin minister goma wanda ka tarkato,

Waye talakka cikin su mai muku tambaya?

65.Daga wane sai dan wane su aka tarkata,

Kun san abin nan nasu babu na gaskiya.

66.Jama'a hadin nan ko kadan bai zauna ba,

Tamkar a dama kunu idan asa miya.

67.Ko ko a bai kura amanar tinkiya,

Jama'a biri ya zai yi gadin gujjiya.

68.Talakan cikin NPC kun yi abin fada,

Gugan dake yasa da shi a yi rijiya.

69.In anka sami ruwan a gun shan banda shi,

Kafin jimawa sai ku gan shi a rariya.

70.Kai dan talakka ka daure gidin zalumi,

Domin a cuci ubanka har ka yi dariya.

71.Mu ba ruwanmu da masu son azzalumi,

Balle fa shi azzalumin wawan tsiya.

72.Talakan cikin NPC ga sunan ka nan,

Kai ne gurufa wanda ke kin zuciya.

73.Tsofonku na noma guminsa yana diga,

Wai kun fi soma kar a gun shi da dukiya.

74.Wannan abin kunya da kun kai zan fada,

Wallahi kun ki ubanku dan kwalamar tsiya.

75.NPC jaba baku son hangen gaba,

Dan mujiya dai ba shi son yaga kurciya.

76.Inuwar giginya banga amfanin ta ba,

Sai dai na nesa ka shanta nata yasha wuya.

77.Maye yakan manta idan yaga an jima,

Amma uwar ‘ya har ta kaura ga duniya.

78.Tubar muzuru ban ga amfaninta ba,

Wani an hana shi rawa yanai mana rausaya.

79.Zan matsa gyare in ji kukan kafiri,

Jama’a idan kun yarda kwashe dariya.

80.Dan na ji miskini guda na fariya,

A kashe mutun wai zai biya shi da dukiya.

81.Da gaskiya ne in yana da kudin biya,

Da ya saye guntun hannunsa ya lankaya.

82.Ba NEPU ce ta saka a yanke hannun ka ba,

Bari ce akar don NEPU don faharin tsiya.

83.Kullum kana yasin kana buga rantsuwa,

Su sunka daste hannunka tun daga duniya.

84.Ka biya marayu dukiyarsu da ka taba,

Ka kashe iyayen don ka ci musu dukiya.

85.Dan fasiki komai akai mar mun jiya,

Ko yai karatu zai gama shi da fariya.

86.Da zamanin tsofansa kowa ya sani,

Dai kyale farkar don da balle zuriya.

87.Zina ko kare ya san da tsohon fasiki,

Shi ke fataucin don ya kwan da magajiya.

88.Jama'a abin nan nasu gara mu baiyana,

Da sun ki ji yau sun gani da idaniya.

89.Babban abin kunyar da sun ka yi zan fada,

Wassu tajirai suka je su gaida Firimiya.

90.Police ya ce babbansu Alhaji dakata,

Koma idan kuwa kaki yanzu ka sha wuya.

91.Wani turdumi duna amale kututtubi,

Kun san shi ko in fada shi gara mu sakaya.

92.Ya tattare cuna ya gangare hel tasha,

Ya dafe kansa yana gudu ba waiwaya.

93.Ya manta rancen dukiya da ya tambaya,

Ya tuna da kwanan yari gara ya sakaya.

94.Im ban da jahilcin sa ba shi da haankali,

Da anka cinye kudinka suma dariya.

95.Bayan watanni ‘yan kadan suka tabbata,

Kudinka yak are su saka a jam’iyya.

96.‘Yan NEPU dan ba suce a cinye kudinka ba,

N.P.C bata biyaka wannan dukiya.

97.Na tabbata dan NEPU bai ci kudinka ba,

Dan Fisi ne ya ci dukiyarka ta dulmuye.

98.Mai so yana da sule biyar a yi mar jaka,

Bana saka shi cikin mutanen gaskiya.

99.Koma Kaduna ka nemi mai maka tsibbu can,

Kuma na ji bashi Kaduna ya tafi Zariya.

100.Jama’a takarda na ga bata da mantuwa,

Na ganta na tuna jahilin tsohon tsiya.

101.Duk fasikai tsohon da bai tsare kansa ba,

Wallahi in muka gaurayazai sha wuya.

102.Wani dan farin tsoho cikinsa bakik-kirin,

Ya manta Allah ya ji rudin dukiya.

103.Mai shekara saba’in ka gan shi da daduro,

Me zan kira shi ku ce da shi tsohon tsiya.

104.Tsohon da bai san fatiha ba munafuki,

Bakinsa na kumfa ya bakin saniya.

105.Duka fasikin tsohon da ba zai tuba ba,

Wallahi zai tozarta tun daga duniya.

106.Kai dankoro mai danne tsaho ke bata,

Sha talla doki ba ido wa zai saya.

107.Daukar macuci ban ga amfaninta ba,

Noman kisan gero a kewaya harkiya.

108.Yau duk mutan NPC in na kididdige,

Maciya amana sai barayin tinkiya.

109.Sai wanda zai baki ya kai su cikin tasha,

Ya gama da ‘yan sane su dauke dukiya.

110.Wa ke shiga NPC ban da munafiki,

Sai Alhajin da ya kasa karasa fatiya.

111.Ko yai karatu in ka bishi a hankali,

Ka tadda imaninsa babu a zuciya.

112.Jama’a masoya NEPU kar ku yi fargaba,

Wallahi kinsu da sonsu ma fadi gaskiya.

113.Duk mai abin kunya ba zai shiga NEPU ba,

Wallahi ko da ya shigota da sakiya.

114.Kai kyankyaso kwadayinka bai fish-sheka ba,

Koma cikin shadda futo daga tsariya.

115.Wani sakare maganarsa in muka bin cika,

Muka buda tarihinsa sai a yi dariya.

116.Dan sai da tsohon yai shiri yai gangara,

Sannan ya memi shiri da shi dan dariya.

117.Jama’ar garin muka taru dai aka lallaba,

Mutuwarsa ke da wuya ya kwashe dukiya.

## JUMHURIYA TA BIYU

A cikin Jumhuriya ta biyu, an zabi waka guda daga cikin wakokin jam’iyyar N.P.N. da kuma waka guda daga cikin jam’iyyar P.R.P.

Daga cikin wakokin jam’iyyar N.P.N. da aka nazarta an kawo wakar “P.R.P. Ta Zama Kaya” ta Muhammad Sulaiman Dundaye kamar haka:

## P.R.P TA ZAMA KAYA
## MUHAMMAD SULAIMAN DUNDAYE

Amshi: P.R.P ta zama kaya – Mu mun koma N.P.N

1. Bismillahir Rahamani,
Arrahimi Gwani Mannani,
Ni na san kai ke ba ni,
Don kai ka fi wanda ya fi ni,
Allahu ka ba ni fahimta.

2. P.R.P ta ban kunya,
Domin ta koma baya,
Ta rushe sai jayayya,
‘Yan santsi ba su da kunya,
Sun jirkita al’amarinta.

3. Shashashu sun daidaice,
Sun waste sun balbalce,
Sun yi hauka sun susuce,
‘Yan santsi sun lalace,
Kungiyar da ta zagi ubanta.

4. Duk ‘yar da ta raina ubanta,
Ta kama masu da uwarta,
Ta kai zagin kakanta,
Ai sai jama’a su guje ta,
Sai dan iska zai so ta.

5. Domin ba mai auren ta,
Sai dai mai son lalata,
Shaidanci hanyar sata,
Allah ka raba mu da cuta,
Sa duk jama’a su fahimta.

6. Malam hakuri zan ba ka,
Cutar da wadansu suke maka,
Mun san Allah zai saka,
Kai ka kama wadansu ka shuka,
Suka girma suke lalata.

7. Na gode Sarkin iko,
Kuma Allah mai fifiko,
Da ka sa ni sanin ‘yan boko,
Ba sauran ai mini soko,
Ko karya ko ko mayata.

8. Jama’a yau gara ku gane,
N.P.N alheri ne,

Don Alhaji Shehu mutum ne,
Kuma shi mai kyan asali ne,
    Kuma N.P.N ba mita.

9. N.P.N goshin jirgi,
Ita ta wuce ai mata gigi,
Kada ma ka sake ka yi wargi,
N.P.N ba ta zagi,
    Domin ta tsare girmanta.

10. Ya Allah Rabbu Ganiyyu,
Ka tsare Usmanu Aliyyu,
Shagari ya zam ya ragu,
Don kai ke raya marayu,
    Kuma kai ke ba da wadata.

11. Ka taya shi a wannan aiki,
Gyara mana tsarin mulki,
Raka Shehu da ba ya raki,
Ya ba marada mamaki,
    Allah kai ne na aminta.

12. Allah na tuba gare ka,
Domin da na sabe ka,
Da shiga P.R.P shirka,
Sai ya ka nufe ni na farka,
    Daga barci mai cuta ta.

13. P.R.P mugun doki,
Wai don ka hau bari doki,
Sai ka ga abin mamaki,
Domin ba ka sami tafarki,
    Hanyar shanu lalata.

14. Allah ka tsare mu da sharri,
Mu guje wa duk asharari,
Mai jin don ya rika jari,
Zai yi wa manya sharri,
    Zai zagi uwa ya buge ta.

15. Kai na ga abin mamaki,
Aka je yaki da aboki,
Har an sare masa doki,
A rabo aka ba shi musaki,
    Aka ce kuma har ya yi mita.

16. Ku guje wa ‘yan P.R.P,
Jam’iyyar ta cika haufi,
Da yawan cewa su sun fi,
Kowa sun maisai wofi,
Bayan kuma sun gigita.

17. Kowac ci amanar Allah,
Ya bar sunna da farilla,
Ya koma kila wa kala,
Wannan ko ya zama gaula,
Abada ba zai yi gwaninta.

18. In tuna muku in kun mance,
Da ma Hausawa sun ce,
Don kuka mugun hoce,
Ya ja ma uwa ya goce,
An jefa an same ta.

19. Da ma karshen su baleri,
Jawo fitina asharari,
Domin bakinta da sharri,
Tusar ta yi mugun wari,
Kuma duk jama’a sun ji ta.

20. Shi jatau shashasha ne,
Da halinsa da goggo guda ne,
Da biri ja duk daidai ne,
Aiki nasa ma barna ne,
Ga raini ga son mita.

21. Shi ya zaci mai wayo ne,
Bayan kuma shi dolo ne,
A zuga shi ya zagi mutane,
Don ya kogo ga Tatsine,
Girman kai ba shi bajinta.

22. Majalisar wawaye ne,
Duka ‘yan amshin Shata ne,
Manajojin said a giya ne,
‘Yan daudu da sabis su ne,
Da kilakawa a cikinta.

23. A cikinsu ina ka ga da nan?
Wa zai tausai a wadannan?

Kuma wa ka ga zai gyaran nan?
Ba sa hanyar kowa nan,
Sai wanda ya fi su mayata.

24. P.R.P ba ta amana,
Ba alhairi mun auna,
Kuma ba kwazo mun raina,
Sharri karya da hiyana,
Ta firgita duk 'ya'yanta.

25. Daga yau mun koma hanya,
Ta Aminci ba jayayya,
Su Akinloye ku ne manya,
Hakkin duka 'yan Nijeriya,
Ku ne renon 'ya'yanta.

26. Kada kui halin P.R.P,
Ku hade kai don mum un fi,
Kai ni ba na P.R.P,
Ban son aikin P.R.P,
A sani daga yau na bar ta.

27. N.P.N ba ta gafi,
Kuma ba ta karnin kifi,
Sakarai sai P.R.P,
Su dugunzuma sarkin tsafi,
Duka manya ne a cikinta.

28. Girma kam sai N.P.N,
Daraja kuma sai N.P.N,
Hakuri ma sai N.P.N,
Cika alkawali N.P.N,
P.R.P sai lalata.

29. Mu dai manufarmu Aminci,
Kuma mu ba ma ha'inci,
Mu ke hana ai cin hanci,
A wajen aiki mu yi naci,
P.R.P na karyatta.

30. Da ma a kasar nan tamu,
Noma ne hanyar sami,
Mu ba ma kin asalinmu,
Kuma duk duniya an san mu,
A karsarmu muna da wadata.

31. Masara da gida ne namu,
Aminci ne takenmu,
Yunwa ta yi nesa gare mu,
Dan iska bai rabon mu,
Sai mai lura da fahimta.

32. Wane ne zai ki Aminci?
Wa ke kaunar lalaci?
Wa zai ce bai da mutunci?
Sakarai ko iskanci?
Mu ba ma son lalata.

33. N.P.N ce jam'iyya,
Manya nata su ne manya,
Ba sa maganarsu su sauya,
Ba za ka ji 'yar jayayya,
Ta rashin ladabi a cikinta.

34. Ni ba na zagin manya,
Kuma ni ba na jayayya,
Ba na tsare kowa hanya,
Kuma ban so ai mini garya,
Ba na yarda da lalata.

35. P.R.P ganyen taba,
Kwas sha ba don dadi ba,
Zai sha ba don dadi ba,
Don ba aikin lada ba,
Ai gara ko bar ta ka huta.

36. Wani dan tsuntsunsu kawali,
Da yawan tonon silili,
Matukar zai ci muku irli,
Zan tashi in ce ba haki,
Karyar da yake na san ta.

37. Mu ne muka san asalinsu,
Sharrinsu da duk karyarsu,
Tau Allah ya tone su,
Sun fallashi kansu da kansu,
Wa zai tanye su bakita.

38. Asali masu zagin manya,
Manufarsu yawan jayayya,

Takensu rashin jin kunya,
Bakin da ya kurbi mugunya,
Tilas shi zai yi amanta.

39. Allah ya sa mun gane,
Yatsu biyu ‘yan sane ne,
Zan sa hannu in danne,
Aljihuna daidai ne,
Domin hada ai mini sata.

40. Kanawa da kun gane,
Yatsun nan mugaye ne,
Ku tsare kaya daidai ne,
barayi ‘yan zamba ne,
Sun san hanyarsu ta sata.

41. In wancan dan jaki ne,
Ai wannan dan bera ne,
Dan satar bin jirgi ne,
Wannan ko dan kula ne,
Kowa ya san kwadayinta.

42. Ni ba na jin tsoronsu,
Ba na kwadayin kayansu,
Ban sauraron hirarsu,
Da rashin ladabin nan nasu,
Shi ne hanyar lalata.

43. A garin can an yi fasadu,
Zabe aka bar masana du,
Mulki aka ba dan-daudu,
Muryar mata ya ta daudu,
Ya hau laka ba mu ji ta.

44. Wasu sun ce a kore shi,
Wasu sun ce gara a bar shi,
Darajar manya ku jira shi,
Amma kuma kanshi da bashi,
Jama’a ko kun hankalta?

45. Tafi gindin Dala ka bushe,
Wai kai mai neman tushe,
Ka zamo jikan Barbushe,
Tsumburbura ma ta rushe,
Balle wani mai bautatta.

46. In mai jirgi ya zo shi,
Mai gora gu zai ba shi,
Haji Shehu idan ya zo shi,
Duka gwamnoni sa tashi,
Har wanda ya kasa fahimta.

47. Gwamnatin N.P.N tamu,
Ta shirya gidaje donmu,
Manufa tata ne renon mu,
Wanda ba shi da yau ya sami,
Ai tilas ne mu yabe ta.

48. Ilimi da sana'a su ne,
Gona da gida daidai ne,
Yar marar bukka yai bene,
N.P.N dattawa ne,
Na kasa sun san gyaranta.

49. Jama'a na ba ku amana,
A cikinku na zo in zauna,
Na z one domin kauna,
Na dai duka ba makiyi na,
Balle kuma mai cuta ta.

50. Dangi ku shigo jam'iyya,
N.P.N babu hamayya,
U.P.N koma baya,
N.P.P ba ki da hanya,
G.N.P.P ba ku huta.

51. Duka jam'iyyun shirme ne,
Sai N.P.N muka gane,
Mu aminci wa daidai ne,
Wanda ma suka kusa su gane,
Allah maido ku cikinta.

52. Fita jam'iyyun makirci,
Zo N.P.N da Aminci,
Da ka zama mai inganci,
Da ko ka sami mutunci,
Da ka dawo gun managarta.

53. Wasu na garyar adalci,
Banza nasaran shedanci,

N.P.N ke da Aminci,
Mu ne muka gaji karimci,
        Kuma tilas mun yi bajinta.

54. Hannu daya bai aza daki,
Kashin bera bai taki,
P.R.P ba ta mulki,
Mai aure ta fi kilaki,
        In ban da shirin lalata.

55. Mun ce fa su taru jimilla,
Su yi aiki domin Allah,
Kwadayi ya ja musu irla,
Sun koma tsilla-tsilla,
        Aikinsu na da sun bata.

56. Nan zan jero manyanmu,
A Kano gyaran lamarinmu,
Aikin N.P.N dinmu,
Sai Alhji Bello namu,
        Maitama ku ne manyanta.

57. P.R.P ta sha kashi,
Haji Bello da ba ya fashi,
Maitama tun sadda na san shi,
Magana tasa ba ta tashi,
        Gaskiya ko dole a bi ta.

58. Ga Alhaji Bello Inusa,
Zakin da idan ya nisa,
'Yan P.R.P sa fasa,
Ni ma ya sa na gosa,
        Na bi N.P.N na huta.

59. Duk wanda ya tarbi gabansa,
Sai yai masa dukan kusa,
Zaben gaba in ya nausa,
Sai ya hana zamba da busa,
        Karyar banza da waninta.

60. Asali ga Kanawa gaya,
Jama'ar Gaya ba jayayya,
Haji Shehu a ce muku manya,
Domin kyakkyawar niyya,
        Bisa N.P.N mu aminta.

61. Sarkin Labaran mai mota,
Shi alheri yaka fata,
Da natso ba ya gigita,
Kuma ba ya kaunar wauta,
Horon manya ya lakanta.

62. Manya da kasarmu ta nuna,
Ta gane suna da amana,
Sarki Labaran goga na,
Allah ka taya ma gwanina,
Da aminci da mun huta.

Daga cikin wakokin da aka yi wa jam'iyyar P.R.P kuwa an kawo wakar

"Jam'iyyar Mu Ce P.R.P" ta Magaji Ciroma Sudawa kamar haka:

**Jam'iyyarmu ce Fi'arfi : Magaji Ciroma Sudawa**

5.Ba hujja wurin mai kin ta,
Mu dai mun riga mun fahimta,
Ko a cikin maza ko mata,
In ka ji wanda ke sukan ta,
Macuci ne wajen talakawa.

24.Kiranmu a nan ya san makabuli,
Fi'arfi muna da dalili,
Za mu tsaya ta kowane hali,
Sai mun ka da mai cin zali,
Mai danne hakin talakawa.

30.Wanda ya san mutuncin kansa,
Shi ne za ya san na waninsa,
Yai aiki saboda kasarsa,
Wadancan sai fadar baka ba sa,
Aikin taimakon talakawa.

31.Su aikinsu ne su yi cuta,
Ko taro na kulla mugunta,
Duk talakan day a arzuta,
Hanyoyinsasa lalata,
Bai da wajen zaman hutawa.

32.Da su ne su kai mulkin mu,
A bi mu gida ana dukan mu,

Su suka karkashe wassunmu,
Ba wani wanda zai cece mu,
Zamaninsu ba walawa.

33.Kai da ma da ka dube su,
Ba mutumin kwarai a cikinsu,
Sai mugun nufi a gare su,
Korar Murtala galibinsu,
barayi ne na kin karawa.

34.A harkoki sukan yi shigege,
Su halinsu ne su yi kage,
A sami mutum kwatsam nan a buge,
Su aka tankade aka rege,
Kan satar kudin talakawa.

35.Bakin halinsu sai mu takaita,
Su ne masu yanke zumunta,
Gun shari’a sukan bata ta,
Hakinka na kanka ya salwanta,
Kai Magana ta kai tsArewa.

38.To jama’a a nan ku fahimta,
Jam’iyyar da za ta yi cuta,
Har jama’a su kai kyamar ta,
Yau mu ma ku zo mu guje ta,
Mu zabo jam’iyyar talakawa.

40.Mai mana jagaban jam’iyya,
Shi ra’ayinsu babu kiyayya,
To jama’a mu dau soyayya,
Shehu Aminu ba jayayya,
Shi ne shugaba gun kowa.

42.Sun dauki salon siyasar hauka,
Kome bas u yi bisa doka,
Kai abu kankani a tsare ka,
Suna da’awar akwai ‘yan doka,
Alkalansu na daurewa.

47.Mutan birni gami da na kauye,
An yi dare gari yaw aye,
Ba sauran macutan boye,
Mai cutar mu yau ko wa ye,
Doka ta hana shi fakewa.

**JUMHURIYA TA UKU**

Wakokin Siyasar Jumhuriya Ta Uku da aka yi rataye da su, sun hada da wakar

“S.D.P. Inuwar Zumunta kamar haka:

**Wakar SDP Inuwar Zumunta**

1.Ya Rabbana Jalla Ubangijinmu,
Yau ga mu gareka da addu'armu,
Don kai kake bamu abin nufinmu,
Kai ne da mulki da iko a kanmu,
kaine da mulkin da ba zai tuke ba.

2.Dukkan salati ya taso ya sauka,
Ya Rabbu Allah zuwa Annabinka,
Manzo Muhammad fiyayye ma'aika,
Wannan da yaz zo cikin al'ummarka,
Sakonka shi ko guda bai rage ba.

3.Ya Rabbana ga mu ga addu'armu,
Mun zo da manyanmu da kankanan mu,
Mun sunkuya gunka mun sadda kanmu,
Fatanmu ka bamu abin nufinmu,
kasa Ummaru Musa za a zaba.

4.Yau Ummaru Musa ne masoyi,
Yau shi Katsinawa dai ka yayi,
To ba wani tsoro babu shayi,
Kowa ka gani murna yake yi
Sai ummaru musa za ya zaba.

5.Na lura da 'yan yara samari,
Birni da kauye a cikin kuzari,
Alhamdulillahi sun sami jari,
Sun lura sun gane yaro da gari,
Ranar tafiya ka dauke shi babba.

6. In Rabbi ya baiwa yaro tunani,
Balle ya bullo cikin shugabanni,
Ya ba shi baiwar hani ko umurni,
To sai ku dauke shi watan-watanni,
hasken tunaninshi daidai da babba.

7.Shi gwamna ba shekaru ne suke ba,
Ba hurhura ce da gemu take ba,
To tunda ba duba tsuhwa ake ba,
Don ba rashin hankali za a yi ba,
Balle kace wane kai za a zaba.

8.Ai gwamnati sai mutane natsattsu,
Sai wanda ya sami ilmi ya kimtsu,
In ba mu son gwamnatin hargitsattsu,
To kar mu dau wanda da can ya motsu,
Watakila haukansa ma bai gama.

9.Shaho da shirwa zuri'ar macuta,
Su dai manufarsu kullum mugunta,
In sun ga kayanmu wai sai su kwata,
Don su manufarsu su sami bauta,
Mulkiinsu ba zai mana fa'ida ba.

10.Shaho da shirwa sana'arsu kwace,
Kullum abincinsu 'yan cuce-cuce,
har ma siyasarsu 'yar yaudara ce,
Alhamdulillahi mu mun yi dace,
Don Ummaru Musa za mu zaba.

11.Don Ummaru Musa shi mutum ne,
Ga dai hakuri, ga son mutane,
Shi ga natsuwa tafe ko a zaune,
Shi mai manufar zaman lafiya ne,
bai yadda da tashin hankula ba.

12.Ranar yaki ba ya gudu ba,
Ranar yaki ba zai gudu ba,
Don bai taba shan nonon gudu ba,
Shi Ummaru bai san razana ba,
Ban sanka da tsoro ran fada ba,
Ya dan Matawalle mai karya gaba.

13.Ranar yaki ba zai gudu ba,
Don bai taba shan nonon gudu ba,
Shi Ummaru bai san razana ba,
Ban sanka da tsoro ran fada ba,
Ya dan Matawalle mai karya gaba.

14. Ga tarkwadi bulala ta horo,

Angon Hajiya Turai na Mairo,
Ni bani shakkak ka ko da a taro,
Don Ummaru Musa bai da tsoro,
Kowa ya zabe shi yaro da babba.

15. Baban su Maryama zakin mazaje,
Baban su Zainabu gwarzon gwaraje,
Babba uban A'isha ki garaje,
Koyaushe fagen fama yakan je,
Raba gardama don ya magance zamba.

16. Shi ba shi kula da aikin magabta,
Manyan makiya da manyan macuta,
Ko sun yi cutarsu ba ya kula ta,
Ya barwa Allahu shii zai hukunta,
Ba zai taya hasidi hassada ba.

17. Sabon gwamnan mu mai son talakka,
Mai son mu da albarka ta sauka,
Kowa ya wadatu rani da kaka,
Mai son mu da arziki ba iyaka,
Sai Ummaru Musa ba ba'a ba.

18. Ya Ummaru tauraron masoya,
Mai son jama'armu yara da manya,
Shi tun azal tarbiyya ya koya,
Shi ba shi da surutu da yaya,
Ba zai yi zancen da ba fa'ida ba.

19. Alhamdulillahi mu munyi dace,
Shaho da shirwa bana sun makance,
Yau babu sata kuma babu kwace,
Ba cin amana kuma babu fauce,
duk dan fashi yanzu ba zai sake ba.

20. An shirya zabe bana in ka lura,
'Yar tinki ce yanzu manya da yara,
Ba tsangwama babu dauri da tara,
Ba magudi babu runton kujera,
Dukkan akwatinmu ba zai bace ba.

21. Ai babu sata da runtun kujeru,
'Yar tinki ce don mutane su taru,
Su za a kirga a layi su jeru,
Don kat talakkan kasarnan ya kwaru,

Kar ai masa magudi bai sani ba.

22.'Yat tinke ce don mutane su taru,
'Yat tinke ce don mutane su 'yantu,
Don nuna kishin kasan nan ta kyautu,
Don ba a so al'umma ta cutu,
Sai anka ce babu satar akwatu,
Layi ake yi da yaro da babba.

23.Shaho da shirwa bana nai batan kai,
Shaho da shirwa da babba da jaka,
Kullum manufarsu danne talakka,
In yai magana suce yayi hauka,
In yai magana suce yayi hauka,
wai har a kama shi ya karye doka,
Ta fuskas su ba za ya san rangwame ba.

24.Ga filin yaki za mu dosa,
To na yi kiran samari matasa,
Don ranar zabe babu wasa,
Ku fito da shirinku don cinye gasa,
Mata da mazanku ba zan rage ba.

25.Har dattijan mu ma nai kiranku,
Mun baku girmanku da martabarku,
Don Allah kuzo a cikin shirinku,
Dukkal lamari idan anyi ba ku,
Shi al'amarin bazai fa'ida ba.

26.Ga Ummaru Musa mai nagarta,
Ga Audu Kusada mai 'yan zarata,
Mai maganin kungiyar masu cuta,
Ya hallaka mikiya ya kasheta,
In ya ga 'ya'yanta bazai bari ba.

27.Ga Dokta Shatanmu manyan mayaka,
Baban su Mamuda zakin mawaka,
Babba na Bilkisu inuwar maroka,
Sai ya kashe shaho ko ta kaka,
Shi bai amince da cin za'ida ba.

28.Wallahi Abdulkadir na zakka,
Wannan mutum jam'iyya ta yaba ka,
In banda Allahu ma ya tsare ka,
Da yanzu kuddawa sun kashe ka,

Ba don hikima ta Ubangiji ba.

29.Alhamdulillahi yau babu gaba,
Mu yanzu munai wa kowa maraba,
Don mai nasara ba zai so fada ba,
Ba za ka ganai yana tsokana ba,
In ba abin dai yazo kaddara ba.

30.Zo Ummaru Musa tausa kora,
Na shehu Tahida mai kauda bara,
Ka kada gunzu da bauna da kura,
Mugun dawa mai manyan hakora,
In yaga shirinka ba zai tsaya ba.

31.Maganarmu da ni da kai na tuna ta,
Maganar mmu da ni da kai nar rike ta,
Allah yasa Ummaru ka tuna ta,
In ka tuna hankalina ya kwanta,
Don share hanyar azo ai zumunta,
Ai Ummaru ba sai na fadi ba.

32.Maganar mmu da ni da kai nar rike ta,
Allah yasa Ummaru ka tuna ta,
In ka tuna hankalina ya kwanta,
Don share hanyar azo ai zumunta,
Ai Ummaru ba sai na fadi ba.

33.Ni bani ganin nisan masoyi,
Amma kusancin makiyi da doyi,
Shi kau masoyinka kamshi yake yi,
Ko da kamar ni dubu goma zan yi,
In nai tunaninsa bazan tsaya ba.

34.Ni Awwalu nasan masu so na,
Na gansu da soyayya da kauna,
Don ni masoya suna kan idona,
Kullum tunaninsu shine a raina,
Ba za ni manta su ko da sekon ba.

35.Ya al'ummar SDP ku shaida,
Cikin dawakinmu na zabi danda,
Na hau da kayan ado masu tsada,
Don tun ga kakanmu doki na gada,
Tun zamani salisu bai wuce ba.

36.In za ni tuna da manyan sahabba,
Na san su Ali ruwa ne gudubbai,
Gun Ummaru mai manyan muhibba,
Su sun kace duk a fito a zabai,
Don Ummaru ba raggo bane ba.

37.Shi Ummaru in da kun kiyaye,
Ya sami albarkaci gun iyaye,
Shi tunda ya riski manyan araye,
Sun sha yi mai addu'a fai da boye,
Ba zai yi aiki akan kuskure ba.

38.Ba zan yi tuya na bar albasa ba,
Ba za ni mance Ali guguwa ba,
In ga shi ga gwamna ba zan raba ba,
Ba zan bi Hussaini in bar Hassan ba,
Don bai iya bata zumuntaka ba.

39.In ko na tuno da manyan masoya,
sai na tuna Ali 'yan doma manya,
Manyan maza masu inganta gayya,
Sai Ali 'yandoma hasken su manya,
hasken tunaninka ba zai gushe ba.

40.Shi Ummaru bai iya yaudara ba,
Bai alkawarin da bazai cika ba,
Bai yadda da cutar 'yan adam ba,
To don haka mu shi zamu zaba,
Gwamnanmu domin ya maganta zamba.

41.Shi Ummaru Musa dai mutum ne,
Mai martaba dan manyan mutane,
Mai son adalci cikin al'umma ne,
Mai son a zauna zaman lafiya ne,
Baya rikon 'yan adawa da gaba.

42.Amma a yau gun Bala kuti zani,
Babban masoyinsa mai kyan tunani,
Shi yai kwamishina  cikin Shugabanni,
Baya hadama Bala ba shi guni,
Hay ya gama bai ci sisin kwabo ba.

43.Sai Hamisu Gambo yaro matashi,
Amma fa manyanmu duk sun yaba shi,
Domin ganin kyautuwar ayyukanshi,

Shi Hamisu Gambo baya da kyashi,
Baya da bakin ciki bai iya ba.

44.Shi dai mutum in yana son ka bishi,
In ko ya nuna yana kinka basshi,
Shi arziki Rabbu keewa mutum shi,
To sai ka ga yaci ya sha ya koshi,
Dukkann bukatunsa ba zai rasa ba.

45.Ya Rabbana shi ka rainon marayu,
Ko ba uwa ba uba za su rayu,
Don za su ci za su sha har su shiryu,
Kuma har su bude idanu da wayau,
Ba za kaji sun yi kukan rashi ba.

46.Ciyaman Lawal acci barka da yamma,
Don naji har jam'iyya ta yaba ma,
Ka rungumi al'umma babu kyama,
Don kayi aiki karamar Hukumar
Ka Allahu ne bai nuhwa ka cika ba.

47.To yanzu gun Amadi Kurfi zanje,
Ya dan halali a manyan gidaje,
Manyan iyayenmu manyan mazaje,
To kaji sadauki ki garaje,
Gwanki kana yaye tarkon maharba.

48. Ba zan yi garaje in wuce ba,
Ba zan wuce da mai martaba ba,
Alhaji Aminu makera babba,
Dattijo barka da yaki da zamba,
Barka da dinke baraka ta gaba.

49.Amma bara in tsaya in ga Murja,
Domin ta ban goro fari na Gwanja,
Murjanatu 'ya ce mai darajja,
Mun lura mun gane aiki take ja,
Bata yadda mata su zauna kawai ba.

50.Yau mikiya babu 'yan tsalle-tsalle,
Mun shake wuyanta sai kalle-kalle,
Yau babu damar aje kulle-kulle,
Ba za mu yadda mu shuka ba balle,
In ta fito ma taje kulla zamba.

51.Tarko a yau mun ga ya kama mage,
Yau ba dabara fa sai waige-waige,
Wai don ku fisshe ta ku masu hange,
Don ba mafita ga 'yan fizge-fizge,
Ko tayi baza su yi fa'ida ba.

52.Ban yadda da shaho dan fashi ba,
Don bai iya cutar al'umma ba,
Ba za mu bi mai cin za'ida ba,
Mu Ummaru Musa za mu zaba,
Ba zalbe mai nuna dogon wuya ba.

53.Ni na fito gun ziyara ta rassa,
Malam Lawal Bindawa na dosa,
Don ya zama jagoran matasa,
Malam Ali kam shi babu wasa,
Manyan maza masu yaki da zamba.

54.Alhamdulillahi nan zan takaita,
Ni Awwalu Isa na cika ta,
Baitinta Hamsin da biyu na rubuta,
To kunji sunanta Inuwar Zumunta,
In za ku shigo ku huta maraba.

A gaba kuma an sami wakar jam'iyyar U.N.C.P. ce ta Haruna Aliyu Ningi kamar haka:

**WAKAR JAM'IYYAR UNCP TA HARUNA ALIYU NINGI**
**AMSHI : Ranar zabe kowa ya fito alheri ne**
**Jam'iyyar UNCP zan yi wa waka patina.**

1. Bisimillah ya Allah ka zamen jagora na,
Domin darajar manzo Rasulu abin da muke kauna
In fada wa kasan nan duk domin su guje wa abin barna,
Su bi hanyar tserewa mu bi UNCP patina.

2. Jama'a mun sami uwa mu yi sauri kar mu sakankance,
Uwa mai goya diyanta dab a ta barinmu mu lalace,
To don haka ne manya suka zo su suna mata zaurance,
Ki fitar da gwani mama gwanin ya zamo magujn barna.

3.A kasar nan na yi kira wa za ya raka nig a ummata,
It ace mai ban mama ita ke koya mini tatata,
Me sa mini albarka mai karfafa karfin guiwata,
'Yan kasa suka amsa min duk za su raka nig a ummata.

4.Na ce UNCP kun san sitirar al'umma ce,
Jama'a ta kasar nan to lallai bana mun yi babban dace,
Mun dau gamzaki nan mutukar haske da ake kauna,
Ku fito manya yara domin mu rika wa patina.

5.Ku kada kililin-kililin kida mai ban tsoro,
A yahai wuro ne Baffa kuina wuro to in ji bororo,
Nasara bat a kare ba har yau a kasarmu akwai gyauro,
Gyauron cancanta ne na wanda suke son patina.

6.Nasarawa ku saurarar wata 'yar Magana na cizo na,
Ku fito yare-yare kowa ya tsaya ya ji baiti na,
Wani sako ne yau za na fada muku shi daga patina,
Shi ne ranar zabe mu zabi uwa makarin barna.

7.Magina ramin keta ku taho ku ga sun gaza binnewa,
Bawa sun yi aron riga da tat sage sun gaza dinkewa,
Bana sun yi aron baki ga babu abincin taunawa,
In kun raba kayinku ku zo ku hada shi da patina.

8.Duk ran da na sha nono ranar na je ni garin Baba,
Chairman Alhaji Shehu ka ja mu zuwa kai ne a gaba,
Makarin ba a daina ba shi ne asali ba a fara ba.
Ka ja mu fafata da masu adawar patina.

9.Kai yo fartanya yau karyar masara karyar Kwando,
Da hannu aka san su ko sun rikide sun zam dodo,
Kuma ban da batunka ba wai zai ki hanu masakin wando,
To ku bar wata in'ina ku zo ku rungumi patina.

10.Wani ba shi da ko jaki muka so mu aza shi a kan danda,
To idan kanari kai to a cikin taguwarmu akwai suda,
Sannan daga patinmu komai wahala komai tsada,
Yaushe masarar ta tsira har kake mana karyar ta nuna.

11.Iyaye patina Ibrahim Kura Mohammed ne,
Da Aminu Sulen Garo, Labaran Ali sun mana jan kunne,
Da Kabir Ibrahim G, haske a ido mai sa kanne,
Daurin in kira Baba in kira Usman daga patina.

12.Asha ruwa tsuntsaye ji Kabir Isah baka zauna ba,
Ga Habu Ibrahim Fagge shi ne deputy a wurin Baba,
Kuma Mus Salisu sakatare ka taro bas u kare ba,
Sai mun cika motarmu muna mu tsaya makarin zauna.

13.Action will never fail actions speaks lauder than voice,
All masses you should raise here we comes with golden chance,
You have to try my mum because masses is mother choice,
You will benefit a lot from the plan of patina.

14. Ku taho ku taho mata bana mun yi kira baku kyale ba,
Mu saka ku a mulkinmu wannan maganar ba mu fasa ba,
Mun bincika halinku a ciki duk babu halin zaba,
Mu fito ranar zabe dukanmu mu zabi abar kauna.

**JUMHURIYA TA HUDU**
**BULALIYA (PDP) BALA IBRAHIM RINGIM**
……………….
3.A kanku miyagun kasa tsiya ce zan zazzaga,
Kun riki kwai mu muna da dutsi a buga mu ga,
Za mu ga mai ja da baya in wahala ta shiga,
Yau ba ku gaskiya ba za ku ji daDinmu ba.

4.Cikinku gare mu a yanzu wa zai yi karo da mu,
Kidan ganga ba wuya da lauje in an gamu,
Yau duka 'yan jam'iyyu mu dai mun sha mun tsumu,
Harbin kibiyar munafukai ba zai ci mu ba.

5.Yau kashin ja'irai macuta ya kekashe,
Masu hawa kan hakin marayunmu su turmushe,
Ya'yan banza hakinmu da suka wawashe,
Allah na san mu yau ba kwa ga tsirecinmu ba.

6.Ku jemagu a yau kuna da shirin shan wuya,
Kun yi hakori da fuffuke ku ji 'ya'yan tsiya,
Can kuma ga kunnuwa a kai nasu sun tsai tsaya,
Bas a tsuntsu bare a dabba ba a san sub a.

8.Ga jam'iyyarmu mai nufin alkhairi ku ga,
Ruwan famfo du da magani a kasa zai shiga,
Har rarrauna marar kabuli shisshiga,
Zai sami rabonsa ko'ina ba wata fargaba.

10.PDP jam'iyyarmu ce mai jin tausayi,
Duk Kyautata rayuwar mutane ita za ta yi,
Dan za ta yi gaskiya gami da nufin kyauta yi,
Allah ya taimake mu PDP ce gaba.

13.Bakar ran ace a yau gurin wasu azzalumai,

Dan talakawan kasa a yau mu ne jarumai,
Ba ma kwana ciki da yunwa da nade da mai,
Allah ya taimake mu mu PDP ce gaba.

14.Sakainun bisa kan ruwa b azan bi akidar ku ba,
Iska c eke kada ku ba wani karfin ku ba,
Dan ba ku da gun zuwan da iska bat a san shi ba,
Ni ban a bin abin da ban san manufarsa ba.

15.Kukan shaho a yanzu du dan kwai zai tsuma,
Dole yakan firgice jiki nasa du na tsuma,
Sai dai in an jima jiki nasa ya tsantsama,
Sannan zai tashi nan da nan ya matsa can gaba.

18.Jam'iyyar bakin ciki b azan yi tab a,
ANPP a yau da gaske b azan so tab a,
Kura ce ko da sasari b azan haut a ba,
Allah wadaran shirinki nib a zan bi ki ba.

19.Ke makara ba a san hawan ki fan a tabbatar,
Dan kuwa ke kin wuce a hau ki a dan shakata,
Dan ba wani mai hawanki sai rai nasa ya fita,
Wannan Magana ba a yi shakka a cikin ta ba.

23.Shirin jam'iyyarmu kun ga mata yau har da ku,
Domin ku ne adonmu yau dole mu je da ku,
Du mai neman daidai shirinsa ya sanyo da ku,
Mata na gida zuwa na har waje ban ki ku ba.

26.PDP jam'iyyar mu yau ke ce kan gaba,
Jam'iyyar ce da ke nufin mu da san ci gaba,
Kan aikin taimakon marayu bat a bar shi ba,
Su ne fa wadanda gun su babu uwa ba uba.

29.Ai kwa kawaici yana da kyau b azan kui shi ba,
Gaba da gaba sun sani b azan zagi ubansu ba,
Gugar zana kwa gat a nan b azan bar tab a,
Domin ita ke bugun su allai bat a bar su ba.

32.Dan mai mugun nufi nake so zan lallasa,
Ko da kyama ga wadansu na Allah ya isa,
Du da hakan yau sirrinsa ni shi zan fallasa,
Zan saka a duniya kwa don wani bai sanka ba.

36.Ya jama'a 'yan kasa a yau sai ku taho mu je,

PDP n kiran ku yau sai ku futo waje,
Kar ku yi sanda ku zo mu je ku taho gurguje,
PDP na kira ba ma kI mu je gunta ba.

**BAKANDAMIYA (PDP) SHU'IBU 'YANMEDI**
……………..
3.PDP siyasar al'umma ba kungiya ce ba,
Ba taw adansu wararrun jama'a ne masu fanti ba,
Mun zabe tam un karbe tad adai ba za mu fasa ba,
Sai ta kai ga alherin nan da ta shirya wa mazanmu da mata.

4.PDP rowan sha ne mai sanyi lokacin zafi,
Kai tsarki ka sha kai wanka ba nuna fin karfi,
Sai ta wanke duk fitina mu ci tozo ba kayar kifi,
'Yan Nijeriya ku fito mu bi PDP ta gyara kasa ta.

5. PDP ruwa tafi sannu game birni da kauyen ki,
Sauran jam'iyya duka sun hadu domin su karya ki,
To karyar su karyar al'umma mu ne kirarin ki,
Du mai son kasa ya taho mui PDP mazanmu da mata.

15.Jam'iyyar masoyan Allah ta zo al'umma ga ta,
Jam'iyya a kan manufar alheri ta yi tsarinta,
Jam'iyyar da babu ruwanta da linzamin mazalunta,
PDP farar aniya ta zo domin mazanmu da mata.

29.Wai dan takarar wasu ya saba laya ba a ka da shi,
Wai sai dole yai gwamna watakil boka ya loba shi,
Ba sa'a gare shi ba PDP ce za ta kada shi,
Ran zabe mu dau inuwar lema ta gyara kasa ta.

34.Tsuntsaye suna kuka jama'a sun kasa ganewa,
Jemage ya zo yai nasa mutane na ta tafawa,
Wai shi ne cikakken tsuntsu assha in ji Hausawa,
Saura kis ya bata kasar sai ga canji ya shiga kasa ta.

36.Na dau kunkuru zan yanka wuyanai ya ki fiddawa,
Har ya yi shawara zan yar sai yara suke cewa,
Dau gashin wuta likawa takashin ja'iri wawa,
Sai ya fid da kan watsa masa reza kar ya bata kasa ta.

49.Shaho yai bayani don haka du dan kwai ya saurara,
Zaki yai kiran 'ya'yan dabbobi sun shige saura,
Yau ga jam'iyya ta zo talakawa sai mu saurara,
PDP kasa duka mun amsa domin ta gyara kasata.

## WAKOKIN JAM'IYYAR A.P.C.

### Lema Ta Yage: Dauda Kahutu Rarara

Lema ta yage ta fatattake nace ta yage,
Mar maza maza kuce mana GMB,
Knawa kuce sai Ganduje,
Kaduna kuce mani sai Malam,
'Yan Jigawa kuce sai Tallamis,
'Yan Katsina kuce sai Masari,
Zamfarawa kuce mani sai Yari,
A Sakkwato kuce mani Tambuwal,
A Kebbi kun ga Bagudo ya haye,
Nasarawa Almakura ne,
Barista Bauchi ya haye,
Jahar Yobe Gaidam ya sami,
Jahar Barno sun ce sai Kashim,
Adamawa Bindo ya kwashe,
A Benue Samial ya sami,
A Pataskum Malam ya sami,
Abdul Fatahi Kwara ya kwashe,
A Naija kuce mani Lolo, Lolo, Lolo,
Ga farin wata sha kallo,
Maso gani idonsa ya bullo,
'Yan malfa mun maku gwalo,
Rarara ya ce ai zigidir,
Ai wanwar,
Ai tumburrrr,
Adamu Zango yake waka na Abdulhamad mai kwashewa,

Ta tabbata an kare zabe kuma mun yi ma PDP zigidir,

Masu gudu su gudu

Masu gudu su gudu bana dai Janaral ya karbi sama,

Mun hallaka PDP bana APC mu ne da kasa,

Mai malfa ne a kasa bana Baba Buhari yana bila dan baiwa.

Ga shi mun lashe zabe a kasa a tsare tai amfani,

Bana PDP sintir mukai mata mai wakar ga ni,

Yau Buhari yana bila zaben bana dai yai amfani,

Ga talakawa ga Jega sun ce bana dai yai amfani,

Bana an yi karon karshe talakawa za mu ci amfani,

Sai Baba Buhari,

| | |
|---|---|
| Talakkawa | sai Baba Buhari, |
| Masu kudi | sai Baba Buhari, |
| birni kauye | sai Baba Buhari, |
| Mata da maza | sai Baba Buhari, |
| Sojoji | sai Baba Buhari, |
| Ga 'yan sanda | sai Baba Buhari, |
| Jama'ar Yaroba | sai Baba Buhari, |
| Ga Hausawa | sai Baba Buhari, |
| Har ma da Ibo | sai Baba Buhari, |
| Ga Turawa | sai Baba Buhari, |
| Samar da tsaro | sai Baba Buhari, |
| Hana cin hanci | sai Baba Buhari, |
| Korar rashawa | sai Baba Buhari, |
| Wuta da ruwa | sai Baba Buhari, |
| Harkar ilimi | sai Baba Buhari, |
| Harka ta lafiya | sai Baba Buhari, |
| Harkar noma | sai Baba Buhari, |
| Ga masana'antu | sai Baba Buhari, |

Kowa ya fadi sai Baba Buhari,
A jahar Katsina sai Baba Buhari,
Sai Dallatu sai Baba Buhari,
Masarinmu ya lashe zabe ya tumurmusa mai gashin baki.
Lema ta yage, nace lema ta yage,
Lemar ta yage, ta fatattake nace ta tsage,
Ga ruwa ya kare na ga dan kada ya cure,
Baba Buhari ya zo, zanen PDP ya goge,
Baba Buharinmu kan a sami ya kai a dage,
Fada da Aljani sai ka shirya sannan sai ka dage,
Ku gafara ku ga aiki, Buhari ya iya ya gode,
Allah ya ta ya ka riko Nazifi ke ta bude baiti,
Nazifi mai wakar gwamnan nan Baba sarkin aiki,
Wannan na kanon nan Baba mai abin mamaki,
Ko ko sai na ce maku Kwankwaso jan hali jan aiki,
Yara ba za su ja da kai ba tuntuni ka saka rigar saki,
Mai takalmin karfe ka take su basa aiki,
Zan dan taba ki kadan kin biyo a ta tsarin aiki,
Nace miki kaza ce ke, kinga sai an baki,
Kin daina butulci karshe jama'a sun barki,
Na barki da yara za ni gangara kan aiki,
Nazifi ne ke tafka bayani na kwankwaso mai aiki,
Rabbana sanata kai watan biyu ne za ka zan a gaba.
Baba Buhari in da rai da rabo mai gida,
zZi gyara kasarmu mun kau da mazambata,
Yau Nijeriya tana hannun gaskiya.

Kai ruwa-ruwa-ruwa haka,
Ga wuta-wuta-wuta haka,
Baba ya wuce haka,
Naga masu kwalliya suna daka,

Gyaran kasa akai niya, lemar ga naga ta fashe tsaka,
Ana ruwa muna daka,
Wasu na ciki suna ta harzuka,
Ku tuba ku bi Baba,
Nace ku tuba ku bi Baba,
Yau shi ya zam ma babba,
Bana ba batu na 'yan ta'adda,
Tun da basu son mu ba su yi mana aiki.
Baba a gyara mana
Masu wuta sun haka,
Ga su ruwan nan ba haka,
Mai 'ya'ya na daka,
Ga mata na daka,
Ga ilimi na kasa,
Ga su tsaro sun haka,
Lafiya tafi karfinmu,
Ga sata tai yawa,
Baba a duba, Baba a duba,
Baba a duba manaaa.

**MASU GUDU SU GUDU: Dauda Kahutu Rarar**

Amshi: masu gudu su gudu bana Baba buhari ya karbi sama,
Mun hallaka pdp bana apc ita ce da kasa,
Mai malfa fara shiri bana dole ka bar bila da gudu gaggawa.
Masu gudu su gudu.
Kai ku bani kidin Janaral a sama,
Kai bana Baba Buhari ake magana,
Mu ne a ciki su ne a kwana,
Ga Rrara fannin magana,
Kai bana dai APC ta karbi sama, aaa!
E! Aminu Bello Masari ya ce mu fadi,
Wancan ya fadi, wancan ya fadi, sama!
Dallatu ya ce kowa ya fadi,
Kun san mazari su ne da kadi,

Wasu sun ce ai dawa da badi,
APC sak! Janaral ya fadi,
Mun san kanwa ku ne da hadi,
Sai Baba buhari, aha!
Kai bana APC mu ne da sama,
Dangin zaki layin su zuma,
Suka ce a daga don mui rigima, aaa!
Ga shi mun kure karyar mai hadama, hai!
Sai Baba Buhari,
Ku gaya masu masu gudu su gudu,
Kai! In kasan kai sata ka gudu,
Hai! Ku gaya ma barayin can su matsa,
Ko way yi sake Janaral ya ritsa,
Ga Baba Buhari janar a sama, hayya!
Sai Baba Buhari,
Rabilu dan ibro tilas na fadi,
Allah ya jikansa ya mai rahama,
Baba na Chinedu yana da kari, to!
Sai Baba buhari,
Baba na Chinedu ke magana,
Na Huntuwa mai bude magana,
E! Abokin Rara mai magana,
In ka manta Malam ka tuna,
Yau dai Janaral shi ne a sama,
Dallatu ya ce kowa ya hwadiiiii,
A'a masu gudu su gudu, bana dai Janaral ya karbi sama,
Mun hallaka PDP bana APC ita ce da kasa,
Mai malfa fara shiri bana za ka fice bila da gudu gaggawa.

1. Allah ahadun samadun sarkin mulki shi ne da sama,
Allah sarkin sarki ka iya mana mui wakar mu gama,
Ana maganar zaki tilas ai lissafi da zuma,
Masu son sanyi da ruwa tilas su biyo hanyar fadama,
Zaben da akay yi bana ga GMB shi ne a sama,
Mun hallaka PDP gyara muka zo ba ma rigima,
Farar tafiya na rike bana ga Janaral shi ne a sama,
Buhari muke magana allah ya taya ka riko ajiyar talakawa.

2. Allahumma salli ala Muhammadu jagoran tafiya,
Dan Aminatu gatana Muhammadu mai kyawun aniya,
Alihi da sahabbansa a cikin tafiyar ba sa gajiya,
Allah ka hada da Janar Buhari mafi kyawun aniyar talakawa.

3. Assalamu alaika salo jama'a na kasa barkanmu haka,
Ga Rararan waka na kahutu gida kun shaida haka,

Jami'a gonar waka in kana mana adalci mu maka,
Ana maganar canji APC sai ta karbu duka,
Mi ya kawo maganar tirmi kowa yasan aikinshi daka,
Shi injin tahuna an fi yi masa lissafi da nika,
Ita PDP tumbur muka ce za ai kuma an yi haka,
Mun hallaka PDP a saman da kasan mu ne da duka,
A kasa a tsaya a raka in ji Baba Janar shi ne waraka,
Yau ga canji ya zo APC kullum na habaka,
Yau dai mune da tuwo mune da miya mune da duka,
Janaral na talakkawa ko Turawa sun shaidi haka,
Buhari muke magana inji rarara Allah ya rika,
Talakawwa sun ce addu'ar da su kai ta karbu duka,
Janaral ya karbi sama, allah ya taya ka riko addu'ar talakawa.

4. Inji masu karin magana wasu sun kare wasu na tafiya,
Wasu sun yi abin kunya su dan baki an fada ma kaya,
Wasu na ta shirin hijira muka ce masu don Allah ku tsaya,
Kasan a karin magana wani zai magana ya tuna da jiya,
Na biyo hanya dodar su na angama an afka ma kaya,
Cikin a saya a biya in an mana adalci mu taya,
Ni nasan iya tsawo ba ya wuce dai ka yi da wuya,
Ga shi karshen PDP ya zo jama'a murna mu taya,
A garinmu mahaifata sun barni ina daki na haya,
Yanzu ga mu da APC jirgin maja Allah ka taya,
Allah ka taya mu riko bBhari ka je bila ka rike talakkawa.

5. APC tai nasara mata da maza sai san ta muke,
Kasa duk ta rude sanadi na bukin murnar da muke,
Masu nuna bakin rami duk sun ji jiki kunyar mu suke,
Ku gaya wa mai kwaba ni da shi idan ya bari ta jike,
Inji masu karin magana wani ya binne wani za ya hake,
Ruwan sama ya sakko sai ku je ku ce da biri ya fake,
Daminar bana ta yi ruwa don duk ta kori farin da ake,
Canji shi ne waraka Allah ya bamu janar mu rike,
Jama'a ku fadi mu fadi APC yau Janaral ne mai talakawa.

6. Kun san wani na da fushin wani an buge dillalin akuya,
Na duba ga mai ciniki in dai da kudi shi ne da biya,
Bana dai muke da tuwo mun kama kasa mu ke da miya,
Maja ita ce da gida ku 'yan abiyo layi ku tsaya,
Duk wanda ya sai guga dole yana neman kudin igiya,
Ku fito ku fadi mu fadi kome tsanani ba ma gajiya,
Sakin layin da kukai yasa komi baya tafiya,
Rokon Allahn da mukai ya iya mana don shi ne ka iyawa kowa.

Ku gaya wa iyalan mai malfa,
Yau mun yi wa PDP tumbur,
Saura kuma zaben gwamnoni sai mun yi wa PDP zindir,

7.Ahadun samadun Allah kenan shi yay yi wa dan kuka koko,
Sarkin sama mu shi ne gatanmu na kwance ya taso ga sako,
Jama'a ku taho ga Rarara jami'a nake na zarce bako,
Ku raba ni da 'yan wawa malfa ta kai kasa PDP sintir.
Ku gaya wa iyalan mai malfa,
Yau mun yi wa PDP tumbur,
Saura kuma zaben gwamnoni sai mun yi wa PDP zindir.
Masu gudu su gudu bana APC muke da sama,
Mun hallaka PDP bana APC ita ce da kasa,
Mai malfa fara shiri bana dole ka bar bila da gudu gaggawa.

8. Ya al'umma na kasa ku taho ku ji labarin da ake,
Janaral ya amshi kasa amma fa kusan halin da take,
Farko ga cin hanci ya yadu akan layin da muke,
Kwarabshin ya yi yawa su dan baki bankaurar su suke,
Aah ga shi babu tsaro kullum ibar rayinmu ake,
Tattalin arziki na kasa duk ya rushe maganar da ake,
Harkar noma ziro wuta da ruwa hanya a hade,
Harkar ilimi ziro kullum yajin aikinsu suke,
Kuma fanni na lafiya likitoci zaluntarsu ake,
Ana ta bukin murna amma fa kusan halin da muke,
Janaral ya karbi kasa shi dai burin gyarata yake,
Amma jama'a ku sani sai mun yi a sannu gudun,
Kar mui gaggawa.

9. Ku taho mu biya ta Kano jirgin maja shi ne a sama,
Gada ta danne wani ko ya danne ta suna rigima,
Maganar tsohon sanata na Kano tsakiya zauren hadama,
Ga ministan nan na wata shidda kalllo ya koma a sama,
Mindirawa zan koma ranar handin oba rigima,
Maganar tsohon kwano an kwashi dala fanshin na kuma,
Kun yaudari mai malfa kun ce a Kano ku ne a sama,
Da kilaki ta je zabe a sahu na Kawaja akai rigima,
Ita PDP sintir akai mata na ga zani a sama,
Kai ku kyale takwaikwaiwa yai ta tarabaraden nan ya gama,
Ran zabe za mu jira sai takai mun taka mu kuma,
A Arewa ta maliya can bana burgu an fada fadama,
An kade ganyan rogo bana ya koma sanata dan baiwa.

10. Ku hada ni da aramma na Madina ina maganar da mukai,
Malaman birnin Zazzau ku tuna mana duk sirrin da mukai,

Wato sirrin fatiya kar o'o ya ce zaginsa mukai,
Shi kau gwamnan banza mata da maza jifarshi sukai,
A Kaduna yake gwamna shekara hudu ba aikin da sukai,
Bana mun ce sai Malam El Rufa'i shirin dora shi mu kai,
Malam kasan boko har da fatiya murnar da mu kai,
Mu wuce birnin Shehu ba sauki ina kullin da kukai,
Kun ce ba sikuiriti sojoji ma zaginku sukai,
Ku kira mani mai rodi 'yan Sakkawato ma jifar shi sukai,
Dogo ka sa malfa sai ka fadi duk kullin da kukai,
'Yan Barno suna murnar sun warware duk kullin da akai,
Tsohon gwamnan Barno ------- sun san yadda akai,
Su ne suka sa malfa a Barno ko mu jifar su mu kai,
Ku raka ni garin Bauchi kauran mata jifar sa akai,
Jifa da ruwa dutse da idona ni naga yadda akai,
Ga Allah yai ikonsa a dukka biranen nan da mu kai,
Yau Janara shi ne da sama, Buhari yana bila murnar Talakawa.

11. Kowa ya fito murna ga Baba Buhari muna da shiri,
Muna maganar gyara dattijo shigo bila da shiri,
Kasa duk tai kamfa damina ta zo mun kori fari,
Ku masu shirin cuta gwamnatIn janar wannan ku bari,
Shi burin GMB a wadata ruwa kauye da gari,
Harkar noma da wuta shi Baba Buhari yake ta hari,
Kuma zai inganta tsaro to kaga da bambanci da biri,
Kuma harka ta lafiya duk mai yajin aiki ya bari,
Fannin noma da kiyo dukkan wani mai rigima ya bari,
Da Buhari muke magana in ji Rrara inganta shiri,
Ya Allah kai ne da duka ka iya mana ga zabinmu Janar,
Dan baiwa.

13. Kyauta dangin sadaka Allahu gwanin iko na tuna,
Yunkurin hana ai zabe wasu sun yi shiri Allah ya hana,
Sharrin da akai wa Janar suna da yawa in za ku tuna,
Sun ce bai da lafiya likitoci sun yi musun magana,
Sun ce bai da takardu na sakandire tarko su dana,
Malamin makarantarsu shi yay yi musun wannan magana,
Sun ce wai tsoho ne tshoho Baban yaro mu tuna,
Dattijo muna murna don kai baka takin fitina,
Yau iyalan mai malfa mu ne a ciki ku ne a kwana,
Ku ake ta yi wa jaje mu gamu muna murna da dina,
Allah shi ne da sama shi ya ba wa Janar mulki ajiyar, Talakawa.

14. Da gudu bana GMB shi ne da sama,

Ku fito mu game kanmu ku mu raya kasa kar mui rigima,
Kun san da akwai aiki a gabanmu kwarai kar mui hadama,
Mu cire duka bambanci maganar Janaral ita za mu kuma,
Yarbawa har da Ibo Hausawa dukka mu yo azama,
Ku fito mu rufawa Janar baya don shi gurinshi yi wa, Talakawa.

15. Kai masu gudu su gudu bana GMB shi ne da kasa,
In ka ji ana a gudu watakila barayi ne mu tasa,
Mai tsoron GMB idan ka tara ya cuci kasa,
Duk mai zagin Janaral watakila munafinci ya dasa,
Ga Janar ya karbi sama ku masu munafunci ku gusa,
Don shi mulkin Janaral ba ya ra'ayin danne na kasa,
Sai Baba Buhari Janar don shi dai alkairi ya tasa,
Masu kin ka barayi ne sun san da akwai kulli a kasa,
A kasa sai mui murna don mun harbo kusu na bisa,
Janaral kai ne da bisa Allah ya taya ka riko Janaral dan baiwa.

16. Su Duna ana ta shiri bana za a Otoke zuwa rakiya,
Tilas na kira anti mai bilicin dawo kiy rakiya,
Wai ina Kauran mata da kai a cikin wannan rakiya,
Da na sakkwato ba sauki tilas ka shigo wannan rakiya,
A rufe ma da fatiya Malam Namadi na waya tu waya?
Ku kira mani mai rodi shi ma zai je wannan rakiya,
Tsohon gwamnan Barno da ya sa malfa mun kori kaya,
A Kano tsohon kwano ya na ciki duk za sui rakiya,
A ministan hayaniya ku kira shi sutufid of za yiya,
Ku tunawa fes ledi ta Otoke bataun magana ta jiya,
An gyara gidan gado a Otoke ana ta shirin tafiya,
Ga Buhari cikin bila haihuwatai na yaye gajiya,
Ga shi albarkar 'ya'ya ita ce sanadi mun kori kaya,
Allah raka taki gona can a Otoke mu kori kaya,
Janar ya amsa janar bana dai bila kaine da rikon, Talakawa.

17. Maganar a kasa a tsare su Atiku suna layin tafiyar,
Turaki mazan fama ga kusoshin wannan tafiyar,
Kai tsawo kuma ka yi kudi kai kar rushe waccan tafiyar,
Ku hada ni da dan musa sanata mai ci linzamin tafiyar,
Ga Buhari Janar ga ni, da Kwankwaso lissafin tafiyar,
Ka ji gwamnan gwamnoni dan Musa linzamin tafiyar,
Bola Ahamad Tinubu wadanda suke kishin tafiyar,
Ku hada shi da Fashola gwamnan Legas tsarin tafiyar,
Ku gaya ma darakta dan muna tafiyar,

Amechi mu ke magana gwamnan Rivers ya gamsu da mai,
Talakawa.

18. Ku kira Osinbajo Furofesa za mui magana,
Bayis na furezdan zan zo ofis za mui magana,
Mataimakin shugaban kasa wasu sun so sui kulli ya hana,
Randa duk na shigo Legas wannan baiti shi za ku tuna,
Ga ciyaman din fati na Kano Dandago kuma ga magana,
Ka ba da tilin kuri'a a kasa naji kowa na magana,
Haji Umar na Doguwa ga Rarara waka ka tuna, kai!
A Kano sai Ganduje dan babu hadi gwanda da guna,
Mustafa Inuwa Dakta jigon fati a jahar Katsina,
Ka ba da dubun kuri'a a kasa na ji kowa na magana,
Shugabannin jam'iyyar APC Rara ke magana,
A fannin gudunmuwa kun bayar ai tilas mu tuna,
Ga Faruku dan Adam na Buhari jigawa muke magana,
Sanata Hadi Sirika shi dan Katsinawa ne ku tuna,
Kuma ga Sabo na Kudu Sabon sanata za mui magana,
Sai Baba Buhari Janar APC ta kore fitina,
Allah ya taya ma Janar Buhari kana kishin jama'a,
Talakawa.

19. Ciyaman fati Cif Onyegoni tilas na fadi,
Shugabanmu na APC ya taka rawa tilas mu fadi,
Ku hada ni da sheikh inda Isaya ma tilas na fadi,
Ku rakani gurin Rocas Okuroca ma dole na fadi,
Ga Layi Muhammed ma ai yana ciki dole mu fadi,
Har da Dino Munaye ma sarkin magana ta fadi mu fadi,
Nasiri Kano sannu aikin da kake tilas mu fadi,
Har da Faruku Adamu kun san fitacce ne dole mu fadi,
Har ma Hadi Sirika shi dan Katsinawa mu fadi,
Katsinawa na magana gwamnanmu Masari muke Magana,
Talakawa.

20. Bari in maganar Janaral ga Malami soba karo da karo,
Kaga angon Hauwa'u Baban su Yazidu ya watsa ciro,
Ku raka ni garin Kurfi dan Arewa Aminu kana da baro,
Na zo na yi ma jaje ka bar makiyanka suna ta karo,
Haji Adamu ‘yan-duna shukar da mukai bana ta yi ciro,
Ni da kai da akwai magana sai na zo gunka a wanga karo,
Bari in tafi Musawa in gai da Yarima muna da ciro,
Yariman Musawa Samir Isma'ila ma su baro,
Garba Kura da kai a ciki a Kano ku ne kuka kora baro,

Kai da Gidado ana magana ba kwa ra'ayin danne hakkin, Talakawa.

21. A yi zanne a zauna lafiya in an hangi akwai rigima,
Maru Bungudu ba haufi bana ga Abdulmalik a sama,
Mu Zamfara ba canji sai shehi kwarai ba ma rigima,
Yanzu mun rufe PDP a Zamfara kam mu ne a sama,
Ku raka ni ga Wamakko sanata mai ci tuta a sama,
A Sakkwato mun shaida kai kai gwamna ba ka hadama,
Kano sai Ganduje zaki ku ne dangi ga zuma,
Kano mun dau layi Ganduje mu ke so ba rigima,
Ga dan Kanawa nan haji Nasiru shi ba ya hadama,
Shugabanmu na CRC na Madobi yana kishin,
Talakawa.

22. Jahar Katsinawa Aminu Bello Masari muke magana,
Shi ne sabon gwamna don babu hadi gwanda da guna,
Dallatu muke buri Katsinawa na murna da dina,
Mu mukay yi wa PDP sintir a jaharmu jahar Katsina,
'Yan Kaduna ku dau Malam El Rufa'i akwai magana,
Don shi aiki ya taho bamban da Kawalli gudun rigima,
A Neja muna murna gwamna sai Lolo kade fitina,
Nufawa har Gwari Hausa da Fulani na magana,
Sakkwatawa mun shirya Tambuwal muke shirya wa dina,
Shi ne gwamnanmu kawai kowa ya taho inganta shirin, Talakawa.

23. Baba na Chinedu mai waka jama'a yau zan yi tuni,
Dan Funtuwa ne da bakori wakata zan ma gini,
Baban Umulkairi angon Zainabu 'ya -- ta zani,
Waka nike wa GMB kullum ina ta tuni,
Difiti gwamna Masari Mannir dole zan yi tuni,
Dan-dutse gaishe ka Funtuwa gagare dukka ture gini,
Abu Na Katsina kaima dole zan yi tuni,
Ga tica na Masari ubanmu fa dole zan yi tuni,
Sabo Musa MC magana ka saba yi da tuni,
Ga kansilanmu na gobe Jamilu na jogana bai gudun, Talakawa.
Ku gaya wa iyalan mai malfa,
Ga shi mun yi wa PDP tumbur
Saura kuma zaben gwamnoni sai mun yi wa PDP zindir,
Yau mun yi ma PDP tumbur; ga shi mun yiwa PDP zigidir.